[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

Bismillah Rahmani Raheem.

https://my.w.tt/EcTsIaOy2ab

_Allah subhanahu wata'ala ya halicci d'an adam domin ya bauta mishi, kuma bawai zaka kare shi da kome bane! Sabida babu abinda zaka yi dan ka biya shi wannan kyautar da yayi mana! Koda miskala zarratin bazamu tab'a karen shi da kome ba! Haka zalika ba zamu rage shi da kome ba!  An karbo hadisi daga d'an Abbas, yace Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama ya fada mana cewa! Da zamu hadu mutanen farkon mu da mutane karshen mu, mu roki Allah. Dukkan mu zai amsa bukatar mu! Ba tare da ya manta daya min mu ba! Ashe kuwa dole bawa ya kasance mai godewa Allah da ni'imar da yayi mishi! A duk cikin halittun da Allah yayi. Babu wanda Allah ya karrama shi kamar D'an Adam, a cikin Alqur'ani mai tsarki Ubangiji yayi batu da yawa akan Dan Adam!  Ya kuma bashi labarin kanshi a cikin Alqur'ani! Ubangiji yana sane yayi mu masu banbancin Halitta. Wasu farare! Wasu bakakke! Wasu kuma zabiyoyyi! Kuma yana sane da banbanta mana ra'ayin mu akan addini! Sannan ya kaddara wasu fararrun alamari zasu iya shigowa tsakanin mu!  Dan haka da wannan nake kuma godewa Allah da ya bamu ni'imar da bamu isa mu saya ba sai dai mu gode mishi!_ Alhamdulillah!

1989/ July/ 21
Jigawa state

Hadeja General hospital.

01

"Dan Ubanki idan kika kuma shigowa rayuwar Ma'aruf sai na saka an yanka min ke. Anyi min Gunduwa Gunduwa da namarki, bake mayya ba sai na cofin Babanki yar shegiya, tsinaniya. Kai idan na kuma see you a najeriya, a go cofin kan uwarki bake magret ba toh ko markade kike babu sassauci a tsakanina da ke, yan banza me manyan idanu, maza take yor culot maki sakawa ki bar garin nan dan uwarki kar na kuma ganin yor lege, a garin nan yar banza me manyan idanu." Cikin shashekar kuka matar da bazata wuce shekaru ashirin da hudu ba, ta durkusa a gaban wata mata wacce idanunta Babu alamun rahama tace cikin bagwaren hausan da bai gama rike bakin ta ba,
"Riƙo yaro sai Maman shi don Allah ku bani baby na, i swear ba zan kuma came back to Ma'aruf ba, please baba"

Tauuu suka dauke ta da mari sai da ta dungura, dai dai shigowar Nurse dakin da aka kai Magret, cikin jin haushi Nurse din tace.

"Amma baku da imani, taya mace daga haihuwar ta ko hutawa bata yi ba, zaku zo ku sakata a gaba! Kuna cin mutuncin ta, haba ku kuwa!" Kallon jelar gashin Magret a hannun Surayyah tayi. Cikin mamaki take kallon tsantsar rashin mutunci a idanun su. Takowa ta yi tare da d'ago matar cikin tausayawa ta ce.
"Mutanen na basu da imani, kuma zasu iya cutar dake, idan kika tsaya sai sun baki yaronki. Kiyi hakuri kinji." Kallon kayan jikin jikin Hauwa. Riko hannunta tayi suka saka kai zata fita, ta kwace hannunta, tana kuka tare da fadin.
"Karku rabani da Yarona, ku bani Yarona." Haka Nurse Salamatu taja ta suka fita. Kuka take kowa ya ganta sai ya tausaya mata, har suka bar ward din, sannan ta kaita wani daki ta bata kaya ta saka, riga daban zani daban. Sai dan kwali, da ta daura. Hawaye na zuba mata. Ta ce mata.
"Please ga Yarona a hannun Allah yana kuma hannunki, ki saka ido akan shi, ki kuma bani layin asibitin nan zan tafi idan na isa, US zan kira ki. Don Allah karki cire idanunki akan shi yaro karami sun hanani shi." Haka ta riko hannun ta suka fita sai da ta samu wani a koru kura, ta sakata wanda zai kaita Kano.

***

Bayan tafiyarta Suka dauki yaron suna kara jin haushin Hauwa wacce yar asalin ƙasar Amurika ce, tafiyar Ma'aruf can karatu ya hadu da ita, inda suka yi aure sannan ya dawo da ita, Magret William yar wani shahararren attajiri ne  a garin newyork, ita kadai  ya haifa, uwarta ta mutu ta barta, shi ne ya dauki son duniya ya daura mata, ya nuna mata wata irin SOYAYYA kamar me, sai dai zuwan Ma'aruf Adamu Hadeja, ya sata juyawa Soyayyar Mahaifinta baya tace tana son Ma'aruf, duk yadda Uban yaso karta fada mugun rayuwa, haka taki fir. Sannan aka yi aure tsakaninta da Ma'aruf, sai da suka shekara biyu. Sannan Ma'aruf ya gama karatu, yace zasu zo ganin gidan zai dawo da ita. Tunda suka biyo jirgi suka dire a kano, taga yadda kasar Najeriya yake, take tsoron barinta ƙasar Iyayenta ya kamata, tunda suka shigo hadeja. Ta haɗu da Muguwar uwar miji, da yan uwan miji, tare da Yayar mijinta, da farko sun dawo da arziki me mugun yawa, wanda Baban Magret ya basu, kafin su koma, amma suna zuwa Yaya Hindatu ta kwashe kome hatta kayan sakawar Hauwa sai da suka kwace. Suka wurga mata wasu matattun kaya, haka ta yi ta rayuwa, watan su biyar aka daura mishi Aure da Surayyah. Yar mijin Yaya Hindatu, tunda ta shigo gidan suke. Mata cin mutuncin, tare da wulakantata. Sun dake ta, sun zage ta. Gashi Ma'aruf yana dawowa zasu fadi karya da gaskiya babu bincike zai hauta da duka, wahala tayi wahala. Tun bata jin Hausa har ta koya dan dole. Abin takaici da ban tausayi, tana samun ciki zasu zubda mata shi, shi yasa wannan cikin tana samun shi ta boye musu baya gayawa kowa ba, har ta fara zuwa asibiti a sace. Zuwa lokacin da ta haihu. Sun kwace yaron ne, wai dan karta tafi dashi dan burin su. Tayi nesa da Ma'aruf karta zauna dashi domin ko sun hada su, sukan shirya. Kuma sun san idan ta tafi da yaron Ma'aruf zai bita, idan kuma suka sake ya bita, sunce zata rike musu shi. Da wannan nazarin Yaya Hindatu ta zuga Baba Mero ta kora keyar Hauwa.
Dan haka lokacin da Ma'aruf ya dawo,  Baba ta fashe da kuka tana kallon shi tace mishi.

"Dama sai da muka gaya maka, Ba zata tab'a sonka ba, gashi nan ta gudu ta bar yaron da yake cike da bukatar soyayyarta, tur da wannan rayuwar, abin tausayi yaron da aka haifa ko dumin

Mahaifiyarshi bai ji ba ta tsallake shi" a zuciye ya amshi yaron, sannan ya zuba mishi ido, kwalla na zuba mishi, ya sumbaci goshin yaron sannan ya kalli Mahaifiyarshi yace.

"Gashi nan sunan shi Aamil! Zan tafi na nima mishi abinda za a na bashi, yana sha. Ita kuma Hauwa Ubangiji ya min Sakayya, Ni da Yarona." Ya mike a hankali ya bar dakin. Murmushin mugunta tayi sannan tace.
"Babu shegiyar da zata mallake min Yarona." Ta cigaba da kula da jinjirin. Har Baban shi ya kawo madarar da za a cigaba da bashi.

A wahale Aamil ya taso, ga rashin uwa. Yaron haka yayi ta fama da cututtukan, irinta Yara. Lokacin da ya fara rarrafe, haka zai bata jikin shi da kashi, Baba cikin jin haushin kulawar da Uban yaƙe mishi zata zage karfin ta ta zabga mishi duka, wani lokaci ya shiɗe. Wani lokaci haka zai yi shiru, yana sauke ajiyar zuciya. Zai yi wuya ta dake shi bai kwanta ciwo ba.

Duk da gidan da suke family house ne, me cike da sassa masu yawa, shi yasa babu wanda yake sanin uƙubar da Baba Mero da Hindatu suke bawa Aamil.

A hankali yaron yake girma, sai ya taso baya shiga cikin mutanen gidan nan. Sai ya zama na ya taso da mugun tsoron mutanen gidan. Kullum yana cikin dakin, yana da shekaru biyar, Baban shi ya samu aiki a Jigawa. Dan haka da ya tashi komawa da matar shi Surayyah, sai ya dauki yaron, dakyar Baba ta barshi, ya dauki Yaron, suna komawa can kuwa ya saka yaron a makarantar boko da islamiyya.
Sai dai idan ya tafi aiki, Surayyah bata taɓa bawa Aamil abincin matukar Ma'aruf yana gida zata cika mishi kwano har yana zuba, idan kuwa baya nan toh, wallahi azabar duniya sai ta bashi, ta dake shi ta kona mishi hannu. Ta zuba mishi gishiri, haka zai ta kuka tana dariya. A hankali ya fara shanye irin azabar da take mishi, idanun shi ba bushewa. Yana wani irin kangarewa, tare da zama mafadaci. A bayan gidan su yan shaye shaye suna zama, idan ta daidaici dawowar Baban Shi zata kora shi gurin, yana Shigowa gida zata ce.
"Yaya nifa na fara gajiya da halin Aamil idan zaka zaga gurin yan shaye shayen nan yake zama. Ka duba ma!" Yana zuwa zai same shi a gurin su, riko Yaron yake zuwa gida yayi ta dukar shi, kamar wani baba.

Ita kuma haka na mata dad'i, haka zata yi ta murna. Gashi Allah bai bata haihuwa ba, duk wanan azzabar ta take bawa Yaron.

A hankali yake girma, rashin jin shi yana kara bunkasa, fitinar shi na kara hauhawa. Har zuwa lokacin da ya cika shekaru talatin cif a duniya..

⤇

Wani irin bakin ciki ne ya tokare mishi kirji, kallon Aamil yayi wanda ya fito daga ban daki, ga budurwa da ta kwana a d'akin shi tana shafa mai, Ganin Alhaji Ma'aruf yasata mik'ewa tana kare jikinta, dauke kai Aamil yayi tare da kallon yarinyar yace.

"Dan Ubanki ba nace kar na same ki a waje ba, ki fita kafin naci Ubanki!" Ya daka mata tsawa. Da sauri ta, dauki kayanta, tare da fita zata saka. Abban shi ya matsa mata. Ta fita, tana mita ganin sai lokacin Aamil zai gabatar da sallar asuba. Karfe bakwai saura Kwata. Wani abin yaji ya tsaya mishi a rai, kwalla na cika mishi ido. Yana tsaye har ya idar da sallah,kallon shi yayi sannan yace mishi.
"Ubangiji kana ganin Bawanka, na fita hakkin shi na bashi tarbiyya, na kuma bashi ilimi. Ya Allah ban san me nayi ka bani shi Zakka ba."
Cikin jin haushin Abban shi yace mishi..
"Idan baka bukata ka kore ni mana kamar yadda kuka raba Ni da Uw..." Tass ya wanke shi da mari, sai da yaji marin sosai, dan haka ya juya tare da cewa.
"Yau zan bar maka gidanka, na shiga duniya, nasan akwai mutanen da zasu rike ni, kasan aka kaunata ka samar dani, baku da wani aiki sai aibata Mahaifiyata, toh wallahi zan bar maka gidanka, tun tasowata ban san soyayyar kowa ba. Ban san dadin Kowa ba, haka na taso cikin kunci da rayuwa mara amfani, idan nayi abu kace ba tarbiyyar da kayi min ba kenan, ka tsane ni, bayan baka san meye yake faru da ni ba, taya nima bazan dasa maka bakin ciki ba, zan tafi na barku ku zauna da mutanen da suka fi maka ni?".
.daga haka ya fice ya bar dakin har ya isa bakin kofar, Baban Yace mishi.
"Kaje kaga Sidrah?"  Cikin zafin rai ya juyo yana huci yace mishi..
"Abba kace baka kaunata mana! Wancan yarinyar da babu wanda ya kaita muni itace zan aura! Yarinyar da bata wuce Jaririyar ba kake cewa naje na ganta! Yar shekaru tara, wallahi ko a yar wanke wanke gidana bata kai ba balle yar da zan aura, Ni babu ita a cikin rayuwa, duk da ana gaya min cewa mahaifiya baturiya ce, karshe sai ka Hadani da bakace, meye nayi da zafi da zaku rasa kyawawan mata, ku bani sai wancan mummunar me kama da kwarangwal, yarinyar da kafin namiji ya moreta sai bayan nan da shekaru ashirin.

Wallahi idan zaka nimawa Ali ita ba laifi, amma."

"Tabbas da kai za ayi auren! Ko kana so ko baka so! Aamil sai ka auri Sidrah, domin ba zan lamunci zubda min mutuncina da kake yi ba, kaka dauko yaran mutane kana lalata tarbiyyar su.

Sanan naka hankoron mace kyakyawa, su matan da kake lalata su ba kyawawa bane? Ko iyayen su basu kaunar su ne? Toh wallahi ka wuce hadeja gurin kaga Sidrah Wallahi ka kuskura na samu labarin baka je ba, tabbas sai na hukuntaka, dan ba zaka zubda min mutuncina ba, wanda nayi kai shekaru aru-aru ina tanadin su, sabida kai na da kimata." Daga haka ya mai da hannun shi baya. Tare da barin d'akin.. wani uban ihu ya Aamil ya buga tare da dukar Kofar dakin shi.

*Alhamdulillahi gani nan na dawo a wani Lovestory  labarin yasha banban da saurar. Ku biyo Alkalamina......🤩. Kuyi hakuri Daula  biyu! Insha Allah sai sabon shekara zaku ji ni, Ruwa biyu kuma Insha Allah! Ko na cigaba a watan da zamu kama ko kuma, A karshen shekara Insha Allah! Ya danganta da lokacin da na samu ne!* *Nagode 🤝 sosai*
#Mai_Dambu
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

https://my.w.tt/U2ZCTqQj4ab
HAZAKA WRITER'S ASSO...

Bismillah Rahmani Raheem

02

"Taya za a ace min na auri ugly girl. Me zanyi da mace munmuna irin Sidrah yarinyar da bata wuce Jaririyar ba. Idan na yarda na shiga Lazza a daure." Ya kuma kaiwa kofar duka, tare da make kanshi. Yana wani haki dan masifa, a fusace ya saka kayan shi ya fito daga dakin.

Tsakar gida ya fito, yana kallon yadda yaran gidan kowa ke shige da fice. Gyara zaman hular kan shi yayi tare da nufar cikin gidan, duk abinda ya gani a gaba shi ball yake dashi. Ba tare da ya damu da koma meye ba, yana isa kofar da zata shiga da shi tsakar gidan su, ya ja tunga ya tsaya. Tare da zabgawa Hasnah wani irin kallon banza, sannan ya kauda kan shi, ya taka a hankali isowa inda Hajiya Surayyah take soyar kosai. Ya gyara zaman facing cap din shi yadda zai kafta rashin mutunci a silale ba tare da ya kalli fuskar kowa ba. Gyaran muryan yayi duk yan kanen shi suka dare, tare da komawa can gefe suna zare ido. Domin sun san shi hukuma ne, bai da mutunci ko na miskala zarratin, bayi da hakuri kamar rina haka yake, fushinsa yafi na mayunwacin zaki, idan yana yinka duk duniya babu wanda ya isa yace baka kai ba, haka idan ba ya yinka babu wanda ya isa yace kayi balle yayi ka, wato Aamil ruwa biyu ne..yana da sassayar hali, kuma yana da baudaddiyar hali, yana iya zama na tsawon watanni bai yiwa kowa magana ba, idan kuma aka kuskura yana gida yara suka cika shi da Hayaniya zai kama yaro yayi ta bashi azaba kamar yadda suka mishi. Mutum ne mai mugun don abu me kyau. Sai gashi ya kasance gidan su bakake ne! Musamman Familyn su.

Shi kuma ya kasance ruwa biyu, Mahaifiyar shi baturiyar Amurka, mahaifin shi bahaushen hadeja. Aamil zai iya juya harshen sa ya dai na magana da kowa cikin harshen Hausa, sai English ba tare da yaji ko dar ba. Sannan yana iya zuwa kofar Church ya zauna, duk bala'in da Christian zasu mishi ba zai tashi ba sai lokacin da yaji a ranshi ya tashi zai tashi.

A duniya ya tsani mutane uku! Baba Mero wacce suke kiranta da Hajiya. Sai Yaya Hindatu, wacce suke kiranta da Goggo hinde, sai Hajiya Surayyah wacce suke kiranta da Hajiyar mu. Dukkan su da sunan su yake kiran su. Sai dai Hajiya Uwani wacce ta kasance matar Alhaji Ma'aruf ta biyu, sai Amarya shi wacce suke kiranta da Hajiya Amarya.

Alhaji Ma'aruf yana da mata uku cif, Hajiya Surayyah uwargida sai Hajiya Uwani wacce take Binta, sai Hajiya amarya wacce take karama, A gidan Sun ware Hajiya Uwani basu yi da ita, gashi itace kusan Alhaji Ma'aruf yake ji da ita, domin itace take jibance da al'amarin Aamil kasancewar ita tayi karatun boko da na addini, sai ya zama na tana kokarin ganin ta karkato da hankalinsa kan karatu. Hajiya Surayyah da Hajiya Amarya wacce sunanta Karimah. Basu da mutunci. Kuma suna tare da Yaya Hindatu da Hajiya. Yanzun haka gidan cike yake da yara Domin wani irin haihuwa ake kirin na gasa. Idan wannan tana da ciki toh Insha Allah ko

Shayarwa kike sai taje ta kwaso ciki.

Sabida jahilci, idan ka cire Hajiya Uwani wacce take tsarin iyali. Saboda tana koyarwa a jami'ar jihar Jigawa,kuma tana yawan tafiya course. Dan haka ta cewa Alhaji Ma'aruf.
"Yallabai! Zaka yi hakuri gaskiya, bazan takura kai na da haihuwa akai akai ba, sabida ni ma'aikaciya ce, kuma ina yawan tafiya karo ilimi, kaga ba zan iya tara yara ina barin su a gida babu kulawa ba, dan haka zan iya daukar lokaci zuwa lokaci kafin na haihu."

Ajiyar zuciya ya sauke sannan ya riko hannunta, ya ce mata.
"Babu laifi! Nima da ace wadancan zasu bani hadin da mun samu tazarar Haihuwa, domin Kinga Karimah sai da aka min magana a haihuwar Yusuf, aka ce mahaifar tana bukatar kulawa da hutu. Da kaina na kaita aka bata maganin da zata na sha na wasu watanin, amma kawai wata biyar sai naji wai tana da ciki, wallahi abin ya dame ni, kuma ba kome ya kawo haka ba. Sai kishi tunda taji Surayyah na da ciki shi kenan, magana ya kare."

Murmushi tayi sannan ta ce.
"Manta da batun kowa, ni bana son damuwa, kai ne a gabana!"
Yaran Hajiya Surayyah, goma ga cikin na sha daya,
Ali shine babba.
Ghali ya yake binshi.
Jamila take bin Ghali.
Sadiya, Harira, Mariya,
Dejangala, Haruna, Muttaka, sai Halima.
Hajiya Uwani kuma duk yaranta biyar ne. Muhammad Aashiq, Aseed, Abdus Samad, Jalil da Jalal, Twins ne. Amma basu kama da juna ko daya.

Hajiya Amarya itace kuma take da yara mata huɗu. Zakiyah, Ihsan, Mufidah, sai Muwaddah. Sai Yusuf. Da kuma ma cikin jikinta.

Yaya Hindatu, tana da yara biyar. Musa, Sai Dayyabu da Abdullahi, sai Hasnah da Baria. Gidan Alhaji Ma'aruf, yana da matukar kokari. Domin bayan Kanwar shi akwai matasa kusan guda bakwai a cikin gidan. Da suke karatu a karkashin kulawar shi. Faruq, Mujaheed, Sulaiman. Ismail, Mahmoud, Saleh. Bala. Isah. Duk suna zama mishi a shagunan shi da suke cikin kasuwar Dutse.

Duk yadda zan muku bayani akan gidan Alhaji Ma'aruf, ba zaku fahimta ba. Domin gida ne wanda baya rabuwa da baki daga kauye. Shi yasa yake noma, yana noma shinkafa, dawa, gero, masara da kuma wake da wanke suya. Sannan yana noman rani. Inda ake fidda mishi kayan lambu. Har da ya'yan itace. Sannan tsarin gidan Alhaji Ma'aruf, a bayyane yake. Domin shi baya bada kudin kome akwai duk abinda ake bukata. Kayan miya idan lokacin shi yayi. Sawa yake a kawo mishi. A yanka wasu a shanya, wasu kuma a markade su a zuba a babban deep freeze, maggi kuwa kullum ake kawo laida daya daga kasuwa. Mangyada da Manja, ana kawo rabin jarka yalo ne. Sai bushashen kifi, da ake kawowa daga numan.

Duk ranar girkin mata, zata jika gero da dawa, a markade shi. Sannan a tacce shi. Washi gari kuma da sassafe yan matan gidan da masu aiki zasu tashi da gyaran wake, kafin karfe bakwai matar da take da girki ta fara soya. Masu aiki na tayata, babu batun masu aiki su zasu miki kome dole ki fito. Sannan kafin ya fita zai tara yaran shi da kuma matan ya tambayi kowacce abun da take bukata, ya ajiye musu dubu uku uku, yaran kuma dubu daya daya. Sai ya shiga dakin mahaifiyar shi ya bata dubu biyar, kanwar shi dubu biyu. Yaranta dari biyar biyar..

A kasuwa kuwa, idan ka cire  Ghali, wallahi hatta Aamil cutar mahaifin shi yake, domin suna diban dukiyar shi, bana wasa ba. Sai dai bai da ikon ya kore su, domin yana da yakinin idan bai mutu ba, Allah zai bashi wanda zai kare mishi dukiyar Hauwa. Dan ba nashi bane, na Hauwa ne. Gashi Allah ya sanya albarka a cikinta. Duk yadda suka kai da su b'arnan Allah sai ya duba niyyar dake cikin zuciyar shi ya kuma bunkasa dukiya. Ba zai tab'a mantawa ba, duwatsunta masu daraja, ta dauka ta bashi lokacin da yake faffutikar niman aiki, bai san dasu ba. Ta cire tace mishi.
"Ma'aruf! Gashi nan ina ga zasu saya da daraja, ka fara yin kasuwanci mu gani kafin ka sami aikin gwamnati, dan ko mahaifina da kasuwanci ya fara aikin gwamnati."  Guda goma sha biyu, ta rike sauran sha biyun dan guda ashirin da hudu ne.

Wannan kenan..
Kerere yayiwa Hajiya Surayyah a kai, tana zuba kullu a wuta ya kalli wanda ta kwashe sunyi kyau murmushi ya sake mata, kafin ta fahimci me, ya juye tass a filet ya kuma dauki wani mug ya cika da ruwan zafin da aka dafawa Abban su. Sannan ya mike tare da nufar kitchen ɗin gidan ya dauki gwagwanin milo ya zuba son ran shi, sannan ya kuma juyawa ya zuba madara. Bai damu da sugar ba, dan yasan suna dafa ruwan zafin da sugar. katon bread ya gani ya yanki wanda zai iya ci. Ya fito tare da nufar dakin Hajiya uwani, yana Shiga Aseed yaja mishi Center table, ya daura abin karyawan.

Cikin nutsuwa ya kalli Hajiya Uwani da suke karyawa ita da yaranta, yace mata.
"Ummi! Yau ba zaki jira Uwar Aliyu bane?"
Murmushi tayi sannan ta ce.
"Bari kai dai, ina sauri ne. Kuma bana son su makara ne, dan seven saura kadan."

Bai kuma magana ba, ya cigaba da karyawan shi, yana cikin cin abincin Ya jiyo muryan Hajiyar mu tana cewa.
"Wallahi idan baka shiga tsakani na da Aamil ba, wallahi zan saya Ghali da Ali su mishi mugun duka, dan iskan yaro. Ka ja mishi kunne ko kuma nayi Abin da zai damu da kanshi." A zuciye ya mike zai fita. Hajiya uwani ta ce mishi.
"Dawo ka zauna!"  Dan dole ya dawo ya zauna, ta cigaba da karyawa, tana gamawa ta shige d'akinta tare da dauko sabuwar Shadda, ta ajiye mishi sannan ta juya tare da cewa.
"Jalil,Aseed, Ashiq, Abdul Jalal maza ku fito. Ina jiran ku zan muyi latti!" Da sauri suka fito tare da ɗaukar school bag dinsu, suna zuwa kusa da Aamil suka karasa gurin shi, tare da rungume shi suna fadin.

"Brother! Idan naje hadeja ka cewa Aunty Sidrah muna sonta"

Abin ya bashi mamaki, zai yi magana tasaka hannu a baki.
"Duk da na gari, burin shi ya farantawa iyayen shi da sauran mutanen gari. Dan haka ga shaddar nan, ka dauka kaje ka ganta, sannan ga jakar can na kayan kwalliya ce, Please And please, karka kunyata mu, a gaban Baban Atiku don Allah kaje lafiya ka dawo lafiya. Muna jiran sakamakon mai Kyau."

Gyada kan shi yayi cikin nutsuwa, yana cizon lips d'inshi. Tabbas sai yaci kutmar kaniyar yarinyar da ake bashi sallahun ya gaida ta.

Tana gama gaya mishi haka ta ficcewarta, dan akwai wani key a hannun ta, idan ya tashi zai ja mata kofar ta ne. Yayi tafiyar shi.

Tana tafiya ya mike tare da fitowa tsakar gidan, yaji ana kus-kus a shashin Hajiya, kamar ba zai magana ba, kawai ya leka domin sun saba cin mutuncin juna yana shiga ya kalli Hasnah da Musa, suna musu akan shi. Bai damu ba, ya shiga dakin da yaji ana gulmar dake window ta baya take.
"Ai Hajiya ina gaya miki ba yace baya son Hasnah ba, toh wallahi yar gidan Iro marigayi za a kwaso miki a jikan da kike cin alwashin sai yar gidan gwamna zai auro miki, domin Sidrah ba budurwa bace yarinya ce karama."

"Ke hinde! Ba dai Sidrah wacce take hannun Lantana ba, wallahi zan kuwa ci mutuncin Ma'aruf. Ni zaiwa bakin cikin."
"Hmm! Ai gwara yayi miki bakin cikin, mata baki san kome ba sai tsantsar mugunta, wallahi ba dan wancan mutumin yaron ki ne ba, sai na karya miki kafarki. Ke kuma Hinde maza ki tattara wadancan gardawan na dawo hadeja muka yi ido hudu dasu sai na baki mamaki, munafukai kawai."

"Bana son rashin kunya ni Kanwar Ubanka ce!" Ta faɗa mishi cikin tsawa.

"Dalla yi min shiru, wallahi nazo na sami yaran sai na karya kafafun su, tunda gidan Uban na ne." Ya faɗa.
"Toh kwashashe, Zuri'ar masu fitsari a tsaye, dan banza jinin masu jan kunne. Zan ci uban mangofak ma. Dan haka ficce min a daki."

_Assalamun Alaikum sisters! Wannan labarin ruwa biyu! Rayuwa ce irinta malam bahaushe! Wanda yake tafe da manuniya biyu! Tsarin hausawa da tsarin turawa! Don Allah idan bai miki ba, karki b'ata lokacin ki gurin karantawa! Domin zaki iya haduwa da abin da bai miki ba kiji Haushi na! And salon shi daban ne da sauran labarai daga sunan kawai zaki fara fahimtar haka thank You 💝💖_
#Mai_Dambu
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**

*<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>*
https://my.w.tt/pvpSrJ4R5ab

ℍAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

_Dedicated to all Black beauty🙎🏿‍♀️
Daga manyan har kananun idan ke baka ce Wannan shafin naku ne!🤩😍😘_

0️⃣3️⃣
Ball yayi da wani jug wanda yake dauke da kunu. Yana huci tare da kallon Hajiya yace mata.

"Wallahi sai na karya kafarki, munafukar mata, kamar yadda kuka rabani da uwata, Allah sai na rabaki da naki d'an."

Ya juya tare da barin gurin su. Yana jan tsaki, tun da ya shiga shashin sa, me dauke da dakuna biyu da kuma kitchen sai dan tsakar gida, da baranda, tare da kitchen ɗin waje, da kuma wani a cikin falon gidan, sai dan gurin wanki da wanke wanke a waje, sai kuma dan backyard da yake dan bayan gidan inda zaka ayi shanya idan aka yi wanki.

Gidan zaman mace daya ce, babu wani abu da za a kara bayan haka. Gidan yayi kyau sosai, domin na yaran da ake ji dasu ne aka mishi. Tsaki yayi tare da kaiwa bangon, yana kuma jan Allah ya isa tsakanin shi da mutanen da suka raba shi da mahaifiyar shi. Dan haka yayi wanka ya shirya tsaf, sai ɗaukar kamshi Oud 24hrs yake, cikin Izzah y kalli madubi yaga yadda Allah ya zuba halittar shi bai san lokacin da ya sake wani irin murmushi ba, dan yayi imani kaf Jigawa babu hadadden gaye irin shi, most ontop population guy, in Jigawa. Penny loafer shoe kiran kamfanin vinci ya saka,. takalmin da shaddar sunyi match yayinda hular shi zanna bukar ya tafi da zaren aikin rigar shi.

Wani sarka ya saka a hannun shi kamar kaca, bayan ya ya saka agogon shi. Cikin kuzari irin ta jajjurtacce namiji yake tafiya tare da cilla key din motar shi sama, yana cafkewa. Turuss ya tsaya dai dai lokacin da ta bude mishi zig din rigarta.

"Aamil! Sai yaushe zaka dai na guduna? Yanzun duba fa, ina haukar ka, baka ciwo na. Ina matuƙar kaunarka" takowa yayi ba laifi yace a ranshi. Kallonta yayi sama da kasa, yarinyar tana wuta. Kallon boons ɗinta yayi wanda suka ƙasance kamar an hura balloon, sun leko daga kayan jikinta suna mishi wani blush! Fincikota yayi cikin nutsuwa yana kallon fuskarta! Kashe mata ido yayi sannan yace mata.

"Gaskiya bazan auri yar Hindatu ba. Da dai kin nemi muyi Shagali ne zan iya gayyatar ki

d'akina, amma aure." Hade bakin su tayi tare da saka hannu a keyar shi,yana kaunar shagali. Rike bayanta yayi. Tare da gyara mata tsayuwa, sannan ya rungume ta suka fara takawa bata san inda yake kai taba, har sai da ya dangana da cikin gidan, Ana gulmar Hajiya Uwani suka hango Aamil rungume da mace.

"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun! Amma wannan yaron anyi kwasa she. Yar waye ka samu zaka lalata musu ita, shine dan ka cika dan isk..." Ture Hasnah yayi tare da takowa gaban Hindatu yace mata.

"Idan zan yi Shagali da Yan mata, Yaran manyan nake nima. Wacce Ubanta zai boye abin kunyar da tayi dan kare martabar ba yar da babu wanda yasan inda dangin Ubanta yake! Ke kuma na kuma kama ki!" Shafa wuyar shi yayi alamun babu abinda ba zai faru ba.

Daga haka ya bar musu gidan, karshe gulmar da aka rufe kenan, daga hmm sai hmm yar me gulma tayi ciki.

***

Hadeja
Unguwar Gandun Sarki.

Babban gida ne mai dauke da tarihi, kuma me dauke da mutane kusan dari da wani abu, maza da mata yara da manyan, a takaice family house ne nasu Alhaji Ma'aruf, gidan Sassa ne daban-daban, gida ne da yake dauke da matan aure sama da arba'in da uku. Domin kowani shashin ba zaka raba shi da mata uku zuwa huɗu ba.

Shashin Haliru nan ne shashin babban Yayan su Alhaji Ma'aruf, sai shashin Baba Mamman! Da shashin Baba Idi, sai shashin Marigayi kamilu wanda rikicin Jos ya ritsa dashi tare da Matar Shi da kuma yaran shi biyu. Sidrah ce kadai Allah ya tsiratar da ita, inda aka samu yan hadeja suka ce sun san familyn ta .
... Kasancewar ana sanyi sosai, duke take jikinta yana rawan sanyi, hawaye na diga a cikin ruwan wankin da aka sanyata yi, gashi ana busa wata irin iska me shiga jiki. Lantana ta leko cikin sababi tace.

"Yau naga abinda ya ishe ni bai ishe Allah ba, zaki gama kizo ko karya ko sai nazo naci kan uwarki, shegiya mara kunya, wankin da bai wuce awa daya ba kin dakile sama da awa biyu a gurin."

A tsora ce ta kalle inda maganar ke fitowa tace.
"Innah yanzun zan gama!"
"Kar ma ki gama shegiya me ruwan mutanen daji."
A sanyayye take gurje kayan tare da kai hannunta daya tana sosa kanta, zuwa wuyar ta. Yarinya ce da bata wuce shekara goma sha daya ba.

Baka ce irin bakin nan da zan iya kiran shi Golder Black! Domin fatarta ya nuna haka, baka wuluk ce, mai wani irin sheki fatarta, sai dai kashh. Ba zaka ga wannan shekin ba, sabida zunzurutun Datti da dauɗa da suka lullube kyakyawan fatarta,

Yanayin jikinta Dan Karami ne, bata da auki dan siririya ce, mara auki. Daga fuskarta hancinsa dogo har baka, amma sanadin makeron da ya cinye rabin fuskarta ya sanya baka hango kome sai wasu irin kuraje kananu.

Wuyarta kuwa zuwa kanta, Ya ilahi. Wasu jerin gwanon kuraje ne wanda kwarkwata take haifar da shi idan yayi yawa akan mutum, hannu bibbiyu ta saka tana sosa kanta, wanda yake dan kare da kitso zanen yawo wanda yau kusan watan shi biyar tun auren Yayanta Atiku wanda yake dab sanda ne a garin Kwara.

Bakinta kuwa wanda ya kasance dan Karami, ya farfashe sabida sanyin hunturun da ake fama dashi,. Hannunta da ta saka duka biyu akanta, wasu irin Kano suka yi, dan fatar hannun har wani tashi yake, da za ayi dace a saka sosan karfe ( 🤭🤣🤣🤦🏼‍♀️🤣😂 Wallahi Aamil ina baya ka buhun ubata 🤔😏😒😎🙆)

Toh tabbas zasu tashi, kafarta wanda suka kasance kananu, wasu manyan faso ne, wanda tsabar girman su, da za a saka Naira ba makawa zasu shiga ciki, kuma su sami mafakar siyasa. Haka samar kafarta ya tsatsage, sabida rashin kulawa. Rigar  jikinta kawai zaka kalla ka fahimci, wata tsohuwar roba ce, da tasha gwagwarmayar duniya. Wato da zaka kalli yadda rigar yake, tasha dinkin zare da allura, amma a haka bai hanata yagewa ba.

Domin kuwa, hannun rigar zuwa wuyar rigar reto yake. Tayi futufutu, ta fita hayacinta ga wani abun yunwar da take ji kamar ba zata rayu ba. Dan jin take uwar hanjinta yana wani irin murɗawa. Tana tsakiya da sosa kanta, aka sake mata rankwashi,. Tsakiyar kanta tana cewa. "Shegiya algunguma, wato kece kawai malam ya damu dake shine zai hadaki da Bature mu kuma gamu banza ya, zaki ci uwarki mara mutunci kwasheshiya kawai.".  Rike kanta tayi hawaye na zuba mata. Tana kallon Innah Azumi da gefen idanunta  tausayi. Can sai ga Iya Larai ta shigo ta samu tsakiyar bayanta, dai dai tana wankin ta dirmata dundu. Cikin jin haushi tace.
"Munafuka me kama da mayu, a rasa wacce ta dace da Amil sai ke, yar banza me muni kamar kashin dare."  Kafin ta gama wankin matan gidan sun mata likis. Dakyar ta samu ta gama wanke kayan ta kuma ɗaukar bokiti ta nufi cikin gidan domin dibo ruwan wanke wanken da zata yi.    A hankali take tafiya cikin tsarin yanayi. Me dauke da nutsuwa da hankali, take takawa. Tana zuwa bakin rijiyar ta dauki guga ta fara jan ruwan sai ji tayi an make kiyarta kamar zata fadi ta juya.  Cikin tsoro tace.
"Yaya Ummu!" Buge mata bushashen bakinta tayi sai ga jini, rike bakin tayi, sauran yan matan gidan suka fito, sai da suka mata duka, sannan suka watse aka barta a kwace a bakin rijiya. Zuwan Lantana da Kande tace mata.

"Toh fa Lantana yar sarki mulki take ji gata can gindin rijiya kwance.". Kwafa tayi sannan tace

mata.
"Bani faskare naje na sheme yar banza yarinya, Ni zata janyowa tereren Bankad'a, biyar bashin dan kishiya. Wai me yasa da aka zo kashe danginta suka bar mana yar banza me manyan idanu kamar na gurjiya."
"Hmm! Wai ai dan ma baki ganta ba, sai kace itace ke sayan omon wanki."
Abinda ya kuma fusata Ran Lantana kenan, ta kuma janyo faskare tayo waje tana rantsuwa sai ta sheme yar banza ayi auren da toshe. Koda ta fito hango Baba Mamman yasata juyawa da itacen gida, ya dawo da Sidrah. Ya kalli Lantana yace mata.
"Kiji tsoron Allah! Duk Yaranki suna daki, sai Sidrah kika tura diban ruwa, Inda Kamilu da Safiya suka tafi muma wata rana muna gurin, bai dace ku hana yarinya hutawa ba. Ke jeki dauki abincin kici." Yana gama fadar haka ya juya abin shi. Ya fita haka ta rab'e a jikin bango. Tana jiran a bata bakin rabonta.

Wani kofi Lantana ta nuna mata, wanda kuɗa suna gama gaɗɗa akai wanda kunun ciki ya kasance kadan ko kasar kofin, sai tukunyar dumame wanda yake gurin wanke wanke.
"Ki dauka Jikar jikar azakafi." Jikinta yana rawa ta nufi gurin wanke wanke, ko hannu bata wanke ba, ta soka wasu mugayen faratan ta, masu ɗauke da mugun datti. Ta fara cin abincin kamar wacce ta samu nama.

Sai da Lantana ta bari hankalin Sidrah yayi nisa da cin abincin kawai ta rufeta da duka, sai da ta mata likis, tana huci sannan ta barta. Bayan ta gama jin dukarta ta mike taje ta dibo ruwan wanke wanken, ta zauna tai tana yi ana b'ata kwanukan, har aka gama abincin rana bata tashi ba, kasancewar dambun tafasa ce, tana samu ta mike aka nuna mata cikin tukunyar dambun, tace mata.
"Sai ki kankara na san zai isheki!" Gyada kai tayi tare da zama ta kankare, sannan ta fara ci a hankali. Tana gama ci tasha ruwa, a gurin ta baza hakarkari sai barci.

(Kyakyawar gabatarwa Jarumar mu! Kuyi hakuri jaruma ta bata kai 💯 dan bata cikin most ontop population Celeb! Bahaushiya ce yar yankin Kasar hausa)

Tunda ya nufi Unguwar, yake yatsina fuska, domin ya tsani shigowa garin Hadeja, musamman unguwar kakanin shi,. A hankali yake tusa kan motar shi, kasar wata bishiyar durumi, wasu irin yara ya hango yan gajajjeru masu rusa rusan ciki, da shafefen duwawu, fuskarsu da kuwa, tagwayen majina ce, wacce ta bushe. Hade da bushashen kunu, sannan kansu gwandal gwandal, gashi sunyi fari sol da kasa, sakamakon hunturun da ake bugawa na kata'i, idanun Aamil ne ya sauka akan wani yaro wanda majina kore shar ya sauko daga kofar hancin shi, aikuwa ya janye ta tare da jan hancin, ya kuma laso inda (🤣😂🤭 Wallahi ban tab'a labari me ban dariya irin wannan ba, ina dalili an sani karewa yaran cikin gari tanadi) da harshen shi kofar hancin shi.
. Wani irin amai yaji, tare da kauda kan shi akan yaran, hango wata yarinya yayi tana cusa hannunta a cikin kofar hancinta tana sakace tasono, zata kai baki ai bai san lokacin da ya nemi sauke amai ba, da sauri ya fita tare da barin gurin bayan ya rufe motar.

Cikin gidan Ya nufa, inda ya hadu da  Sahiya tare da Harira, suna ganin shi suke fara sake mishi murmushi da yalayalan hakoran su. Daure fuska yayi, tare da kauda kan shi. Ya nufi cikin gidan. Bakin shi dauke da sallama, a hankali yabi sassan gidan ya gaishe su, sannan ya nufi shashin Baba Haliru. Da sallama ya shiga cikin gidan. Ya tsaya a bakin kofar.
"Lale maraba da zuwa! Sannu mutanen dutse Barka da zuwa."

Murmushi yayi sai da Khaleesah ta had'iye yawu, dan tana karanta littafin hausa, bata tab'a cin karo da wanda aka tab'a fasalin namiji Irin Aamil ba, kai ko zata mutu ta dawo, tayi imani zata fi wancan sakaryan da aka bashi yarinyar da ko girma bata yi ba, nan aka shiga jera mishi ruwa, da abinda zai ci. Shi dai idanun shi na nima mishi gimbiyar da ake ihun yaje ya ganta.
Sati Uku da suka gabata.
Alhaji Ma'aruf  shi da Wan shi da suke Uba daya suke tattaunawa akan yanayin cigaban da ake samu na kasuwancin shi anan yayi shiru cikin damuwa kafin yace wa Malam Haliru.
"Wato Yaya wannan dukiyar da ake kasuwancin dashi ba nawa bane! Na Hauwa ne! Ina son Aamil ya nutsu ya kuma rike dukiyar Mahaifiyarshi, amma abu yaci tura dashi ake wawar dukiyar ma. Gashi baya jin magana shine kwaso yan mata kwaso samari azo a cika min guda da shaye shaye."

"Toh kayi mishi aure mana!" Kallon wan yayi sannan yace.
"A ina zan sami wacce zata iya zama dashi?"

"Akwai mana! Ba za a rasa ba. Ni zan duba mishi ko nace na duba Mishi. Akwai Yar Kamilu. Yarinyar, tana shan azaba a cikin gidana, idan nayi magana kamar na kuma kunna mata azabar ce. Bata da wani girma sabida bata wuce goma zuwa sha daya ba.

....idan aka bashi ita, zata zame mishi karfen kafa, domin zata zame mishi reno zai yi. Kafin ya gama haukar shi ta shiga jikin shi. Wanda haka zai sanya. Ya gane cewa ana hakuri dashi, idan tayi mishi kuskuren kuma ya had'iye. Amma kayi nazarin abun yarinyar tana wahale na gaji da ganinta cikin kangin rayuwa....
#Mai_Dambu..
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***
https://my.w.tt/sGJtOL2t7ab

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem
#Abun ki
04
Raba idanun shi yake, a hankali yana niman inda halittar zata fito mishi. gefe  guda kuma yana sauraron kus-kus din da mutanen gidan suke. A ranshi yace.

_Ashe ko ina ba a rasa wahalallu_

"Ke Altine! Ina Sidrah take?" Tura baki yarinyar tayi sakamakon tambayarta da Babatar tayi mata, ta juyawa tayi ta tab'e baki tare da nuna mata Kofar madafin tace mata.
"Innarmu gata can ya she kamar asara a gidan biki"

Juya idanun shi yayi ya sauke a can arewa maso yamma na gidan ya hango wata buntuntuna, tana kwance sai barci take. Tun bai ga fuskarta ba yaji amai ya taso mishi, dakyar ya mike tare da cewa.
"Toh zan tafi."
"Toh Alhaji karami, dan bature. Mungode yanzun zata zo." Yana fita Inna Lantana tana bin shi da mugun kallo.

Sabuda mugun kyashi da hassada da ta sakawa ranta, Sahiya ta nufi inda Sidrah take kwance ta kifa mata mari, tare da shureta da kafa tana fadin "algungunman kawai. Bak'ar kaddarar kin hana kowa farin ciki, gwara ma ki mutu da yanzun nice da wannan zukekken ganyen!"

Tashi tayi jikinta na rawa, tace mata.
"Ya..." Kifa mata mari tayi sai da ta daina gani.
"Kiyi hakuri ba zan kuma ba!"
Ta faɗa tana shasheka kuka,
"Maza dauki wancan kazamin hijabin An dubu kije gurin shi jaka kawai."

Daga haka ta fita jikinta na rawa, har ta kusan fita waje sai da Ado da ƙarara, kamar wacce ta mishi magana. Ya samu gaban Hijab din, ya watsa mata tare da guduwa. Kaɗe jikinta tayi tare da fita. Tun daga nesa ya hango ta.

Bakin cikin da yake ji, kamar ya kashe kan shi dan haushi. Yana ganinta ya shiga motar tare da nuna mata inda zata zagayo. Daga cikin zauren gidan Sahiya Ummu, Mabaruka, Kibɗiya, suna kallon su. Ganin ta shiga motar shi basu san lokacin da suka ja wani mugun tsaki ba, sabida sun gama mutuwa akan shi.

Wani irin wulakantaccen kallo yayi mata sannan yace.
"Ba zan kuma zuwa ba, idan kuma na kuma zuwa ki sani zan baki kyauta mutuwa ce! D'aga min rigar ki na gani!" Jikinta na rawa ta shiga cire hijab din jikina wanda yasha mugun dattin Bala'i.

Sannan gaban Hijab ta yage har kasa, wuyar hijab din ne a rike da hijab din, sannan wani irin zarni da warin Datti yake fitarwa, sabida rashin wanki da kulawa. Wani banzan kallo yayi mata me kunshe da bakin cikin kana da kyakyaminta wani karin malolon takaici ne ya tsaya mishi me cike da tashin hankali, sannan yace mata.

"Dama a haka suke tunanin zan zauna dake? Babu kome a kirjin ki? Toh idan kika ce zaki aure

ni yankan rago zan miki keee!"
Ya but mata tsawa, wanda ya sanya ta zabura, take fitsari ya fita a jikinta, zunzurutun tsoron shi da ya kama ta, wani irin ɓaci rai yaji kamar ya rufe ta da mugun duka, aikuwa ta d'ago dagwala dagwalar idanunta akan shi.

Dukar motar yayi cikin tashin hankali ya juya tare da watsa mata wani mugun kallo tare da bude aljuhun motar shi ya fidda kudi yan dari biyar, ya watsa mata, sannan ya kuma ce mata.
"Bude min rigar ki na gani?" Ya faɗa yana bude mata idanu, cikin cool Voice tace mishi.
"Malam ya ha..!
Toshe hancin shi yayi tare da kakarin amai, ya bude motar ya shiga sheka amai, kamar wanda yaci mugun abu. Sororo ta tsaya tana duban shi. Kallon me cike da tsoro yana juyawa yace.

"Na shiga uku na lalace, meye nayi da zafi aka hada ni da wacce zata kashe ni, ke sidira kike ko Sidrah, billahil azim zan b'atar dake matukar aka kuma ce miki zan zo ki gudu kawai, domin zan kai ki inda ake yanka mutane na sayar da wannan karamin kanki, su yanka ki.".

Shiru yayi cikin takaici da jimamin wannan hadin gwarmai da aka mishi, kamar wanda aka ce Mishi ya kalle ta yaga tayi hamma, "innalillahi wa'inna ilaihi rajioun Ya Allah, ke fitar min a mota!" Ya daka mata tsawa.
Wani irin abu taji ya tokare mata wuya, cikin zubda kwalla tace mishi.
"Kayi hakuri bazan kuma ba!"

Sake tozali da yayi da red teeth ɗinta wanda suka yi wani tsatsa daga jikin dasorinta, ya dashi cewa da ƙarfi. "Am deeply death, ke zombia ce, idan mutum yayi kuskure kika cije shi da wannan hakoran ki, zama dodo zai yi dan haka fita idan na kuma zuwa garin nan a sanya ni a Lazza a daure.

Munmuna me kama da, dark ghost get out." Ya daka mata tsawa, ai kuwa ta juye mishi sauran fitsarin dake cikin maranta. Ji yayi kamar yayi ta kurma ihu, tare da jibgarta ko zai samu sassaucin abinda tayi mishi.

Allah Sarki, tana fita ta koma bayan durumi ta zauna tare da cusa kai a tsakanin cinyoyinta, ta fashe da kuka tana faɗin.
"Me yasa baku tafi dani ba? Me yasa da zaku mutu baku janyo ni mun mutu tare ba?

Mama na gaji da kome bana so kudawo ku tafi dani, wallahi bani son zama a nan." Ta fada cikin kuka me ban tausayi, yadda take kukan sai jikin mai sauraro ya mutu.
"Ke Sahiya ga munafuka, ko kumar uban me take? Shegiya annamimiya,  dama nan kika fito ina kudin da ya baki?"

Cikin rawan jiki da rashin dabara ta mika musu kuɗin,suka kuwa rufe ta da duka, tare da jan ta a kasa, zuwa cikin gidan.
"Lantana! Kizo Kinga abinda Yaya Bature ya bata, Shegiya munafuka take zata haƙa rami ta

binne, sabida uwarta da Ubanta sun biyaki kadan renonta.

Kai wannan yarinya akwai bakin ciki yar banza me gadon tsiya, ince Ubanki ma da ya tafi cirani, abin arziki bayi wa kan shi ba balle ya ajiye miki. Toh wallahi Lantana sai ki dage domin rijiya ta bada guga ya hana, yarinya da mugun hali, ace a baki wannan makudan kudaden ki fara tunanin b'oyewa Yo Allah na tuba idan aka yi auren ai ruwan gidanki ma sai mun roka ki bamu. Hattara dai Lantana domin kifi na ganin ka me har koma, kinyi renon wahala."

Inji Iya Larai, wani irin bakin ciki ne ya turnuke Lantana. Ta kamo Sidrah, ta shiga dukarta tare da kwallon da ita, tana faɗin.

"Dan uwaki nan aka kawo min ke, an kashe iyayenki wato bari na gama wahala dake, shine xaki gode min da boye abin da saurayi ya baki yar banza dangin asara toh wallahi bani isa ba, koda zaki mutu dan bakin hali sai nasha arzikin gidan ki, yar banza me mugun nufi, zai kare akanki maha'inci."

Tsabar duka ko motsi bata iya yi, sannan ta watsa mata ruwa, wanda ya d'ago da dattin tare da kaikayin ƙarara da Ado ya watsa mata, ihu take na birgima babu wanda ya kuma bin ta kanta, duk suka watse abin su, suka barta a cikin wannan yanayin. Har sai da. Allah ya kawo Sabitu, dan Lantana na uku, ya ga halin da take, nan ya dibo ruwa a rijiya ya zuba yayi mata wanka shima ba ace wanka ba, dan da toka ya mirza mata tayi wanka rabonta da wanka tun auren Atiku. Shima sabida ganin Idanun jama'a yasa Lantana ta bata wata ajiyayyen kaya da aka b'oyewa.

Saratu, yar ce Lantana kenan. Itace Sa'ar Sidrah. Komawa gefe tayi tana sauke ajiyar zuciya, shekaru biyar kenan da kawo ta Hadeja, tun bayan rasuwar Iyayen ta, bata kuma samun kulawa ba, wani irin kuka ne ya ke zuwa mata, amma bata da ikon yi. Sabida sanyin da ake busawa yana shiga jikinta, tare da rawan sanyi. Wata riga da skirt na Amintako aka bata, skirt din yayi mata yawa sosai, sai da ta daure k'ugun. Sai rigar shima har gwiwarta, sai wani bakin pant me shegen datti, ta saka tare da komawa gefe tana ajiyar zuciya. Haƙoran ta yana haduwa da juna.

---

Yayi tsaki ya kai sau hamsin zuwa sittin, sabida bakin cikin, haka yake tukin gangancin tare da nazarin al'amarin. Cizon lips d'inshi yayi, tabbas dole ya nemi mafita dan ba zai tab'a sadaukar da Rayuwar shi a tare da yarinyar can ba.

..... Zaune suke a tsakar gida, Hajiya Surayyah, ta mike ta barsu dama sun hadu ana zagin Hajiya Uwani ce, sai Hajiya Surayyah ta mike zuwa ban daki. Kamar jira Ya Hindatu take tace.

"Ban da rashin girma da hankali, ai ko cewa Surayyah aka yi ta haihu ba zata yarda ba, dube fa nan da sabon wata za a kan kayan auren Ali da Ghali, ga Yan matan ta nan suma aurar dasu za ayi amma matar nan ta baza zani ta kuma dauko ciki. Gaskiya budurwan zuciya tana damunta."

"Hmm! Yaya kenan, ai ita burinta ta tara dukiya, dan ta sami kason gado. Kome zata yi da shi oho, yara goma ina zaki kai su, Ahtoh maji ma gani. Na mu ido.". Hajiya Amarya na dire aya Hajiyar mu na fitowa, hannunta dauke da lakar inyamurai, wato farar kasa. Zama tayi tana leka hanyar waje, suma kuma ba zaka tab'a yarda anyi gulmarta ba. Kallon Agogon wayarta tayi sannan tace.
"Karfe biyu! Uwar yan boko an kusan dawowa. Ai matar nan ina kallon ikon Allah, karfi da yaji. Ta hana Alhaji bada cefene fa, amma ai da shi yake bada cefene."

Cabewa Hajiya Amarya tayi sannan tace.
"Yanzun kayi magana ta nuna maka ita tafi karfin ka, kiga lokacin zuwan mu bikin Atiku hadeja, kin bin motar mu tayi karshe dan bakin munafunci sai gata a motar Alhaji..wai ta tsaya aiki shi yasa ta rasa motar mu.

Kuma karki manta nice da girki fa!"

Jin hayaniyar Yaran gidan sun taso daga makaranta, yasa su katse hirar, mik'ewa tayi tare da nufar kitchen, tana duba dafuwarta, amma tana tana sauri dan kar su yi gulmarta. Tana barin gurin Ya Hindatu tace.
"Ke dai zaki sani, sakarya kome sai kin nuna son a sani, sai kace ba a nan aka hanata Daukar ciki ba, sabida matsala amma dan rashin sanin ciwon kai ta kuma kwaso ciki, yaron da ko shekara daya da da rabi bai yi ba.

Ita nan sai tayi goggaya da mutane."
"Ai na fahimce ta, ko zani na sauya sai tayi ki duba shekaranjiya nake bawa kafinta sauran kudin kujerun da za a min sabida bikin yaran nan ashe matar nan.".
Shiru tayi, sakamakon fitowar Hajiya Amarya tana zare idanu, tare da shan jinin jikin ta, alamun nayi da ita, ganin babu kome a fuskar su, yasa ta karasowa dan a cigaba da zagin Hajiya Uwani.
"Ina gaya muku, wallahi badan bana son damuwa ba, ai da sai na nunawa Uwani iyakarta. Domin ranar abun ya bata min rai, taya ni da mijina ke ki makale mishi."

Fakon idanunta Ya Hindatu tayi ta mata gatsine (😂🤦🏿‍♀️🤦🏼‍♀️ please don Allah kar mu zama fitinannun a cikin al'umma! Mu zama mutanen kirki wanda duk rintsi zaka ji ana bada shaida akanka, ina dalili a lokaci guda ya Hindatu ta haɗa gulma tayi da Amarya a bayan Hajiyar mu, tayi da Hajiyar Mu bayan Amarya,kuma yanzun ta zauna ana yi da Ummi. Me muke nima? Ace baka da aiki sai gulma, Allah ya kyauta."

"Mama kizo ki zuba mana mita wallahi yunwa muke ji." Dake bata son ta tashi ayi da ita, sai ta kasa koda motsine tana son a zagi Hajiya Uwani...
#Mai_Dambu...
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

https://chat.whatsapp.com/GIIFqCembtoD3Bp6yWve7C

Don Allah idan kana Groups dina karka shiga wannan na masu bukatar Free Pages ne! Please karku shiga 🙏🏼

*Masu tambaya akan Sunan Labarin! Kusan zan fada muku cewa aya ce ta Alqur'ani kamar Yadda Allah madaukakin sarki yace. He released the two seas, meeting {Side by side} between them a barrier [so] either of them, transgresses 55:19:20! Da fatan zaku fahimta, and indai ruwa biyun zasu zauna a guri guda daya ba zai shiga daya ba, sannan koda ya shiga zai fita! Toh taya haka zai faru? Labari ne akan Halayyar mutane biyu! Duk wanda ya karanta PROLOGUE zai fahimci ainihin kan labarin! Halayyar mai kyau da Mara Kyau! Shine Ma'anar Ka sayi daya ka samu daya kyauta Shine ruwa biyu! Daya me dad'i daya me gishiri! Taya zamu banbance su koda kuwa sun kasance a kofi biyu! Sai ku tayani duba su*
#Taƙaddama
05

"Wai lafiyarki? Ki tafi ki basu abinci mana, kin wani kasa kin tsare, tare da addabar mu da tsida yawu, sai kace wata farin shigar ciki." Inji Ya Hindatu, cike da jin kunya me hade da jin haushi ta mike, ranta bai so ba, ba dan kome ba sai dan gulmarta da tayi imanin zasu yi.

Tana mik'ewa Ya Hindatu ta tab'e baki tana faɗin.
"Algunguma, kin iya ta wasa baki son ayi taki, dani kike zancen sakarya."

"Hmm! Ita nan mai wayo sai da Jamilah suka je shagon kafin ta aka ganta gurin wai ta kama kame kame, ita gata nan mara gaskiya biris nayi da ita na zubawa gudu ruwanta ido, naga iyakatar."

"Assalamun Alaikum!" Inji Hajiya Uwani. "Wa'alaikimun Salam, Uwar biyu kyautar Allah, Barka da zuwa, ya aiki? ". Murmushi tayi sannan tace masu.
"Alhamdulillahi ya gida!"
"Lafiya lau,"
"Toh sannunku da aiko!"
"Yawwa sannu da dawowa.".
"Yawwa sannunku da gida, "
Tana wuccewa suka bita da zunɗe, tare da nuna bayanta, da baki.

Wato gidan Alhaji Ma'aruf, babban gida ne,  domin a sauran jikin gidan ya fidda wasu shashi

kusan tara, idan ka cire na Aamil wanda yake ciki. Sauran duk suna wajen gidan ne, amma akwai hanya ta cikin gida.

Kowani shashin na wajen gidan flat ne na zaman mutane biyu, Ali da Ghali. Flat din su biyu, kowa da shashin sa..
Faruq da Mujaheed, shashin su suma ɗaya. Kuma dukkan su kusan ginin su irin na Aamil ne.

Sulaiman da Ismail suma gidan su daya Mahmoud da Saleh suma haka Bala da Isah. Duk suna zama anyi musu...... Dakin Hajiya Surayyah, yara biyar zata aurar. Ali da Ghali, Jamila Safiya, harirah. Wadannan sune za ayi auren su nan da wata uku.

----
Bayan sallah azhar ya shigo gidan, ya samu ana dambe akan abinci,
"Wani wani irin rashin mutunci ne? Dan Ubanku." Sake kwanon suka yi tare da kamewa guri guda, suna rawan sanyin tsoro.

Tsaki yayi sannan ya wuce dakin Hajiya Uwani, yana shiga ya zube a kujera, ya kalli Aseed, cikin damuwa yace.
"Bani ruwan sanyi!"
"Kai wuce kitchen ka dauko mishi ruwa mara sanyi a gora, Son zanga ranar da zaka bar shan ruwan sanyi babu amfani a jikin d'an adam balle ka samu abin yi kullum."

Zuba mata rinannun idanun shi yayi cikin damuwa, yace mata.
"Wallahi idan ban sha ba, toh ba makawa zan zuki wiwi! Dan ina jin kaina kamar zata yi bindiga, Ummi wai meye yasa sai ni ne zaku hada da wancan halittar?

Duk cikin gidan nan a rasa wanda zaku yiwa wannan yankan kaunar sai ni, idan baku sona ku gaya min mana? Wallahi ban tab'a ganin abin da ya d'aga min hankali kamar wancan halittar ba, yarinyar da babu komai a tare da ita sai Warin Datti haba Jama'a."

"Shine matsalar ka?" Cizon bakin shi yayi cikin baƙin ciki yace mata.
"Wallahi bana sonta, koda kun bani zan iya guduwa na barta, karshe ina nufin zan iya saketa na barta don Allah karku hada ni da ita, kamar yadda nake nan kamata yayi na samu Yarinyar da aka yi ta dan ni ba wacce aka yi ni dan ita ba..kin gane maganar gaskiya nake gaya miki amma tabbas zan gudu na bar auren nan."

Kura mishi ido tayi, na wani lokaci kafin ta kauda kanta sannan tace mishi.
"Meye matsalar yarinyar?"
Gyara zama tayi, sannan yace mata.
"Wallahi ba zan boye miki ba, ni bana sonta ne! Ummi ni a rayuwata ina son abu me kyau, ina son abu me daukar ido da hankali. Ina son abinda zan gani na tabbatar me kyau ne, Ummi ki duba lamari na, idan bai min ba taya zan samu dashi."

Shiru tayi tana mamakin shi, tabbas ta yarda da batun shi, domin shi din mutum ne mai mugun don kyale kyale, duk abinda zai samu ko zai baka toh zaka samu dangin kyale kyale ne. Sannan abu ne mai matukar kyau da kyale kyale, dan haka ta fahimci abinda yake cewa. Da gaske baya son Yarinyar ne, koda an bashi zai iya wulankata ta, karshe a samu matsalar zumunci. Amma taya zata fahimtar da Alhaji ba tare da ya zarge ta ba? Dan tayi imani da Allah, cewa zai iya take sányan shi botsarewa. Numfashi ta sauke kafin tace mishi.
" Amma Ni dai ka Hadani da jagwal domin babu abinda zai hana ace nice na hana ka don kayi hakuri da yarinyar mana, domin zata."

"Ummi wallahi ba dai da wancan me zubin halittar mutanen b'oyen ba, domin ni na zan aureta ba Allah ya gani. Duk abinda zai faru sai dai ya faru."

Zuba mishi ido tayi, jikinta yayi mugun sanyi tunda ya fadi haka wallahi ba zai zauna da yarinyar ba, dan haka ta shiru.

.. wani irin murmushi Ya Hindatu tayi lokacin da taji tattaunawar su, dan haka  ta shige dakin su ta fesawa Mahaifiyar ta, suka zauna tare da kitsawa Ummi karya da gaskiya.

Wanda zai tashe ta daga fadar Alhaji Ma'aruf, ya kuma bindige Soyayyar Hajiya Uwani. Murmushi Hajiya tayi sannan tace.
"Rabu da yar banza dani take batun, wallahi sai tabar min D'ana tunda ba tare na haife su ba, na gaji da makircin Uwani."

"Ai Hajiya ba ita kadai ba shima Dan Sarki ya kamata a taka mishi birki ki saka uban y mishi barazana, akan Ya auri Hasnah domin wallahi haka zai kuma hade mana kan shi a ruwan sanyi."

"Wannan ifiritun yaron zaki samu kanshi da wuri! Bar mafarkin haka domin kafiyar bala'i ce dashi." Inji Hajiya.

Haka suka yi tattaunawa, har zuwa lokacin da yayi musu.

Al'adar gidan Alhaji Ma'aruf, abincin da ake dafawa da rana,ana kaiwa Kasuwa..sannan na dare kuma ana juyewa Babban kula ce. Sannan akan ajiye kwando Babba da kulolin samarin gidan, domin diban abinci, haka ya samo asali ne daga Hajiya Uwani, wacce zuwanta ta samu ana b'arnan abincin a gidan, idan aka zuba a kulolin ba lallai bane, suzo su ci. Domin yayi sanyi. Amma idan aka kwashe a cikin babban abu aka saka laidar siga aka rufe, har washi gari da zafin shi. Ka'idar abincin gidan za a dafa kome da rana, da dare kuma ayi tuwo miyar da kika san me gidan yana ci. Nama kuwa ana kawo na dubu biyu daga kasuwa, domin akwai kifi na rana, na dare akwai namar miyar.( Wannan shine kadan daga cikin gidan ɗai-ɗaikun masu kudin mu! Musamman Hausawa! Asalin wannan shine yadda suke tafiyar da gidajen su, amma idan akwai wacce take da sani bayan haka ta min magana, zan gyara sosai 😍😘🤩)
Akwai doya, da dankalin Hausa, da na turawa. Akwai taliya wanda koda b'acin rana zai

saka a makara, akwai wanda za a dafa sabida gudun b'ata lokaci, wannan tsarin Na Hajiya Uwani ne.

Sannan ba kullum ake soya kosai ba, da kunu. Idan girkin Hajiya Uwani ce, har ta fita ba a cin kosai da kunu, dan akan soya dankali turawa rabin buhu ne, na hausa kwata, sai a dafa shayi da kayan kamshi, sannan tayi miyar kifi, wanda yake kasancewa. Miyar da za aci dankalin dashi. Wani lokaci kuma takan gayawa Alhaji Ma'aruf yazo mata da kayan cikin rago ko na saniya, sabida ita gwana ce a girki, kuma baya jin kunyar a kawo abincinta kasuwa, dan har makotan shi. Tambayar shi suke,
"Alhaji Ma'aruf! Girkin Maman tagwaye ne? Dan muna son girkinta.".cikin farin ciki yaƙe gabatar musu da abincin. Shi yasa da ya gaya mata, taji dad'i kuma dama kular da ake kai abincin kasuwa nashi ne shi ya saya, dan haka tafiyarta wani course Lagos, ta shiga kasuwa ta sayo manyan warmes guda hudu, tare da manyan tire na zuba wasu abubuwan dangin salat, dan haka ranar girkinta ta fito dashi ta fara aiki dashi.

Haka ya bawa matan gidan haushi, suka shiga gulmar ta, tare da nunawa cewa ta cika iyayi da sanabe..

Bai dame ta, ita abinda ta sani mijinta da yaranta, sai Aamil. Kuma duk da wannan surutun ranar girkin ta, hatta tuwon dare baya kwana, domin idan ya kwana ana sake yin dumamen shi ayi a cikin abincin karyawa toh na Hajiya Uwani baya kwana, idan kayi latin zuwa diban abincin toh zaka kwana ciki. Sannan ita daya ce duk dare sai ta dafawa mijin su shayi. Abin har ya zama Aamil yana zuwa sha. Shima da flast d'inshi.

A hankali Ghali shima ya shiga sahu, sannan Aliyu. Duk su ukun nan itace Uwar dakin su. Domin da ita suke sirri ta kuma san sunawa Baban su barna, dan haka take zama tayi musu nasiha, amma sun zama sai addu'a, Aamil tana mishi Uzuri sabida rashin uwa, su kuma Ali da Ghali, asalima uwar su ce take kara bude musu hanyar cutar da mahaifin su.

----

Idan muka duba ta yanayin kasuwancin Alhaji Ma'aruf, yana da shagunan sayar da abinci. Sannan yana da shagunan sayar da babur, wato irin su Bajaj. Sai kuma shafin sayar da magani abinda ya karanta, duk wani kudin da zai shigo daga wandanan shagunan ta Office din Aamil yake shigowa kasancewar shi wanda ya karanci accaunter.

Amma abin tausayi, shi ne me rubda ciki akan Dukiyar, dan wai Uban ya gaya mishi gaskiyar dukiyar mahaifiyar shi ce, Aamil yana da almubazzaranci, amma abin yana masifar b'atawa Uban rai, babu yadda ya iya dashi ne sai yake binshi da ido.

Faruq da Mujaheed, suna inda ake sayar da Bajaj, Bala da Isah suna inda ake sayar da magani, Ali da Ghali, suna shafi Daya. Na sayar da abincin. Mahmoud da Saleh, suna dayan shagon sayar da kayan aikin gini, idan akayi ciniki misali dare yayi sukan tura gundarin kudin aiki. Office din Aamil.

Idan ana niman mutumin da ya fidda hakkin Iyalin shi Alhaji Ma'aruf ne, ana ganin Hajiya Uwani itace yar gaban goshin sa ce, kawai amma kowani zuciya tana son mai kyautatta mata, Hajiya Uwani kuwa bata tab'a jin ko sau daya ta cuci mijin su ba, koda nawa zata kashe idan da zai zo ya tambaye ta, mika mishi takardan take. Bata tab'a jin a ranta ko sau daya ta zalincin abinda yake bata ba. Haka shima ganin tana kokarin kare kimar shi da dukiyar shi sai ya sashi kokarin ganin ya cusa soyayyar ta a zuciyar shi yadda babu wanda ya isa ya faɗa mishi abu akanta, ya dauka..

Toh su sauran matan gani suke ba haka kawai ta bar shi ba, suna ganin kamar ai ta mallake shi. Da wannan tunanin suke kallonta, bayan ita kuwa halayyar yan boko ke bin jikinta,bata da lokacin kowa sai na aiki. Bata da lokacin kome sai na yaranta da mijinta. Wannan kenan.

....... Har Aamil ya bar d'akin, bata daina nazarin abinda zata gayawa Mahaifin shi ba, shi kuwa ganin ya zareta cikin damuwa, kawai ya nufi Ofishin Abban su,ba tare da damuwa da mutanen da suke Office din ba ya gaya mishi abinda ke ran shi,zai fita Abban shi yace mishi.
"Duk abinda zaka yi sai dai kayi amma aure babu fashi, kuma wallahi ni da kai ne,mutumin banza."

"Nifa wallahi bana sonta duk abinda zaku yi sai dai kuyi amma wallahi babu abinda ya dame ni!"

. Idan ran Uban yayi dubu ya b'aci. Sai da Alhaji Ahmed abokin shi yace mishi.
"Tuntuni kayi wannan kuskuren! Yaron nan baka tab'a yunkurin hada shi da Magret ba, gani kake kamar kana kai shi zata kwace shi, da ace tun fil azal ka ja shi a jiki da babu abinda zai tab'a faru. Kaga illar rashin bincike, gashi ya girma ya kai minzalin da za ace yana da yara sama da uku amma ya zama mara kirki a gareka. Baka san wani abu ba. Allah ya bamu dama domin muyi amfani dashi amma kai da kasamu sai kayi watsi dashi, wata uwace zatayi wurgi da d'anta, sannan taki dawowa, kayiwa kanka Adalci, wallahi ba haka kawai Magret tayi fushi ba, karka manta a ranar da abin zai faru diamond ɗinta ta baka, kazo ka sayar ka daina yawon bin neman aiki, amma sabida rashin adalci, da aka ce maka ta gudu baka bi bayanta ba, duk da lokacin na gaya maka kayi maza kabi sawunta kace kai a'a. Yarinyar da ta bar dukiya me tarin yawa tabiyo soyayyarka, me kake tsammaci zata yi wallahi bana raba dayan biyu koranta suka yi gidanka sai kai,.duk wanda yayi yayi yunkurin juyin musu hali zasu bashi mamaki."
_Wannan Littafin na kudi ne_
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/JAgNlnN98ab

**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Kayan aure
06
"Alhamdulillah! Ya zanyi? Na kasa fahimtar kome akan Hauwa, duk abinda zanyi dan ita nayi amma sabida son kai tayi tafiyarta, shi yasa ban bi bayanta ba. Ba wai!"   Katse mishi magana Alhaji Ahmed yayi cikin nutsuwa yace mishi.

" Baka da wani excuse! Domin kuwa da saka hannunka kome ya faru, kai da kanka ka gaya min kasha dukarta, amma haka bai sanya ta bar ka ba,karka manta tunda ka saka hannu a jikinta kimarka ta fara raguwa, a hankali tana hakuri da kai baka fahimci tsawon lokacin da ta dauka tana share kwalla ba.

Ni da kai Mahaifinta yaƙe gaya mana cewa. Ba zaka iya rike ta ba, dan ya rene ta da SOYAYYA ce,ya rene ta, ta yadda babu abinda ta nima ta rasa, haba Ma'aruf. Wai yaushe ka zama mara kirki ne? A ranar da abin zai faru, kake gaya min baka san tana ajiye da dukiyarta ba, sai da kazo zaka fita niman aiki.

Ta ciro ta mika maka, sannan ta kuma ce maka bata jin dadi, kai kanka kayi imanin ba zata iya tafiya ba a rana, yarinyar da muka zo da kayanta sama da kwati bakwai sai da aka wayi gari , rigar da take sawa babu maraban shi da ta almajirai, sannan kace ta gudu ne dan tana da dukiya a hannunta, kai a  tunanin ka da tana son guduwa ai da ta tafi, tuntuni amma sabida soyayyar da take maka yasa ta tsayawa. Kayanta da ta dauka ta baka, sannan ta ta tashi gudun da kake fada bata tafi da kome na ta ba,sai wannan duwatsun Haba Ma'aruf idan mai magana wawa ne, ai majiyin shi ba wawa bane. Kayi nazari da kyau shi yaron da ake son yabi ra'ayin ka,. Ka tab'a tambayar shi meke damun shi? Baka tab'a ba, da zaran an gaya maka yayi kaza ranka a b'ace zaka hukunta shi. Sabida zunzurutun son kai.

... Toh wallahi matukar ka ɗore a haka Tabbas akwai matsala, domin kuwa za a wayi gari yana adawa da duk wani abun cigaba da zaka kawo mishi kayi nazari da magabata, kayi dubi da abinda na gaya maka. Matsalar Aamil daga cikin gidan ka aka faro shi. Ba wai daga ko ina bane laifin uwar shi ya shafe shi.    A wannan duniya kowa son ka shi yake kowa na shi yake so.

Kai kuwa kayi watsi da naka, lokacin da ake bukatar ka more shi ya juya maka baya, sannan maganar gaskiya indai yadda ya kawo korafin Yarinyar bata mishi ba, mishi ba  hakura da auren nan haka."

"Ba zai yiwu ba! Yarinyar zai aura, naji nayi laifi batun auren Sidrah ko Aamil yana mutuwa ya dawo sai ya aureta. Balle kuma babu abinda zai faru, aure ne sai yayi shi. Indai Ni na haife shi." Duk wannan musayar  yawun da suke, Alhaji Abubakar yana jin su. Gyara zama yayi bayan ya kalli Alhaji Ma'aruf, ya sauke numfashi sannan yace musu.

"Wato wani kuskuren da muke aikatawa, bamu sani ba, shine hada iyayen mu mata da matan auren mu, ba dan kome ba sai dan babu wata uwar da zata jure ganin wata ta juya Mata D'anta, musamman iyayen mu da suke da duhun kai! Gani suke sun gama wahalar su, lokaci guda kinzo kin juya mata hankalin D'anta, sannan suma matan mu, basu iya hakuri ganin an juya musu akalar mazajen su. Sabida ai su, suka fi dacewa da juya mazajen su ba iyayen mazan ba.

Kaga irin wannan al'amarin. Ya sani raba gidana biyu, mahaifina tana can bayan layin mu, har da yan aikinta da duk wani abun da take bukata na tura mata, har mota nata na kanta, na saya mata. Da driven ta, gudana kuwa nayi kokarin tsayawa namijin duniya, babu macen da zata rena min uwa, kuma naki yarda na dauki damuwata da Matana na kai na gayawa Mahaifiyata.

Badan kome ba, sai dan kawai na tsira da kwanciyar hankali na, ka nutsu da kyau, taya za ayi a ce da kome sai Mahaifiyar ka ta sani, wannan shine dalilin da ya rabaka da matar ka! Shine dalilin da ya rabaka da Yaronka. Babu wani wanda zai gaya maka gaskiyar da muka gaya maka.

Kayi ƙoƙarin raba gidan ka, koda mahaifiyarka bata da matsala akwai me kaiwa da komowa, dan haka kayiwa kanka Adalci wallahi wata rana zaka ji kunyar wofantar da shi da kayi fa."

Shiru yayi yana nazarin abinda suka gaya mishi maganar gaskiya haka ne, babu karya a cikin maganar su, amma kuma ta ina matsalar take?
"Na rasa fahimtar kome? Wallahi sai naji kamar bani ba."

.... "Eh mana! Sabida baka nazarin abinda kake kawai zartarwa kake da umarnin mata, su kuma nazarin su bai da tsawo kamar namu, sannan ka nazarci,maganar Auren nan mana."

"Alhaji Ahmed, ba naki maka bane Yarinyar tana bukatar Aamil a rayuwarta, mareniya ce yar kanin mu da aka kashe a rikicin kabilanci na garin jos, shine aka dawo da ita, Hadeja, toh yarinyar tana fama da gallazawar jama'a gidan da take shi yasa nake son aura mishi ita, yayi renonta dan bata wuce shekara goma sha daya ba"

... Sake baki suka yi suna kallon shi, ganin da gaske yake yasa su mik'ewa suna faɗin.
"Amma baka da mutunci, wallahi ba dani za a fara batun child abuse ba, kawai ka nima mishi manyan yan mata, amma yar sha daya, ina magidabci irin shi zai hakura da ita, idan ba so kake a bugaka a jaridar Daily trust ba."
Inji Alhaji Abubakar,

Murmushi Alhaji Ma'aruf yayi sannan yace musu.
"Babu abinda zai yi mata koda anyi auren karatu zasu tafi shi zai tafi masters ita kuma zata karasa primary zuwa secondry, kafin ya dawo tana secondry."

Sake baki suka yi suna kallon shi, ya sake murmushi sannan yace musu.
"Ba zan hana shi tafiya da ita ba, amma kuyi nazarin lafiyar shi, kafin ya rabu da ita dole zai so

alaƙa da ita kodan yaji haushin renonta da yayi, sannan dole shakuwa zata shiga tsakanin su. Kun ga kenan haka ya ishe ni amfani ya sauya halin shi."

Zama Alhaji Ahmed yayi sannan yace mishi.
"Kuma kayi kyakyawan tunani! Domin kuwa, shi zai more kuruciyarta amma mutumina kai fa mugun kwaro ne." Dariya suka saka abin su. Tare da bin yaran da addu'a.

**

Koda Alhaji Ma'aruf ya koma gida, nan Hajiya da Ya Hindatu, suka kitsa masa kome, murmushi yayi tare da godewa Allah da ya hada shi da abokan arziki, domin kuwa zai yi wuya ka fahimci yadda mamaki ya rufe fuskar shi, yanzun da a ce Aamil bai zo ya fadi ra'ayin shi ba toh ba makawa, laifin Uwani zai gani dan haka da yabar dakin suna tsammanin zai haurawa Uwani ne, sai suka ji shiru bai kuma bin takan zance ba.

***

Tana tsaye kamar wata Status, sai had'iye yawu take, tana kallon yadda kowa yake diban tuwon masara miyar karkashi, gashi tayi kyau Koriya shar. Sai wani daukar ido take, har tuwon ya kare ba ta samu ba, a wulakance. Lantana ta kalle ta, sannan tace mata.
"Toh uwar haladu, kakar Musa. Zaki zo ki dauki sauran mara ki dama ga dandano can a daki ki saka sai kisha,dan babu miyar ta kare, ni kuma bani da Manja ko mangyada da zaki ci tuwon dashi, yar banza nan da wasu watanin zaki daina cin cimar mu, zaki koma ta yan birni, ja'ira kawai."
Jikinta na keerrma ta wuce, inda taga tuwon yayi sanyi, da ta kula sai ta ga ashe najiya ce ma, dan haka bata da zab'i ta shige cikin dakin ta dauko dandanon ta dama tuwon ta diga ta fara ci, haka kafin wani lokaci har ta cinye. Hamdala tayi sanan ta koma can gefen kitchen ta zauna, tana kallon saratu, Sahiya, sannan takiya tazo, sai sauran Yan matan gidan suka shirya suka nufi maciyar da take kofar gidan su. Ita kuwa bata da ikon fita.
"Sidira!" Da sauri ta mike tare da cewa..
"Na'am Innah"
"Zoki kashe min kwarkwatan nan wallahi sun dame ni."
Da sauri na iso kofar dakin Lantana, ta bude wani dambun kanta, Ya ilahi. Wato tsabar kazamta gashin har baka hango layin kitso, ga kan a duskure. Lantana irin siraran matan nan ne, gata baka mai tamushashen fuska. Hancin ta kuwa ba laifi dan yaso zama siriri amma ya koma babba, jin yan yiririn. Hannun Sidrah akanta tace mata.
"Yar banzan baki dan cewa bakwai mike ce ke ba? Ai ke yar wata bakwai ce shi yasa baki girma, sai shegen wayo da idanun kamar babanin tsaka,

Wannan aka aurar dake ai daren farkon sai da a fidda gawarki, yar Kwankwanso uwa, Yar kashi kanwar tusa.". Haka take kallon Sidrah take kare mata tanadi.

**

After few weeks.

Babban taburama aka Baje a tsakar gidan, ana fidda kayan auren da Hajiya Uwani ta hado, tare da Aminanta matar Alhaji Ahmed da Hajiya Sakinah matar Alhaji Abubakar, da Hajiya Ubaidah ana Baje kayan a hankali, sai tab'e baki Ya Hindatu take, dan ba haka taso ba. Ita a tunanin ta a bawa Hajiya Surayyah kudin su shiga kasuwar Dutse a sayo yar ka gudu ka sami lafiya.
Toh asalin hada kayan ba ma a gidan Hajiya Uwani ta haɗa ba, dan kaiwa Gidan Abokan shi tayi, domin turamen atamfofin kwatono suka je suka sayi su. Tsaf lace kuwa Hajiya Ubaidah da zata tafi Chaina aka bata kuɗin shi da kayan dakin Jamila da mafiya, Safiya da Sidrah. Dan ya dauki nauyin zai mata kome. Sauran kayan ne da kayan kitchen suka sayo a dubai, dan ya sake kudi kuma bai tab'a aurar da yara ba, sai wannan karon. Duk a cikin kayan da aka sayo na Sidrah ne babu bra.. amma ba laifi kayan sun hadu iya haɗuwa.

Kuma Ghali da Aliyu sun bada karin kudin su. Abun gwanin sha'awan. Kallon kayan Alhaji Ma'aruf yayi sannan yace mata.
"Allah yayi miki albarka Rabi! Nagode sosai, gashi keda Yan team din ku. Kun hada min abinda ban zata ba." Bayan an gama hada kayan kowa tace musu.
"Ni zan dauki kayan Aamil! Sauran kuma su dauka su kai dakin Iyayen su, Na gama nawa, sannan ga wannan yan kunnen da sarkokin su, da zobban su. Azurfa ne na saya musu nawa gudummawar kenan,!

"Hmm!" Inji Amarya, wato bata gamsu ba. Sannan ta mikawa Alhaji Ma'aruf wani karamin akwati tace ya bude..yana budewa yaga wani kyakyawan zoben arzufa  tare da set din shi duk yafi na sauran haduwa an rubuta A&S. Murmushi yayi sannan yace mata.
"Allah yasa ki gama da duniya lafiya!"
"Mu kuma mu kare da duniya a lalace ko? Alhaji Ma'aruf wallahi kama kai kanka wutar jahannama? Ko"

Murmushi yayi sannan yace mata.
"Habbaratu baki da hakuri, kome na duniya dan hakuri ne, kin san nawa kuɗin abin da ta saya ne? Toh bana son haka!"

Shiru tayi tare da kauda kanta, ita ko Hajiya Uwani ko a jikinta, tace mishi.
"Abban su,  kayan kitchen na yan matan na saka musu nawa gudummawar, har da zanin gadon na kara musu, yadda suma zasu fita rasa."

Jinjina kai yayi tare da jin kaunar ta yana kuma kara hoda zuciyar shi. Matar tasan me take yi. Bayan ta gama mishi bayani sannan ta ciro sauran canjin shi Naira dubu talatin da biyu ta mika mishi tace mishi.
"Alhamdulillahi na gama aikin da ka sani, ga sauran canjin ka da fatan kome lafiya, ga list din abinda muka kashe duk zaka gani anan sai kayi min bayani idan ban rubuta kome ba." Ta faɗa mishi tare da mika mishi wani dogon takarda, sannan ta shiga kwasar kayan Aamil ita da yaranta, suka kai d'akinta. Dan tana kokarin danne Zuciyar tane, amma tana jin yadda suke mata magana kasa kasa, tare da tsaki. Ita ba mutum me son rigima ba. Shi yasa ta bar musu gurin su cinye kan su, ina dalili.

Bayan ta tashi shima Alhajin ya mike ya bar su a gurin, ai kuwa suka shiga kushe kayan wasu na cewa. An cuci Abban su ne, zagi irin na rashin da'a haka suka yi, suna cikin haka Oga Aamil ya shigo, yana jin yadda suke zagin Hajiya Uwani, tare da yaran su. Kawai ya gyara murya sannsn yace.
"Ku da aka zagi Ummi daku, ku tashi ku fara tsallen kwad'o kafin na shiga dakin na fito."

Sun san tunda yace ba makawa sai sun yi shi, dan haka suka mike tare da fara tsallen, shi kuma ya bar su a gurin basu isa su koda hutuwa ne sabida halin shi, yana shiga dakin shi ya ga kayan..kamar wanda aka zage shi ya hau fada da fushi karshe ya bar gidan ma, ba tare da ya yafewa masu tsallen kwad'o ba.
#Mai_Dambu
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

https://chat.whatsapp.com/GIIFqCembtoD3Bp6yWve7C

Don Allah idan kana Groups dina karka shiga wannan na masu bukatar Free Pages ne! Please karku shiga 🙏🏼

#Juyayi
07
Babu wanda ya kuma bi ta kan Aamil, sabida sun fahimci fitinar shi yake kawai, dan haka babu ruwan kowa da damuwar shi auren babu fashi. Ya buga ya buga aure babu fashi.

.... Dan haka ya shiga daki ya zauna na wuni guda yana nazarin abinda zai aikata. Bayan kwana biyu, Hajiya Uwani da Kawayenta tare da Ya Hindatu suka kai kayan auren Aamil Hadeja, bayan an Baje kayan. Tana can bakin rijiya, tana jan ruwa, da wani mummunan kayan jikinta, riga da zani ce, zanin an mata sanda, amma bai hana tsakiyar zanin darewa na.

Gashi kwana biyu tana fama da kasuwa, dan haka idan ruwa ya tab'a jikinta susa take har tana zubda kwallar dad'i, gashi ciwon ya kama duk wani gabb'a na jikinta, sosawa take kawai. Bata san me ake ba, dan haka ta tsayar da Mati ya daura mata bokitin paint. Ta nufi hanyar shiga shashin su, taga mutane, dan haka ta karasa da sauri, tacewa.
"Altine sauke ni don Allah!"

Tsaki yarinyar ta mata tare da cewa.

"Toh ki dawamma da ruwan a kanki, banza kawai."ta fadi haka cikin jin haushin Sidrah,
"Toh don Allah ku sauke ni, wuya na!" Ta faɗa tare da fashewa da kuka, mik'ewa Hajiya Uwani tayi ta hango ta kanta yana rawa zata sake bokitin.
"Lantana Sirikar tawa aka bawa wannan katon bokitin, baku san yana maida mace baya ba? Yarinya karama an daura mata wannan bokitin, ku matsa min na wuce, baku da amfani" haka ya bangaje yaranta yi ta saukewa Sidrah bokitin, a ranta tana cewa.
*Insha Allah ƙarshen wahalar ki tazo!* Yanzun ta kuma yarda da hadin domin ko babu kome yarinyar zata samu kulawa.
"Hajiya Uwani! Ina in-law din mu take?" Inji Hajiya Ubaidah, murmushi tayi sannan tace musu.
"In-law na me tsada ce, idan kuka ganta prize d'inta ya sauka ku bari sai nan da wani lokaci zaku ganta! Idan kun gama kuyi min magana."

Riko hannunta tayi suka fita, tare da nufar shashin Baba Mamman, tana kallon Yadda matan gidan suke hararar Sidrah, shimfid'a mata taburama aka yi, ta zauna tana murmushi. Tana kallon yarinyar tare da tausaya mata, a ranta. Tabbas idan Sidrah ta samu kulawa, mace ce sosai ta bugawa a jarida.
"Shekarunki nawa?"
Ware idanun tayi tare da d'aga kanta tace mata.
"Ban sani ba"
"Yayanku Aamil ya? Me yace miki?"
Shiru tayi na wani lokaci kafin tace mata.
"Bai ce min kome ba!"
"Bai miki barazana ba?"
Sunkuyar da kai tayi kasa, sannan tace mata.
"A'a bai ce min kome ba!"
D'ago kan yarinyar tayi, tana yabawa da zurfin cikin ta, tace mata.
"Toh babu damuwa! Kina zuwa boko?" Ta kuma tambayarta.

"Eh kafin kayan makaranta na su yage, ina zuwa amma yanzun Baba yace min ba zan kuma zuwa ba." Ta fada a sanyayye,
"Toh!" Kar'ar wayar ta ya katse mata maganar da zata yi, ta dauki wayar a sanyayye ta saka a kunne, "ok!" Mik'ewa tayi sannan ta fito ta samu har sun fito.
"Uwani wai boye mana Sidrah kike?" Inji Ya Hindatu,

"Sidrah!" Ta kira sunanta, a sanyayye yarinyar ta fito tana rab'ewa da bango, har ta iso gabansu, cikin wani irin soyayyar da ita kanta Hajiya Uwani bata kawo Kawayenta zasu yiwa Yarinyar ba, wanda tafi zaton tausayi ne.
"Zo nan Y'a guda ba bari ba, sannunki Yar mu!" Nan suka shiga janta a jiki kamar babu wani abu a tare da ita, nan bakin cikin ya kuma rufe yan gidan, suna jin ina ma da Yar su ce ta samu kanta a cikin surukar Alhaji Ma'aruf, sunyi imani za a fifita ta sama da yadda ake fifita kowa, sai wancan bakar me munin kamar zunubin. Haka suka mata kyaututtuka masu yawa, sannan suka fita daga gidan.
Kamar jira ake subar gidan, kuwa aka kwace kome tare da mata shegen duka. Sannan aka

korata sai kallon kayan suke.
"Wallahi idan nice sayar da kayan zanyi, makira ai ta samu"
" Amma baki da hankali, Lamiyo, waye ya aike ki, baki ga sun tafi da wasu abubuwan a cikin yar karamar akwati ba, toh wallahi, kome na su a kirge yake babu ruwa na."inji Lantana, sanan suka kwashe kayan aka kai dakin ta.

A hanya suke jajjanta yanayin da suka ga Yarinyar, cikin jin haushi haushi Hajiya Sakina tace musu.
"Wallahi yana cikin dalilan da yasa bana son family house, ina dalili yarinya mareniya an maida ita baiwa, wallahi ta bani tausayi sosai, aurenta da Aamil shine mafita a rayuwata."

"Mhh! My dear, shi yasa bana kaunar Nadrah tayi auren a family house, domin yarinyar bata da sittings yanzun wani ya kai ni ya baro ni, tunda kome kika gaya mata dauka take." Ganin zasu sake baki Hajiya Uwani ta juya musu harshe take suka an kara da Ya Hindatu, suka ci-gaba da tattaunawa da harshen turanci. Har suka iso gida.

***

A hankali kome yake tafiya sauran ma an kai kayan su, tare da kawo nasu Jamila, bikin na karatowa, ana musu gyaran na musamman yaran da ake so fa. Ita kan Sidrah me ta sani da za a mata gyara mata.

... Ana saura wata guda bikin yana kallon kowa da ido, gashi Alhaji Ma'aruf ya kuma basu kyautar mota, inda yace zasu biya rabi shi ya biya musu rabi. A gurin Alhaji Abubakar ya saya musu, amma na Aamil duk yafi nasu kyau datsa. Duk da haka bai hana wasu jin haushin Aamil ba.

Sannan wani adalci da yayiwa mazan haka yayiwa matan, inda matan dukkan su ya biya musu Umrah har da Sidrah dole aka tura Aamil yaje ya dauke ta a hoto wanda za a musu passport, tana can gidan bishiya a kofar gidan yazo, tayi shiru tana kallon masu carafke, dan wasan yana nishadantar da ita, sai dariya take, yau karon farko ta samu farin ciki sakamakon, Lantana basa gari sun tafi Auyo, kusan ma duk matan gidan. Kallon yadda take ware yalon hakorinta ya sashi jin haushin yana zuwa inda take ya suri kafarta tare da watsa mata kayan hannun shi.
"Na baki nan da minti talatin kiyi wanka ki fito muje wani guri." Kamar mara gaskiya haka ta tashi ta nufi hanyar cikin gidan, taje taja ruwa a tsorace tana zare idanunta, tare da niman soson danga, dan shine nata, sannan ta nufi ban daki tayi wanka da ruwan sanyi, bawai tana jin daɗin shi bane kawai bata da yadda ta iya, gashi Kazuwa ya rike mata wandonta, a hankali tayi ta zuba ruwa har ciwon ya jike ta cire wandon. Ta fita a hankali sabida ba wai ta yarda da kanta bane, kayan da ya kawo mata ta dauka riga da skirt ne yan kanti, sai wata fashion hijab iya wuya,me hade da hular shi. Ta shafa man shafawar ta, dangwali yabe. Sannan ta fito fuskar nan kamar anyi barin mangyada a cikin dan wake. Kauda kai yayi dan duk wani dakika kara tsanar yarinyar yake ji. Ta shigo kaddarar shi ta lalata mishi goben shi.

Ta lalata mishi farin cikin shi, ta mai dashi abin b'oye kai a cikin abokan shi, ko jiya da dare sai da aka yi ta mishi dariya a club. Sabida zai auri yarinya karama wacce bata fi hanjin cikin shi

ba, kauda kai yayi lokacin da yayi tozali da katon makeron fuskarta.

Wanda yake kan cin jikinta, daga nan suka wuce wani shagon hoto, suka je aka mata passport. Daga nan ya dawo da ita, gida Allah cikin iko. Shi basu dawo ba, dan haka ta cire kayan ta ninke ta ajiye a bakin kofar Lantana.

Koda ya juya ji yayi motar shi tana kamshin manda tashafa me warin kalanzir bude glass din motar yayi iska na shiga. Har ya iso garin dutse.

...

Ran shi a b'ace yake sosai, dan haka yana shiga gidan yaji Harira tana yiwa Ummin shi rashin kunya dan tace mata wanke wanken da wuri zata fita, shine take cewa.
"Ai kina da yara Me zai hana kisaka su suyi tunda sauri kike!"

Yana shigowa ya kwashe ta da mari, ya kuwa zaro bulala ya shiga zaneta, Ali ya fito.
"Wai kai Aamil me ka dauki kanka? Ina ruwanka da ita, idan ka ji haushi kayi wanke wanken mana!"

Sake bulalar, ya kalli Hajiya Surayyah, cikin tsantsar rashin mutunci yace mata..
"Surayyah baki gaya mishi kece kika yi sanadin korar min Uwata a gidan nan ba keda wadancan algungunman matan. Ko karya na miki? Sarkan da kike alfahari dashi na Uwata ce! Kome da kike sakawa na kawa keda su Mero da Hindatu, dukiyar Uwata ce, dan haka wallahi ko tattaro min ko kuma na jininku yayi malala a tsakar gidan nan."

Shiru gidan ya dauka kafin. Hajiya ta fito tana faɗin.
"Toh anamimi, ba zamu bada ba, wato ka zauna ka samu wata ta gaya maka kayan mu na mahaifiyarka ce toh karya ce da Arzikin Ma'aruf ta same shi idan kuwa ka dage sai na tsinewa Ubanka,"

"Ji min abin dariya, toh ki tsine mishi mana! Idan zai dame ni, d'anki ne ke ce da...." Tass Ummin ta wanke shi da mari.
"Hajiya ba sa'arka bace! Girmamawa ita a tsakanin ku!"

"Ummi!"  Ya kira sunata  a sanyayye, Tabbas bayan ita ta mare shi ba da yau gidan nan sai anyi bala'in da ba'a ta yin shi ba ko da a yakin duniya.

....juyawa yayi  ya bar musu gidan karewa ma, kenan. Ran shi ya kuma b'aci, dan haka ta kalli Hajiya cikin damuwa tace mata.
"Kuna tunanin na mare shi ne dan kawai na dakatar dashi? Ko daya na nuna muku idan ban isa da yaran ku ba, shi da ban haife shi ba na isa dashi, yaushe aka haifi harira, shi kuma da hakoran shi na same shi, Harira sa'ar Muh'd ce, amma kuka baza kune yana min rashin mutunci.

Ban san me kuka dauki rayuwar gidan nan ba, amma kusani duk abinda kuka shuka a

baya, da sannu zai dawo. Koma yaya kuka boye zai bayyana, Hajiya ke uwace! Ki raba kanki da shiga rayuwar Aamil tunda babu wani abinda zaki mishi ya burge ki. Idan ba haka ba zai cigaba da zaginki tare da tozarta ku.

Karki ga yau na dakatar dashi, idan kika tsinewa Ma'aruf kece kika yi asarar bashi ba, sabida ya rigada ya gama mishi wani amfani ya bashi ilimi da wasu abubuwan, sannan kai Ali da kake cewa me yake takama dashi dukiyar Uwar sa! Wanda kowa yake kokarin ganin ya hamdame shi,. Shi yake diban shi a duk lokacin da ya kalle ku yagan ku a matsayin bayin shi sai yaji kome yazo mishi dai dai, dan haka ka rage tambaya wata rana zaka tambayi abin da zai dame ka. Hajiya Surayyah kiyi kokarin ganin kin nuna Yaranki tarbiyya, da ace shekarun baya kin daura Yaron da aka bar miki bisa tarbiyya, da yau Allah ya dubi naki ya baki wanda ba zai ja miki zagi ba.

Kuna tsammanin dan ya lalace ba zai tankawa kowa bane zuciyarshi bata yi wannan lalacewar ba, dan haka a kiyayye abin da harshe zai furta, zuciya zata iya fadawa matsala."

Daga haka ta bar musu falon ta koma d'akinta, dama kwana biyu Ya Hindatu ta kora musu nasu aiki wai kar a dami dan uwanta wanda bai damu da ita ma irin son a sani farkan kusa da gida.

.... Tun daga ranar suka rage wani tsiyar, gefe guda kuwa Malam Aamil yana shirya musu tanadi.

Kallon kowa yake bayan yasake ran shi kamar da gaske, abin da ya daurewa Hajiya Uwani kai yadda yake shige da fice, kamar da gaske, dan makaranta yake zuwa yayi wasu abubuwan tabi didigin shi amma bata ga kome ba. Dan haka ta share batun shi.

Ga bikin yana kuma karatowa, kuma dan banza shiri yake kamar Kowa, masu zuwa Umrah an daga dai bayan bikin zasu.

---

Yau saura kwana uku, bikin abin mamaki sai sako aka Alhaji Ma'aruf ya samu Office din Aamil a rufe yau kwana bakwai baya zuwa aiki. Da aka shiga ciki kuwa aka samu Zungurerren takardan ya bar musu kasar..
_Nasan amarya tana gudu idan bata son aure Amma ango ya gudu🤦🏼‍♀️🙆🏾‍♂️🙏🏼 Muazzam fito ka kare kanka Wallahi ba ayi kome ba a labarin ko sunawa ba ayi ba, amma nasan mun dauki hanyar Chakwakiyya 🤦🏼‍♀️ Ango ya gudu_

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/GbW5hwzNbbb

***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Juriya
09

"Meye abun bakin ciki? Cikin dake jikinki? Toh Allah ya kyauta." Ta bar dakin abinta, dan ta lura baki daya jahilci na damun Hajiya Surayyah.

Washi gari da safe bayan an gama abin karyawa aka kira amare, suka shigo da farko zasu yi rawan kai, ganin yadda take musu bayani, wani abubuwan na girki ma basu sani ba, sai jikin su yayi sanyi, musamman yadda take wurga musu turanci, take duk suka sha jinin jikin su, bayan ta gama sannan tayi musu sallama zata tafi aiki.

Raba kan su, suka yi wasu suka dauki wani aikin wasu suka dauki wani.
Sun nutsu suna aikin kawai, zaka dauka wani abun Arziki zasu aikata,
"Sannunku amare aiki ake haka?" Inji Hajiya, d'ago kai suka yi tare da zuba mata ido, kafin aka samu Ummita tace mata.
"Eh Hajiya!"
Gyada kai tayi sannan tace musu.
"Hala bata gaya muku ana kaiwa Kasuwa ba? Wannan matar akwai bakin ciki a ranta, dan haka kuyi abinda yayi muku kawai karku dauki tsarinta."
""Toh Hajiya" suka ce mata.

. Hajiya na fita Hindatu na Shigowa, kallon su take kafin tace musu.
"Uwani bata gaya muku muna son yaji ba? Toh ku zuba mana gishiri sosai!".
"Amma kuma tace mana Abba bai da lafiya bay..."

"Ke Ummita! Babu ruwanki da wata mata a gidan nan idan ba zaki iya girkin ba, wacce shashin ki!" Inji Surukata Hajiya Surayyah,
"Toh umma." Dan haka taja bakinta ta shiru, sai ya zamana tsakanin Hajiya da Ya Hindatu anawa juna wani irin kallo. Kafin kowacce ta bar kofar.

A hankali suka gama aikin aka zuba na shago, tare da zuba na cikin gidan, suka dauki nasu suka watse.
Bayan wasu mintuna aka dawo da abincin Alhaji Ma'aruf, da kanshi ya kira Hajiya Uwani, yayi fada sosai. Sannan yasata dole ta dawo gida ta mishi abinci yana jira. Hakuri ta bashi daga haka bata kuma cewa kome ba. A hanzarce ta dawo gida, tare da fara aiki babu shiri.

Matar Ali ce ta shigo gidan ta ji kamshi na tashi, kasa hakuri tayi ta leka kitchen ɗin taga Hajiya Uwani da Aashiq da Aseed tare da Abdus Samad, suna aiki su yaran sun mai da hankalin su kan abinda suke mata, itama ta kuma mai da hankalinta kan girkin ta. Wanke namar kaza Aashiq yayi tare da ajiyewa a choping board, ya shiga yankawa yana zuba mata a cikin kwando, Aseed yana barbada mishi garin flour me mix din kayan kamshi dangin curry da thyme, ingredients da sauran su. Abdus Samad yana yanka Albasa, tare da tomatos. Sun mai da hankalin su sosai. Ita kuma tana fama da hada cus-cus, jollop din shi.

Dake Yarinyar wayayya ce, shigowa tayi tare da gaisheta tace mata.
"Da wanne za a taimaka miki?"
D'ago kai tayi tare da sake mata murmushi tace mata.
"Huta abinki latifah!"
"Ai bazai yiwu ba, kawai ki gaya min abinda zan yi, indai har Mazaje zasu shigo aiki meye amfanin mata irina."

"Da kin barshi wallahi!" Ta faɗa mata cikin lumana,
"Don Allah."
"Shi kenan! Jalil!" Ta kira yan biyu, da gudu ya fito.
"Gani Ummi! Kiyi sauri ana spider man."
"Lallai zan kashe kallon nan, tunda lokacin islamiyya ya kusa..ka je frig ka dauko min fruit maza ka kawo min, kace Jalal ya tayaka dauko min, kayan salat din nan."

Haka yaran suka yi ta kwaso mata duk abinda take buƙata, sannan tana aiki tana duba agogo, tare da turawa Alhaji Ma'aruf sakon hakuri, dauko wani katon bowl tasa Aashiq yayi ya kawowa Latifah, tana gama wanke ya'yan itacen ta shiga yanka su, Hajiya Uwani tana nuna mata yadda zata jera.

Shigowa Hasnah tayi tana kallon yadda Hajiya Uwani da Latifah suke aiki, sannan tafita, can suka kuma shigowa ita da Hajiya.
"Uwani aiki ake haka!"
"Eh hajiya!" Ta bata amsa a takaice.
"Toh kar a manta da tsufar mu dai, a tuna da cewa dana ake aure."
"Hajiya kiyi hakuri! Amma wannan abincin na baki nayi bana Alhaji bane, gurin aikina zan kai."

Wani irin shiru ne ya gifta tsakanin su, Latifah tace.
"Ummi duba, haka yayi da ace akwai Strawberries honey ko Apple honey, sai a zuba a kai. Sannan a saka sweetened condensed milk a zuba yummy."

Murmushi Hajiya Uwani tayi sannan tace mata.
"Bani da honey's din amma ina da condensed milk."

"A kawo kiga yadda ake yin shi, i holp Abba bai da diebetis?"

Ta tambaya, murmushi Ummi tayi wanda kusan zan iya cewa dabi'arta ce, sannab tace,
" Bai da shi!"

Ana kawowa ta zuba a kai, sannan ta dauki foil pepa, ta nad'e tiren dashi, sannan ta kalli Hajiya Uwani, tace mata.
"A ina zan saka?"

"Toh saka a wannan freezer din, kafin mu gama kar yi dumi,!" Ta nuna mata firij din dake kitchen din. Kallon Juna Hasnah suka yi da Hajiya, sannan suka fita da guntun kwadayin su.

Amsar kasar da flour din tayi, tare da kallon Ummi tace mata.
"Wannan muna kiran shi Orange chicken, amma India suna kiran shi briyami."

"Kina da experience Sosai akan girki." Inji Hajiya Uwani ni..
"Eh Ummi, nayi diploma na akan girke girke ne, sannan na kuma yi HND na akan girkin, shi yasa nake da ɗan sani kadan akan girki. Toh da zan tafi University ne, Baban mu yace na bari idan mijina yana bukata na tafi a gidan shi!"

"Goodluck! My dear. Kice bani daya bace nake da sani a bangaren girki ba, lallai zamu ci dad'i. Ina koyarwa a jami'ar nan Dutse, amma na shiga class na girki 2002-2003, na sami kwarewa akan sarrafa abinci,

Yanzun Muh'd nake so kafin ya shiga SS1 na saka shima ya fara samun horo akan girki, Babana yace zai yi wani aiki ba, mr Chef ne shi, ko Abdus Samad."

Dariya suka saka lokacin da Hajiya Surayyah da Amarya suka shigo, juyawa Latifah tayi hannunta kwaɓe da ruwan kwai wanda aka dama da flour za a soya, kazar d'anyen ta.

"Mamarmu ina wuni! Yanzun zan shigo ina taya Ummi aiki ne."
Ta faɗa kanta a kasa..
"Ya kamata kan dan kin san nice Mahaifiyar Aliyu! Wasu tsabar rashin tsoron Allah, sukan janyo abinda ba nasu ba, su maida nasu.  Amma Latifah ba Aliyu yace miki karki na shiga harkan kowa ba, sai d'akina ba?"

Wani irin kallo Yarinyar ta bita dashi sannan tace mata.
"Inji Aliyu?" Mamaki ne ya kama kowa, jan wayarta da yake samun window tayi tare da kiran layin shi, tace mishi..
"Wai kacewa Mamarka kace kar na shiga cikin hidimar mutane sai na ta, Aliyu kasan a gidan mu, ba a koya min tashin hankali ba, sannan ban iya ba, idan kasan gidan ku akwai damuwa maza zoka mai dani gidan mu, ban sha'awa damu."

Kome ya ce mata ta sake tsaki tana fada mishi  dalilin da yasa takura shi, cikin murna yace mata tayi ta shigowa tana kuma samun kwarewa akan girki dan Ummi ba karamar gwana bace,

karshe suka yi sallama, kallon Hajiya Surayyah tayi sannan tace mata.
"Muje Hajiyar mu na baki hakuri."

Wanke hannu tayi suka fita, kome ya faru, sai dai yarinyar tafito hankalinta kwancen. Suka ci-gaba da aikin su. Anan Hajiya Uwani take mata fada akan abinda tayiwa surukarta, ta kuma ce bazata kuma ba.

Koda suka gama, ta dauko wani babban kula, ta cikawa Latifah abincin sannan ta nufi hanyar gidanta.

Koda aka kai abincin kasuwa, mutane ribibin abincin aka yi har da Ali dan yasan matar shi tana cikin aikin abinci.

***
Zaune take a gaban murhu, tayi futufutu da ita, sai jan majina take, sabida sanyi da ake na watan Janairu, sake jan hancin tai, a kawo na biyu. Gashi babu wani rigar sanyi a jikinta.
"Kwasss!" Aka kafa mata rankwashi, agigice ta d'ago kanta tare da murza hannunra a kan.
.dan ji take kamar ta sake fitsari.
"Munafuka, wutar abincin har yanzu bata kama ba."

"Wallahi bata kama ba," tana sosa kanta, cikin jin zafin rankwashin.  Komawa daki Lantana tayi ta kuma kwaso kayan wankin su, ta labta mata, sannan tace?
"Maza ki fara aiki ina jiranki!"
Cikin rawan jiki. Tana aikin girkin tana kuma wankin, har dumamen ya fara konewa, sannan ta sauke amma sai da ruwan zafi ya zuba mata a kafa.

Kara tasaka, tare da yarfe hannun. Tana cikin wannan yanayin ashe bakin zaninta dake roba ce ta kama da wuta, lokacin Sahiyah ta fito daga dakin su. Ganin yadda take tsalle da ihu, tare da wurgi da zanin ta faɗa cikin kwatar da suke zuba wanke wanken. Tana kuka sosai. Sabida ruwan roban da ya koma cinyarta.

"Subhanallahi! Me ya faru?" Inji Malam Haliru, tab'e baki Sahiyah tayi tare da cewa.
"Wasa da wuta take ya kama zaninta"

Cike da mamaki yake kallon Sahiya, sannan yace mata..
"Shine baki kai mata a gaji ba? Sahiyah anya zuciyarki akwai imani a cikin shi? D'an mutum ya kama da wuta ki tsaya kina kallon shi, wannan rashin Imanin har ina?"

Fitowa Lantana tayi zata shiga bala'i, amma ganin Yadda Sidrah take cikin kwata, ta tashi tare da dibo ruwa ta fara wanke mata jiki, wani irin tsoro ne ya kamata, sakamakon ganin yadda fatar jikin yarinyar yake salubewa. Jinjina girman rashin Imanin Sahiyah tayi, ta juya tare da ɗaukar tsagun itacce ta shiga maka mata, tana faɗin.
"Bani da mutunci! Amma ina da birbidin imani, ba zan tab'a barin dan adam ya kama da wuta,

ba ina kallon shi wato gaji nan mara tausayi da jin kai, Ni zaki jawa magana, Dangin Uwarta suna gari su zo, suga abinda ya faru. An bani na iya sukara nasu akai, yar banza mara imani, tabbas zaki iya barin yan uwanki tunda kika kasa jin tausayin ta."

"Kyaleta ki shirya yarinyar mu kaita gidan Sarkin makera, a zuba mata magani, dan wallahi ban san me zancewa Binto ba, idan tazo. Tunda Munki basu sannan mun kasa riketa."

Haka suka wanke mata jikinta, sannan suka dauke ta zuwa d'akin suka saka mata hijab, sannan suka fito da ita, zuwa gidan Sarkin makera, suna zuwa yasa aka sayo madara ta ruwa, sannan ya kuma sanya aka dama mata da magani aka bata, sannan ya shiga zuba mata maganin.

Kafin su dawo har ya kame tsaf. Dama cinyoyinta ne suka sabule, ta gama. Sai samar kafarta, shima ba sauki.

Koda mutanen gidan suka sani, kafin kace me! Har an kaiwa dangin Mamanta gulmar, ai kuwa suka zo dayawan su, ana aka shiga rigima karshe suka dauketa aka dawo da ita gurin yan uwan Mamanta.

Gatar da bata samu ba, shi aka shiga bata, kulawa na musanman,aka kuwa wanke kan nanda kumfar lux, aka saka wata me kitso ta mata kitso da maganin kwari.

Washi gari aka sayo maganin makero aka shiga shafa mata.

"Yaya Binto! Ina ga ki tafi da Sidrah Kano mana, dan wallahi ba wani kulawa take samu ba, duba kiga yadda ta koma, jiki duk Kazuwa, ga rashin abincin gina jiki." Inji wacce take bin Maman Sidrah Hakama,
"Toh Hakamah idan na dauketa ai zasu ce an dauketa bayan akwai Maganar aurenta a kasa, ni bana son damuwa shi yasa zan na zuwa duk bayan wata uku ina dubata. Kuma kin san ma ai ba bamu zasu yi ba."

Tunda taji suna maganar zasu mai data ta fara kuka, domin tasan ba zata tab'a zama a hannun su ba, gashi har kiba tayi
....
Dutse.
Bayan wata uku..
A cikin wata ukun nan matan su Faruq kowacce ta fidda halinta, idan ka cire matar Ali da kusan halin su daya da Hajiya Uwani.

Dan har tafi Hajiya Uwani, tsayar da Iskancin gidan take kuma bata shiga gulmar cikin gidan, da aka ga bata da lokacin su, sai suka shiga ce mata tana da girman kai, halin su daya da Hajiya Uwani.

Amma a bayan su, ake fadar haka. A cikin gidan babu wacce aka rena kamar Baria, matar

Isah, wulakanci suke mata, idan kuwa tayi musu abu su rufeta da duka, gashi sun mai da ita kamar jaka.duk abinda ake itace zata ci aiki kamar baiwar su...

----
Washington DC.
Federal capital state. USA...
Destination
Yau wata uku kenan da barin shi kasar shi ta gado. Kuma ya fara karatun shi cikin nutsuwa ba tare da wata damuwa ba. Wani abin burgewa, a can unguwar su, akwai masu maida tsohuwar mota sabuwa, dan haka jiya ya cika musu takarda kuma sun dauke shi.

Shi yasa yanzun yake tunanin ko zai juya karatun shi zuwa Injiniyar kere kere. Kawai bai gama tunanin shi ba yaji an kai mishi wani bugu a kafad'arshi..
Zafaffe ya tashi zaune tare da juyawa yana kallon su.

"Kai dan Ubanka, wato dan munce ka haɗa gwiwa damu, shine bari ka je gurin su Anthony ko! Toh yanzun zamu karya maka kafa."

Kallon su yayi tare da jan wani iska, kafin ya nad'e hannun rigarshi. Tare da ɗaukar wani kujeran katako ya shiga rufe su sa mugun duka, sun ɗauka wasa ne sai da Aamil ya raka su har wajen makarantar. Sannan ya dawo yana haki.
Sai lokacin dayawan mutane suka ganshi cike da al'ajabi suka zagaye shi suna fadin.
"Yallabai me kake bukata? Yallabai ko a kawo maka karin abin motsa baki ne? Yallabai."

"Mr rogers ka kyale shi bai cika son hayani ba, dan ko jiya mun hadu nayi mishi magana mr Gorge yace na rabu dashi."

Kallon asalin mahaukata yayi musu, ya ciro kudi zai biya coffee da ya sha, suka ce mishi "Yallabai ba zamu amshi kome daga gare ka ba. Dan burin mu ka maye mana gurbin Mr Robert William." Ajiye musu kudin yayi tare da barin guri.

Ko minti goma bai yi ba, sai gashi ya kuma dawowa, da sauri mutanen suka zagaye shi suna kuma mishi bayanin da suka yi d'azun nan. Murmushi yayi sannan ya bude baki dakyar kasancewar shi mutum ne da bai cika son dogon zance ba yace musu.
"Mr Rogers! Nagode sosai," daga haka bai kuma cewa kome ba, kallon saurayin da yake bawa kowa coffee zai magana ya kawo mishi Green tea. Murmushi yayi sannan yace.
" jackson bani coffee, nake so!" B sake yake kallon shi d'azun yace mishi Green tea yake so.....🤔🤦🏼‍♀️ Kuma dai.
Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu..
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**

*<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>*

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem.

#Alhini
08

Bude wasikar Alhaji Ma'aruf yayi cike da bakin ciki zai karanta Alhaji Ahmed ya kwace wasikar a hannun shi.
"Kayi hakuri!"
"Ahmad! Allah Ya Shirya mana Zuri'ar mu, Amma kasan Aamil ya tozartani!"

"Ka gama kome! Tunda ka nima mishi shirya, Allah ya tsare shi duk inda yake Allah ya duba Alamarin shi"

"Ni ya tozarta! Insha Allah aure babu fashi bazan zarga mata igiyar shi ba, amma tabbas dashi za a daura auren nan duk ranar da ya dawo. Mutumin banza mara kirki."

Bai kuma magana ba ya fita, ya d'ago kan tare da cewa.
"Ahmad me zancewa Haliru? .me zan gayawa yan uwana, da wani fuska zan fuskance su? Yaron nan ya kunyata ni saura kwana uku bikin ya tsalleke yayi tafiyar shi kaji yadda nake ji kuwa?"

"Kayi hakuri! Yayi laifi amma ka bishi da du'a'i, Allah ya shirya mana shi" inji Alhaji Abubakar, gyada kai yayi cikin jin tausayin kan shi, domin duk inda ake niman mara kirki Aamil ya kai.

Kallon Garzali yayi driven shi yace mishi.
"Kai ni gida!"
Cikin tsananin tausayin, Abokan shi suka yi sallama dashi, ya nufi gida. Tun a hanya yake rike da kirjin shi. Kwalla na zuba daga idanun shi. Ba kuka yakewa Aamil ba tausayin Maraicin Sidrah yake, ya kuma san gidan shi ba zai yiwu ya dauko ta ba. Domin Idan Hajiya Uwani bata nan zata zama abin tausayi.

Har suka isa gidan shi da yake bayan gidan gwamna, ya fita a hankali, ya shiga cikin gidan. Ya samu mata anata hidimar suyar cincin, kallo daya Hajiya Uwani tayi mishi ta fahimci yana cikin tashin hankali, dan haka yana shiga dakin shi ta bishi.

Zama yayi, ta juya tare da dauko ruwa ta zuba mishi a glass cup, yasha sannan ya kalleta da idanun shi da suka cika da kwalla yace.

"Aamil ya tafi! Ban san me zanyiwa Yaron nan ba, ya fahimci gatar da na mishi, ya tafi ya bar ni da kunyar mutane, meye na rage shi da  shi?"

Cikin nutsuwa sannan tace mishi.
"Ka dauki haka matsayin kaddarar mu, Allah yana sane dashi da kuma mu, muyi mishi Addu'a a duk inda yake, kar mu watsar da Al'amarin shi.  In yaso sai a dakatar da auren shi kafin nan yarinyar ta kuma girma, Yanzun ba zamu daukota ba, sai nan da wani lokaci.

Domin idan muka daukota zai zamana zata yi ta walagigi a cikin gidan nan, dan haka ka barta Insha Allah zai dawo kuma zai amshi tayin da ka mishi da hannu bibbiyu. "

"Toh ya zanyi? Me zan faɗa musu a fahimce ne, dan kowa zai ga kamar na barwa Aamil daman yayi abinda yake so ne!" Ya faɗa a raunane,
"Duk wanda ya zargeka, bai san me ake kira tarbiyya bane, domin ai kayi ƙoƙari, Insha Allah Ubangiji zai dube ka da idanun rahama ya duba Alamarin ka."

Sosai take gaya mishi magana masu taushi da dad'i, har ya sata ta kira sauran matan ya gaya musu, auren babu Aamil an d'aga nashi. Sun sha jinin jikin su. Suka yi ta kame kame, ko zasu ji me ya faru amma basu ji ba.

Ya kuma je dakin Mahaifiyarshi ya gaya mata an fasa auren Aamil dan haka ta sake guɗa. Tare fadi,
"Ga irin ta nan, ka haifi d'an da ya juya maka baya, tirr da ni ne na haife shi sai na tsine mishi albarka"

"Hajiya ba zan iya tsine mishi ba, tunda ke da kika haife ni baki tsine min ba, akan me zan tsine mishi.!" Numfasawa yayi cikin damuwa sannan ya cigaba da cewa.
"Hajiya lalacewar da Aamil yayi bai kai na wasu yaran ba, amma kuma a haka iyayen su suke jingina kome su rungume su.

... Akan me zan tsine mishi bayan Ni na koya mishi haka,ko sau daya ban tab'a damuwa da halin da yake ciki ba, kai na kawai da abinda kike gaya min nasani, shi yasa zan cigaba da mishi Addu'a har Allah ya dawo min dashi."

Daga haka ya mike zai bar dakin, jiri ya nemi yar da shi ya dafe bango. Dakyar ya dawo dakin shi ya zauna tare da dafe kanshi da hannu bibbiyu.  Karshe dai zazzaɓi ne ya rufe shi me mugun zafi.

**
Hadeja
"Wai ni Lantana ban gane ba, ba zaku yi kome na biki bane? Naga ita kanta amaryan baku gyarata ba, balle a mara wani abun Arziki.".  "Baraka bana cikin da munafunci. Wani abin biki bayan kin san cewa Alhaji yace kar ayi kome haka zamu kaita daga ita sai kayan auren da suka

kawo mata."

"Yo ai zaku ja mata abin gori, har tsofarta. Kuyi mata abinda zaki yi mata na uwar goyo idan ba haka ba, wata rana zaku ji kunya shi rayuwar duniya babu kome a cikin shi sai rudu."

Banza tayi da ita, bata kuma kulata ba, sabida bata ciki da gulma injita, dauko wata kodaddiyar nera goma tayi ta baddawa Saratu da take taya Sidrah tsifa tace mata.

"Toh amara kirjin biki maza, zoki amsowa kawarki kumfar lux, ta bera goma a wanke kwarkwatan kanta, ko zamu huta karta bamu kunya da sosa soshe." Da sauri Saratu ta amshi kudin ta falla a guje kamar wacce aka cillata.

Wato Lantana yaran ta biyar ne, Biyu maza uku mata. Atiku shine babba, sai Babangida na biyu, sai Sahiya. Sai Saratu da altine yar autan su, Saratu itace Sa'ar Sidrah, kusan tsayin su daya.
. Kuma bata da matsala kamar sauran yan uwanta, idan ka cire masifa. Amma bayan nan bata da matsala dan wani lokaci idan taga Sidrah bata ci abinci ba kawo mata nata take, a boye dan Sahiya bata kaunar taga Sidrah tana walwala.

Da gudu ta sheko da kumfar. Ta ajiye tare da washe hakori tana cewa.
"Innah ta kara mana gyara, wai nima nayi da nace mata za a wankewa Sidrah kai ne sabida aurenta, shine tace ashe ni babbar kawa."

Tsaki Lantana tayi sannan ta dangware goshinta tana faɗin.
"Karki dame ni, yar banza mara zuciya."

Tura baki tayi sannan tace .
"Toh ni ina ruwana, meye na rashin zuciya, aure da abin taya murna ne. Sidrah Kinga wallahi muka je dutse sai na haura gadonki me shegen kyau dan nasan ba mamaki..."

Make mata baki uwar tayi cikin jin haushi, sam Yarinyar bata da zuciya.
Karshe ma tayi zuciya tace ba zata saka mata kumfar ba, taje mijin yazo ya saya mata.

***

Cike da jin kunyar abinda zai gayawa D'an uwan shi, amma haka ya daure ya koro mishi jawabi, tare da niman a d'aga auren zuwa nan da shekara daya ko biyu, Insha Allah.

"Toh babu damuwa, kamar gobe ne sai ka ga abin yazo kamar ba a tab'a samun jinkiri ba."

Sun tattauna sosai, kafin suka yi sallama.

......
Da sallama ya shiga ya samu ana taje kan Sidrah sai yarfe hannu take, Lantana tana

rankwashinta, zama yayi kafin ya fara bayani wa Lantana. Wani uban shewa ta buga tare da dukar cinyata, tace mishi.
"Ba dai ya tafi yaki auren  kazamar mata ba? Toh ai abu yayi kyau"

Daga nan aka shiga yadawa Sidrah,(🤭🤦🏼‍♀️🤣😂🤣) ita kuwa baiwar Allah bata san meye ake nufi da aurenta ba ma. Wallahi, haka suka yita haukar su. Har zuwa lokacin da maganar ya gana yawo a cikin gidan, abu daya kawai yarinyar ta nuna shine bata iya koda shiga yan uwan ta, ba sabida tayi kuka, sabida ta gaji da damuwar gidan

***

Ranar Juma'a aka yi walimar mata, Ranar Asabar aka yi na maza bayan an  daura aure, kafin aka Cigaba da hidimar biki, amma ta bangaren Alhaji Ma'aruf daurewa yake, sai da aka dangana dashi asibiti, jinin shine Ya haura sosai, dole aka kafa mishi sharudda da zai k'iyayye sabida ciwon shi.

Dole aka rage wasu shagalin, tare da hakura da su. Aamil kuwa ya sha tsinuwa sabida, jin haushin ya b'ata musu shagali, haka a ciki gaba da hidimar har aka gama bikin. Kowa burin shi yace ya tsinewa Aamil, amma yaki yace kome,asalima blaming kan shi yake da laifin duk abinda ya faru.

.... "Ai Hajiya wato Magret ta gama da zuciyar Ma'aruf har yau yana jin sonta a ranshi. Gashi wancan dan banzan da muka hana ta tafi dashi ya zame mana karfen kafa, tunda gashi nan ya kuma raunana mana kome. Wallahi nayi bakin cikin yadda yaki tsine mishi."

Ga baki daya hankalin su ya tashi burin su, kawai su ji ya tsinewa yaron, shi kuma bai ce musu qala ba.

..... Bayan bikin da sati biyu, ne aka samu wani karamin tashin hankali a cikin gidan, tsakanin Hajiya da Hajiya Surayyah, badan kome ba. Sai dan tace ba za'a yi mata iko da surukatan ba, matar ali da Matar Ghali. Nan tone tone ya tashi aka kare babu dad'i, abin dai sai a hankali. Dan haka Alhaji Ma'aruf yace musu.
"Suna zuwa amsar abinci kafin su fara nasu girkin,"

"Haka yayi kaga dole wasu su hakura da aikin su. Tunda gidan dai bamu kadai bane!" Inji Hajiya Surayyah,

Gyara zama Hajiya Uwani tayi sanan tace mishi.
"Abban Aamil! Haka sam bazai yi ba! Idan aka yi dubi da yawan abincin da ake girkawa, ana daga musu takwas, sannan da dare shinkafar tuwo mudu biyar, yanzun kuwa dole zamu kara yawan abincin sannan maganar gaskiya nice zan cutu, sabida bazan iya barin aikina sabida girki ba, tunda da abuna ka same ni.

Idan su matan zasu iya fitowa su girka na rana  a ci baki daya,. Da dare kuma matar gida tayi  toh bismillah, ai munyi na sati biyu, idan kuma bai musu ba kowacce ta kama girkinta babu

kare bin damo,domin ba zan kashe aikina sabida su ba idan yayi muku toh bismillah."

Shiru falon ya dauko, daga bakin kofar shigowa Hajiya tace.
"Amma Rabi kin kawo shawara, ai suma mata ne, idan bai musu ba sai su bari su girka abin su, sannan ita Surayyah da take fadar haka, ina ce sabida matan yaran ta take wannan ihun,wato ga bayi ku girka ku basu su ci. Kar Allah yasa ko wacce yar bujen uwa ta shiga kitchen tayi girki."

Shiru falon ya dauka, sannan Alhaji Ma'aruf, ya dauki wayar shi ya kira yaran shi maza tare dasu Muhmood, suka iso. Aka yi maganar a gaban su. Tuni Ali ya zare kan shi tare da cewa.
"Ni bana ra'ayin abincin gamayya, mata na zata girka min."

"Abba na amince Ummita zata shigo ayi da ita." Inji Ghali, Bala da Isah, sale da Faruq, Muhmood, duk sun amince. Daga nan Alhaji Ma'aruf yace musu.
"Uwani kiyiwa matar da take kawo muku yan aiki. A kawo me wanke wanke, koda su uku ne, zan na baki kudin su. Sai Alamajirin da zai na sharar gidan da sauran bangarorin ku nemi yara biyar maza, sai a basu aikin. Uwani idan suka zo ki nuna musu yadda za ayi aikin. Karki Barsu kara zub'e."

"Insha Allah! Zaka same ni da zama me adalci akan kome."
Tsaki Hajiya Surayyah tayi sannan ta tashi zata fita, kamar zata bangaje Hajiya Uwani, bata hanya tayi tare da cewa.
"Allah ya kyauta, wannan al'amarin ya kamata ya tsaya haka sabida akwai surukai ga kuma ciki ake jikinki,fada ba namu bane, tunda mun girma muna dab da ajiye jikoki."

"Kina bakin ciki ne da cikin jikina? Dan ke baki samu ba."

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/ucS0zPJzcbb

**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***
https://my.w.tt/pvpSrJ4R5ab

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Sawun Barawo

10

A hankali yake kurb'an tea din jikin shi da zuciyar shi tana ingiza shi, zuwa wani guri na daban. Bai gama sha ba, ya ajiye kudi da cup din ya bar gurin. Cikin sauri.

Mamaki ya kama su, wannan mutumin da baudaddiyar hali yake, share batun suka yi. Yana tafiya wani mutum ya tare shi. Yana kallon shi, yace mishi..
"Yallabai!" Kafin ya amsa mishi AM rufe Aamil da duka, sosai fa. Suna fadin..
"Mara mutunci, shi ne ya dakar mana Yan uwan, dole shi ma mu dake shi." Zuwan yan sanda ya sasu suka bar gurin. Da gudu suna zuwa suka tambayi abinda ya faru. Cikin jin jiki yace musu.
."babu kome"  ran shin son maganar shi ta karu fiyye da baya ma, kawai yana abu kamar ba shi ba.

Haka suka rabu ya wuce gida.
--- yana tsaye gurin aikin motar su, Ya mike zai dauki abu, kamar ance ya juya tana zuwa ta kifa mishi mari, sake baki yayi tare da kallon ta.
"Ka same ni a gida, tunda abin da ka zab'a kenan!" Ta juya ta shiga BMW dinta, tana huci har zata wuce tace mishi.
"Zan rufa maka asiri amma yau sai mun je casu!."

Cikin jin haushi ya nufi inda take zai bude motar ta ja motar da mugun gudu, tare da saka sunglass dinta, tana dariya.

----
A hankali yake fitowa daga Station na yan sanda bayan ya an mishi gargad'i kar a kuma samun shi da laifi, cikin jin haushi da takaici wanda yake kwance bisa fuskar shi. Yake tafiya. Mota aka bude mishi ya shiga ya zauna.
"Mr George!  Meke faruwa dani ne? Ban san me yake faru ba, sai dai kawai yanzun muje titin Church, ina son zuwa gurin"

Da sauri aka ja motar, koda suka isa. Sun sami wasu matasa irin kartin nan, suna rike hannun su. A hankali yaji zuciyar shi tana tilasta mishi ya fita daga motar, ya rufe su da duka, koda ya fito suka yi ido biyu dashi. Guduwa wasu suka yi dan sun san ko minti biyar ba ayi da suka sha mazgar shi ba, amma ya kuma dawowa sabida ya mai dasu jakuna.  Da gudu suka bar gurin. Gayen ya fitina su gaba daya garin washington, babu layin da bai sani ba. Bin dayan su yayi da gudu, ai kuwa ya kamo wandon shi. Mutumin na juyawa ya zabga mishi naushi a fuska yadda zai kwace. Aikuwa nan ya zube hancin shi ya fara zuba da jini.

Da sauri Mr George ya fito yana me rike shi, ya tashi zaune. Yana fad'in.
"Ban dan meke faruwa dani ba! Yanzun zan yi abu zuwa an jima zai zama kamar bani ba. Idan zaka fahimta ina wasu abubuwa kamar me mutum biyu a tare dashi, ina jin tsoro sosai."

"Yallabai ana jiranka muje daga baya zamu tattauna akan batun."

---

A garejin da Aamil yake aiki kuwa, yau Lahadi babu aiki. Dake da shi daya ne, sai yaji yana sha'awar ya nufi Church abinda yazo mishi kenan. Dan haka ya dauki key din motar  Max, yana tafiya tare da niman Church din da yayi mishi yaga wasu guda biyu amma bashi yaji zuciyar shi ya aminta da su ba. Dan haka ya cigaba da tafiya har ya isa wani babbar Church me suna santi mary, anan yayi parking hango wannan yarinyar da ta mare shi yayi da sauri ya tsallaka, yana zuwa inda take kawai ya tsinka mata mari, dukda akwai jami'an tsaron da suke kula da ita bai hanata su mishi caaa ba. Juyawa yayi tare da zabga musu harara.
Sannan ya bar gurin.

Ko minti biyar bai yi ba, da barin gurin sai ga shi sun kuma dawowa da Mr George tare da Mahaifin yarinyar suna isowa ta kuma kifa mishi mari, rike fuskar shi yayi tare da jan hannunta suka bar gurin.
..
"Meye matsalar?" Ya tambaye ta. Sanyayye, kai bakinta tayi ta sumbaci bakin shi tana kuka, kauda kan shi yayi sannan yace mata.
"Kinga ni bana son irin wannan abu,nasha gaya miki rayuwata da taki a kwai, banbanci don Allah ki bari zamu sami matsala akan haka!"

."amma mari na kayi." Kafeta yayi da ido, sannan yayi kasa da murya yana fadin "kinyi hauka ne?"
Cikin hasala tace mishi,
"Ga zahiri! Idan baka daina min rashin mutunci ba, zan cire maka zobensa!"

"Toh sai me?"
"Kunga ku daina wannan shirmen, kun kusan zama guri guda."
Bai idda rufe baki ba, sai ga yan sanda, mika musu shaidar kama shi yayi dafe goshinsa yayi cikin gajiya da damuwa yace.

"Toh muje!"
Haka suka tasa keyar shi har ofishin yan sanda suka fara bincike.

***

Jigawa state
Dutse.

Wai-waiye Ummita tayi sannan ta saka hannu ta kwashe namar miyar da ake, ta juye a cikin kwano, sannan ta rufe murfin tukunyar ta taso zata fita suka haɗu da Ya Hindatu, kamar zata sake kwanon, amma cikin karfin hali ta daure fuskarta ta wuce.

Tana fita itama Ya Hindatu, ta bude zata fita sai ga Raliyah matar Mahmoud, da sauri ta

sauke murfin miyar a kafarta.

"Innalillahi! Dama Goggo kece kike kwashe mana naman biya ake zargin mune muka kwashewa da kan mu?" Ta faɗa da karfi yadda kowa na gidan zai ji.
"Ke Yar nan, dubi kaina cike yake da furfura, me zanyi da namar miyar kuma?"
"Ai Sharri nayi miki? Wato karya nayi miki a kafar waye murfin tukunyar ta fado?"

Cike da bakin cikin Ya Hindatu take kallon Raliyah ga sauran matan gidan sun zo.
"Amma Yarinyar nan Allah ya isa tsakanin mu! Yar banza ina namar yake da nadiba."

Ya Hindatu ta tambaya a fusace, lokacin da yar ta Hasnah tazo. Bude tukunyar Amarya tayi taga an kwashe namar Sosai.
"Toh gashi nan dai! Babu namar an kwashe rabin namar."

Wani malolon bakin ciki ne ya kama ta, tare da jin kunyar da bata tab'a jin irin shi ba. Idanunta na cika da kwalla tace musu.
"Wallahi na rantse muku da!"
"Babu rantsuwar da zaki yi mana, sabida Allah da. Mu girka ke da wadancan Yaranki kuna zaune. Gyaran albasa baku mana balle bare maggi, baku da aiki sai gulmar wancan da fadar wannan. Mu dai Allah ya isar mana?" Daga haka suka ja tsaki suka fita daga cikin Kitchen din..
Kusan abinda ke faruwa kenan a cikin gidan, da can baya ba a sata. Amma yanzun gidan wallahi ko bera sai haka, Ummita da Fa'iza matar Faruq. Idanun su bakan abun mutane, suna gani zasu dauka. Na Ummita ya b'aci domin kuwa ita har dakin mata idan tafita tana shiga ta diba mata abinci tafito.

Amma dake sun rena matar Isah, ita suke daurawa sata domin ita irin mutanen nan ne, masu shishigi bala'in.

..... Bayan kome ya lafa, Ummita ta shekawa mijinta tuwo miyar eguzi, tare da tsokar nama,da za a kai kasuwa ta haɗa har da na mijinta, haka ya taro abokan shi, suka ci. Sai murna yske matar shi ta sheka miya me dad'i.
***
Hadeja

An shera mata kitso me shegen yawa, gashi bakin gashin nan siɗi, har bayanta. Kuka take idanunta madaidaita, sun kumbura, dan bakinta nan sai wani bari yake kamar an jefata cikin ruwan ƙanƙara, tana zaune ta saka abinci a gaba, tana shasheka.
Su kansu tausayinta suke ji, dan har ga Allah basu kaunar rabuwa da Yar mareniyar su.
"Sidrah!"
D'ago jajjayen Idanunta tayi sannan ta maida shi akan abincinta, idan aka cire kwayar idanun ta, da hakorinta, da tafin hannunta. Kome na Sidrah baki ne wuluk ma kuwa, gata da kyau me sanyi, tare da nutsuwa a tare da ita, gashin giranta wanda ya kasance mai laushi da sheki ya kwanta, kwalla ne ya jika Eyelashe ɗinta, sai suka wani fito zarara, matsa lumshashen idanunta

tayi sannan ta dan ciji lips dinta, kafin ta sauke wasu kwalla masu zafi.
"Innah! Don Allah karku kai ni, ku bar ni anan gidan, wallahi duka ake min."

"Toh Sidrah ya zamu yi, sunce lallai amai dake, sabida akwai baikon Yayanki akanki, kuma babu amfanin mu barki kar wani abu ya taso." Inji Kanwar Mamanta.

Cikin kuka tace mata.
"Ni bana son zuwa gurin su, kawai ku barni anan mana!" Tasowa tayi ta zauna a gabanta, sannan tace mata.
"Kiyi hakuri! Wata rana sai labari, kiyi kokarin rike mairaicinki." Gyada kai tayi sannan Kanwar Mamarta ta fara bata abinci tana karb'a wanda tayi imanin daga yau tayi adabo dashi tana ci tana kuka har ta gama.
Sannan aka wanke mata kafarta, da hannun ta wanda, wanda aka mata lallen yayi kyau sosai, sai har yayi kyau da ita. Jaka guda suka hada mata na kayan sawa, sannan suka tattara ta, bayan sun saka mata. Hijab ɗinta yar Karamar, yayi mata Kyau. Haka suka tawo da Kanwar Mamarta me suna Sabuwa, kafarta sanye da takalmin Sino, kai Yarinyar taga gata babu iyaka,

Tunda suka doshi kofar gidan, gabanta ya fad'i, rike hannun Kanwar Mamarta tayi, jikinta yana sanyi zuciyarta yana girgiza.
Idan baka tab'a fuskarta halin da, Sidrah take ciki ba, ba zaka tab'a gane yadda take ji ba, ji take wani tsoro da laifin da bata san tayi shi ba, take zargin ta aikata. Duk sai ta fara tsarguwa da kanta, har suka shiga cikin gidan da sallama, wani irin kuka ne ya zo mata, amma haka ta had'iye, har suka shiga shashin Lantana.
"Lale maraba, da zuwanku Sidira, kece haka. Lallai kin sha gida yarinya kinyi kyau da kiba abinki, sannu Sabuwa, an dawo min da ita"

"Eh Lantana gata nan, kin san da D'a da dukiya ba a musu,, mugunta, koda Uwan Baba ta haifi Sidrah tasaka rai zata moreta, amma da Allah ya tashi ikon shi sai ya dauke ta, gashi irin wandanan zaki samu. Su fitina ce a cikin al'umma. Su din kamar haske ne a idanun duniya, shi yasa ba a cika kuntatta wa maraya ba sai ka ga an sami matsala, ga amanarta dan nasan wata rana goyon guba, zata iya sonki sama da mu, kin ga kenan ka shirya mai kyau kaga me kyau duk yadda kika shirya al'amarin ki sai ki samu Ubangiji ya shirya nashi. Shi Alkhairi ko sharri yan aike ne! Da zaran ka tura su zasu dawo maka da abinda ka aika dasu,ba abin mamaki bane wata Rana idan Sidrah ta zama wani abu kafin Ni na moreta kece zaki fara moranta, kinga kenan kinfi Ni kusa da ita, don Allah a kiyayye gaba konewar da tayi banda a lokacin sanyi ne da jikin Yarinyar nan ya lalace, kuma nayi imani da Allah, ba zaki so kiji ance kinyi sanadin Yar kishiya ba, shi hisabi tun daga nan duniya ake yinta idan ka je lahira sai kayi bayani da larabci, Allah yasa mu dace....

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu..

[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/AHFSeMVsfbb
**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

12
#Jajantawa

"Yallabai! Ka bari mu maida ka gida, akwai matsala. Wannan rigimar ba sabo bane dole Madam ta dakatar da Rio! Dole a dakatar da wannan badakalar."

Zafin da yake ji ya sashi fara fita hayacin sa, tare da juya kanshi. Kafin su isa gida motar asibiti ta iso, sabida kiran su da akayi, can suka nufa. Aka shiga bashi kulawa tare da allurai. Sabida sun fahimci ciwon shi ne yake son tashi.

*
Hadeja
Tun dawowarta, suka kwashe kayan da tazo dashi, basu bar mata wasu na kirki ba.

Wanda aka bar mata shi ma, wai dan kar a kaita gidan Yan uwan Mamanta babu wani sakakken kaya ne aka bar mata na fita kala biyu.

Wata Jumma'a, taje gidan Kawunta Yakubu, ranar Lantana ta mata wani irin duka, wanda ya kwantar mata da jini, a gefen idanunta, shine da tazo Yakubu ya hanata komawa sai Washi gari, ya saka matar shi Balaraba, tayi mata wanka tare da wanke mata kanta domin kwarkwatan sun dawo, kuma ga wasu kuraje da suka fito mata su ba Kazuwa ba, kirci dan sun fi kazuwa ma masifar kaikayi.

Ana gama mata wanka, ya shirya ta suka zo gidan, dake da safe ne.

Ya samu mazan gidan, a kofar gida, suna shirin tafiya kasuwa, ya sauke ta a babur din shi, sannan ya mika musu hannu suka gaisa. Kafin ya ce musu.
"Zaku yi hakuri da abinda zan fada muku amma iyakar gaskiyar kenan, Mun so kwarai mu rike Sidrah, amma kuka ce mu bar muku ita, ta zauna da yan uwanta, sai dai bamu ki ba. Amma kuna daidaita adalci, a tsakanin su kuwa?
.dan girman Allah, ku dubi fuskar Yarinyar nan mana! Ku duba ku gani, dan bata da uwa sai ta zama mara daraja? Dan bata da uba sai ta zama Allah sarki. Mu dai don Allah idan ba zai zama damuwa ba ku bamu ita don Allah zamu zauna da ita, don Allah, domin yau an mata wannan

dukar, gobe bamu san wani irin duka za a mata ba. Yarinya sai kace ba jininku ba.

Dube yadda jini ya kwanta a idanunta, haba inda Kamilu da Safiya suka tafi kuma zaku tafi. Dan duniya ba matabbata bane, dan haka kuyi hakuri ku barmu mu tafi da ita, dan mu muna kaunarta."

Shiru suka yi, tare da rasa tacewa. Suna kallon fuskar yarinyar da har zuwa lokacin bai sab'e daga dukar da Lantana tayi mata ba.
"Malam Yakubu, muna baka hakuri Insha Allah ba za a kuma ba, don Allah kuyi hakuri. Mun san ana cutar da Sidrah, amma Insha Allah, daga yau ya zama tarihi ba zamu kuma aikata haka ba, kuma zamu riketa domin nan da wasu watani za ayi bikinta, kaga kenan dole mu kula da al'amarin ta."

Sun jima suna tattaunawa, kafin yayi musu sallama, yana tafiya suka shiga cikin gidan, kaf mazan gidan sai da suka yiwa matan su tijara, haka ya kuma fusata Lantana, ta kuma cin alwashin ba zata bar Sidrah ta huta ba, shine ta tsira mata, wani mugun hali, idan aka yi sabon abinci ba zata ci ba, a lokacin sai kowa yaci ya koshi an jagwalgwala, sai a zuba mata shine mata, idan kuwa tayi laifi bata da abinci sai dai a dama mata tuwo da dandanon. Shine bakin rabonta. Gashi gidan akwai wasu masu sayar da rake, da dabino, suna daurawa a tire. Sunan fita dashi.

Idan dare yayi mazan gidan suka shige cikin iyalan su, toh Kananun yan matan gidan, soron gidan suke zuwa inda masu sayar da raken suke, suna lalata dasu, domin kuwa. Zasu zo matasan suna goga musu gaban su, har mazan suyi realizing. Gwanayen abun dama Sahiya da takiya, sai Zubaina, sauran yaran matan basu sani ba.
Kuma karku ce wani abu ake basu, bai wuce Naira dari biyu zuwa sama bane, sai ko take da dabinon da ake basu. Sidrah tasha ganin su, amma ita ba irin mutanen nan ne, masu yawan magana ba, kuma tsoron su take.

....
Idanunta ne cike da kwalla, tana kallon damammen tuwon da aka bata, juya shi tayi tana kallon yadda kowa yake cikin sabon abinci, shinkafa da miya. Wacce yaji wadataccen kifi, kasancewar hadeja akwai babban dam, sunkuyar da kai tayi tana had'iye yawunta.

Kafon idanun mutane Saratu tayi, ta raba abincinta rabi, sannan ta zuba a cikin takardan kosai da suka ci na karyawa, duk da Sidrah ce ta sayo musu, amma haka suka hanata, sai da Saratu ta ɓincina mata, ta ajiye wurga mata. Tura mata takardan shinfaka tayi, da sauri Sidrah ta dauka ta fara ci, hannu baka hannu ƙwarya.

Suna gama ci, suka nufi bakin rijiya, diban ruwa. Takiyah tana zaune tare da Haule, sai Sahiyah. Tare da Zubaina. Suna diban ruwa, su kuma suna faman wasan banza, wannan na tab'a nonon wannan, sunan faɗin.
"La naki yafi girma!" Inji sahiya, takiyah tace.

"A'ah naki akwai guda a cikin shi, tab'a kiji."

Haka suke ta tab'a kukan su, tare da maganar, banza irin na batsa. Zuwan Sidrah yasa suka zuba mata ido, kafin Zubaina tace musu.
"Laa kuzo mu duba na Sidrah ba ita ba ce amaryan da za ayi aurenta ba."

Daure fuska tayi, cikin tsoron karsu mata. Tsiya, tana jan ruwa ta zuba zata kuma ja,.suka fincikota tare da yaga mata gaban rigarta, aikuwa ta fasa ihu tana fad̃in.
"Wayyo Allah na, ni bana so, Inna Lantana Kinga su ko!"
Buge mata baki Sahiyah tayi tare da barin gurin duk suka watse, ta koma bakin rijiya tana jan ruwa, tare da share kwalla da ya cika mata idanu.

.. tana gama jan ruwan ta nufi hanyar gida, Allah ya taimaka bata shiga ko ina ba, Cigaba tayi da aikinta Saratu na ta mata surutu, Lantana tana kwance a dakin sai da Inna Larai ta shigo.

Tana shigowa ta kifawa Sidrah mari, cikin fada tace mata.
"Dan Ubanki bani Naira hamsin dina da kika dauka!"

"Wallahi ban dauki kome ba! Na rantse da Allah, ban dauki kome ba, ki duba ni." Haushi ya kuma cika zuciyar Larai, ai kuwa ta rufe ta da duka, tare da cewa.
"Bani kudina ko naci iyayen ki da suka karkashin kasa"
Cikin kuka tace.
"Billahil azim, ban dauka ba, idan na dauka Allah ya tsine min!" Ta kuma buge mata baki.
"Kai Larai! Bana son cin fuska. Duk gidan nan kin tab'a jin nace wata Sidrah, ta tab'a daukar min kudi?
Ko kawai cin zali ta motsa haushin kaza ta sauke kan dami, maza ki nemo wanda ya saukar miki kud̃in ki."
"Innarmu wallahi ita ta dauka, a duba kayanta mana," inji Sahiyah, ta nufi hanyar dakin aikuwa Saratu ta bita, tana saka kudin A kwalin Sidrah, Saratu tace.
"Alqur'ani Allah Sahiyah ce barauniyar wallahi, naganki kece kika saka, kudin a cikin kwalinta. Dan tunda ta dibo ruwa bata shigo daki ba, wallahi kece. Kika d̃auka."

"Kai bani son fitina, Sahiyah dama kece kika dauka?" Lantana ta daka mata tsawa.

Fashewa da kuka, Sahiya tayi tana kallon Saratu, tare da yanko karya ta makawa Sidrah. Huci kawai Lantana take, fitowa tayi ta mikawa Larai kudinta, sannan ta nufi hanyar kitchen, ta dauko itaccenta, ta d'aga tare da makawa Sidrah, tsautsayi yasa Sidrah d'ago hannunta zata kare, aikuwa sai jin wani irin kara suka yi hannun Sidrah yayi.
"Kasss" yana lilo, wata razananniyar kara tayi tare da zuɓewa kasa sumamminya.

Bata san lokacin da tayi wurgi da itaccen ba.
"Innalillahi! Lantana da hankalinki ni da nace ta daukar min kudi bafa cewa nayi ki kashe marainiya ba, toh wallahi babu ruwa na, can ta matse miki. Ai gaskiyar Saratu ce, domin Sidrah

ta rantse bata dauki kudin ba, amma dake munafukar da ta dauka Yarki ce, kika fito zaki kashe marainiya.

Toh ba dani ba, domin wallahi bazan yi shaida ba, kuma kina jin rantsuwar da suka yi akan Sidrah zasu iya sake mace, shine kika mata irin wannan mugun dukar."

Sannan ta fito bakin kofar shashin tace.
"Gudummawa Jama'a, kuzo Lantana da Yarta Sahiyah sun kashe Sidrah, wallahi kuzo kuzo. Kasheta suka yi, akan Sahiyah ta dauki Kudina, daga magana tace min wai ai taga lokacin da Sidrah ta dauka, shine na biyo amsar kudina, kawai Sahiyah ta shige dakin da gudu wai zata dauko kayan Sidrah. Daga nan kawai Lantana tana fitowa bamu yi aune ba, sai kawai ta saukewa Yarinyar da ko bakin mahaifi bata bari ba.

Wannan rashin Imanin har ina, zasu kashe musu Y'a."

"Ahha lallai. Lantana kin tabo mai tsada, wallahi zaki gaya musu badai kashe ta kika yi ba? Toh jama'a nayi nan" inji Iyar gida.
"Don Allah ku taimake ni, wallahi ban da wata manufa, kawai tsautsayin ƙaddara ce ta faɗa min, na rantse da Allah ban tab'a.."

"Wa zai taimake ki? Mu din? Wallahi bamu isa ba, tab dijam. Tunda kika kasheta sai kisan yadda zaki yi ita, wallahi babu wanda ya isa ya shiga wannan lamari tab kice zawarci ya kama ki."

Kafin kace me tuni sun watse, sun barta da Sidrah a kwance. Hannu ta daura akai tare da cewa.
"Wayyo Allah na, na shiga uku na lalace. Saratu bani ruwa."

Duk sun rud'e, ba tare da sanin su ba, sai ga Malam Haliru. Ya iso, an sami munafukin da ya kira shi a waya, ba shi ba hatta sauran yan uwan shi sun tawo tare. Gabaki daya Lantana ta rud'e cikin fitar hayaci tace.
"Wallahi kaga itaccen can, shine na buga mata, ban san zata suma ba, Allah shine shaidana, ban yi da niyyar cutar da ita ba.

Kawai ƙaddara ce ta faɗa min, wallahi babu wata manufa a raina, don Allah karka."

"Lantana ki fita ki bar min gida! Idan muka dawo na same ki a gidan nan wallahi zan sake ki! Kuma ba zan dawo dake ba."
Ya fada mata yana fidda wani irin huci. Ran shi yana kara b'aci sosai. Dan ji yaƙe kamar ya rufeta da duka, sai dai ya san cewa. A madadin ya samawa Sidrah yancin sabon k'iyayyar tace zata kuma samun matsuguni a zukatar mutanen gidan. Shi yasa yake ganin gwara ya kora Lantana gidan

Itama Larai Mamman yana zuwa yace ta fita ta bar Mishi gidan shi, domin itace silar abinda ya faru. Wannan abin ya gigita yaran uwaye biyun nan.

Sabon k'iyayyar Sidrah ya kuma samun mafakar siyasa a zuciyar yaran su. Gani suke sabida Sidrah aka kori iyayen su mata, dan haka Lawali yaci alwashin sai ya gigita rayuwar Sidrah yadda aka kori Mahaifiyar shi Larai.

Sahiya itace yake kullace da Sidrah dan sauran yaran sunce babu wani abin da zasu yi dan abin da Innarsu tayi babu wanda zai iya dauka, suna bayan Baban su. Duk hukuncin da ya yanke duk daya ne, dake maza ne kuma suna da hankali, ba kamar Sahiyah da Altine ba, wacce take ta ihu innarta ta dawo.

Sauran matan gidan kuwa tsoro ya hana su, shiga cikin lamarin dan suma gani suke za a iya korasu gidajen su. Tunda ka iya koran Larai da Lantana.

Tunda suka dauke ta, aka wuce da ita Asibiti, sun samu an karb'e su dakyar, sunyi jum. Kafin likitan ya fito, yana kallon su yace.
"Zaku iya ganinta, amma ba yanzun ba, don Allah ku kula damuwa tayi mata yawa, sannan kuma akwai karaya kashin hannunta, zaku iya mata daurin gida, dan yafi kyau. Sannan ku kula da lafiyar ta, zuwa dare zaku iya tafiya gida."

Ajiyar zuciya suka a tare, sannan suka leka dakin ta window, tana barcin wahala. Duk ta lalace, "Anya Bara mu maida ta gurin dangin Mahaifiyarta ba? Wallahi ina matuƙar tsoron karsu kashe masu yar mutane, mu shiga uku. Ga Ma'aruf da muka yi maganar auren shima bai kuma."

"Ma'aruf yana fama da kanshi dan ko kwanaki naje na samu yana fama da hawan jini. Kaga kenan babu batun aure dole mu tsaya a gidajen mu, don wallahi babu macen da zata juya mu don ranta, dole mu kula da al'amarin...
Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu..
Kuyi hakuri! Weekend ne, kuma Uzuri yayi yawa....
[11/13, 8:05 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/UenPpAMydbb

**RUWA BIYU**

**<*Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta*>**

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Hali zanen dutse
11

Sosai jikin Lantana yayi sanyi, dan idan zata nutsu nasiha ce Sabuwa take mata, a fakaice har sabuwa ta gama zata bar gidan Sidrah da take makale a bango tana shashekar kuka, bata fasa ba. Riko hannunta Sabuwa tayi sannan tace mata.

"Kiyi hakuri! Zaki ga amfanin haka domin shi Mahakurci mawadaci. Ance karyanka ta kare amma gaskiyar ka da hakurinka ba sa karewa, sai da akasin haka. Kowa yace zai iya sai kabarshi da iyawar shi. Insha Allah zaki kasance wacce zata ribanci hakuri a duk inda ta taso miki. Lantana na barki lafiya."

..... Kamar ance Sidrah ta kalli, Lantana ta zuba mata jajjayen Idanun, tana na nazarin yadda zata ci uban Sidrah a nutse, yadda babu wanda zai fahimci abinda take aikatawa sai ta gama, dan haka ta yayi gyalenta sai gidan kawarta Aminiyarta, kuma kawar cin mushenta, tun daga soron gidan take kwad'a sallama.

"Lale maraba, Lantana shigo mana. Ai gidan ne nan. Karki ji kome" dake a fusace take tana shiga ta nemi guri ta zauna tana huci. Ruwa ta kawo mata daga randan sanyi, sannan ta kurb'a.

"Mai dan wake! Kinji yadda nake jin bakin ciki kamar zai karni lahira! Kinji yadda kirjina take wata irin bugawa!

Wai Nice za acima mutunci a cikin gidana"

"Kamar ya? Meke faruwa, ince kome ya wuce akan wancan yar rikon ku?" Mai dan wake ta tambayeta,
Cikin tsannanin b'acin rai tace mata.
"Hmm! Akanta ne, kuma wallahi sai na dauki mataki akanta." Lantana ta faɗa tana hura hanci,

"Dadi na  dake baki da hakuri, me ya faru kin barin a duhu?"

Nan ta gyara zamanta ta shiga mata bayani, wani dogon tsaki taja sannan tace mata.
"Amma wallahi babu sakarya lamba daya. Akan yar da kika haifa zaki zauna kika ihu. Toh bari ki ji, toh bari na gaya miki, babu duka babu zagi, wai ma Lantana duka duka nawa Sidira take da ake baki tsoro akanta?

Yarinyar da ke kanki kin san ba kome bace a gurin ki da gurin sauran mutane, dan banten Ubanta daura mata talla, idan bata sayar ba, a bakin abincin ta, dole ta fara karuwanci naga yadda za a dauke ta abawa Bature ita bayan ta zama karamar karuwa."

Zaro idanu Lantana tayi tare da cewa..
"Ke ruwa min asiri wasitira wa alaika z rabani da abinda ya turewa buzu nadi, ke kina tsammani zasu bar ni je dangin Ubanta, bayan basu daurawa yaran su talla, ai zasu cinye ni d'anye. Ke

dai Zan iya zabtar da ita sai ta rasa inda yake mata dad'i."

...."ji sakarci! Haka shine mafita" inji mai danwake,
"Bafa zai yiwu bane! Domin na tab'a kuskuren hakan malam ya kusan sake ni, da girmana gotai gotai, ban zauna a d'akina ba. Nace sani zawarci gida ai babu tsari, kawai zan a zabtar da ita dai amma talla kan akan aurena ne dan duk yaran gidan basa talla."

Shiru suka yi suna niman idea, kansu ya kwance,
"Toh kawai ki cigaba da a zabtar da ita domin na lura mutane basu san cewa kina kokari ba, ki a zabtar da ita a boye a gaban mutane ki sota yadda babu wanda zai fahimci ainihin abinda kike mata!"

Shiru suka yi kafin suka kuma fashewa da dariya, ana kuma cigaba da hada rigima sosai.

***
Jigawa dutse.

Aiki suke na karyawa masu wanke wanke suna aikin shi. Latifah ta kalli. Hajiya Uwani tace mata.
"Ummin mu! Ko zamu saka curry a wancan kwai din, sabida yana karni kuma kin san bawai kan agric bane na kazar gida ce!"
"Saka mana In-law, gran Son baya son karni ko? Jiya ma miyar kukar dare an saka curry sabida karni, girkin rana ma, curry. Za a haifa min yellow miji ko yellow kishiya"

Shiru tayi cike da kunya, tana aikinta, dan Latifah ta ki yarda da gulmar gidan duk abinda ake bata shiga, wani lokaci ma zaka same ta tana kallon tashar girke girke. Idan kuma Hajiya Uwani tana gida zasu fito kitchen suna girka abinda zasu ajiyewa bakin su. Dan Latifah bata rabuwa da baki. Suna cikin haka. Hajiya Uwani ta shige d'akin sabida wayar da ake kiran ta gashi yaran suna islamiyya, kamar wacce aka kora Latifah, bayan wani lokaci suka dawo a tare abun mamaki. Sun samu an kwashe fiye da rabin cincin da suke soyawa, kuma ga mutane a tsakar gidan,. Fitowa Hajiya Uwani tayi tare da tsayawa tace.

"Yau anyi Kuskuren tab'a, wallahi duk ranar da na kuma saka abu ina girki na tashi wata karamar mara kunya ta shiga ta diba min zan bata mamaki domin sai ta tozarta a cikin gidan nan. Na gaya muku wannan shine farkon kuma karshen na kuma."

"Latifah! Ina kike tawo kika bar daki a bude an shiga tare da kwashe min kudin ajiyar mutane da aka bani, wannan wani irin sakarci ne?" Wani irin shiru ne ya gifta a tsakanin su, ran kowa ya b'aci, dan haka ta nufi cikin gidan su. Ta kalli kofar ta tabbas yanzun aka debi kudin ta shigo tayi uzurinta tare da manta key a jikin kofar, tana shiga dakin taga har buhun shinkafa, aka bude sabo dal, aka diba. Abun ya bata haushi dan haka ta zauna tare da fashewa da kuka. Ta rasa waye yake musu wannan renin hankali.

Shigar ta uwar dakin ta, ta samu har wardrob ɗinta da kuma karamin akwatin kayanta, a tsora ce ta fara sauke kayan ta, tana duba gold ɗinta, ajiyar zuciya ta sauke tare da kara boye shi, dan tasan Allah yana sonta ne ya bar mata shi a boye. Tun da ta samu ta boye cikin gidan da bata koma ba kenan, karshe Ummi ce ta karasa aikin aka kawo mata nata, amma sauran yasha ruwa..

Wannan abun dake faruwa, ya sanya kowa ya fara kaf kaf da kan shi, cikin gidan ma basu yarda da kowa ba, musamman Ya Hindatu, dan anfi zargin ta.

"Wallahi Hajiya ban tab'a daukar abun wani ba, kawai ranar ma tsautsayi ne, matar Ghali naga ta fita da abu a hannunta, kuma nafi zargin itace take musu." Inji Ya Hindatu,

"Ke nima na jima ina zargin Ummita, domin idanu ta,baya zama guri guda, shi kan shi Ghali jiya ina jin yana Jajjen ana kwashe mishi kudi ko wani abu, jiya suke hira da dan uwan shi na fito ban dakin."

"Amma babu wanda zai yarda ai! Sabida bata yi kama da Barauniya ba!"

"Aikuwa mama wallahi zaki ja mana koran kare! Ki rufa mana asiri, tunda bamu da gidan da zamu zauna baban mu ya gudu abin shi." Shiru Hasnah tayi tana kallon uwarta dan iya gaskiyar kenan. Gyada kai tayi.

Aminah matar Bala ta shigo, suka kafa gulma. Suna haka Raliyah itama ta shigo, dan su nan dakin su. Hafsah matar Muhmood, ta shige dakin Amarya, suka fito tare, zuwa dakin Hajiya, wato idan kaga irin gurmin da ake bugawa.

Sai dai muce idan ta fito ta tsaya iyakan su.
***US.
Mika mishi takalmin shi da agogon shi aka yi, yana me b'ata rai kamar an zage shi.
"Yallabai kayi hakuri! Amma an tabbatar kai ne ka duke su, kuma badan Lauy yazo da wuri ba, tabbas babu abinda ba zai faru ba, dan zasu iya mika ka ga kotun Unguwa. Kai da mahaifiyarka take kokarin ganin ka samu damar shiga Whiter house, kaga dole a kiyayye abinda zai b'ata maka suna. Dan ma Mahaifiyarka bata ƙasar."

... A sanyayye yake tafiya yana gyara zaman agogon shi,kawai sai jin kara akayi, tare da nufo kan shi, dole Maza body guard din shi suka shiga musayar wuta, tsakanin su, tunda aka saka shi a motar suka bar gurin, domin motar irin wacce bullet baya fasata ce.

Da gudu suka bar gurin, ana cikin haka sai kamar wanda aka hankado shi, juyawan da maharan suka yi akan shi. Ai kuwa suka sake bude mishi wuta,

Cikin rashin sanin madafa, harbin ya same shi, a kafadar shi. Sai da motar ta nemi kwacewa a hannun shi me ya kawo shi nan din nan ya faɗa, cikin son tsira da ranshi yana kallon fuskar

mutane, tare da cewa. "Sai na kashe ku!" Yaja motar da gudu kamar wanda kamar a cikin shirin film fast and furious, take gudu da motar, yayinda Yan sanda suka rufa mishi baya, suna bin shi. Sai da suka bar cikin garin sannan yan sanda suka daina bin shi.

Domin ya yanki cikin daji, ne zubar jinin da ya dame shi ya sashi kashe motar, tare da hakki. Zaro wayar shi yayi tare da ya kira layin Max. Nan ya gaya mishi inda yake yazo ya dauke shi.

Bayan wasu mintuna, ya iso yana zuwa ya fitar da Aamil, sannan ya zubawa motar fetur ya kona ta.

"Me yasa?"

"A'a, akwai matsala domin zamu iya fukarta barazana ga yan sanda, dan haka muje kaga likita, domin akwai harsheshi a jikin ka, kuma idan ba a cire ba akwai matsala dole za a cire maka shi."

" Na ga fuskar shi, wanda ya harbe ni, dole na dauki fansa ta. Meye matsalata da su. Waye yake son ganin bayana,!" Yana magana cike da taurin kai, tare da jin wani irin azaba, amma taurin zuciya. Da mugun gudu suka bar dajin, kafin su isa yan team din su, sun kira likita. Ana zuwa suka shige dashi cikin gidan shi.

.... Tun da ya shiga ƙungiyar gyara motocin, ya zama mara mutuncin kamar me, kuma bai da hakuri na miskala zarratin, kungiyar su a bayyane ta gyaran mota ce amma a zahirance yan daba ne na bugawa a jarida. Basa kisa amma kuma suna illatar da mutum.

Tunda ya shiga cikin su ya zama masifaffen sama da baya, kangararre wanda babu wanda ya isa ya lankwasa shi. Kuma idan ya saka kanshi abu ko su basu dakatar dashi.

. Shi yasa yanzun duk wanda yayi Mishi babu yake cin uban shi, a yanzun yake bakin cikin me yasa tun farko bai ci uban yan gidan su ba, da suke rena mishi hankali, sai yanzun ga damar yayi abin da yake so babu su a tare dashi. Kallon shi Jerry yayi sannan yace.

"Zan gane shi." Dan haka yana rufe baki ana kiran wani mutum, tsoho, dan kasar China. Aamil ya shiga gaya mishi kamanin mutumin, ana cire mishi harsheshin cikin masifar zafi tare da mugun taurin kai yake juya kan shi , zufa na karyo mishi yana fadar kamanin mutumin,ana cire harsashin, yana sauke ajiyar zuciya bayan ta gama fadar yadda mutumin yake, sannan ya bingire ya fara barci sabida alluran barcin da aka mishi.

"Lallai Frank ya kwaso bala'in dole mu dauki fansar abokin mu, Duk tabargazar da muke bai tab'a shiga ba, amma mara mutunci ya harbe shi bari ya tashi.

----

Haka kawai yaji yana son komawa inda ake harbin, juyawar da zai yi ya kama zubda jini ta bakin shi, tare da rike kafad'arshi, yana cewa.

"Ku mai dani! Inda ake harbin ku mai dani."

Wani irin zafi yake ji a cikin ranshi da kafadar shi, ganin yadda yake rike gurin, yasa P.A ya shiga bude rigar, gurin ya tara jini kamar zai fashe, da bai fita ba shine shi kuma yake aman jinin, abin da ya kuma firta su kenan, domin a sanin P.A din Maman shi, a duk lokacin da wannan yanayin ya bayyana, toh akwai matsala a kwayoyin halittar jikinsa, yana aiki kenan bai

cika jin haka ba. Sai dai a cikin shekaru bai fi sau biyu ko uku ba, yake zama haka, amma ko lokacin da yake yaro sun sha wahala dashi sosai domin sai da suka kai shi India gurin masu maganin gargajiya....
Akafta 😏

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu..
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/sWKmMfn3gbb
**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

🤦🏼‍♀️ Har abada wutsiyar Raƙumi tai nesa da kasa🤩

#Manta baya
1️⃣4️⃣

Sake daya harbul yayi a kafa, daya kuma a hannu, dole suka yasar da bindigar, yana zuwa ya dauke daya da mari, dayan kuma ya dake shi da bakin bindigar din.

Ihu suka saka tare da komawa gefe, jikin su na makarkyata.

Takowa yayi kuma yi dai dai wayar dayan su na kara, yana dauka ya saka a kunne yace.

"Xsezza! Kun kashe shi?"  Aka yi tambayar a kagaucce.
"A'a sai dai ni na kashe su, Banza kawai!"
Kawai ya sake musu harbin cikin nutsuwa, dan abun ya bashi haushi. Wato ma so ake lallai a ga bayan shi, sannan yayi ta dukar su da kafa, kafin ya juya ya bar su a kwance cikin jini.

...... Dawowa yayi ya dauki wayar su ya dauki Numbern da aka kira , sannan ya juya tare da barin gurin. Yana jin a ranshi yayi ta cin Uban yan iska da suka so kashe shi zai tayi har sai yaga bayan banzaye.

Bayan tafiyar shi, sai ga Yan sanda. Suna zuwa suka kira motar asibiti, zuwa asibiti.

---

Babbar jirginta wanda ya kasance nata da d'anta ne ya dauke ta a filin tashi da saukar jiragen, na cikin ƙasar. Sannan suka taka zuwa gaba inda karamin privet jet ya kuma daukarta zuwa cikin gidan ta,  sabida gudun kar a kai mata, farmaki.

Tafiyar minti goma kacal ya isa dasu. Wani katafaren Mansion wanda yake da kusan girman gari guda, dan yakai girman wata kauyen, gidane a tsakanin wasu tsauni na ciki garin sannan gidan yana kudu da bakin teku.

Body guard dubu daya da dari biyar ne suke gadin bakin tekun, tare da manyan bindigogi, sai ta Yamma da tsaunin, (mount wato) shima akwai body guard dubu daya da dari tara, da musu duba sararin samaniya, sabida kota kwana. Sai ta arewancin gidan, akwai masu gadi suma sama da ɗari huɗu, sabida akwai karamar gurin shakatawa.

Sai bakin gate din shiga Mansion din, inda aka girke masu tsaro da ta kwana,  sannan duk bayan awa daya ana sauya masu tsaron, sabida kula da abubuwan gidan.

Ta cikin gidan kuwa, gidan sama ne mai dauke da dakuna bakwai, tare da manyan manyan falo uku, a sama. Sai a kasa dakuna biyar ne dauke da falo hudu. Falon farko mai dauke da wasu. Wasu kujerun alfarma na royal. Masu matukar kyau da daraja. Sannan wall din falon na katako ne.

.....falon babba ne na fitan hankalin wanda yake dauke da wasu manyan manyan, frame na hoton Mss William da Allison William. Gefe guda wani tsohon attajiri ne cikin shigar Alfarma. Gefen shi wata mace tare da matashiyar budurwa. Wacce ta kasance Mss William. Dan gaba kadan hotonta ne na aure Ita da wani mutum, suna sanye da Wedding dress. Murmushi suke baki dayan su.

Gefe da gefen falon cike yake da manyan wall labrary. Me dauke da Littafan.  Tare da wasu tarkacen da ake kawata falo yayi kyau.

Shigowa tayi zaratan maza masu kula da lafiyar ta, suna biye da ita, suka ja tunga daga bakin falon farko. Sabida idan ka nufi falo na biyu, akwai masu tsaron kofar.  Suna tana isa aka bude mata, sanye take da doguwar rigar, wuyarta sakale da karamin gyale, gashinta da ya kasance ja me dauke da ratsin fari, ya kuma fitar da fuskarta. Ba zaka tab'a yarda ba idan aka ce tabawa Hamsin da shida baya ba.

Sabida yadda take kula da jikinta, ya sanya tsofarta boya, sannan ko akan fuskarta yar karamar ce mara nuna girma, mace ce mai tsumammen fuska.

Domin kuwa, ba zaka tab'a ganin dariya akan fuskarta ba. Amma baka raba fuskar da murmushi ba, sabida yanayinta mace ce mai yawan Alkhairi.

Tana isa falon Allison yana mik'ewa, ta rike kunnen shi, suka nufi wani kofa, zata bude ya riko hannunta.

"Kiyi hakuri! Na fita, ba sai kin duba ba, kuma ba laifin su bane nawa ne! Mom yaushe zan daina b'oya? Yaushe zan zama me tsayawa da kafarshi?

Mom sabida Rio Lucifa kike boye ni? Sabida shi kika hanani sukuni? Toh ni Mom ba zan iya wannan rayuwar ba? Sabida bata dace dani ba.

Mom ina son nayi rayuwa kamar sakakkun tsuntsaye masu yanci, Mom duniya da girma take me zai sanya ki takura ni ki turani wani gurin nayi rawa wannan duniyar da kika tara, basa gaba na."

Daga hannu tayi zata mare shi,
"Madam!"
"Mark! Na manta baya, me yasa Allison yake kokarin dawo min da kome?"

"Mom ni bana son wannan dukiyar ki bar ni na zab'i rayuwar da ta dace dani. Mom ko Emily, zan amsheta ne saboda bani da zab'in kome a rayuwata,

Mom ni zan amshi Emily amma ki bar ni nayi rayuwa da duniyar da nake so! Kudi motoci, Industries, companies, Mom ni basu ne nake bukata ba, ga guard sama da dubu biyar a gidan nan, kai ne ban isa nayi rayuwar yancin ba. Gaskiya gwara na fita Su rio su kamani ke ma..."

"Allison!!!" Ta daka mishi tsawa, juyawa yayi da sauri ya haura sama, cikin jin haushi.
"Barka dai Mom! Ko zan iya zuwa gare shi."

Nuna mata saman tayi, tabi bayan shi, zama Tayi idanunta nakan zoben aurenta, hawaye na zuba daga idanun ta. Kukan da take rike wane na tsawon shekaru yau take yin shi, kuka me mugun cin rai, bude jakarta tayi tare da zaro inhelarta, ta shaka. Tare da zubawa hoton mahaifinta idanu.

Mss William mace ce, da take da sa'a a Rayuwarta, mace ce da ake kiran ta, Alkhairi a cikin biliyoyin mata, ita kadanta alumma ce, balle kuma an hada da halayyarta duk da kasancewar ta, Christianity amma kuma tana da zuciya mai kyau da taushi.

Tana cikin mutanen da Allah ya basu kwarjinin sosai, domin tana da irin Immunity bata cika shiga hatsari ba, sai ta bar guri sharri yake wanzuwa. Kowani dan Adam tara ne haka itama tana cikin tara.

Idan za a kira ta mace mai Alkhairi da Alfarma toh Mss William ta kai haka, shi yasa ake mata sha'awar shiga siyasar U.S,

Amma saboda Allison ta hakura da wannan matsayin ta gwammace shi ya tsaya, amma yaki sabida kasancewar shi mutum mai raunin zuciya, yana da hali irin nata, amma bai da karfin zuciya da rashin tsoro.

Abokan gabar Mss William, har yau basu tab'a nasarar , cutar da ita ba koda kuwa kwarzane ce.
Har yau suna ka na bakin cikin rashin cutar da ita, ansha kawo mata Mutanen da suke harinta, tace a sake su, su tafi sabida suna da tasu rayuwar da zuri'ar su.

Har yau babu wanda zai ce ya ganta cikin damuwa ko bakin cikin, sai dai zaka ga fuskarta aways keeping smile, sabida ta yarda da cewa. Murmushin kan fuskarta yana kunshe da abubuwa kamar huɗu. Na Farko shudaddiyar duniyar da aka binne shi a cikin kasar zuciya. Na biyu fuskarta sabuwar duniyar da kake rayuwa cikinta. Na uku, rike sirrin boye da take bayyane a kan zuciya.

Na huɗu, gigita abokin gaba yayinda yake ganinka ya firgita, saboda kwarjininka. Yana ji yana gani zai ta tsammanin kana shirya mishi wutar kashe kan shi ne, alhalin kai taka manufar da ban. Ba tashi kake ba. Ta kanka kake. Shi yasa haka ya zame mata kwarin gwiwar ta. Dan da shi take yakar abokan gabarta.

Wannan dalilin yasata rike sirrin murmushin ta, a duniya babu wanda bai san cewa Allison shine weakpoint ɗinta ba,. Duk abinda take aka ce mata, gashi an kai mishi hari zata bari. Sau dayawa ta sha saka hannunta akan wasu cantract sabida Allison. A kullum burinta Allah ya kawo mata ranar da Allison zai zama mutum yadda zai kare dukiyar su. Allison yana da degree a kasuwanci, yadda yake iya sarrafa dukiya abun burgewa ce. Amma zuciyar shi bata da karfi ko daya. Zuciyar shi bata iya jure damuwa, shi yasa kullum zaka same shi a study room, yana nazarin kasuwanci.

A yanzun haka baya fita ko ina, amma duk wani aikin cigaba yana yi a cikin gidan su. Mutum ne da yake da hakuri da son zaman lafiya, amma a duk lokacin da ran shi zai b'aci kowa sai ya razana, Mutum ne da zai iya zama na tsawon watanni bai cewa kowa cikanka ba, sabida Izzar kudin da yake bin jikin shi.

Sam haka baya burgeta, burinta ya zama mutum mai fada aji, amma sam ba haka ba, lusarancin shi yasa ta hana kowa kusantar inda yake sai Emily, itama sabida Mahaifin yarinyar shine na kusa da ita, kuma d'an uwan ta na gurin Mahaifiyar ta, idan akwai abinda Mss William take so, Auren Allison da Emily. Amma Allison yace baya son aure yanzun asalima shi bai gamsu da soyayyar da take mishi ba. Amma kuma bai hana yarinyar takura mishi da soyayyar zamani ba, tana fara tab'a shi yake kaucewa. Dan ce mata yake shi mata maza ne (🤣😂🙆🏾‍♂️) dan karta sanya shi aikata mugun abu. Akwai wani lokaci da ta shirya mishi Birthday party, ta wurga mishi kwaya, a cikin abin shan shi.

Koda abin yabi jikin shi kallonta yake, tare da riko hannun ta. Yana kallon ta, murmushi yayi sannan yace mata.
"Bana jin kome akan ki! Ba zaki ji zafi ba idan muka kasance tare? Ni mutum ne da bana son abiya bashin da naci, dan haka kiyi hakuri soyayyata idan zata nutsu sake zaki fi kowacce mace

Sa'a, idan kuma ba zata nutsu sake ba, zaki fi kowacce mace jin zafin abinda na miki.

Ban damuwa da mace mai kyau ki kyalkyale ba, Ni duniyata bana son ta zama me cike da Ƙawa, kawai SOYAYYA nake bukata a gurin macen da nake bukata, ta zama ni zan daurata a cikin tsarina da ra'ayina. Ina da buri! Ina da yakinin zan yi farin ciki amma ba ta wannan hanyar ba, wannan yanayin naki ne, baki san zan cutu ba?

Idan na fara darajar ki, toh ba zan iya tsayawa akanki ba, zan iya samun wata ma na fara da dajarar ta, don Allah mu mabiya ne masu kamun kai, don Allah karki kuma shayar da ni abinda zai dame mu, kira min Dr Patrick"

Tun daga ranar bata kuma kuskuren bashi wani ba, sai dai inda taga yana fushi tana ƙoƙarin kwantar mishi da hankali. Yanzun ma sa ta haura falon shi yana tsaye a jikin window yana kallon yadda tsuntsaye suke rayuwar su cikin yancin da samun kulawa daga jinsin su.

"Allison!" Ta kira sunan shi a sanyayye, banza yayi da ita, kafin tace mishi.
"Wancan ranar da naga ka tafi tsuhuwar unguwa tana gyaran mota, na zata dan cika farin cikin ka ne? Daga baya kuma kazo ka mare ni ranar Lahadi zan shiga Church, bai sani jin na rabu da kai ba.

... Allison rayuwarka Mom take karewa, domin dan itace zata iya tafiya wani gurin tayi rayuwa, amma sabida kai take zaune anan, kasan iya adadin dukiyar da take kashewa dan baka kariya?"

"Emily! Bana son dukiyar? Bana son kome! Ta barni nayi rayuwa na fita daga cikin wannan duniyar da ta kirkiro min shi. Duk abinda yake faruwa itace silar shi. Ta bar haɗa kanta da kowa, tayi rayuwa irinta Yancin. Babu amfanin goggayya da mutanen da basu da kirki.

Ina son Mom ne dukiyar da muke dashi ta haɗa su mu koma wani gurin muyi rayuwar mu,sai Yaushe zan sami Freedom?

Idan zan fita men in Black suit, tare da manyan bindigogi, haba kiyi nazarin rayuwa mana, talaka yana barci cikin nutsuwa kai kuma dukiya ta hanaka barci cikin nutsuwa. Ko yaushe ka juya zaka sami mutane sama da goma suna lura da lafiyarka! Idan aka ji ka motsa za a buɗe kofar a ga lafiyarka! Meye akayi da duniyar da zubda jini ya zama kwalliya a cikin shi. Ni mutum ne mai san zaman lafiya, koda matsayin da take niman zai zama na tashin hankali ba zan amsa ba, ni kwanciyar hankali nake buta kin fahimce ni...

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/iAhygLXSfbb

**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Inuwa biyu
13
"Babu matar da zata juya mu, dole mu juyata gidan mu ne, ba gidan su ba."
Shiru suka yi, kafin Malam Haliru, ya ce musu zai tafi ya kira mai dauri, amincewa suka yi ya fita, tare da yin shiru. Kowa da abinda yake sakawa a ranshi.

Bayan mintuna arba'in suka shigo da wani, dattijo yana shigowa ya duba hannun, yace.
"Kashin gefen hannun ne ya karye, Insha Allah zai hade."

Dutse
Aikin abincin dare Hajiya Surayyah take, ita da Ummita wacce ta shigo taya ta, aikin hankalin su yayi nisa, sosai nan aka Raliyah ta shigo. Tana kallonta. Tare da kura mata ido, dake idan suka yi abincin rana, zuwa yamma sai su shigo cikin gidan hirar maraici.

"Ummita ya nake jin kamshin turare na a jikinki, kuma yau sati biyu kenan da aka sace?" Inji Raliyah.

Cikin wani irin tsoro ta kalli Raliyah, sannan tace.
"Wani irin magana ce wannan? Fisabillahi ana zaman lafiya zaki kawo wani irin."

"Kinga dakata! Karki mai dani sakarya, ina kallon ki ne kawai, domin haka kika saka muka tsangwami matar Isah nan kuwa munafuka kece barauniyar, kina shiga dakin mutane ko, toh wallahi baki isa.

Domin haka kike kwashe kayan mutane ana miki Hakuri Wallahi bazan yi hakuri ba, kiji Dakyau, maza tashi ko na kunyata ki."

"Ke bana ciki da rashin kunya, gidanku ba a koya miki girmama manya bane, da kike wannan rashin kunyar wuce ki bani guri."

Cikin rashin mutunci, tace mata.
"Hajiya babu inda zani, haka kawai yarinya tana mana sata ace na wuce wallahi sai ta bani turare na ko kuma nayi rashin mutunci a gidan nan"

"Yanzun don Allah ba zaki tashi a kaina ba, yau naga rashin hankali, ke Ummita kin daukar mata turaren ta ne?" Cikin tsannanin tsoro tace.

"Me zan mata tunda part din mu ba d'aya ba, sannan ga masu ɗaukar abu bata bincike su ba sai ni, dan turaren yayi kamshin turaren ta, sai tace nata ne.  Wallahi ba nata bane!" Ummi ta faɗa tana kuka, kafin kace me gidan ya cika sabida yadda Raliyah take ihu shi ya janyo hankulan mutanen gidan.

Ga kuma Kukan da Ummita take wanda ya sanya da yawa ganin kamar sharri tayi mata, musamman da uwar mijin Ummita ta amshi rigimar ya zama nata, wannan al'amarin ya masifar b'atawa Raliyah rai.

Dole Hajiya Uwani ta fito ta kashe rigimar Raliyah tace.
"Wallahi na kyale ki ne..sabida Maman su Abdus Samad, amma na rantse da Allah, sai na baki mamaki. Mara kunya kuma zaki kuma ai ba yau kika fara ba."

Tayi ficewarta, ta bar Ummita tana kuka sosai,sabida tana kiran abinda Raliyah tayi mata da cin fuska..

---

"Hmm!" Inji Ya Hindatu, tsabar gulma na cinta, ta kalli waje, a ranta tana jin ciwon sharrin da Aka mata, tab'e baki tayi sanan tace.
"Insha Allah, sai na rama nima, baki yi kuka ba, yar banza muguwa karfi da yaji, kin sani na koma mujiya a cikin gida. Ni dake ne sai na rama."

Wannan shine abinda take fada tana kuma shan rantsuwa..

**US

"Rio Lucifa, shine mutum na gaba da ake tsamanin zai zama sakataren na musamman a fadar Whiter house, toh amma matsalar da aka samu. Manyan mutane da yawa suna niman wannan mukamin, a cikin su kuwa akwai shahararriyar attajiran nan Mss William! Dattijuwar kirki mace mai mutunci da kima."

Kallon Jerry Aamil yayi sosai, kafin yayi shiru idanun shi yana rawa, kafin ya mai da gefen shi yana cewa.
"Ina jinka."
"Kasancewar Mss William, matar sau uku tana fitowa takarar shugaban kasa, kasar nan amma bata samu ba. Duk da mahaifinta mutum ne da kasar nan babu wanda bai  san shi ba,

Haka yaja mata farin jini, sosai kuma mace ce da take ƙyamar auren jinsi, haka ya saka kowa yaji a ran shi ya zab'e ta, sai dai wani abun da na kasa fahimta. Shine a lokacin da ta fito takarar sai Mr Rio ya dawo da ita kasa koda kuwa tana dab da cin nasara ne, haka yasa ta hakura, shima kuma bai yi nasara a nashi hankoron ba.

Sai ya kullace ta, har yana iya kai mata hari a ko ina, Mss William tana da Yaro daya tal, kuma bata kaunar ya fita koda kofar gida ne, sai ya zama dole.

Ya hada degree din shi na farko a fannin binciken kimiyya, daga baya tasa shi ya koma kasuwanci, inda ya koma jami'ar havart, inda ya karanci kasuwanci a degree na biyu, yana gamawa ne, ya fara harkokin kasuwancin shi da nata, dan tace tana son ya gaji iyayenta ne musamman mahaifin ta.

Gabar da ta kullu a tsakanin mutane biyu, sabida muradun siyasa da cigaban ƙasa. Ita Mss William tana kokarin kiyayye wasu abubuwan, domin dayawa kungiyoyin mafiya, sun nemi ta shiga cikin su. Tace musu dukiyarta tsarkake ne. Ita kuma tsarkakkiya ce, ba zata iya hada wannan kazamtar da dukiyarta da rayuwarta ba.

Koda suka nemi Rio ya amince domin abin da yake nima kenan kuma ya samu cikin kankanin lokaci, dan haka yana samun wannan babbar damar ya kuma dawowa da karfin shi niman shugaban kasa, haka yasa aka hana shi sai yake ganin kamar ai itace ta saka baki aka hana shi. Abun ya dame ta.

Ana cikin haka kawai aka tura mata da sakon za a naɗa D'anta Allison a matsayin babban sakataren harkokin ƙasar, dan haka hankalin rio ya tashi. Nan yayi ta shiga da fecce yayitawa Yaronta baraza, har ya ce baya son matsayin, uwar tayi baƙin cikin mara iyaka, duk da ban san shi ba, amma naji mutane suna cewa yana da sanyin hali, yana da matukar hakuri, amma kuma ance mahaukaci ne, domin wani lokaci yana iya juyewa kamar mara lafiya, yayi ta wasu abubuwan. Lokacin da suka harbeka sun je harbin motar shine. Sun san baya fada kuma bai da abokin fada shi yasa suke wannan abin, dan ko zasu kashe shi ba zai amsa musu ba.

Shi yasa kwanakin baya mahaifiyar shi ta hana shi kifuta ko ina idan ka ganta, toh mahaifiyar shi bata gari ne, idan kuma tana gari kuwa ko get na bai isa zuwa ba balle na karshe sabida yana zaune ne a guri guda, Amma idan aka kama Alexander shi zai yi bayanin inda Mr Rio yake."

"Toh ni meye nawa a rikincin su, da zasu harbe ni?" Ya tambaya yana huci tare da fisgar da iska.

....
Haka ya wuni yana nazarin abinda ya faru dan haka ya watsar da al'amarin tunda bai shafe shi ba, kawai abinda ya Sani. Idan aka kuma mishi gangancin haka toh zai cigaba da cin uban kowa.

*
Kwanar Lantana biyar a gida, taji kamar ba zata dawo ba, dan haka abin da ta fara shi, kwashe kayan Sidrah ta kai can dakin wani dakin ne inda kaji da agwagi suke kwana a cikin d'akin, da

babu kowa sai tarkace, , ga uban beraye, suna hanata barci da kusur kusur,..

Wannan abun da ke Lantana take, yayi masifar d'agawa kowa hankalin domin ba iya yarinyar ka dai takewa wannan mugun halin ba hatta matan gidan, gashi mazan gidan basu sani ba, kuma bawai tana da hakuri da zata iya daukar nauyin wasu abubuwan bane shi yasa ta kuma boye mugayen Halayyar ta, yadda babu wanda zai  iya dakatar da ita.

Uƙubar da yafi nada, shi take sha, duk yarinyar ta kuma karewa sai uwar hanci da ba idanu, sannan da tana zuwa gurin dangin Mahaifiyar ta, toh yanzun ta daina zuwa Konace an hanata, haka ya sa yarinyar ta koma kamar wata sauna, ita ba zuwa makarantar boko ba, ita ba islamiyya ha, ga tarin kazamta, da rashin kulawa.

Haka yasa Lantana ta rabata da yaranta, sabida  kuntatta rayuwar yarinyar, yadda ba zata mori kanta ba, kuma haka ce ya fara samun rayuwar Yarinyar, gashi karfi da yaji sun cusa mata tsoron mutanen, bata iya zama cikin su.

..... Zai yi w
uya ka fahimci halin da take ciki, sabida a yanzun ko aiyukan gida bata yi, kome Lantana da yaranta ne suke. Karka kayi tunanin ko asiri ne a'a kawai tsabar bala'in  masifa ce da Allah ya jarabcin Kanana dashi shi yasa take abubuwan irinta marasa hankalin.  Kuma tana rike da Sidrah a ranta, shi yasa take azabtar da ita fiye da kima. Kuma take jin ba zata yi nadamar abun da take aikatawa ba.

**

"Kina can duniya! Niman duniya toh ki kira ki ji shin d'anki yana raye ko ya mutu? Idan yana raye Alfarma nayi miki, idan kuma ya mutu toh har abada babu wani namijin da zai tab'a taimaka mishi ba tare da na kashe shi ba.

....kinyi nasarar sakani na rasa matsayina har sau uku, kema zan yi nasarar sakaki rasa tilon d'anki da kike ji dashi. Idan kuma kinyi kokarin sanar mishi da cewa shi din dan kwaroro ne babu uba sai kare"

Kashe kiran tayi tare da dafe goshinta, idanunta yana wani irin cika da kwalla, yaushe Allison zai iya karban kan shi a gaban jama'a? Yaushe zai zama namiji kamar sauran mazan,?

Bata rene shi da kome ba, sai soyayya da fansa. Tayi fatar ya zama me ra'ayin kan shi, amma ina kawai ya zame mata wani irin mutum me kama da hawainiya ne, duk yadda taso yayi gabar wani lokaci sai ta karkata yamma, idan tayi dashi arewa sai ya koma kudu. Wannan abun yana damunta.

Kiran gaggawa tayi. Cikin mintinan ƙalilan, ta kashe wayar, tare da dafe kanta, tabbas akwai matsala, tunda sunki daukar wayarta haka yana nufin zuwanta Canada bai amfane ta da kome ba, duk da zuwanta akan taron kasuwanci ne na nahiyar Turai, gashi bai amfane ta ba sai ma b'ata lokaci da tayi dan haka dole tabar kasan yadda zata isa U.S cikin gaggawa sabida taga

halin da tilon danta yake wanda take jin zata iya bada kome domin shi.

Zata iya sadaukar da Rayuwar ta, dan shi. Ina ba zata iya daukar kasadar zama a Canada. Ganin nisar komawar ta tayi, domin kuwa haka ya mugun d'aga mata hankali, har ta isa inda jirgin ta yake, kiran layin P.A take amma yaki d'agawa, haka ya kuma tunzura zuciyarta sosai dan gani take kamar an kashe mata Yaro ne.

.......
"Gareth kalli gayen wanda aka bamu hoton shi mu kashe shi." Inji wani baƙin fata.

Kallon hoton wayar shi suka yi, "tabbas shine. Mubi shi"
Suka fada tare da bin bayan Aamil.

Shafa bindigar mugun shi yayi, bai taɓa kisa ba, kuma baya fatan ya fara, amma dole ya gano waye yake son kashe shi, sunyi tafiya me dan nisa, suka nime shi suna rasa, juyawa suka yi zasu bar gurin kawai suka hango shi tsaye, yana saka salansar bindigar, tare da zuba musu ido. Kafin suja kunamar bin.....
Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/sWKmMfn3gbb
**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

🤦🏼‍♀️ Har abada wutsiyar Raƙumi tai nesa da kasa🤩

#Manta baya
1️⃣4️⃣

Sake daya harbul yayi a kafa, daya kuma a hannu, dole suka yasar da bindigar, yana zuwa ya dauke daya da mari, dayan kuma ya dake shi da bakin bindigar din.

Ihu suka saka tare da komawa gefe, jikin su na makarkyata.

Takowa yayi kuma yi dai dai wayar dayan su na kara, yana dauka ya saka a kunne yace.

"Xsezza! Kun kashe shi?"  Aka yi tambayar a kagaucce.

"A'a sai dai ni na kashe su, Banza kawai!"
Kawai ya sake musu harbin cikin nutsuwa, dan abun ya bashi haushi. Wato ma so ake lallai a ga bayan shi, sannan yayi ta dukar su da kafa, kafin ya juya ya bar su a kwance cikin jini.

...... Dawowa yayi ya dauki wayar su ya dauki Numbern da aka kira , sannan ya juya tare da barin gurin. Yana jin a ranshi yayi ta cin Uban yan iska da suka so kashe shi zai tayi har sai yaga bayan banzaye.

Bayan tafiyar shi, sai ga Yan sanda. Suna zuwa suka kira motar asibiti, zuwa asibiti.

---

Babbar jirginta wanda ya kasance nata da d'anta ne ya dauke ta a filin tashi da saukar jiragen, na cikin ƙasar. Sannan suka taka zuwa gaba inda karamin privet jet ya kuma daukarta zuwa cikin gidan ta, sabida gudun kar a kai mata, farmaki.

Tafiyar minti goma kacal ya isa dasu. Wani katafaren Mansion wanda yake da kusan girman gari guda, dan yakai girman wata kauyen, gidane a tsakanin wasu tsauni na ciki garin sannan gidan yana kudu da bakin teku.

Body guard dubu daya da dari biyar ne suke gadin bakin tekun, tare da manyan bindigogi, sai ta Yamma da tsaunin, (mount wato) shima akwai body guard dubu daya da dari tara, da musu duba sararin samaniya, sabida kota kwana. Sai ta arewancin gidan, akwai masu gadi suma sama da ɗari huɗu, sabida akwai karamar gurin shakatawa.

Sai bakin gate din shiga Mansion din, inda aka girke masu tsaro da ta kwana, sannan duk bayan awa daya ana sauya masu tsaron, sabida kula da abubuwan gidan.

Ta cikin gidan kuwa, gidan sama ne mai dauke da dakuna bakwai, tare da manyan manyan falo uku, a sama. Sai a kasa dakuna biyar ne dauke da falo hudu. Falon farko mai dauke da wasu. Wasu kujerun alfarma na royal. Masu matukar kyau da daraja. Sannan wall din falon na katako ne.

.....falon babba ne na fitan hankalin wanda yake dauke da wasu manyan manyan, frame na hoton Mss William da Allison William. Gefe guda wani tsohon attajiri ne cikin shigar Alfarma. Gefen shi wata mace tare da matashiyar budurwa. Wacce ta kasance Mss William. Dan gaba kadan hotonta ne na aure Ita da wani mutum, suna sanye da Wedding dress. Murmushi suke baki dayan su.

Gefe da gefen falon cike yake da manyan wall labrary. Me dauke da Littafan. Tare da wasu tarkacen da ake kawata falo yayi kyau.

Shigowa tayi zaratan maza masu kula da lafiyar ta, suna biye da ita, suka ja tunga daga bakin falon farko. Sabida idan ka nufi falo na biyu, akwai masu tsaron kofar. Suna tana isa aka bude mata, sanye take da doguwar rigar, wuyarta sakale da karamin gyale, gashinta da

ya kasance ja me dauke da ratsin fari, ya kuma fitar da fuskarta. Ba zaka tab'a yarda ba idan aka ce tabawa Hamsin da shida baya ba.

Sabida yadda take kula da jikinta, ya sanya tsofarta boya, sannan ko akan fuskarta yar karamar ce mara nuna girma, mace ce mai tsumammen fuska.

Domin kuwa, ba zaka tab'a ganin dariya akan fuskarta ba. Amma baka raba fuskar da murmushi ba, sabida yanayinta mace ce mai yawan Alkhairi.

Tana isa falon Allison yana mik'ewa, ta rike kunnen shi, suka nufi wani kofa, zata bude ya riko hannunta.
"Kiyi hakuri! Na fita, ba sai kin duba ba, kuma ba laifin su bane nawa ne! Mom yaushe zan daina b'oya? Yaushe zan zama me tsayawa da kafarshi?

Mom sabida Rio Lucifa kike boye ni? Sabida shi kika hanani sukuni? Toh ni Mom ba zan iya wannan rayuwar ba? Sabida bata dace dani ba.

Mom ina son nayi rayuwa kamar sakakkun tsuntsaye masu yanci, Mom duniya da girma take me zai sanya ki takura ni ki turani wani gurin nayi rawa wannan duniyar da kika tara, basa gaba na."

Daga hannu tayi zata mare shi,
"Madam!"
"Mark! Na manta baya, me yasa Allison yake kokarin dawo min da kome?"

"Mom ni bana son wannan dukiyar ki bar ni na zab'i rayuwar da ta dace dani. Mom ko  Emily, zan amsheta ne saboda bani da zab'in kome a rayuwata,

Mom ni zan amshi Emily amma ki bar ni nayi rayuwa da duniyar da nake so! Kudi motoci, Industries, companies, Mom ni basu ne nake bukata ba, ga guard sama da dubu biyar a gidan nan, kai ne ban isa nayi rayuwar yancin ba. Gaskiya gwara na fita Su rio su kamani ke ma..."

"Allison!!!" Ta daka mishi tsawa,  juyawa yayi da sauri ya haura sama, cikin jin haushi.
"Barka dai Mom! Ko zan iya zuwa gare shi."

Nuna mata saman tayi, tabi bayan shi, zama Tayi idanunta nakan zoben aurenta, hawaye na zuba daga idanun ta. Kukan da take rike wane na tsawon shekaru yau take yin shi, kuka me mugun cin rai, bude jakarta tayi tare da zaro inhelarta, ta shaka. Tare da zubawa hoton mahaifinta idanu.

Mss William mace ce, da take da sa'a a Rayuwarta, mace ce da ake kiran ta, Alkhairi a cikin biliyoyin mata, ita kadanta alumma ce, balle kuma an hada da halayyarta duk da kasancewar ta, Christianity amma kuma tana da zuciya mai kyau da taushi.

Tana cikin mutanen da Allah ya basu kwarjinin sosai, domin tana da irin Immunity bata cika shiga hatsari ba, sai ta bar guri sharri yake wanzuwa. Kowani dan Adam tara ne haka itama tana cikin tara.

Idan za a kira ta mace mai Alkhairi da Alfarma toh Mss William ta kai haka, shi yasa ake mata sha'awar shiga siyasar U.S,

Amma saboda Allison ta hakura da wannan matsayin ta gwammace shi ya tsaya, amma yaki sabida kasancewar shi mutum mai raunin zuciya, yana da hali irin nata, amma bai da karfin zuciya da rashin tsoro.

Abokan gabar Mss William, har yau basu tab'a nasarar , cutar da ita ba koda kuwa kwarzane ce.
Har yau suna ka na bakin cikin rashin cutar da ita, ansha kawo mata Mutanen da suke harinta, tace a sake su, su tafi sabida suna da tasu rayuwar da zuri'ar su.

Har yau babu wanda zai ce ya ganta cikin damuwa ko bakin cikin, sai dai zaka ga fuskarta aways keeping smile, sabida ta yarda da cewa. Murmushin kan fuskarta yana kunshe da abubuwa kamar huɗu. Na Farko shudaddiyar duniyar da aka binne shi a cikin kasar zuciya. Na biyu fuskarta sabuwar duniyar da kake rayuwa cikinta. Na uku, rike sirrin boye da take bayyane a kan zuciya.

Na huɗu, gigita abokin gaba yayinda yake ganinka ya firgita, saboda kwarjininka. Yana ji yana gani zai ta tsammanin kana shirya mishi wutar kashe kan shi ne, alhalin kai taka manufar da ban. Ba tashi kake ba. Ta kanka kake. Shi yasa haka ya zame mata kwarin gwiwar ta. Dan da shi take yakar abokan gabarta.

Wannan dalilin yasata rike sirrin murmushin ta, a duniya babu wanda bai san cewa Allison shine weakpoint ɗinta ba,. Duk abinda take aka ce mata, gashi an kai mishi hari zata bari. Sau dayawa ta sha saka hannunta akan wasu cantract sabida Allison. A kullum burinta Allah ya kawo mata ranar da Allison zai zama mutum yadda zai kare dukiyar su. Allison yana da degree a kasuwanci, yadda yake iya sarrafa dukiya abun burgewa ce. Amma zuciyar shi bata da karfi ko daya. Zuciyar shi bata iya jure damuwa, shi yasa kullum zaka same shi a study room, yana nazarin kasuwanci.

A yanzun haka baya fita ko ina, amma duk wani aikin cigaba yana yi a cikin gidan su. Mutum ne da yake da hakuri da son zaman lafiya, amma a duk lokacin da ran shi zai b'aci kowa sai ya razana, Mutum ne da zai iya zama na tsawon watanni bai cewa kowa cikanka ba, sabida Izzar kudin da yake bin jikin shi.

Sam haka baya burgeta, burinta ya zama mutum mai fada aji, amma sam ba haka ba, lusarancin shi yasa ta hana kowa kusantar inda yake sai Emily, itama sabida Mahaifin yarinyar

shine na kusa da ita, kuma d'an uwan ta na gurin Mahaifiyar ta, idan akwai abinda Mss William take so, Auren Allison da Emily. Amma Allison yace baya son aure yanzun asalima shi bai gamsu da soyayyar da take mishi ba. Amma kuma bai hana yarinyar takura mishi da soyayyar zamani ba, tana fara tab'a shi yake kaucewa. Dan ce mata yake shi mata maza ne (🤣😂🙆🏾‍♂️) dan karta sanya shi aikata mugun abu. Akwai wani lokaci da ta shirya mishi Birthday party, ta wurga mishi kwaya, a cikin abin shan shi.

Koda abin yabi jikin shi kallonta yake, tare da riko hannun ta. Yana kallon ta, murmushi yayi sannan yace mata.
"Bana jin kome akan ki! Ba zaki ji zafi ba idan muka kasance tare? Ni mutum ne da bana son abiya bashin da naci, dan haka kiyi hakuri soyayyata idan zata nutsu sake zaki fi kowacce mace Sa'a, idan kuma ba zata nutsu sake ba, zaki fi kowacce mace jin zafin abinda na miki.

Ban damuwa da mace mai kyau ki kyalkyale ba, Ni duniyata  bana son ta zama me cike da Ƙawa, kawai SOYAYYA nake bukata a gurin macen da nake bukata, ta zama ni zan daurata a cikin tsarina da ra'ayina. Ina da buri! Ina da yakinin zan yi farin ciki amma ba ta wannan hanyar ba, wannan yanayin naki ne, baki san zan cutu ba?

Idan na fara darajar ki, toh ba zan iya tsayawa akanki ba, zan iya samun wata ma na fara da dajarar ta, don Allah mu mabiya ne masu kamun kai, don Allah karki kuma shayar da ni abinda zai dame mu, kira min Dr Patrick"

Tun daga ranar bata kuma kuskuren bashi wani ba, sai dai inda taga yana fushi tana ƙoƙarin kwantar mishi da hankali. Yanzun ma sa ta haura falon shi yana tsaye a jikin window yana kallon yadda tsuntsaye suke rayuwar su cikin yancin da samun kulawa daga jinsin su.

"Allison!" Ta kira sunan shi a sanyayye, banza yayi da ita, kafin tace mishi.
"Wancan ranar da naga ka tafi tsuhuwar unguwa tana gyaran mota, na zata dan cika farin cikin ka ne? Daga baya kuma kazo ka mare ni ranar Lahadi zan shiga Church, bai sani jin na rabu da kai ba.

... Allison rayuwarka Mom take karewa, domin dan itace zata iya tafiya wani gurin tayi rayuwa, amma sabida kai take zaune anan, kasan iya adadin dukiyar da take kashewa dan baka kariya?"

"Emily! Bana son dukiyar? Bana son kome! Ta barni nayi rayuwa na fita daga cikin wannan duniyar da ta kirkiro min shi. Duk abinda yake faruwa itace silar shi. Ta bar haɗa kanta da kowa, tayi rayuwa irinta Yancin. Babu amfanin goggayya da mutanen da basu da kirki.

Ina son Mom ne dukiyar da muke dashi ta haɗa su mu koma wani gurin muyi rayuwar mu,sai Yaushe zan sami Freedom?

Idan zan fita men in Black suit, tare da manyan bindigogi, haba kiyi nazarin rayuwa mana,

talaka yana barci cikin nutsuwa kai kuma dukiya ta hanaka barci cikin nutsuwa. Ko yaushe ka juya zaka sami mutane sama da goma suna lura da lafiyarka! Idan aka ji  ka motsa za a buɗe kofar a ga lafiyarka! Meye akayi da duniyar da zubda jini ya zama kwalliya a cikin shi. Ni mutum ne mai san zaman lafiya, koda matsayin da take niman zai zama na tashin hankali ba zan amsa ba, ni kwanciyar hankali nake buta kin fahimce ni...

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/Yv5BKGNphbb

**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

*Wancan posting din da nayi bani bace Khadijah Candy ce aka ce wai ta rasu, ita ta manta bata saka sunan ta ba, Nima kuma ban yi azancin saka mata ba da fatan zaku fahimta🙏🏽*
#Kullaliya

1️⃣5️⃣

Shiru tayi tana kallon shi, cikin yanayin damuwa ta taka har gaban shi,ta rungume shi ta baya shi tare da kifa kanta a gadon bayan shi. Lumshe idanunshi yayi cikin nutsuwa, sannan ya janye ta daga jikin shi yana kallon yadda take jin ba dad'i sabida shi.

"Ba wai bana son faranta mata ba ne, kawai ta bani damar na fita na rayu kamar kowa, haka zai sanya ni jin nima ina da yanci amma a tarani a guri guda babu adalcin a cikin shi. Zata fahimci haka domin itama tana cikin kaɗaice."
Yana kai aya yabar mata falon.

.....
"Wannan wani irin abu ne? Kana nufin Allison shi ya aikata duk laifin da yake faruwa?  A'a akwai wani Inuwa a  bayan D'ana akwai wani wanda yake bibiyar shi.

Akwai wanda yake bin sawun shi, haka kawai Allison ba zai aikata abin.."

"Mss William! Ina son ku biyo ni asibitin dashi, domin akwai wasu da suka tabbatar da

cewa,Allison shine." Inji Anthony General na yan sandan.

Mik'ewa tayi zuwa sama inda yake ta sami Emily a zaune ta zuba tagumi tare da kurawa dakin da ya shiga idanu, cikin damuwa ta shiga ta sami yana zaune akan laptop yana zanen a ciki. Yana zane wata matashiya. Yadda yake amfanin da Black paint ya sata fahimtar baka ce. Daga kafadar shi, tare da kallon fuskar zanen.

"Wacece ita?" Murmushi yayi sannan yace mata.
"Kawai zuciyata ce ta sani zana ta! Ina ji a jikina kamar dama can akwai ta a duniyar, tayi min yanayin da na zanata tana kuka!"

Murmushi tayi sannan ta shafa kan shi, tare da sake wurga mishi tambaya.
"Jiya da dare ka fita ne? Ina kaje?"
"Ni kuma! Mom ai rabona da na fita yau kwana uku, ki duba dakin Tsaro mana." Ya fada mata haka kai tsaye.
"Toh taso muje! Akwai matsala domin Anthony General na yan sandan yazo tafiya da kai."
Kura mata ido yayi sannan ya rufe laptop din shi, ya biyo bayanta, suka sauka kasa kallon Lauyan su yayi, aka shiga tattaunawa kafin suka fita tare, Office din Yan sanda suka isa aka kai Allison har asibitin suka tabbatar shine. Bincike da yayi bincike aka Fahimci a daren bai fita ko ina ba, dan suna da cigaba .

Sosai, akwai camera a kowani ɓangare na unguwa da kuma titi, da wannan Allah ya kwace shi ya dawo gida,
Amma kuma tabbas Mahaifiyarshi ta hana shi fita ko ina. Gudun b'acin sunanta.

---
"Ka tabbatar Jerry! Allison yana tare da kai? Domin kuwa zan so na kashe shi da hannuna yadda mahaifiyar shi zata dawamma a cikin bakin ciki na har abada."

Gyara zama Jerry yayi sannan ya kalli Chris yace mishi..
"Ba zan maka aikin banza ba, amma tabbas yana tare damu, idan dare yayi baya zama a gidan da yake,komawa Mansion din su yake.

Sannan kuma asuba yana yi zai dawo, Breth da su Max sun dauka da gaske ba shi bane ni kuma nasan shine, dan baya cika barin fuskar shi a gani, idan kuma ya bari toh tabbas zai maka dukar da sai ka manta da i da kake. Ni dai idan zaka kashe shi karka sanya ni a cikin mutanen da zasu maka aiki dan ya yarda dani, sama da kowa."

Gyada mishi kai yayi sannan ya cilla mishi dollas, na sallamar shi. Haka Jerry ya bar gurin, Steven ya kalli Benni cikin damuwa yace mishi.
"Gani nake kamar kashe shi zai iya kawo matsala, kuma abinda na fahimta shi Jerry munafuki ne,ya kawo gulmar abokin shi da ya yarda dashi, kai kuma za kayi amfani da haka dan cikawa Rio Lucifa kudirin shi anya kuwa?"

Mik'ewa yayi cikin nutsuwa yana kallon kofar shigowa yace.
" A koda yaushe bana barin hujja. " Kawai ya harbi kofar, sai ga jini yana zuba ta kasar kofar.

Fita suka yi suka ga wani mutum ne, rike da kwalin pizza. Tsallake shi suka yi tare da barin, cikin gidan. Suka saka yaran su dauke gawar.

.... "Benni! Ka fahimci abinda na gaya maka, karka aikata abinda zai dame mu, domin wannan shine karo na uku da muke kaiwa. Mss William hari kuma tana tsallake rijiya da baya.

...kar muyi abinda zai dame mu, domin tana da karfin  tsaro da kulawar gwamnatin kasar nan, karka yi abinda zai faru ka ja mana tashin hankali."

Murmushi yayi sannan yace masa,
"Karka damu, ba zan yi abinda zai dame ka ba, amma na san zaka ji dadin abinda zan yi."

***

Dambe yake da abinda masu dambe suke kara koyar fada, ya hada zufa Sosai, kamar ba shi ba, burin shi da tunanin shi niman mutanen da suke niman bayan shi. Sosai yake zufa tare da niman mafita, amma kan shi ya kule wani shashi na zuciyar shi tana kuma tunatar dashi duniyar da yaƙe.

Zaburar dashi kuskuren da yake tafkawa ne yake, tabbas da yana da hali da ya kawo karshen Labarin yan iskan da suke kawo mishi hari, amma sai kuma ya zamana bai san su ba, asalima karatu ya kawo shi kasar ba rigima ba..

***

Bayan wata goma.

Hadeja.

Rayuwa babu abinda ta bari, na yau da kullum, haka zalika mutanen cikin ta babu abinda suka bari na zalinci da son kan su. a cikin watanni baya, idan ka ga yadda kowa yake nuna son kanshi sai abin ya baka mamaki. Uwa uba suyi ta kallon wasu abubuwan kamar basu suka kirkira ba.

....haka ya kasance a cikin gidan da ake rikon Sidrah, ta dan kara girmar wahala, tare da kazamtar da taci uban nada, makeron ta cinye rabin fuskarta da kashi talatin cikin dari na gashin kanta, azabar tayi sauki sabida shigar da su kara da Yan uwan Mahaifiyarta suka yi kuma sunki bada ita kamar Bala'i.

Yanzun haka saura wata biyu, ayi aurenta  da Aamil domin kuwa Malam Haliru yace ko ya dawo ko karya dawo aure babu fashi za a an daura in yaso suyi ta zama kar ya dawo.

Hira suke tare da shewa, tana can gefe tana lashe bakin ta, sabida dan abincin da aka gama jagwalgwalawa aka ba, tana jin hirar duk irinta manyan ce dake akwai wata Ladi mai kayan mata ta kawo musu kayan manta sai sake manyan magana suke, gashi yaran su, suna ganin yadda wasu hotunar yake da alauran maza da mata, suna shewa da bankad'e.

"Lantana ba naji ance nan da wata biyu zaku saka Diyar ku, a lalle ba ko karya ce irinta shaɗi fadi?" Inji Ladi,

Tab'e baki tayi sannan ta kalli Sidrah wacce take wanke hannunta, cikin ruwan wanke wanken. Ta kuma kauda kai tace mata.
"Eh ba za'ida bane? Wai wancar kaskantaciya...." Da gudu Sahiya ta fito tana sheka amai, cikin tsananin tsoro Lantana ta mike tare da bin bayan yar ta, tana ce mata.
"Wannan aman tun shekaranjiya, kike anya ba shawara bace ta kama ki ba?"

Sai da tayi aman ya ishe ta, sannan ta mike Saratu ta rike hannun ta zuwa dakin su, aka aika Saratu ya sayo mata maganin zazzaɓi, tana sha ta kwanta, Sidrah ta shiga dakin domin sallah, tagan Sahiyah tana kuka. Toh bata san me zata ce mata ba.

Asalima tsoron Sahiya take, dan haka ta koma gefe tana sallah, cikin nutsuwa. Kamar daga sama taji Sahiya ta naushe ta, tare da ce mata.
"Munafuka kin zo kallon ko me nake yi ko?"
Bata kulata ba, ta cigaba da sallar ta, tana idarwa ta mike zata bar d'akin. Janyo ta tayi da karfin isa tace mata.
"Kije shagon waje, kicewa Lawali, ya baki maganin idan kika sake wani yaji na aike ki wajen shi sai na karya ki munafukai."

Da sauri ta bar d'akin. Murmushi tayi, ko babu kome ba ita kadai zata lalace ba, dole ta samu abokin cinikinta ta tsani Sidrah fiye da kome na duniya.

---
Ita kuwa zuciyarta daya ta shiga cikin dakin shagon, ta same shi da Takiya, tana zaune akan shi sai wani groaning suke lokaci guda, gashi suka kallon wani shaidanun Film a wayar su da gudu ta fito, kamar mahaukaciya, tunda ta nufi gidan Baba Mamman bata kuma leka shashin su ba.
Ta tsaya bayan kofar gidan, tana raba idanu,kamar wacce taga abin da yafi zare tsayi (😂)

..... Hiran Ladi mai kayan mata taji suna gulmar Lantana..
"Ke wallahi ciki ne da yar fa! Kuma balagazzar bata sani ba. Gwara ku raba yaran gidan da naku." Buuuutu ta fito daga maboyinta tana zare musu ido. Tana shirin artawa a guje suka kusan kamota, tuni Allah ya bata sa'ar guduwa.

......
"Hahhhh! Shiiiiii! Washhh." Inji lawali mai rake, Takiya tana kai mishi 💯, jinta yake har tsakiyar

kan shi, kallon kofar yayi shi sai yaga kamar Shigowa amma bai ga wanda ya shigo ba, shi yasa bai wani damu,.kawai dai yana buga tashi ne kawai. Sai da yayi sosai sannan ya d'ago kan shi tare da matsan yan kananun nonuwarta, sannan ya ture ta, yana sauke ajiyar zuciya.

Itama komawa gefe tayi tana kallon shi, tace sauko yar pant dinta ta saka, sannan ta kuma gyara zamanta, zata fita tace mishi.
" Kace min Sahiyah ciki gare ta?"
Wani kallon banza yayi mata sannan mai da hankalin shi, kan wayar shi Wato Indon ƙauye, yana maida videon da suka gama gani har tayi. Mishi yadda matar ciki tayi wa namijin,.tsaki yaja mata tare da daka mata tsawa.

Ya nuna mata hanyar fita, da sauri ta bar dakin, tana tura mishi baki.

Koda ta shiga cikin gidan kai tsaye cikin gidan su ta shiga tayi wanka sannan tazo tana fesawa uwarta, Nan itama ya tashi ta kai gidan su Azumi, daga nan dai magana ya fara yawo har waje, Lantana bata sani ba, matan gidan sun ninke ta bai bai.

Sai da maganar ta isa gidan mai danwake sannan itama tazo suka saka Sahiyah a gaba sai Asibitin wani inyamuri mai suna ogomu, ana zuwa aka ce ciki ne dan sati bakwai za a iya cire mata shi. Aikuwa ta dawo gida ta kwashe kudinta tsaf, sannan ta nufi asibitin. Likita da yaga Sahiyah ya shiga lashe bakin shi ne an biyan kudin suka shiga cikin dakin da ake burge cikin.

Shegen kwaro, talle yar banza yayi sai da ya darjeta bayan ya zuba mata alluran barci, yayi yadda yake so da ita, sannan ya tura mata karfen ya ciro dan tayin, ya zuba a wani kawo, sosai ya burge cikin sannan yayi mata alluran kashe zafi da wanda jini ba zai zuba ba, ya fito tare da saka wasu Nurse suka fito da ita.

... Cikin tashin hankali Lantana take kallonta, dan ji take kamar Yarinyar ba zata rayu ba, ga kuma tsoron mijinta kar yasan abin da Sahiyah tayi ya kore
Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu..
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***
https://my.w.tt/aprwHkaoibb
HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

_Gaskiya kun sanyawa Lantana Idanu. Ba ita daya ba hatta Oga Aamil 🙆🏾‍♂️ Fatan Alkhairi

Team Lantana!_

'''Sadaukarwa gare Black Women na Online baki daya🙎🏿‍♀️ tare Da Jarumar ku! Sidrah😂.Yar baka mummuna Mrs Aamil Insha Allah black and white couple 🤣🤭'''

#ita ce mafarkina
1️⃣6️⃣
"Adama baki tunanin wani abu ya same ta, idan ta mutu da?"
Tsaki mai dan wake tayi sannan ta zauna tare da sauke ajiyar zuciya, tana faɗin.

"Da ban yarda da nan ba, ai ba zan kawo ki ba. Wannan yadda take alluran barci aka mata, dan haka ki kwantar da hankalinki babu abinda ya faru da ita."

Gauron numfashi ta sauke tare da gyara zama tace.
"Mai dan wake, yarinyar nan da ɗaukar magana take, ta rasa me zata dauko min sai cikin shege kuma nasan yanzun haka maganar ya karade cikin gidan mu.
..... Amma zunzurutun bakin ciki da hassada aka min shiru, ana kallona dashi duk sai na ci kutumar Ubansu dani suke batun."

"Eh mana, ai abun ya jima ya a faruwa sannan maganar gaskiya, yaran gidan ku, duk suna bin mazan da suke cirani a kofar gidan ku, wanda ya gaya min ba zai musu karya ba, dan haka ki ja mata kunne kafin wani abu ya kuma lalacewa babu ruwana." Inji Mai dan wake,

Sai da Sahiyah tayi awa uku sannan ta farka, da ciwon ciki. Allura aka kuma mata, sanan suka sallame ta, suna dawowa gida Duk Lantana tana cike dasu.

Ruwan wanka, ta daura ta gasa yarinyar sosai, sannan ta dauko mangul ta jika mata ta sanye, bayan ta kwashe kayan jini ta wanke.

Kafin ta daura musu, abincin rana, dan tazo ta samu Sidrah ta haɗa mata wuta, tare da wanke wanke.
Suna shigowa ta bata kuɗin kayan miya, yanzun haka ta wanke tana kirbwa a turmin ne.

Tana idarwa ta kwashe a cikin tukunyar, ta d'aga labulen d'akin Lantana tace mata.
"Innah!"
"Uban me kike d'aga mana labule munafuka." Inji Sahiyah,
"Ke bana son hauka, Sidrah juye wancan manjan a cikin miyar ki dauki naira hamsin ki sayo kafi zabuwa ta Ashirin dunkule talatin."

Gyada kai tayi tare da fita da sauri, tana aiwatar da abinda aka sakata.
"Innarmu! Yanzun kina nufin nan da wata biyu zaku aurar da Sidrah?" Inji Sahiyah,

Kwafa Lantana tayi tare da jin haushin abinda yake shirin faruwa, kallon Sahiya tai sannan tace

mata.
"Wani shegen ne kika bashi kanki ya dirka miki ciki?"
Uwar ta tambayeta tana me hararar ta.

Cikin rashin kunya, wanda ya bi jikinta, tace mata.
"Toh ai bani daya ce, Zabaina da takiya, duk suna tare da Lawali da Karibu,"
Buge mata, baki uwar tayi sannan tace mata.
"Dan Ubanki idan na kuma ganin ki, a soron waje sai na mutsike ki."

"Toh ni wallahi sai dai ayi auren nan dani" ta faɗa tare da zubda kwalla, tsaki uwar tayi dan tasan kome zata yi tunda aka ce auren na Sidrah ce babu wanda zai hana sai Allah. Dan haka ta shareta bata kuma bin ta kanta ba, karshe ma girkin ranar Sidrah ce tayi sabida idan ta haɗa abu zata gaya mata.

Har ta gama ta ajiye a gefe tana kallon suka ci sannan suka zuba mata jagwale, tare da kanzo. A binka da wacce ta tayi girkin, tuni taji abincin yayi mata zio (🤣 Black Girl in kitchen)

Tana gama cin abincin ta wanke tunkuyar aka mai da na dare, nan ma itace tayi kome tuka tuwon ne, Lantana ta amsa.

.... Cikin gida basu san cewa an cire cikin jikin Sahiya ba, har kusan kwana uku, ana ririta alamarin. Wasa wasa sai da maganar ta kai sati biyu sannan mazan gidan suka ji labarin, Allah ya kub'utar da Lantana da Yarta, aikuwa aka kwashe su zuwa asibiti, binciken Sahiyah aka ce babu ciki.

Da farin cikin ta, ta koma gefe. Sannan aka kuma yiwa Takiya, take aka samu, sai Zubaina Allah ya sota tana haila, ai kuwa tun asibitin ake dukar Takiya, ta Kum dage ai ba ita daya bace. Dukkan su uku.

(Ta fashe da🙆🏾‍♂️😂🤣)

Dan haka suna dawowa gida, aka ɗauki matakin farko shine koran su Lawali, bayan Mahaifin Takiya ya sanya shi a kotu, sabida na farko yaci amanar su, na biyu ya lalata tarbiyyar yaran su. Na uku dole ya amshi auren takiya, ko yana so ko baya so.

Bai yi taurin kai ba, sabida yayi alakari da suna da Yan uwan masu kuɗi idan yaja zasu iya rufe shi. Ita kuma Sahiyah,aka hadata da Karibu, Zubaina kuma wani Yan uwan su ta gurin Uwarta yace yana sonta dama, shine aka saka bikin da na Sidrah.

Dan haka Lantana ta shiga rashin hankali, sabida basu tab'a tsammanin haka ba, kuma da tayi magana, Malam yace sai dai ta bar Mishi gidan shi.

Sanadin wannan al'amarin ya sanya suka fita harkan Sidrah, domin basu da ma lokacin ta,

takan su suke ma, gefe guda suka Lantana ta sake mata girkin rana da na karyawa.

Tun tana shirme har ta kai idan tayi zai ciwu, sabida tana daukar gyaran idan tayi na yau ya samu matsala dukarta Lantana take tare da gaya mata gidan da zata shiga ba karamin gida bane kuma abincin su ya ci kaniyar na gidan da take yi yanzun.

.idan da wuya da azaba. Zata yi kisa, toh da gawar Sidrah ta tube, amma sai Allah ya daura mata wani irin juriya da hakuri, a da idan suka mata kuka take, a yanzun babu kukan sai dai kuma. Bata tab'a faraa ko wani abun farin ciki kaga dariya ko murmushi.

Bata cika shiga damuwar kowa ba, nata ya ishe ta kuma bata tab'a kawo karar kowa, balle yanzun da gidan kowa yake kokarin b'oye damuwar shi. Gefen Lantana kuwa, tana hada Sahiyah da magungunan mata, tare da wanda zai matseta.

... Gyara sosai takewa yar nata, tare da mantawa da wata Sidrah, sabida tace, ba zata bata kudinta a koro ta ba.
(🤔 Ni kuma nace haka yafi ko? Domin idan aka dura mata an san ranar da Oga Aamil zai zo ne?).

***

"Ranka shi dad'e! Ga me zanen yazo!" Kallon shi Allison yayi tare da nuna mishi guri ya zauna, sannan yace mishi.
"Ga hoton ka cire min ita!"

Gyada kai yayi, mutumin ya fara fitar da kayan aikin shi, ya ajiye katakon da kuma kayan zanen. Lumshe idanun shi yayi tare da cewa.
"Ka fara!"
Bude idanu yayi yana kallon mutumin yana zana hoton laptop din, ganin yayi kamar ya rage mata, wasu abubuwan rufe laptop din yayi. Mutumin ya kalle shi.
"Me yasa kuma?" Inji Mom tana saukowa daga sama.

"Mom ya rage mata abubuwa dayawa, ita baka ce haka kwayar idanun ta, tsakiyar baki ne mai dauke da farin digo, gefen idanunta fari ne kal, Mom nayi mafarkin ta. Baka ce Sosai. Hakorinta farare ne. Mom yarinya ce, karama tana da gashi bak'ikirin, dube yadda ya zanata."

D'ago kansa yayi, sai yanzun ya fahimci, wacce aka zana, Emily ce, haushi ya kama shi.
"Kuyi waje da dan banza, ku bashi ladan aikin shi."
"Son ka bar wannan shirmen, mafarki ba gaskiya bane, kuma yadda kake rayuwarka da yadda kake tunanin zaka iya zanata a same ta, ba zai yiwu ba. Sabida ita kirkira ce, kai kuma kana raye."

Kallon Mahaifiyar shi yayi, sannan ya mai da idanun shi kan laptop din shi, ya dauki inda yake aikin zanen ya fara zana hotonta, yana fad'in.

"Zuciyata ta ce min kar na bari, ba soyayya bace, kawai tausayi ne. Kukanta yana hanani barci, damuwarta kullum kara ta'azara yake, ina ganin ta a tunanina na, ina jinta a cikin jini na, tana yawo a fitar numfashi na, koda banyi katarin haduwa da ita ba, naji a jikina zan so Yesu christ ya kawo mata dauki."

Yana gama fadar haka yayi daidai da gama zanata,tana zaune ta kifa kanta tana kuka, tare da rungume kafarta.

Abinda ya rubuta a kasar hotonta *_Ke ba mafarki bace gaskiya ce ke_* , ya sanya Emily wurgi da Laptop din, tare da fashewa da kuka tana fadin.

"Allison! Meye amfanin rayuwata!"
Riko hannunta yayi cikin sigar rarrashin ta yace mata.
"Ke ni fa wasa nake ita yarinyar ai kirkira ce inji Mom, ke kuma ba gaki a gabana ba, dole dai ai zan aure ki, kuma muyi Shagali me dadi..bar damun kanki da wata zanen hoto."

Da haka ya lallabata, suka rabu lafiya, Mahaifiyarshi sai dariya take, tare da jinjina mishi sabida lokaci guda ya tsarata kuma ta tsaru, kuma suka ci-gaba da hidimar su.

Zana hoton mafarkin shi ya fara zame mishi jiki, domin har kafaffen sadarwan na intanet yana daura hotonta, wasa wasa ya samu mutane suna bin kowanne posting din shi, tare da niman ya dauke su aiki.

***
Jan kunamar bindigar yayi ba tare da damuwa ba, ya sakewa Benni a kafar shi.
"Ba a haife ni domin kawo karshen Labarin ba, an haife ni ne domin farkon labarin, kai waye da zaka yi yunkurin kashe ni!"
Ya kuma sake motsawa ya sake mishi harbi.
"Toh kai waye?" Inji Benni.

"Ni kake tambaya? Lallai aiki ya same ka, sauka lafiya." Ya zuba mishi harbi a goshi sannan ya saka kai ya fita abinshi.

..... Bayan mins biyar da faruwan Al'amarin, sai ga Aamil yazo koda ya shigo ya samu ai abin har ya faru, dukar kasa yayi sannan ya fita kafin a kama shi.

Shiru yayi, bayan ya isa gidan shi. Dan kwana biyu nan baya zama a cikin gari a makarantar yake zama, sabida karatun shi. Kuma kullum fuskar shi a tushe take, sabida abinda yake faruwa, dan ana bibiyar shi sosai. Shi yasa yan kungiyar shi  suka ce ya bar zaman unguwar ya koma cikin makaranta, haka zai sama mishi tsaro, tunda mutanen basu san cewa bashi bane.

***
Dutse.

Ana ta hidimar sunan Latifah, wacce ta rike Hajiya Uwani a matsayin uwarta,, duk da surukarta bata so haka ba, sai dai ta fahimci ba zata tab'a juya Ali da yarinyar ba, sabida ra'ayin su daya ne.

Tunanin su daya ne, domin daga baya ya sawun matar shi, ya tare a jikin Ummin Abdus Samad, dake mace ce da bata damu da kowa ba, sai gashi ana mata kallon ta mallake Ali da matar shi, tun uwar tana dauka karshe dai ta watsar dan kome zata yiwa Hajiya Uwani ba zata tab'a kulawa ba, dan ko da Hajiya Surayyah ta haihu, Itace akan ta, da farko haihuwar taso matsala. Itace a kanta har ta haihu karshe babyn bai zo da rai ba, ga zubar jini. Da wasu abubuwan marasa dad'i, dole Alhaji Ma'aruf ya saka aka juyar da mahaifar, sabida yace bai ga amfanin wahalar da kai ba, tunda yara goma nan dai sun wadatar da ita me take bukata..

Hajiya Amarya itama ta sauka lafiya, inda ta sami d'a namiji, aka sanya mishi Adam, suna kiran shi Aasim.

Tun da ta haifi Yaron ta kakkaro rashin mutuncin, kana mata magana zata ce ita ta haife Uban gida..

Hidimar sunan yayi sosai, Latifah ta haifi mace , sauran matan duk suna da ciki, kuma fatar su ayi hidimar da taci Uwar na Latifah, kuma dadin dawa, Iyayenta da yayunta suna da rufin asiri, shi yasa da aka tashi yin abin sai aka yi tuwon girma miyar nama, sai dai kashe a cikin kayan fitar sunan da aka kawo mata daga gidan su, an sace turmin Super wax..

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/XNggHNp0ibb

**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Tarzoma
17

Wani irin takaici ne ya kuma kama Raliyah, dan tasan Tabbas Ummita ce ta dauka, amma idan

tayi magana za ace dan basa shiri ne yasa ta share zancen ta cigaba da jajjantawa mai jegon. Har yamma ana niman zanin ba a gani ba.

Karshe abin ya zama gulma, kowa ya shigo sai ya san an zabga satar rashin kunya, a cikin gidan. Dole shakku ya kama shi domin al'amarin sata ba wasa a cikin shi. Yarinya za a kira da Aafreen.

Ba a kuma mamaki ba, sai da dare yayi aka yanke cinyar Ragon suna, anan ne fa kowa ya yi caa akan yankar namar, da gari yawaye sai aka tsinci namar a gurin wanke wanke, kamar abune yaja, dan anyi surutu tare da fatar Allah ya tona asirin barawo.

..... Gidan ya koma ko dan abu ka ajiye kafin zuwa anjima, zaka niman karasa kuma an rasa waye ke wannan aikin, domin Ummita ta rufe kofar da zaka zarge ka, a hankali har aka gama hidimar sunan. Ana cikin soya namar ragon Ummita tayi ta shiga da fita, har dai karshe wata Kanwar Mamar Latifah tace mata.
"Ke! Kar na kuma ganin kafarki ' a nan dan kinyi na farko kinyi na ƙarshe, dan na lura baki da kunya, ina zaune anan yar banza mara zuciya sai tsame nama kike. Na kuma ganin ki tunda baki da aiki sai na sata yar banzan mara kunya, ki je can Allah zai tuna miki asiri."

Simi simi tabar dakin, ta koma nata, tare da jin mugun kunya.

..... Kallon takardun gaban shi yayi, sannan ya d'ago kai ya kalli Hajiya Uwani,.kafin ya saka hannu ya nade takardan yana sauke numfashi,.kafin wani lokaci yace.
"Saura kwanaki ƙalilan, kuma ban san ya zanyi da yan uwana ba, ban me zance musu ba. Kuma sun gaya min yarinyar tana cikin kunci. Ya zanyi?  Su kansu sun matsu da a d'aga yarinyar daga cikin gidan, ko haka zai sama mata daraja da sukuni.

Ni kuma wannan mutumin banzan ne nake gudun kar yazo ya cutar da yar mutane, yarinyar da bata tashi a gaban iyayen ta ba,babu amfanin mu hadata da wanda zai wulakantata."

Murmushi Hajiya Uwani tayi sannan tace mishi.
"Ni kuwa nake ganin kamar zai zo, dan ina jin haka a raina zai dawo da izinin Ubangiji, kawai abin da zamu mishi Addu'a, shine matakin da ya dace mu dauka. Amma Insha Allah."

Cikin zakuwa yace mata.
"Kuma kina ganin idan yazo zai amshi auren Yarinayr da muka bashi?!"

"Wannan kuma sha'anin Ubangiji ne, amma nayi imani da Allah ba zai ki amsar ta ba,!"

Shiru yayi kafin yace mata.
"Am bored"
"Dame fa?"

Ta tambaye shi, "da halin Aamil, baya gudun zuciyata, duk abinda zai jefa ni cikin damuwa shi yake aikatawa. Yanzun don Allah meye amfanin haka? Meye ribar abinda ya aikata,  duk cikin y'ay'ana shine ya fita. Zakka ga baki daya abun da ya gadama yake aikatawa kuma ko nayi mishi magana baya kulani."

"Sabida kai ka bada goyon bayan a cutar da shi." Ta faɗa tare da tsare shi da idanu.

Girgiza kai yayi cikin damuwa sannan yace mata.
"Ko kadan bani da hannu akan abin..."

"Me yasa baka nime Mahaifiyar shi ba? Ka tab'a bashi labarin mahaifiyar shi? Ka tab'a gaya mishi cewa soyayya ya haɗa ku ba k'iyayya ba?

Abin da bakin ka ya iya furtawa shine dukiyar ta da yake hannunka, me yasa baka tab'a tunanin cewa dole wata rana zai bukaci Mahaifiyarshi?"

"Me yasa kuke zargina da nuna a halin ko in kula akan shi?" Ya tambayeta a gajiye,

Murmushin gefen baki tayi sannan tace mishi.
"Me yasa kake tattalin Hajiyarka? Ka tab'a tuninan shima yana da burin tattalin mahaifiyar shi haka?

Me yasa baka tab'a cewa Hajiya tabar gidan ka ba, kai ko Hindatu tabar gidanka?  Baka tab'ayin haka ba, amma kana blaming Yaron da ya taso a karkace, tare da tallafawar ka, sannan kayi tunanin zaka mikar dashi, how? Toh a ajiye a gefe yayi laifi ka hukunta shi sai ka kashi a jikinka yadda babu wanda zai iya cutar da shi, ka nuna musu shine farin cikin ka, toh ka nuna wofantar dashi a gaban kowa, ba dole ya wofatan da duk wani abinda ka kawo mishi domin cigaba ba.

Kana ganin kamar muna takura maka ne, amma ni a tuninan kaine ka lalata mishi tarbiyya ba kowa ba, da ace ka nuna mishi gata baka iya sakewa da kome amma sakewar da zaka yi dashi yafi na yadda zaka yi da kowa toh babu wanda ya isa ya raba maka hankalin shi da kai.

Amma yanzun an gama b'ata kome tsakanin ku, domin babu boka babu malam kawai tsantsar azabtar dashi da akayi yasanya baya tausayin ka, baya jin kanka.

Ka nutsu da kyau mana, ka tab'a kama shi da laifi? Sai dai ace kama, yayi laifi baka kama shi dashi ba. Karfi da yaji an mai da shi mai laifi ba tare sanin ka ba, sannan yau kayi tunanin zai bi ra'ayinka ko sau daya ka tab'a mishi adalci? Baka tab'a ba, wallahi nayi imani da yau Hauwa zata zo, taga yadda ka wulankata mata d'a zata ce dama sabida dukiyarta ka damu da ita, gashi bayan bata nan, ka gaza rike abin da tabar ka, kai Hajiyarka bata kaunar wata mace ta juya ka, amma ta gaza samawa Yaron da aka rabashi da Mahaifiyar shi a tsumar goyo."

Cikin zafin rai ya kalle ta, sannan ya kauda kan shi yace.
"Ba raba ta akayi dashi ba, itace ta gudu tabar shi."

"Ba guduwa tayi ba, koranta akayi tare da barazanar za a kasheta idan ta kuma dawowa rayuwarka da ta yaron." Cikin rawan jiki ya d'ago zai mata magana, ruwa ta zuba mishi yasha, sannan ya cigaba da cewa.
"Sam bata da manufar tafiya, sai dai masu gidan sun juya maka akalar rayuwarka, ba tare da ka fahimci cewa akwai kuskuren da ka tabfka ba.

Zaka iya kallon kowa da ido biyu, amma mafi girman gani da idanun zuci ne, sabida shi kullum a bude yake asalin idanun mu kuma a rufe suke.

Insha Allah Aamil zai dawo soon."
Daga haka tayi feccewar ta, ta duba yaranta ta kuma musu addu'a, sannan tazo ta kwanta.

Shiru yayi yana kuma yarda da batun ta, tare da jinjina karfin yarda da batun su, itace mutum na uku da suka bashi damar ya bincika abinda ya faru da shi. Kuma yana shirye ya bincika Sai dai matsalar, yadda zai shawo kan kome kafin lokaci ya kure mishi.

Hau saman gadon tayi tare da ce mishi.
"Me kake tunawa?"
Furza da iskar yayi daga bakin shi, sannan ya ce mata.
"Toh yanzun idan naje gurin Hauwa ta ce zata dawo fa?"

Dariya ta saka mishi sannan tace mishi.
"Wai? Malam ango, don Allah rabani da batun nan, ai ba wani abu bane dan an gyarota, kawai sai dai ka rufe idanunka ka shige dakin Babynka!"

Dariya suka saka a lokaci guda, yana kuma kallon ta ya kuma cewa.
"Baki kishina kenan?"
"No a batun rayuwa irin yadda kuka yi a baya babu amfanin mutum yayi kishin Hauwa.

Ba ganin bata nan ba bari na gaya maka wani abu ni bazan baka kudi kayi jari ba, dan nasan aure zaka b'allo ina dalilin na baka damar yin auren karshe maza ba kunya ce ya cika ku ba, sai kaje la dauko mana sa'ar harirah."

Duk yadda yazo hana kanshi dariya sai da tasanya shi dariyar,
"Don Allah Uwani barni da dariya haka, cikina ciwo yake. Ina ni ina budurwa bayan na tara manyan mata, a cikin gidan ai na kawo budurwa sunanta Allah sarki, domin kuwa ba zaku tab'a barinta ta huta ba, kuma ba zaku tab'a barina na huta ba.

Ku hura mata wuta, ita kuma ta hura min, yan mata sai su Aamil ni bana da ra'ayin su yanzun."

Tab'e baki tayi, sannan tace.
"Hmm! Ai ku maza ba a iyar muku, dan nasan abinda yafi haka ma zaku yi, kuda baku da. Aiki sai tara mata da yara."

"Gaskiya yau kinci tuwo a kaina, zan rama amma ba yanzun ba, akwai lokaci dole ma kiyi kokarin ganin kin bani hakuri domin idan lokacin yazo babu sauraron ki."

Dariya tayi tare da kashe wutar gefenta, tace masa.
"Yallabai zan bi lafiyar gado, idan ka tashi sallar dare, ka tashe ni muyi tare."

Shima kwanciya yayi tare da aza hannun shi a kirjin shi, yana kallon yadda kome na rayuwa suke tafiya mishi, dole ko yaki ko yaso, ya nime mafita, amma ba zai manta Ahmad da Abubakar ba, tare da matar arziki Rabi'ah.

Maganar su gaskiya ce, duk abinda ya faru shine babban mai laifin, kuma ya bada gudummawar kome da ace zai iya gyara kome da babu makawa da ya gyara laifin da ya faru, gashi nan ya janyo kome ya lalace, daga matar shi mai kaunar shi zuwa yaron da suke matukar kaunar shi tun yana cikin Mahaifiyarshi, yau an shiga tsakanin soyayyar su. Gashi nan tayi nesa dashi.

Wannan al'amarin yayi mugun d'aga mishi hankali, kuma ya sanya zuciyar shi raunin, dan bai san bai tab'a kawowa Hauwa zata iya daukar wannan matakin guduwa ba, da farko amma jin zigar Mahaifiyarshi ya sanya jin Lallai zata iya.

Gashi ta tafi tabarshi da dukiyarta nan dai gashi nan kome ya gaza tafiya mishi yadda yake so. Why?

Sabida ya zalince ta, juyi kawai yake ba zai iya cewa ga lokacin da ya dauka yana nazarin abinda yake damun shi ba, amma tabbas yasan ya tafka laifukan da ba zai iya gogewa ba, yayi amfani da rashin bincike ya wulakantata, ya kuma juya mata baya...
Anya Allah zai yafe mishi kuwa? Wannan Ita ce ta tambayar da zuciyar shi tayi mishi. Tashin hankalin ya kuma shiga a cikin wannan daren, haka ya tashi zaune. Kafin ya shiga ban daki yayi alola yazo ya gabatar da sallar nafilla. Jan yatsar kafar Hajiya Uwani yayi ta farka, gyaran murya yayi mata, ta tashi zaune.

***
Tarzomar da ɗaliban makarantu suka tadda yayi masifar d'agawa kowa hankalin, musamman kafaffen sadarwan zamani, ba kuma kome ya kuma haifar da tashin hankalin ba, sai hasko fuskar Ɗan Attajiran nan wato Mss William. A cikin zanga zangar.

Wanda ba kome ya haifar da shi ba, sai samun gawar dalilin da yafi kowani dalibi hazaka ya rataye kansa, wannan abun yayi musu zafi dan haka suka bazama titi sai an nima mishi

adalci, saboda yayi Rubutu a bangon dakin shi a inda yace.
MUTUWA TA BA KASHE KAI BANE KISAN KAI ne sun sanya ni aka yi ko kuma su aikata mugun nufinsu a kan dalibai.
. wannan abin ya d'agawa kowa hankalin, shine dalibai suka fusata sosai aka shiga zanga zanga.

.... Kai tsaye daukar hoton abun ake, dan haka ganin Allison a cikin tattakin yasan Abokan cinikayyar Mss William, mata magana, take ta kunna tv kasancewar bata kasar, tana kasar Australia, aikuwa ta ganshi akan gaba, yana d'aga hannu sama sai an musu adalci. A rikice ta shiga kiran Layin shi, dai dai lokacin da Camera ta dauke inda yaƙe.

....
Wayar na shiga tace.
"Kana ina Yanzun?"
Kamar ba zai magana ba, yace.
"Mom ina gida mana!"

"Toh zan kiraka video call"
Kashe kiran tayi, ta kuma buɗe data, sannan ta kira shi, yana shiga ya dauka, yana tsaye a gaban allon da yake zana hoton mafarkin shi, ajiyar zuciya tayi sannan tace mishi.
"Ka kunna tv yanzun ko zaka ga abinda na gani."

Kunna tv yayi bai ga kome ba, "ba kallo Zaka yi ba ka samu P.A ku nimo shi, karka sake na kuma tambayarka kuma zanyiwa P.A magana tabbas akwai shi a gurin," duk da ta tabbatar amma zuciyarta yana girgiza har lokacin.

..... Tsayawa yayi tare da sake murmushin jin dadi, ganin yadda ake zanga zangar, har ya kauda kanshi, a fisge ya hango mai kama dashi, zaro idanu yayi tare da juyawa yana kallon tv, tab'a fuskar shi yayi bakin shi na rawa. Yana shafa fuskar shi tare da nuna tv.

Kiran P.A yayi suka fita, shi kuma ya kira Yan sanda..

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/KKSuC7CWjbb

**RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#Ruwa a jallo.
18

Cikin mintinan talatin suka isa inda ake zanga zangar, tare da niman shi tare da yan sanda, a kai kai suna waya da Mom din shi, tare kuma da P.A ɗinta.

Shiru Allison yayi bai fita ba, sabida kar fitar shi ya kuma haifar da rudani, zurfaffa bincike yake sosai, tare da nazarin me yasa Mom ta rud'e?

.... Me yasa ta damuwa, yanzun haka takira waya na biyar kenan, meye matsalarta da son sai an kama me kama dashi? Duk da kuwa bata ƙasar. Akwai abinda take boye mishi na tsawon shekaru masu yawa. Toh meye abin da bata son ya sani.

Toh meye ne wannan abun? Shiru yayi na wani lokaci, kafin ya dauko laptop din shi, yana duba wasu hannayen jarin da kuma adadin kudin su da yake banki, bai fahimci kome ba. Haka ya ture laptop din, sannan ya kuma kiran P.A ya shigo da sauri, tunda yaga yadda Allison ya tsume fuska, tare da daura daya akan daya, ya shiga nutsuwar shi.

"Har yanzun baku same shi bane?"
Ya wurga mishi tambaya, girgiza kai yayi sannan yace mishi,
"Yallabai."

"Ku cigaba da niman shi, kuma, wannan ya zama sirri a tsakanin mu, bamu son mutanen gari su san da batun, ba iya nan ba."

Kasa yayi da muryan shi, ya cigaba da Magana.
......
Aamil kuwa, ba kome ya sanya shi barin gurin ba, sai hango wasu fusatattun kartin maza, suna d'aga mishi rigar su, ya hango bindiga, murmushi yayi sannan ya juya tare da barin gurin.
Aikuwa suka rufa mishi, mutum kamar iblis, jan su wani lungu yayi. Suna shiga suka hango shi yana cin pizza, cikin kwanciyar hankali, gefen shi kuwa karfe ne da ya b'alla na (tap) wato panpo.

A hankali suke takowa inda yake, kallon su yayi sannan yace musu.
"Kunga nasan a fusace kuke! Kuma nasan ba zaku kyale ni ba,mai zai hana ku barni na ci abinci na koshi, sai na mika muku kaina salin alim."

Cikin hargagi suka yo kanshi, ajiye kwalin pizza yayi tare da rike karfen hannun shi, dayan na zuwa kafin ya kamo shi ya buga mishi karfen a kafad'arshi, sai da hannun shi ya

kwab'e.
"Cewa nayi ku jira ni na gama cin abincin ko? Idan kuka hana ni, cin abincin Uwar me zaku nan bani?  Jakuna kawai."

Ya kuma ɗaukar kwalin ya cigaba da ci, ga mutumin akwance kasa, bindiga daya daga cikin su ya dauko,.kafin yaja kunamar shima, ya jefa mishi kwalin pizzar, tare da ɗaukar karfen ya shiga rufe su da duka.

.       "Zaku gaya min meye nayi muku? Waye yake son kashe ni? Zaku gaya min ko sai naci ubanku."  Sosai yake dukar su kamar Allah ya aiko shi, da gudu suka bazama, ya kuwa bi bayansu, jifar su yayi da karfen sai kan Glass din motar Allison.

Sai da tayi tsawa, ta rugugguge, tsoron yasa Allison ya kare fuskar shi da kan shi, yayin da yaji babu wani abu ya d'ago kan shi, ido biyu suka yi da juna.

Kowanne sun ya firgita, cikin wani irin yanayi suke kallon juna, kuma a lokaci guda suke shafa fuskar su. Bude motar Allison yayi zai fita gurin Aamil. Shima kuma burin shi ya isa gare shi, sabida bai tab'a jin ko a tarihi akwai me kama da shi kwaf daya haka ba, hango guard din Allison ya sanya shi juyawa da gudu ya bar gurin.

"Kubi bayan shi yayi gaban?"
Allison ya faɗa da ƙarfi, aikuwa suka bi bayan shi dan banza me zubin almatsutsai ya gudu, dawowa suka yi aka canzawa Allison mota,  rike kan shi yayi tabbas sunyi ido biyu dashi, idan haka ne toh waye shi.

Toh amma ai ance masu kama da wani uku ne a duniya, me yasa bai yi tunanin cewa akwai masu kama dashi ba. Toh kuma haka ne, dan yayi imani mom bata tab'a nuna mishi wani abu bayan mr Richard, shine mahaifin shi. Ajiyar zuciya ya sauke tare da cewa.
"Ba mamaki yana cikin jerin mutanen da suke kama dani, toh koma me nene, dole a kawo min shi na gan shi, na kuma tabbatar da cewa babu abinda ya haɗa ni dashi."
... Haka suka bar gurin babu wani abinda suka samu domin Aamil ya bar gurin.

***
"Tabbas akwai matsala! Waye shi? Meye haɗi da shi? Toh ko nima ina cikin mutanen da suke kama da wasu ne?

Anya kuwa? Toh ko dama shi ke son kashewa aka buge da nima na, lallai akwai matsala. Mss William! Toh ko shine D'anta da ake son kashewa?  Hmm biri yayi kama da mutane."
.take kuma ya fara zafaffa tunanin shi, idan har wancan ake nima toh tabbas, shi bai da alaka da mutanen da suke nima, toh tabbas bai da alaka da tashin tashinan da ake yi dashi kenan?

Toh waye shi? Kuma meye dalilin da suke niman rayuwar shi, bayan bai ga Alamar tashin hankalin a fuskar shi ba.

Kai meke faruwa ne? Ga baki daya kan shi ya kunce, tunanin shi ya tsaya cak, nazarin yadda yake tunani ya kuma tsayawa, dole ya nutsu, yana isa gidan Max.

Cikin rudani yake bashi labarin abinda ya faru, take shima ya shiga rudani.
"Toh Aamil me kake tunanin zaka yi? Tabbas wanda ka gani sunan shi Allison, amma ban tab'a ganin shi ba, sai dai jin labarin shi.

Kuma yana da kyau ku fahimci juna, domin kuwa babu yadda za ayi ana niman shi amma kai ne ake samu, kuma idan kuka fahimci juna dole kai ka bar ƙasar nan domin kuwa zasu cigaba da kawo maka hari, akan cewa shine bayan kuma ba shi bane kai ne!"

"Nima nayi tunanin haka, kaga dai shi akwai masu kula da lafiyar shi, kuma duk kasadar da na jefa kaina, sabida shi ne..idan na bar garin dole zasu kyale ni. Amma abun da ban mamaki kaga yadda muke kama,.idan aka ajiye mu guri guda ba zaka tab'a banbance mu ba, sabida kamar tayi iyaka ba na wasa ba."

---
Sintiri yake hannun shi duk biyu a cikin aljuhun wandon shi, kiran shi Mom tayi ya dauka, sun jima suna magana, kafin ta kashe. Wayar akan nan da kwana biyar tana dawowa, a cigaba da binciken da ita.

Zama yayi a kujeran Emily ta kawo mishi ruwa, amsar goran yayi sai da ya shanye tass. Sannan ya koma, inda ake ajiye kwalaben kayan sha, dan gurin kamar bar yake.

Ya shiga hada manyan beer tare da wines masu karfi, kafin ya jefa musu ice block, juyawa yayi tayi, yana kuma kallon yadda suke kallon juna da Aamil.

Yadda Aamil ke kallon cikin idanun shi, ya kuma karya mishi zuciya, tabbas akwai wani abu. Ruwa yafi jini kauri, yadda yake jin labarai dayawa akan mutane bai tab'a ji akan shi da wancan gayen ba, kurb'an giyar yayi tare da kuma zuba wani, yana sha yana kallon yadda suke tab'a fuskar junan su dsame time, abin kamar almara, idan za a tab'a samun masu kama da juna, tabbas tasu tayi tsananin. Sai da yasha sosai ya kuma bugu. Sannan ya bar bar din, zai fadi suka kai mishi dauki ya zabga musu harara, dole suka matsa. Dakin zanen ya shiga, yana kallon fuskarta me dauke da kwalla.

Murmushi yayi sannan yace mata.
"My baby! Ki bar kuka Mom da Emily sunce baki wanzu a duniyar ba, ni kuma nace kina nan a cikin duniyar nan. Me yasa ba zaku tawo gare ni ba."

Hango murmushi yayi akan zanen, yace.
"Na sani ai! Kema kina jin yadda nake ji, toh tsaya mutum na gani sak ni, kuma ya gudu ya bar ni. Taya zan damu da halin shi, sabida zuciyata tana bugawa da tunanin shi. Waye shi." Nan ya

buge da barci, tare da mafarkin Baby, da Flower crown.

Tayi mugun kyau cikin wasu fairy gown, dan tsabar rashin mutunci na giya, wai a mafarkin ma fuffike tayi tana mika mishi hannu, Shashanci shi kuma ya riko hannunta suka tashi tare, sama suna dariya..

Koda Emily ta shigo d'akin yayi barci, sai ma janye shi da suka yi tare da kai shi dakin shi daya da yake kasar kusa da na Maman shi.

***

Hadeja.

Dake Lantana tana da yan uwa a danbuwa, na jahar yobe, dan haka ta shirya Sahiyah ta kai musu ita, tare da labarta musu tsiyar da tayi.

Nan kuwa aka shiga girketa, anan zuba mata kayan mata sosai. Kamar zata yi hauka sabida yadda take zubda ruwa a jikinta. Idan dare yayi kasa barci take, sai da tayi ta juyi. A ranta tana jin cewa idan ta kama namiji Tabbas fyade zata mishi domin ita kaɗai tasan abinda take ji.

Dake kwanan Lantana biyar ta koma, Kanwar Lantana da take can, ita ke mata gyaran jikin.

"Sahiyah ya kike jin yadda maganin yake a jikinki?" Ta tambayeta,
"Gaskiya yana sani ciwon ciki, duk nayi ta zubda wani irin ruwa."

Murmushi Matar tayi sannan tace mata.
"Toh ga kanwa ko lemon tsami, idan kin fara jin haka kina jikawa."

Amsa tayi ta ajiye matar ta Cigaba da nuna mata yadda zata gyara gabanta, amma ita yarinyar nan ba wannan ne a ranta ba, matsalarta namar wandon ce. Dan har ta gama hango yadda karibu zai Zungure ta sosai, yana shiga lungu da sako na jikinta, had'iye yawun tayi domin tasan ranar zasu yi kwantar shagalin arziki ne, ita kanta tasan zata ciwu ba na wasa ba. Idan bata manta ba. Ya taba gaya mata yace shi kwararre wajen kai mace duniyar gajimare, kuma ta yarda da hakan, domin yafi Lawali buga iska.

Sannan bata raba dayan biyun cikin da tayi da aka zubda mata shi kamar na shine, domin ranar da tayi wanka ya nime ta, kuma bayan sun gama, ta jima a dakin shi dan kusan asuba ta dawo, washi gari kuma Lawali ya gayyace ta, bata wani jima ba, dan shi baya tab'o mata G spot, ɗinta. Sai dai ke ki haura saman shi.

Gaskiya duk da tasan Karibu bai da Arziki, amma idan zai buga mata tashi, toh babu damuwar ta da wani arzikin shi. Ba kawai kayan shagali ya isheta. A kwana ana abu daya shine Shagali.

Da wannan yanayin take kwana take tashi a koda yaushe, tasan abinda zai kasance a

tsakanin su mai dadi ne.

....
A gidan kuwa, baiwar Allah tana nan, duk da yanzun sun rage yawan takurata, amma bai sanya sun ji tausayinta na marainiya ace nayi mata wani abin da zai kankaro darajarta ba, asalima babu wanda yake bin ta kanta sabida basu ga ta yadda auren zai tabbatar ba, tunda sunji labarin sabida muninta mijin ya gudu ya bar aurenta.

Shi yasa suke mata ba'a da akwai a hantse sai kyakyawa, bata tab'a kallon haka a matsayin abin cutarwa na, dan ita gani take kamar bata cancanci samun auren Aamil a matsayin ta na mareniya munmuna ba.  Kamata yayi a nima mishi wata a cikin dangin su, tunda akwai masu kyau da haduwa.

..... Kayan auren da aka kawo tun shekara daya da ya wuce, Lantana bata taɓa ba, amma Azumi da Yarta sun zo sun kwashi bra da wasu kayan kwalliya da pant, dan ma pant din dai dai Sidrah ce, sauran kayan suna cikin diba Lantana ta bude musu Bala'i tare da tara musu mutane. Dole suka bar gidan ta, tana kallon Sidrah a gindin murhu ko ta d'ago kai ta kalle su. Wani lokaci idan yarinyar tayi banza da su, kowa shakkar ta yake, shi yasa yanzun suke ganin matsa mata bai da amfani dan karta juye musu jakar tsabar su akan su.

.... "Ke sakaryan ina ce da ba zaki fasa ihu sun shigo zasu daukar miki kaya ba?"
Sosa keyarta tayi wanda kwarkwata suka sake samun damar yada zangon su a gurin, ta Cigaba da hira wutar kasancewar damina ake fama dashi itace bai cika ci sosai ba.

Idanunta sunyi jajjur, daukar itace Lantana tayi zata rufe ta da duka, Malam yace.
"Koda wasa indai ba so kike ayi kome kina gidan ku ba. Saura kwanaki ne da basu wuce sati biyu ba, ki bari na kai ta gidan mijinta lafiya idan ba haka ba, zamu shiga jikin juna."

Sake itacen tayi tare da kwafa, ta gaya mishi abinda ya faru, bai kasa a gwiwa ba yaje ya dawo da kome da suka dauka. Sannan ya mikawa Lantana kudi ta wanke mata kai tare saya mata maganin kurajen jikinta...

***
"Allison! An kama shi! Yanzun haka yana hannun yan sanda, amma mun.....

*Kuyi hakuri labarin bana gaggawa bane kome yana tafiya da tsarin labarin ne! Da sauran free Pages har yanzun... Sai dai muna gab da cimma matsaya guda😘😍*

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**

***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***
https://www.wattpad.com/980262254?utm_medium=link&utm_source=android&utm_content=share_published
HAZAKA WRITER'S ASSO...

Mai_Dambu

Bismillah Rahmani Raheem

🤣🤣🤦🏼‍♀️🤔🤭 Jama'a ina niman Uwar Tankwali 😂

#Sassauci
20

Haka aka raba su dan dole, bawai dan sun so haka ba, sai dai fahimtar indai suna tare Toh zasu yi ta faɗa ne kamar wasu zakarun tsare. Ran Allison ya gama b'aci musamman idan ya tuna da ce mishi da Aamil yayi dan daudu. Sake shafa bottom fi shi yayi tare da cewa.

"Banza jahili, Ni zai kira Gays!"
Can kuma idanun shi suka cika da kwalla, yana kallon P.A, bakin shi yana rawa yace mishi.
"Wai da gaske ni lusari ne? Sannan ni dan daudu ne? Don Allah ka fitar dani duhu mana"

Shigar da shi mota yayi tare da mika mishi wines, ya kurba. Tari ya fara, yana buga kanshi kafin wani lokaci ya shanye tare da niman kari, ko kafin su isa gida ya bugu sosai.

Dakyar aka fidda shi motar bayan sun isa gidan, kwantar dashi suka yi a dakin ƙasa, tare da lullaba mishi duvet,suka fito. Hawaye ke zuba mishi dan. Babu wanda ya tab'a cin zarafin shi haka, wai shine ɗan daudu. Shafa Manhood din shi yayi, yaji ta gim. Lumshe idanun shi yayi tare da budewa. Take giya ta fara mishi huɗubar tsiya. Sabida lokaci guda, My Baby tazo mishi, tare da jan hannun shi. Fincikota yayi ta fado kan shi. Yana kallon fuskarta, kurawa juna ido suka yi yana kallon cikin eye Ball ɗinta wanda yake da wani color na musamman. Wani sabon kasala ce ta dauko mishi bai san lokacin da ya matseta a kirjin shi yana faɗin.
"Ki kasance dani, har abada"

Jan kumatun shi tayi sannan ta bashi light kiss a bakin shi, kafin ta janye daga jikin shi, zata sauka.
"Ina zaki?"

Murmushi tayi tare da mik'ewa, dake giya ta gama gaya mishi gaskiya,hangota yayi tana tashi samar,tare da mika mishi hannu. Yana son bin ta, amma gabaki daya ya rasa kuzarin shi.

Lumshe idanun shi ya cigaba da yi har barci yayi gaba dashi. A gurin cike da mafarkan baby, a cikin wasu lambu masu kyau, sai zagaye shi take, tana dariya, tare da hayewa jikin shi. Tun yana biye mata suna dariya karshe suka zube a gurin sai bar numfashi suke ajiyewa, shafa fuskarta yayi, a hankali ya kai bakin shi goshinta, zai sumbata yaga tayi mishi nisa, sake murmushi yayi tare da riko ta yaga kamar ana janta, a hankali ya kai hannun shi. Gani yayi wannan me kama dashin ya shiga tsakanin su.

Tana mika mishi hannu, shima yana mika mata, amma wannan me kama dashi ya hana, kome. Dake zuciyarshi ta gama rike dan daudun take kuwa Aamil ya juya tare da gargad'in shi yana fad'in.

_Kai da kake ɗan daudu, me zaka yi da mace irin wannan! Tawa ce ita din_

Daga fadar haka yaja hannun my Baby ya tafi da ita, yana son bin su ya kasa, itama my Baby. Tirjiya take tare da mika mishi hannu, karshe ta juya ta gantsara mishi cizo, kawai ya sake ta, ta dawo gurin Allison da gudu.

Bude mata hannun yayi ta shige jikin shi, duk yadda yaso ya amsheta kin zuwa tayi tare da rungume Allison sosai, tana kuka.
A zahiran kuwa, shida Emily ce tana rungume a kirjin shi, sai cewa yake.
'Karka raba ni da ita, itace burina karka shiga tsakanin mu"

Kallon shi Emily tayi haushi yana kamata, bata san lokacin da ta kai mishi maka a cinya ba, tare da cewa.
"Dalla bude ido, ka kuma sake ni. Daga ranka ya b'aci kake shan giya. Ko waye ya b'ata maka rai Oho kazo kana shirmen mafarkai marasa dad'i."

Sake baki yayi yana kallon inda ta make shi. Tashi yayi ya zauna tare da kura mata ido. Kafin ya gyada mata kai.

"Fita kafin na fitar dake!"

Banza tayi dashi, ta zauna ganin yadda ya mik'e tsaye, tare da ɗaukar.. Wani igiyar cajin laptop din shi..da gudu ta fice mishi a daki, ya bita da Zungurerren harara, dan ji yaƙe kamar yana duniyar zungura ta dawo dashi. Musamman mafarkin My Baby.

***
Dutse..
Da safiyar yau Alhaji Ma'aruf, ya tashi da wani irin nutsuwa, sannan ya sanya aka fitar da kayan cikin gidan Aamil, ya tsaya da kanshi aka kwashe kome zuwa cikin shashin sa, ya sanya aka fasa cikin gidan, tare da gyara tsarin gidan.

Kudi ya zuba a kasa, tare da jin dadi a ranshi ya kuma yi imani idan ya gyara gidan ya

zamanantar dashi, Aamil zai sauko daga fushin da yake dashi. Duk wani nau'i na more rayuwa, sai da yaje Shagon Alhaji Abubakar ya sayo dan ya samu ya kawo wasu Jacuzzi masu kyau, dan haka ya sayi kala biyu.

D'aya fari kal, daya kuma ya barwa Sidrah Pink, duk wani abinda yake bukata na cikin gidan, ya sayo. Hatta paint din da za ayi a cikin gidan, duk ya zab'a musu, kasancewar yasan Aamil yana son combinet color, dan haka ya haɗa mishi da Black And Whiter.

Ita kuma Sidrah d'akin ta, yadda ya hada mata kome, sai ka zata yar tsana, haka ya kira me tsara daki, daga kano yazo ya tsara mata d'akinta. Da yadda zata iya rayuwarta babu damuwar kowa.

Kitchen ɗinta kuwa, wani irin tsara shi aka yi kamar yadda ake tsarewa babbar mace kitchen ɗinta, an shirya zuba mata kome. Yadda zata sake da rayuwarta babu kowa da zata takura..

A iya yanzun ya gama gajiya da girkin da ake na cikin gidan shi, badan kome ba, sai da. Zunzurutun ta'asar da ake mishi. Ana wani irin b'arna me mugun cin rai, buhun shinkafa da yake wata biyu, amma abun mamaki ko wata daya bata yi, last da yakare sati uku da kwanaki.

Yana son ya dakatar da girkin amma sabida gudun tashin hankali ya sanya shi zuba musu ido, yana kuma Addu'a Allah ya dawo mishi da Aamil, Ubangiji ya bude mishi hankalin shi da nutsuwar shi ya fahimci kuskuren da yake aikatawa, ya fahimci cutar dashi da ake.

Babban tashin hankalin shi , shine yadda suke niman karya dukiyar da yake tattalin arzikin Mahaifiyar shi, gashi ya tafi, yabar baya da kura. Tun yana musu magana, yanzun ya daina magana ya zuba musu ido, domin kwanaki da ya cika magana. Ido da ido Ali yace mishi. "Wato Abba idan da Aamil ne, ba zaka mishi magana ba, amma dake mune kake mana fada,

Duk da wahalar da muke sha, domin sanyawa dukiyar hannu ta bunkasa baka gani ba, shi kenan. Zamu bar maka dukiyar ku, sabida kar ya kare, tunda naku ne."

Ranar Alhaji Ma'aruf, sai da ya kwana zaune gashi ranar yana dakin Hajiya Surayyah ne, koda ya gaya mata abinda Ali yayi mishi budar bakin ta, tace..
"Ai yayi maka ma magana mai taushi domin bazai yiwu suna wahala baka gani ba, gwara su bar dukiyar kayi yadda kake bukata dashi."

Kuka ne bawan Allah nan bai yi ba, amma tabbas ya kwana cikin damuwa da b'acin rai, a duk lokacin da ya tuna abinda ya faru sai yaji kirjin shi yayi mishi zafi, washi gari dole ya tafi yaga likita, ya gaya mishi jinin shi yayi mugun hawa, dole suka bashi gado.

Faruwar haka ya kuma sanyawa suka kuma rub da ciki akan Dukiyar, gashi likita ya hana shi fita kasuwa, gashi idan yana gida baya samun nutsuwa, tashin hankali kwaraniya, hayaniyar mutane.

Dan haka ya koma dakin Hajiya Uwani,  domin d'akinta yana can karshen gidan ne, baka sanin me ake a cikin gidan, idan baka fita ba. Wannan abin ya kuma kara mishi tashin hankali, domin matan sun daina girki kowa sai ta girka daga ita sai y'ayanta, dalilin da ya janyo ake mishi.satar fitar hankali kenan.

Koda yaji sauki ya fara fita kasuwa Alhaji Ahmed ya same shi akan su fara shigowa da keke napep, cikin farin ciki su uku suka shiga da kudaden su, aka sayo napep daga India, kira biyu wato da TvS da kuma Qualia, dukkansu masu mabanbanta priza.

Abun mamaki da tashin hankali, kowani dan kasuwa yana burin ya sayar da kaya ya kuma sari, amma banda Alhaji Ma'aruf bai san haka ba, saboda koda yayi sarin, karshe keke napep din suna zaune saboda tsuga musu kudin da aka yi, tvS ana sayar dashi 770k sai kuma Qualia 700k, madadin haka sai karshe suka mai da TvS 970,  Qualia 900k, abin da ya hana kowa saya kenan.

Koda ya tambayi Alhaji Ahmed, ya gaya mishi zai tafi sari na uku kenan, nan ya gaya mishi ai tun satin farko bai koma ba, nan ya Alhaji Ahmed ya wakilci wani makocinshi ya je yaji yadda priza din keken yake, ya zo ya gaya musu. Abin ya kada. Alhaji Ma'aruf, cire hular shi yayi tare da safe kanshi.dama haka mutane suke.

Gyara zama Alhaji Abubakar yayi sannan yace mishi..
"Ina gani me zai hana kazo na kaika gurin Baffana a can Auyo. Insha Allah zai tsaya maka akan matsalar Aamil, babu musu suka nufi garin.

.......
Shiru Baba Malam, bayan ya gama jin bayanin Alhaji Ma'aruf, ranshi ya b'aci amma bai nuna musu haka ba,
"Wato duk abin da ya faru, kai ne mai laifi, duk abinda ya faru. Kai ka fara, baka ja shi a jiki ba, sannan ka dauko mishi abinda baya so ka bashi, taya zai iya rike musu ita, bayan tayi kankanta da fahimtar shi, amma tunda aure ne babu abinda baya faruwa.

Karka kuma irin abinda kayi Insha Allah zai dawo cikin nan da wani lokaci, karka kuskura ka ce zaka sanya mishi tashin hankali ka barshi da izinin Ubangiji zai kawo mishi dauki, kayi hakuri da halayyar shi, domin kai ne ka samar da kome,

Insha Allah kome na gab da zuwa karshe su kuma masu kama wasa da dukiya karka damu dasu Insha ALLAH zasu wayi gari dukiyar sai tafi karfin su.  Ka kuma Cigaba da hakuri kana hidima dasu."

Haka yayi ta musu nasiha, tare da bashi addu'o'in da zai cigaba dayi har Allah ya dawo mishi da Aamil. Sannan ya gaya mishi. Sannan ya saka ana mishi sadaka, domin ita kanta maganin masifa ce. Kuma haka ce ya kasance.

Bayan sun dawo ya saka aka fara abincin sadaka, ana kaiwa waje tare da almajirai. Haka ya cigaba da wannan aikin gidan Aamil yanzun haka an kusan kammalawa.

Kowa sai jin haushin abinda yayi yake, musamman Ali wanda yake ganin kamar son kai da wariya  Baban su yake musu, shi kuma a nashi bangaren yana yin haka ne domin idan Aamil ya dawo ya ga yadda ya tsara mishi ko ina, hankalin shi zai kwanta yayi Na'am da dukiyar Mahaifiyarshi.

Sabida yadda yake jin Yaron a a ranshi, hatta tsakar gidan intelock aka saka, cikin gidan kuwa an bishi da tiles, har jikin bango, kitchen din wajen ayi shi kamar na zamani, duk cikin gidajen babu inda yayi musu wannan gatar kamar na Aamil sannan ya kuma fitar mishi da dakin wanki ya saka a kawo mishi injin wanki.

Duk yadda ake bukatar gyara yayi mishi sabida bukatar shi yazo ya ga yadda zai fahimtar dashi ya tallafi dukiyar Mahaifiyarshi, kullum da wannan tunanin yake kwana yake tashi.

A cikin sati biyu da suka rage aka gama gyara kome dake akwai kudi na gwamna masu gidan rana, babu wanda zai ga gidan bai yi maganar shi ba, sannan ya fitar da tsarin kofar gidan biyu, akwai kofa daya ta wajen gidan, wanda yake hade da gareji, akwai kuma a cikin gida wanda Sidrah zata iya shigowa cikin gidan, sai dakin baki da aka yi shi a waje, sabida karsu sawa matar gidan ido, (🤔🤭 Irin su Oo, masu zuwa gashin amarya 😂🤣🙆🏾‍♂️ Jar ubancan Aamil da Sidrah, kwamacala..)

Duk yadda ake bukatar kome yayi karewa ma, har da Inverte Yasaka a gidan Aamil tare da solar shi, sabida yasan tunda ya dandana zaman kasar waje, zai yi wuya bai bukaci masuburbudar sanyi ba, dan rayuwar su da mu akwai banbanci.

Kuma duk wanda ya zauna acan sai ka ganshi baya son zafi....

Bai zama tilas na kai talatin  da biyar ba..🙏🏽
Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: https://my.w.tt/YIEwi83Nkbb

**RUWA BIYU**

***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***

HAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Ɗambu**

Bismillah Rahmani Raheem

A wise woman wishes to be no one’s enemy, a wise woman refuses to be anyone’s victim.

*Shin har yanzu kuna sayan data,airtime, TV subscription da biyan kudin wuta diga banki???*
Ya kamata ku dena *wadatar da bankuna kuxo ku sayi VTU portal a kudi kalilan (5k) sannan kudinga samun akalla 1k zuwa 20k a rana.
Mai buqatar karin bayani tayi min magana😃🤝🏽 ga masu bukata zasu iya tuntubar Mimiqueens ta wannan Number+2348036319148*
#Waye kai?
19

Cikin nutsuwa yake shiryawa, hankalin shi da nutsuwar shi yana ga shawarar da zuciyar shi ta bashi,kuma ya amshi shawarar hannu bibbiyu, domin yayi na'am da ita. Kara wayar shi yayi, cikin sanyi jiki ya ɗauka tare da sakawa a kunne. A hankali yace.

"Mom!"
"Allison! Naji ance an kama wannan mutumin! Shin da gaske ne?"
Ta tambaye shi a kage,
Ajiyar zuciya ya sauke sannan ya lumshe idanunshi kafin yace mata.
"Karya ne! Asalima nine na fita Zanga-zangar "

"Allison!!" Ta daka mishi tsawa,
A shagwaɓe yace.
"Mom! Kiyi hakuri ba zan kuma ba."
Yadda yake maganar sai jikinta yayi mugun sanyi, nan ta shiga mishi nasiha, tare da mishi faɗa kamar tana gaban shi, lumshe idanun shi yayi cikin damuwa sannan ya bude baki yace.
"Nagode Mom!"

Sannan ya kashe kiran, tare da fesar da iskan bakin shi, yana gyara neck tie din shi, yana gamawa ba, ya shiga saka links din hannun shi. Tare da makala agogon hannun shi. Daukar bluetooth speakers, ta manna a kunnen shi. Gyara gashin shi yayi tare da fesa turare.

A hankali ya saka cap toe Oxford shoe, wacce ta dace da suit din jikin shi, zama yayi a bakin gadon shi yana kallon closet d'inshi, cikin nutsuwa kafin ya mike daga zaunen ya nufi hanyar waje, a sanyayye yake sauka daga step din gidan, yana kuma kallon wayar hannun shi tare da tab'a bluetooth din kunnen shi.

Yana iso falon duk suka zuba mishi ido, kafin ya nufi hanyar waje, suka rufa mishi baya, idanun shi lumshe bayan ya zauna cikin motar yayinda zuciyarshi take tsananin Bugawa.

Yau bai duba paint work din shi ba, amma tabbas yana bukatar hakan, lumshashen idanun

shi ya kuma ware su akan fuskar Emily da bai san shigowar ta ba.

A ranshi yace..
"Wannan ba dai bakar naci ba,".

Kallon ina zaki yayi mata, take ta shiga hankalin ta, tace mishi.
"Zan.."
"Sauka!"
Babu musu ta sauka domin ta san halin shi tunda yace mata sauka, matukar bata dauka ba, zai iya fidda ita da kanshi ba tare da yaji ko dar ba, haka halin shi yaƙe bai cika so ana mishi shishigi ba.

Idan kuma zaka iya tafiya dashi babu kai babu gwatselewa, musamman ita yafi gwatsaleta, amma dake bata da zuciya, sam haka bai damunta, idan zai shekara yana ɓata mata rai toh ba zata tab'a nuna mishi ba.

Shi yasa wani lokaci, idan ya koro wulakancin shi, sai ta yi sati Uku bata leko gidan ba, sabida rashin mutuncin da yake mata, amma da kanshi zai je niman ta, idan kuma ya nimota ya shiga shareta, kamar ba shi yazo da kan shi ba.

Idan tayi zuciya zata bar gurin ya janyo ta jikin shi dan dole take zama, tunda shi dai idan yaso zai. Mata hira idan bai so ba kuwa, kirb'a mata wulakancin yake tana fara damun shi zai ce mata.
"Fita can kiyi surutunki, tunda ke hakan ba wani bakon abu bane a gurinki, ni kuma takurani yake."

Idanun tane suke cika da kwalla, ta rike hannun shi sannan tace mishi.
"Nasan watan wata rana zaka so na zauna da kai, nayi ta maka."

"Kinga dauko min abin sosai kunnen idan kin gama zaki iya tafiya."

Bata tab'a fushi ba, bawai dan bata da abun yi bane sai dai kuma tayi imani da cewa, dole wata rana zai so ta.

Da wannan take kuma shige mishi, amma bai hana shi buga mata rashin mutunci ba, kuma bata da zuciya.

Wani sirrittacen ajiyar zuciya ya sauke, wanda ya boye duk wani damuwar da yake tattarar dashi,

Cizon lip shi yayi cikin jin kewar wani abun da bai san dashi ba, amma tabbas yana missing wani moment, bai da wani abu da zai ce ya sashi nishadi but  yayi kewar wani abu me muhimmanci. Musamman My Baby wacce take kuka.

Amma cikin mafarkin shi ba ta, kuka.

Kiran shi aka yi yaga Number na Australia, sakawa yayi a kunne tare da cewa.
"Mom! Kina bukatar wani abu ne?"

"Son kana boye min wani abu, ina zaka da ka kore Emily daga motar ka?" Ta tambaye shi,

Shiru yayi cikin nutsuwa, kafin yace mata.
"Mom tun ban aure ta ba, ta fara kawo miki gulma na, lallai dole na rabu da ita, na fasa auren."

"Son baka da kirki, meye na fasa auren daga cewa zaka fita ka kore ta, shine abin gulma toh shi kenan, kayi abinda kake so amma batun fasa aure bai taso ba."

Aikuwa kamar wanda yake jiran tayi mishi magana ya kuma ririta alamarin, inda ya shiga botsare mata, tana taro shi tanan yana kaucewa ta can, karshe dai kashe wayar yayi, kusan yaran turawa kamar Yayan agwagi ne.
Suna gaba uwar na baya, wasu na bayanta.

Wasu na karkata hanya, zata bisu, na bayan na juyawa zata juya gare su. Haka yaran turawa suke, ba a musu fada musamman Allison da bai san fada ba a rayuwar shi, duk abinda yake bukata ya samu. Toh me ya rage mishi.

Kawai cikar burin shi ne ya fita yayi yawon duniya, tunda aka haife shi a U.S Bai taba barin kasar ba, karewa karatun shima anan yayi tun daga farkon har yanzun. Yana bukatar Fresh air,

So yake ya zaga kasashen duniya har da Afrika, domin ko kwana biyu da suka wuce wani abokin kasuwancin shi ya gaya mishi ana samun irin yarinyar da ya zana, a kasashen Afrika. Kama daga South africa, Central republic Africa, sai Kenya, Niger da kuma yankunar Nigeria, can yankin arewa maso yammacin kasar, musamman yankin da aka samu hausawa asalin original Hausa ba, mix Hausa Fulani ba.

Ya kuma gamsu da da bayanin mutumin, dan haka yake shirya wani project, da zai kai yammacin Afirka, ko Allah zai sanya ya tsinci wannan bakar zinariyar da ta samu damar ya zanata.

Matukar ya same ta, ba zai tab'a kasa a gwiwa ba, zai dauko ta cak ya kawo nan. Domin yayi alkawarin shirya mata duniyarta ita daya.

Murmushi ya sake kamar bai da wata damuwa burin shi kawai yake hangowa.
Kuma yana jin a ranshi zai cika, lumshe idanunshi yayi lokacin da suka tsaya a kofar Office din yan sanda, bude mishi motar aka yi, ya fito a sanyayye, yana kallon yadda ake gudanar da al'amuran yau da kullum, a hankali ya gyara zaman rigar shi, sannan ya saka kai suka shiga p.a

na biye da shi.

Har cikin office din, samun guri yayi cikin nutsuwa, ya tsaya bayan ya mikawa Babban supeto na Office din hannu, sun gaisa sannan ya isa gaban dakin da Aamil yake ciki, suna kallon shi ta glass.

"Ko zaku iya nuna min, wasu bayanai na na'urar daukar hoton garin nan da wasu madakatai?" Allison ya bukaci hakan,
Kallon shi dan sandan yayi sannan yace mishi.
"Yallabai wannan ba hurumin ka bane"
A fusace ya juya gare shi, tare da mishi kallon banza sannan ya gyara mishi kwalar rigarshi, yace mishi.
"Hurumina ne! Na binciki waye shi, me yasa da kuka yi ta kamo ni kun tab'a bincikar taya haka ke faruwa? Da saka hannunku ake ta b'ata min suna, idan na shigar da kara kotun dole a kwatar min hakkina, dan haka kayi abinda nace ko kuma nayi abinda zai dami kowa, kasan dokar shi yasa na nime muyi magana cikin doka.'"

Babu musu, suka wuce zuwa dakina da ake ajiye na'uran,a hankali ake bibiyar duk abinda ya faru, daga ranar da aka fara kama shi, zuwa ranar da aka kawo mishi hari, tabbas Aamil ne a cikin madaukar, sai dai shi yana taka sawun shi ne, fita yayi tare da sawa aka bude mishi kofar da Aamil yake ciki. Da mamaki a fuskar su suke kallon juna.

"Waye kai?"
Cikin tsannanin tsokana da zolaya Aamil yace mishi.
"Ni da kuma ni."

Cikin tsannanin b'acin rai, Allison ya cukume wuyar Aamil, tare da kai mishi naushi.
Dariya ya saka mishi tare da cewa.
"Kai WAYE kai?"
" Sake haushin sa yayi, tare da zaunar da shi da karfin tsiya,, mik'ewa Aamil yayi cikin fusata ya cikomo wuyar Allison, yana zare mishi idanu, Da sauri Yan sanda suka nufi dakin, Allison ya hana su, ya kuma rike hannun Aamil.
"Waye kai?"
"Ban sani ba!"
"Wannan zancen banza ne! Taya zaka yi kana aikata laifi ana tuhumata da su? Kasan yadda ka nemi lalata mana sunan Zuri'ar mu kuwa, sabida banzan fuskarka da take kama da nawa."

"Dalla sake ni! Banza mara amfani, wanda zuciyar shi bata da amfani kasan ni hatsari nawa na tsallake saboda banzan fuskar ka take kama da nawa."

"Ka gaya min waye kai? Zan saka a sake ka ka tafi kayi rayuwarka, amma idan baka fada ba, zaka mutu a banza."

"Kai ne kake tsoron mutuwa, tun daga ranar da aka haife ni nasan nazo duniya ne domin dalilai masu yawa, kai kuma lusarancin ka ya sanya ka kasa fita."

"Kai dan gidan Uban waye da zaka kirani da lusari? Uban waye ya gaya maka ni.."

"Dalla sake ni, idan ka kuma dukana zan baka mamaki." Cikin fushi sosai yace.
"Mamakin kaniyar ka, waye ya tsaya maka fadin garin nan. Sabida Shashanci ka, ka sanya waje tayi mini nisa, ina raye kamar matacce, ka san iya adadin bakin ciki da nayi, ga dukiya amma ya zame min mara amfani kazo kana ta kashe mutane tare da amfani da fuskana, banza kawai mara mutunci ka gaya min waye kai, idan ma turoka aka yi zan baka, miliyan dubu biyu, ka fita a rayuwata."

Murmushi Aamil yayi tare da ce mishi.
"Banza dama kana da miliyan dubu biyu
kake ihu, zauna mu fahimci juna, kasan a duniya ina martaba abubuwa guda biyu!

Abu me Kyau! Da kuma kuɗi, akan su zan iya kome, amma koda yake tunda ka iya saka, kayan dubu dari biyar da talatin na dallar Amurka tare da agogon miliyan daya, tare da takalmin dubu dari uku, ka hadu turaren miliyan saba'in wanda kampanin Omar Dubai, suka yi kaga ai ba wani abu bane!

Ni rayuwata bani da wasu buriruka, amma ina son kudi da abu me kyau, kuma zan yi tafiyata idan ka cika min aljuhuna da makudan kudade, na tafi nayi ta shagali."

Cike da takaici yake kallon Aamil yadda yake bashi labarin kaunar shi da kudi. Amma yana gamawa ya gaya mishi bakakken magana, suka kuma kaurewa da faɗa kamar zasu daki juna, karshe haka P.A yazo ya fidda Allison Aamil yana gaya mishi cewa.
"Banza dan daudu, daga ganin ka kai dan daudu ne, shi yasa kullum kake toshe a cikin gida. Baka da katabus, sai yadda akayi da kai.

Sha-sha-sha banza, lusari kawai, maza an sansu da kare kansu da dukiyar su, kai ka ajiye naka jarumtar ka boya a bayan babarka koda yake ai bata da laifi,kuma ka jawa mutanen da suke niman kashe ka kunne kar su kuma biyo ni domin zan ta karya mutane ne ina ajiye su a gurin, banza wawa."
.ya karshe maganar yana wani cizon lip din shi tare da nuna mishi hanyar fita.

Kasa hakuri Allison yayi. A fusace yayo kan Aamil, a bika da wanda bai san tashin hankali, koda yazo mangaje shi Aamil yayi yawani tafi can ya bugu da bango, Aamil ya kuma ɗaukar kujeran da yake cikin dakin zai buga mishi, kurawa juna ido suka yi lokaci guda zuciyar su na bugawa, wurga da kujeran yayi cikin b'acin rai ya nunawa Allison hanyar fita.

"Nasan na samun mutane masu kama da juna a duniya, kai Kuma ina da yakinin kana cikin mutanen da muke kama da juna. Don Allah kayi tafiyarka ka kuma daina lalata min suna, idan

da hali kabar kasa..."
.rike shi P.A yayi tare da janyo hannun shi suka fita, can suka gana magana, kafin suka dawo.

Nan ma, zama suka yi da Aamil, inda suka fara magana kamar abin Arziki, kafin minti goma sun kuma hargitsewa..

Ba lallai na kai 35 ba, idan nazo asalin inda ya dace toh zan gama free Pages..

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:06 PM] My Zahrah: **RUWA BIYU**
***<Ka sayi Daya ka sami daya Kyauta>***
https://my.w.tt/iR709OBtmbb
ℍAZAKA WRITER'S ASSO...

**Mai_Dambu**

Bismillah Rahmani Raheem

#last free page
🤔🤔 Mom Sayeed! Dake da masu goyan bayan Aamil ina mika muku taya murna! Kuma dole a zauna da yar baka mummuna😂😒
2️⃣1️⃣
Hadeja..

Iyayen yara kowa sai kokarinta ta fidda yarta kunya, banda Sidrah. Wacce gabaki daya wahala ya kuma mai da ita baya, kana ganinta kaga wacce take ƙoƙarin kare lafiyar ta, kasancewar wasu irin kuraje sun kuma fesowa a jikin ta, ga shi har bakinta da matse matsinta, idan dare yayi bata barci, sosai ya taba mata, idanunta gashi ya hadu da hayaki. Idan tana jin barci idanunta yayi ta zubda kwalla tare da yaji da raɗaɗi.

Kasa barci take, sabida duk jikinta,yayi ta ciwo kenan. Sai goshinta, asuba barci yake daukarta gari na waye. Lantana zata watsa mata ruwan sanyi..haka zata mike jikinta na rawa zata tashi. Shi yasa take ta karewa sabida babu ishashen lafiya.

Dake bikin yazo dab yasanya Lantana fara taimaka mata da gyaran wanke kafarta sabida fason da suka kama kafar, sai ta shiga daura mata lalle, sabida gab kwanakin idan ta taka kafar har kuka take, sabida shiga ruwa da aikin wahala.

Dan kar ace ta nakasa rayuwar yarinyar, shine ya fara kunsa mata lalle, amma a haka bai hanata fahimta tana fama da ciwon kafar ba, sabida bata tafiya normal. Zayi wuya kaga kuka

akan fuskar yarinyar idan tana wahala, amma da zaran ta fama ciwon. Tayi ta shashekan kuka.

Bangaren hannunta kuwa, cin ruwa ne suka tsaga tsakanin yatsunta, farcen hannunta kuwa fita suke da karfin tsiya, sabida sanyin da ya shiga jikinta, shi ya haifar mata da rashin girman jiki.

Kuma babu wanda ya damu da yasan halin da take ciki.
Burin su ayi a kai kowacce gidan mijinta, a huta, wannan yanayin yana daga cikin abu mafi muhimmanci da Lantana da sauran matan gidan suka dauka na bikin Yaran su, Takiya itama sun b'arar da cikin, dan haka ana gayawa babanta cikin ya zube yace musu toh ko babu kayan daki ta nufi hanyar gidan Lawali..

Dangin Maman Sidrah, sun mata kayan aiki da wasu abubuwan da ake bukata, sabida kare mutuncin Yarinyar, amma lokacin da suka zo suka ganta, sai da jikin su yayi sanyi, dan haka suka ce zasu dauke ta, a gyarata na kwana biyu, Lantana tayi tsalle ta dire, tana fadin.
"Babu inda zata tafi, ai wannan lokacin tsautsayi yana fadawa amare dan haka a barta ta zauna a cikin gidan nan a gama kome, tunda kunyi naku kokarin sai."

Ganin zata rena musu hankalin Sabuwa ta dauki Yarinyar da wata Yayar Maman Sidrah me suna, Indoh suka nufi asibiti da ita, a yadda likita ke musu bayani sai da suka zubda kwalla, na banza. Haka ya rubuta musu magani tare da musu bayanin yadda zata yi amfani dashi.

Basu maida ita gida ba,suka riketa, tare da fara duba ta yadda za ayi mata jinyar kanta kafin ranar bikin. Musamman gashin kanshi, sabida kurajen da yayi tare da kuma kwarkwata, ga ciwon sanyin da suka feso mata.

Dan haka suka fesa mata piya piya, tare da bata maganin zazzaɓi, washi gari suka wanke kan, tare da bata magani da ruwan dumi tasha. Kafarta kuwa babu yadda suka iya da ita, amma tabbas yarinyar akwai jinya a jikinta kamar yadda likita ya faɗa musu.

Shi yasa suka yi iya nasu tare da bata maganin ciwon har ta fara murmurewa, sai da tayi kwana goma wanda yayi dai dai da saura kwana hudu kacal, a daura auren. Sanan suka mai da ita, gidan. Bayan an hada mata sabulun wanka na maganin ciwon ta.

Zunzurutun bakin ciki da hassada, Lantana tana ganin kayan maganin ta kwashe tare da bawa Sahiyah wacce ta dawo shekaranjiya, dan haka Sidrah ta zuba musu ido, yarinyar bata da cikakkun lokacin magana, dan haka duk abinda zasu mata, nata dasu Idanu wanda ya ishe uban kowa.

.... Washi gari aka kira su, zuwa cikin gidan, inda mazan gidan suka sanya su a gaba da nasiha ko nace fada, akan bin miji. Har suka gama basu ce musu tambaye su farillan alola guda nawa ne ba, kawai sun ce musu miji ba a mishi rashin kunya,kuma ba a mishi rashin mutunci.

Duk abinda yace kayi kawai kayi, is a oda ba ayiwa miji gardama, duk abinda yace ya faɗa dai

dai,kuma ba kwashe sirrin miji, suka yi point din Sidrah, suka ce mata.
"Gashi dai kace karama, amma duk lokacin da dangin Mahaifiyar ki, suka dauke ki, sai sun kawo korafi akan an miki kaza anyi kaza.

Toh gidan da zaki warki ne dai dai da k'ugunki, idan zaki shirya ki shirya, idan kuma kika ga ba zaki iya ba ki dawo mana, toh zawarci zaki yi dan babu wnda zai iya da rigimar Hajiya da Hindatu, tunda suka kori baturiya da arzikinta, babu wacce zasu bari. Dan haka ke mareniya ce,baki da kowa sai Allah sai kuma mu da zamu iya tabuka miki wani abu, ki zauna. Gidan ki, lafiya dan naji wai mijin naki ma zai dawo nan da ba da ajimawa ba...."

Nuna Sahiyah da Takiya yayi tare da Zubaina, yace musu.
"Toh tunda ku dama kun jangwalo mana abin kunya, sai ku yi hakuri, sannan duk wanda ya ci mutuncin ku, ku gaya mana sai inda karfin mu ya kare, banda rashin kunya, ku zauna lafiya zamu kai ku da kayan aiki. Ke kan Sidrah Uban mijinki babu abinda bai ajiye miki ba.

Sannan a kula da kyau banda yawo, ban da shiga makota, sannan ku zauna lafiya da kowa kema Sidrah gidan ku akwai yan uwan mijinki da matan su, dan haka karki rena kowaccen su, ban da gardama, anan kece kike kome karki ga an barki kice zaki mike kiyi barci, kina shiga cikin gidan kina taya su aiki. Ku kuma banda shiga abinda babu ruwanku, kar naji wata yarinya ta shiga harkokin kowa, ta zauna iya inda take! Toh Sidrah anan dai baki sata, kuma baki daukar abinda ba naki ba, dan haka ki nutsu karki ga kome kamar banza kice zaki tsiro da halin banza anan kan ba zamu shirya ba kuma ba zamu goyi bayan karya ba, idan kika sake muka kamaki da wani laifin daukar ko sata, toh karki shigo mana gidan nan, domin ba zamu lamunta ba, kuma ba zamu dauka ba. Dan haka ki nutsu ki zauna lafiya babu ruwan ki da kayan wani. Da fatan babu wani damuwa."

Gyada kai suka yi, duk cikin fadar nan babu abinda Sidrah bata dauka ba, dan gani take kamar fadar Allah ne suke gaya mata, shi yasa take kuka. Tun ba ayi auren ba, wani irin girma ya shige ta, kadaice da kewar iyayenta sun shigeta.

Damuwa da wahala, sun saka ta zama mai yawan tsentseni da duk abinda za a fada mata, yanzun haka fadar da aka musu gani take kamar an ce mata, idan bata bi abinda ake ce mata ba, ta tabbata yar wuta, shi yasa take kuka da zubda kwalla, sauran kuwa wani rawan kai ne yau ana musu fadar aure.

Daga nan aka tura su gurin matan gidan, inda suka musu fada, idan suka tawo kan Sidrah sai su ce mata.
"Toh Uwar muni! Ke ai ana kai ki zaki dawo, sabida babu namijin da zai zauna da bakar Mace munmuna."

Haka kowani shashin da abinda suke gaya mata, da dare aka kawo Kayan kallo daga Kano, tare freeze, sai kayan gara, da ake na alada, daga yan uwan maman Sidrah, haka abin yayi ta tsuma Yan gidan kowa sai yazo ya duba, ya tab'e baki sabida zunzurutun kishi da bakin cikin da

yake cin ransu.

. The next day, aka kawo dubulam, cin-cin da tawaita, tsatsafa, gireba. Kayan abinci tare da kayan da za a rabawa dangin miji, na gara. Wannan abu ya tsone musu ido. Ya hana kowa sukuni, domin duk wanda ya shigo gidan sai an gaya mishi ga kayan da dangin Yar gwal suka mata.

.... Irin izgilanci nan da akewa mutum, haka suka yi ta mata, ana cewa.
"Yanzun yar wannan abun ce zata dauki namiji? Ina nonon ma? Balle inda zai dauki nauyin wani gardeden kato, lallai akwai aiki bari mu gani ko daga ranar da aka kai ta, za a kira ku kuje gashin ango ya farketa."

... Dariya Lantana take, tana fadin.
"Ai kuwa maji magani an binne tsohuwa da ranta, gidan Alhaji ai ba na zaman mutanen irinta bane, idan ta samu ma ta zauna toh tabbas zata ci kwal ubanta, domin Hindatu muma bamu wanye lafiya da ita ba, kuma suma matan gidan juya su take kamar dan bujenta.

Wannan idanun masu kama da na Mayun sai sun kote sunyi fari zasu gane yadda duniya take ciki.

Wallahi har na kagu ayi auren ma, na huta domin nasan watan cin banten Ubanta ya kama, ba sunce ni zan kashe ta ba, zata je inda za a kasheta da hujja, maza kiyi kokarin ganin cewa baki shiga gidan ba, domin kuwa na lahira sai yafi ki jin dadi, domin da ranki zaki yi fatar mutuwa ta dauke ki, yar banza me baki kamar zunubin."

Ire-iren waɗannan zagin bai tab'a sanyata jin haushin su ba, asalima suna abun ne, amma tana musu kallon kanku ake ji, dan bata amsa musu, a yadda suke kallonta bata magana, cewa suke ai sabida bakin munafunci yasa ta daina magana, wanda ita kuma hakan kamar ya koma yanayinta ne, irin lifrstyle ɗinta kenan idan zaka shekara kana mata bazata kalle ka ba, da ta kulaka gwara ta shige daki tayi kwanciyarta ko tayi ta sosa kanta.
***Yau kimanin sati biyu kenan, a Office din yan sanda, duk wani abinda za ayi anyi mishi, tare da saka hannun Jakadar najeriya na amurka, suka sake shi sannan aka kuma dauke shi zuwa gidan shi inda ya kwashi kayan shi domin jami'ar da yake karatu sun sallame shi, Sakamakon samun shi da akayi yana da hannu da tadda tarzomar zanga zangar da akayi sati biyu da suka wuce.

Bayan ya kwashe komin shi, ya shiga motar da aka kawo shi, ba a tsaya a ko ina ba, sai A Mansion na Mss William. Tunda daga shigar shi yaga yadda aka shirya duniya da tsinketa, take ya fara hangowa kanshi yadda yake zuba mulki da rashin adalci, yayi ta hawa Biken, yana zaga gari.

Amma Tabbas Allison mugun ɗan daudu ne, yanzun da wannan duniyar yake rayuwa bai ci uban yan iskan da suke d'aga mishi kai ba, ai da shine tuni ya ci uban kowa ya kwana lafiya,

shegen gora. A ranshi yana faɗin.
"Dan iska da Allah zai bani damar damawa dan Ubanka da na dama na kuma fantsama a cikin U.S, ya zamana ni ne kaɗai mutane suke ambata, na shiga na fita na murkushe yan iska da yan sa'ido. Na ci Uwar yan bakin ciki tare da toshe yan banza."

Da wannan ya shiga cikin gidan, tare da tozali da shirgegen hoton Mss William, tsira mata ido yayi cikin jin wani irin yanayi yana ratsa ranshi da ruhin shi. Kaunarta. Kamar wanda aka cire mishi hakan ya juya inda yaji takun Allison. ya kura mishi ido.

"Dan kauye kaga kayan Arziki hankalin ka ya tashi, nime guri ka zauna.". Murmushi Aamil yayi sannan yace mishi.
"Toh katon lusari, dan daudu. Nagode daga nan ma ya ishe ni.".

Sanin cewa idan ya kula shi ba zasu rabu lafiya ba, nan kuma cikin gidan shi ne, ya saka shi share shi sannan ya gabatar mishi da abinci.

"Sallah zan yi, bani da lokacin abincin ku da kuka jibga mishi shirme."

Nuna mishi dakin da yake zane yayi, zanen da ya dauke shi daga sama. A hankali ya tura kofar yaga yadda aka shirya dakin iya haduwa ya hadu, alola yayi sannan ya gabatar da sallar kafin ya fito daga cikin daki,

Bayan ya gama cin abincin wanda mafi akasarin shi, namar ruwa ne, sannan ya tura mishi a kwatin kuɗi, sannan ya mike ya da cewa.
"Ban san kai waye ba, amma tabbas nasan kana da naka labarin gashi zamu rabu da juna bamu san kome akan juna ba.

Zan so wata rana muyi magana kota internet ne, gashi wannan shine Number, muje na rakaka airport."

A hankali suka jera suna kuma jin wani irin karsashi a tare da juban su kamar karsu rabu, har suka shiga motar, kallon shi Aamil yayi, sannan yace mishi.

"Naji kabarinka, kai ne baka san nawa ba, amma ni labarina ba wani abun burgewa bane, amma nasan na baro wasu rikitattun mutane masu mugun son kansu, bayan sunyi yunkurin hada ni da wata irin yarinyar wacce bata da banbanci da mugun abu..."

A hankali yake gaya mishi irin girman rashin mutuncin da aka yi mishi shima ya bar musu, gidan, amma bai yi masarar gaya mishi waye shi ba.

Har suka isa airport, kamar bazasu rabu da juna ba, haka suka yi sallama, Allison ya rike hannun Aamil yace mishi.
"Kayi ƙoƙarin ka zama mutumin kirki, ka kuma bi abinda mahaifinka yace,"

"Nayi maka alkawarin haka, amma kai ma ya zama maka dole ka tashi ka kare dukiyar Mom da lafiyarta, domin kuwa akwai manyan mutane da suke son ganin bayanta, ka fita ka zama jan wuya da ni ne, tuni na gyarawa kowa zama,,"

Murmushi suka yi sannan Allison yace mishi.
"Duk da mun kasance masu kama da juna,, ba zai tab'a yiwa halayyar mu yayi daya ba, dole a sami banbanci. Ina da buri? Kai ma kana da shi, gashi kuma haka zamu hakura da samun wanda yake gaban mu."

Sake rungume juya suka yi sannan Aamil ya juya fuskar shi dauke da murmushi me cike da tsantsar rashin wani abu na shi, haka ma Allison ya juya tare da jin kewar mahaifiyar shi, da kuma na Aamil, har yayi nisa suka kuma juyawa, tare da d'agawa juna hannu, haka ce ta kuma faruwa kamar basu son rabuwa da juna, har suka daina ganin juna. Yana tsaye a gurin har jirgin Aamil ya tashi, sannan ya bar tashar jirgin....

🤔🤭
Toh anan na kawo karshen free Pages. Domin ai na gaya muku.
Allison da Aamil kowanne su yana da buri! Kuma suna fatar cikar burin Nasu... Ga kuma Aamil zai komo ya samu auren da ya tserewa.. Ga burin Allison na nimo My Baby, ga matsalolin cikin gidan su, ga kuma matsalar mutanen da suke son ganin Bayan Allison da Mahaifiyar shi, Taya labarin zai amsa sunan shi, ga kuma. Shin Aamil zai amshi Sidrah, Taya zamu fidda asalin sunan Labarin... Wasa farin girki! Ko?

Wannan book din na kuɗi ne akan 300₦ haka ma katin mtn 300₦
0472282105 Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK, zaku iya tura shaidan ku ga Zahrah +2347035133148. Yan Nijar su sami Nana Aicha+22784506476
#Mai_Dambu.
[11/13, 8:15 AM] Anum Muhammad Bello❤️: I crush...
BIYU da kari.. Yanzun labari zai koma bakin jaruma...
Shiri sosai ake yadda kasan bikin dan gwamna za ayi, sannan idan ka ga yadda ake hidima zaka rantse da Allah, Alhaji Ma'aruf bai san darajar kudin shi

Yau tunda ya tafi masallaci, Addu'o'in kawai yake, ga jin shi da yake sukuni ya same shi, shi kanshi ba zai iya cewa ga ranar da yayi farin ciki haka ba, tun ranar da ya auri Hauwa, amma yau ya tsinci kanshi da farin ciki, kodan bikin Aamil da ake yi ne oho. Ko yazo ko kar yazo babu makawa za ayi shi. Shi yasa yake ta niman zab'in Allah akan bikin.

..... Ana ta gulmar yadda ake shirin bikin, musamman Hafsah da Raliya, sai habbaratu, tare da Ya Hindatu, da Amarya suna kallon yadda ake shiga da fita, idan suka tuna amaryan yarinya ce sosai sai su ji, basu da wata damuwa, musamman Ummita. Domin har Addu'a take Ubangiji Yasaka Sidrah ba mai magana bace yadda zata idda manufarta akan ta..

...
Hadeja..
A yadda nake kallon su, kawai ina bin su ne da toh, amma har abada bana jin zan iya rabuwa da auren ba, a haka ma ban san shi ba, kawai auren ake shirin zarga min. Idan na tuna ban iya kome ba, babu sallah babu karatun Addini, sai naji na muzanta. Nasha zama ina niman meye laifin Marainiya irina?

Shin ban cancanci a tausaya min bane? Ko dan yadda Ubangiji yayi Ni, ya saka ake guduna, idan na tuna da haka zai naji ina ma da mutuwa zata iya daukata, tabbas da nayi farin ciki har karshen rayuwata, amma ina kawai dai ina raye ne amma dai dai nake da matacciya, gyara zaman buleliyar rigar jikina nayi, ilahirin jikina ciwo yake min. Ina son na kwanta na huta, amma babu hali. Jin ana shirin tashi a labaran gidan rediyon ya sani yin maza na mike tare da nufar ban daki nayi nayi fitsari, tare da yin alola na fito.

A hankali na fara gabatar da sallar, bawai na san kome akai bane amma ina jin zan sami nutsawa. A hankali na fita tare da niman daki na Kwanta. Kafin na tashi na fara gabatar da Sallar isha, sannan na koma na kwanta a saman tsimokarar mu. Ina barci dake a gajiye nake, asuba nayi aka tashe mu, zuwa gidan makota, tunda muka nufi can kowa yaci abinci, ban dani da nake jin kamar cikina zai hade da baya,. Sai can rana aka dauko me saka kida anayi.

.... Tun karfe biyu na rana mutumin yake kida, gashi yau duk zasu sakamu a lalle, dan haka muka nutsu gashi kaina baya tabuwa domin har wani wari yake yi, a hankali nake gyara zamab wani kodaddiyar zanin jikina,sannan tashi nayi zan fita daga cikin taron, ina sauri na nufi hanyar cikin gidan nan.
.. "ina zaki? Kowa na farin amma ke zaki shiga cikin gidan me zaki yi a cikin gidan?" Inji wata mata da tazo gurin..

Murmushi nayi mata sannan nace mata.
"Zan shiga ban daki be, amma ba zan jima ba." Gyada min kai tayi, sannan na bar gurinta, bayan na nufi cikin gidan, Toh yunwa nake ji, ban ci komai ba, haka na shiga ciki na samu hankalin su yana wani gurin sun bar abincin a ko ina na dibi abincin da sosai, sannan na bar musu gurin. Naje naci abincin baya jin dad'in kome domin ina cin abincin wuya na yana wani irin shake ni.

.. bayan na gama cin ne na sha ruwa sannan na fito daga cikin gidan, wajen da babu hayaniyar mutane naje na zauna ina kallon yadda suke rawan sago, suna ta budiri amma ban da ni, sam bana son damuwa domin idan na zauna a kusa dasu korata suke, shi yasa na zabi zaman nan da akan na zuwa na a cikin su.

Ji nayi an zauna kusa dani, dake naji kamshin turaren da Sahiyah ta saka ba d'ago kai Saratu ce. Murmushi tayi min, na dan matsa kadan daga kusada ita, sake matsowa tayi na matsa, zata kuma nace mata.
"Don Allah wari nake, ki bar ni haka, ba sai kin zauna a jikina ba,"

Kura min ido tayi kwalla suka fara cikawa, kauda kaina mai tare da gyara zamana, ina kallon wani gurin.. "wato Ubangiji shi ya fimu sanin dalilin da ya haɗa ki aure da wancan mutumin."
Juya idanuna nayi akanta, kafin nace mata.
" Mutane marasa amfani a cikin al'umma ake zabawa takardan mutuwa, mutumin da yace sai yayi Gunduwa Gunduwa dani zan dauki auren shi da wata manufa."

..... "Ke raba ni da shirme, irin su ne kina shiga nan da wata shekara sai dai muje suna." Da sauri na toshe mata baki, ina zaro idanu, tare da waigawa ko wani yaji mu, kasa nayi da muryana kamar me rad'a nace mata.
shine mafi alkhairi ba, fatar Abba ya dawo ya rike dukiyar su, Tabbas Addu'a bata faduwa kasa banza, da Allah ya tashi sai ya kawo musu Allison, kuma ya zo lokaci ƙalilan ya maida dukiyar kamar Yadda take da! Babu wanda yayiwa Aamil baki 🤣 Shaidanci ne, da rashin soyayyar Iyaye, suma fushi yake dasu, Amma da zai fada wata jarabawar rayuwa wallahi sai yafi kowa tsoron Allah, dan haka karki damu kanku, Insha ALLAH shirya tana tare da wanda yayi Imani da Allah.... 🤣🤭 Wai bana son Aamil! So kuma ganin su Aamil shine Jarumin no.They were born of one! But their destiny is the same! While it makes their world different! Bad and good!_

Aamil and Allison

Story of identical twins

Wani irin kallo muka bishi da shi, cak Allison ya tsaya tare da dafe kofar fita gidan. Cikin wani irin kaduwa na zube akan gwiwata, lokaci guda zazzaɓi ya rufe ni, kasa kuka, hawayen ma ya tsaya cak. A hankali Baba ya taso yazo gaba na.

"Tashi muje, Allah zai isa miki, hakkin ki sai Ubangiji ya saka miki! Ki amshi haka a kaddarar ki!" A hankali na mike tsaye na zo zan wuce Aamil ya sha gabana.

"Baby Love! Dube ni nine ba Aamil bane." Abin mamaki lokaci guda, Aamil ya kuma rudar da hankalin mutane, Allison yana son magana, amma

Sabida firgicin da yayi,lallai Aamil tantirin mara mutunci ne, wasu tagwayen kwalla ne suka shiga tare a fuskar mu, ni dashi lokaci guda ya kasa ya tsare ya juyar da hankalin kawo.

Cikin zuciya da fushi Allison ya ture shi tare da gargad'in shi, da hannu.

Duk rashin imanin mutum idan yaga yadda Allison yake bina sai ya zubda hawayen, zunzurutun tausayi, ya kasa cewa kome sai bina yaƙe, shi kan shi Baba Haliru daurewa yake domin yaga tsagwaron tashin hankali, koda na shiga d'akina biyo ni yayi ganin ina kwasar kayana. Hawaye na zuba min daga Idanuna.

"Na san na ci amanar ki, amma wallahi ban tab'a kawowa kece zaki zo min da sauki haka ba, Sidrah kece mafarkina. Tun daga ranar da na ganki na fahimci kece nake zanawa! Don Allah ki tsaya ina sonki."

"Ka yaudare ni, dan uwanka ya ci mutuncina, sabida ni marainiya ce, bani da yancin bani da wanda zai karb'a min hakkina, Allison."

Rufe min bakina yayi da hannun,
"Ina sonki!"
Murmushi nayi tare da hada kayana, sannan dauki jakar zan fita ya fisgoni.
"Me yasa ba zaki gane zuciyar mu daya ce?"

"Me yasa? Meye nayi maka a duniyar nan? Me na tsare maka?  Amsarka babu! Amma kiyi hakuri! Kasan baka da aurena kayi ta koya min sonka? Simple and easy , wancan lokaci sai aka gaya min kai ba musulmi bane?"

...  A hankali na tako gaban shi, na tsaya ina kallon shi, kafin nace mishi.
"You no how u broke my heart! Ba ka sani ba, Little girl like me, i fell in love da bad man irin, ba kana sona ba?"

Na tambaye shi, cikin sauri kamar yaro karami ya shiga girgiza min kanshi.
"Sosai kuwa?"
Gyada kai yayi cikin ban tausayi, tabbas Aamil yayi gaskiya da yace mishi lusari. Amma kai na ne yake haka, zai iya daukar kome amma banda rasa ni, a sanyayye na kauda fuskana,
"Zaka iya min kome idan na roke ka?"

"Sidrah babu abinda zaki sani na kasa yi!" Murmushi nayi sannan na juya bayana, ina shashekar kuka, nace.
"Don Allah! Dan darajar shi kar ka kuma tunani, ka rabu dani."

Juyar dani yayi yana kallon fuskana. Nima shi nake kallo, zunzurutun tashin hankali ya ksa boyewa.
"Bazan iya ba"
"Kenan dama ba sona kake ba? Jikina kake sha'awa shi yasa kayi ƙoƙarin raping dina a dub...."

"Shi kenan, na yarda na amince. Amma ki yarda ina sonki." Daga haka ya dauki kayana, ya fitar min dashi waje,. Inda Baba yake jirana. Jin hannun shi nayi yana lallubar nawa, na d'ago kai ina kallon shi.
"Keep me in your heart, a will be with you!"

Sunkuyar da kai nayi, ina kuma share kwalla.
Muna tsaye Aamil yazo ya ture shi, sai da ya fadi. Sannan yazo zai min magana, Baba yaja hannuna muka bar gidan baki daya. Har mun fita bakin get, naji bazan iya tafiya ba, amma babu yadda na iya, juyawa nayi naga ya biyo ni, zare hannuna nayi. Na juya da gudu, tun kafin na karasa, Aamil ya shiga tsakanin mu.  Ture shi nayi tare da isa gurin shi.
Ina haki, a hankali na zare zoben shi na mika mishi, sannan na barshi rike da zoben, niman abun hawa Baba yayi, muna shiga ya iso.
"Ke ce kika ce idan ina sonki ba rabu dake, kuma nayi haka. Toh meye na raba tsakanin mu?"

"Sabida ba zai yiwu nayi rayuwa da maza biyu ba, idan kai baka fusata ba wata rana shi zai fusata, balle bana fatar sake shimfida wani abu a rayuwarka, thank You."

Ajiye min zoben yayi, ya juya bai kuma, wai-waiye na ba, haka muka bar garin na shanye kuka na, sai dai nayi mamaki da Baba Haliru ya wuce dani kano.

A tunda muka isa ya nufi inda ake lodin Kwara, nan ya kai ni. Ina zaune ya biya kome, sannan yace min.
"Kiyi hakuri! Gashi nan ki isa lafiya, ki rike wannan ko zaki ci abinci a can dan nasan tayu sai gobe ku isa, sannan kuma baki da waya, toh Allah ya tsare. Zan kira layin driven, sannan na bashi Number yayanku, shi zai zo daukar ki Insha Allah. Kiyi hakuri ki bar min kome a hannuna, daga yau ba zan kuma barinki kiyi kuka ba, Insha Allah."

"Toh Baba!" Nace mishi.
Bayan ya gama min kome ya juya shima ya bar kano, tare da alwashin sai ya hukunta duk wanda yake da saka hannun b'ata min rayuwa, mai dani bazawara a 15yrs ko tausayina basu ji ba, daga rufawa juna asiri."

..... Sai karfe sha biyu na rana muka bar Kano, a hankali muke tafiya kasancewar driven tsohon drive ne, gashi ya iya tuki cikin nutsuwa, muna tafiya yana bamu labarin irin gwagwarmayar da suka yi a hanyoyin lanjeriya.

Har muka bar kano, muka nufi Kaduna, inda muna biyo ta kafanchan, sannan muka mike nasarawa. Karfe goma na dare muka iso suleja, anan muka sauke salollin kan mu, na kasa cin kome. Idan na zauna sai naji kuka yana son kwace min, awa daya muka mike, inda muka dauki hanyar.

Tafiyar da ta dauke mu, har kogi state, karfe biyar na asuba, anan muka yi sallar asuba. Sannan muka kuma dauki hanyar kwara, karfe shida na safe. Karfe sha biyu dai dai muka sauka a garin ilorin. Muna isowa tasha, driven na kiran Ya Atiku.

Ina zaune har ya iso, yana gani na, ya karaso cikin damuwa. Ya riko hannuna, tare da cewa.
"Sidrah!"
Kasa nayi da kaina, riko hannun na yayi tare da ɗaukar kayana, muka bar tashan bayan munyiwa driven godiya, muka nufi police barrack na ilorin. A motar oganshi ya tawo ɗauka ta. Tun da na shiga motar nake kuka, sosai na kasa magana, fushi sosai Ya Atiku ya ɗauka, tare da cewa.
"Ki bar asarar kwallarki, Insha Allah sai na rama miki wulakancin da yayi miki."

Share kwalla nayi sannan nace mishi.
"Da kabar shi da Allah, duk rama min da zaka yi, bai kai wanda Ubangiji zai mishi ba. Kawai ka hakura kamar yadda na hakura."

Duk sai ya ji babu dad'i, cikin tausayawa min muka nufi gidan shi dake cikin barrack din, har cikin gidan yayi min jagora, ban san Saratu tana nan ba, aikuwa da wani irin ihu ta rungume ni, muka zube a falon gidan,na gaida gaida matar shi, Sannan na zauna, na sunkuyar da kaina ƙasa, ina wasa da zoben shi. Dan koda ya dawo min da shi, ban iya ajiye shi a ko ina ba, sai a

hannuna. Ina jin b'acin rai, amma babu yadda na iya, abincin suka kawo min, na kasa ci sai da nayi Wanka, sannan na zauna kasa cin abincin nayi na koma kwanta. Ina jin babu dadi a kasan raina. Sai dai haka ba zai sani barin Allison a raina ba, domin ya cuce ni. Idan na kuma duba wani wurin, sai na ga shima ba laifin shi bane, haka nayi ta sakawa ina warwarewa...

Dutse..
Tunda ya shiga gidan, bai kuma samun damar ya leka wani ba, rufe kan shi yayi, sabida bakin ciki.

....
"Idan kai ne Allison shi wancan din fa waye."
Cikin tashin hankali ya karya wuya tare da cewa.
"Shine Aamil Mom!".yadda ya rena musu hankali abin ya dame su, karshe ya tashi ya fita, inda yaje ya jiwa kanshi ciwo, tare da komawa kamar da gaske yazo ya zube a gefen Mom, yana share kwalla. Rike kanshi tayi sannan tace mishi.
"Allison nayi maka alkawarin nima maka Sidrah, amma kuma me yasa?"

D'ago kai yayi tare da zuba mata ido, har zuwa lokacin mutanen gidan suna tsaye, kafin ta mike tana faɗin.
"Zomu bar gidan nan, duk abinda ya sami d'an uwan ka, sone silah. Sune suka lalata rayuwarmu da ta mahaifin ku, suka kwace min Alben, ko nono bai sha ba, suka min barazana zasu kashe ni. Wadannan mutanen mugaye ne, sun cutar da rayuwar mu. Dan haka ka kira min Alben mu tafi dashi."

Haka ya gama yawon shi, sannan yazo ya rike hannunta, cikin damuwa, yace mata.
"Mom!"
"Babu inda zaki! Ana zaki zauna, babu inda zaki, ni yadace nayi magana ban yi ba, sabida rashin hankali irin naki, kin tafi ba tare da dan jariri ba, nasan nai miki laifi. Amma meye laifin jaririn?"

"Ka bar min ihu, domin kuwa mahaifiyar ka da Yayar ka, tare da yarinyar da zaka aura lokacin zaka tambaya bani ba, kai muje."

"Hauwa ranki zai b'aci."
"Sai dai namu ya b'aci dan ba zan zauna da kai ba, su karasa kashe mu da Yayana ba,"

"Toh kuwa naga wanda ya isa ya biki tsakanin Aamil da Aalim din!"
Cikin masifa tace mishi..
"Kana nufin Allison shine Aalim? Toh ba zan yarda ba, sai na tafi da Yarana."

"Kai zo nan"
A hankali Aamil ya isa ga Abban shi, ya zauna kusa dashi cikin fada yace mata.
"Da na aure ki, ke daya kika zo ba da wani yaron ba, ina bukatar yarana zaki iya tafiya babu

abinda ya dame Ni, tunda kin zama zuma sai da madaci."

Haka ya bata haushi, har Ya Hindatu ta fito zata mata rashin mutunci, ta kwad'a mata mari, sai da ta zauna, kawai kamar wacce aka bude tap.sai ga fitsari.

Take kowa ya shiga hankalin shi, take Ummi tace a ranta.
"Jagalinyanci Aamil gado ce, domin ga abinda Mamarshi tayi "

Nan Aamil Yasaka baki ta amince zata zauna amma a shashin shi.

Kafin kace me a cikin awowi Aamil ya tabbatar musu shine Allison, suma iyayen sun yarda da hakan,

.---
Ya fita hayacin sa, kuma bai nemi kowa ba, dan haka ya tattara kome na shi, ya bar cikin gidan. Ya koma wani shashi da Abban shi, baya amfani da shi. Ya zauna baya shiga cikin gidan, dayawa ma basu san yana nan ba, sai suka zata Ai Aamil ne yayi zuciya yayi fushi da su.

Shi kuma Aamil yana musu haka ne, dan yaga yadda suka damu da shi, har kusan kwana biyu. Kafin Allison ya fito, nan ma Abbana ganin shi ya fara mishi faɗa, tare da nuna mishi yadda dan uwansa yake kokarin b'oye damuwar shi, amma yayi saki kuma ya damu da kanshi.

Yaso kare kan shi, amma haka bai samu ba, sabida yadda Aamil yake karawa Alamarin wuta, nan mahaifin ya nuna b'acin ran shi, hakuri ya bashi bai ce kome ba. Har zai wuce yace mishi.
"Karka damu zan Barka kasha iska, amma sai ranar da naji labarin Sidrah tayi wani auren tukun."

Shake wuyar shi Aalim yayi cikin zafin rai yake, huci karshe sai da aka kira Abban su. shi ya kwaci wuyar Aamil tare da kifawa Aalim mari a gaban kowa, yayi ta mishi fada haka yayiwa.

.... Mutum ne da bai iya fada ba, kuma bai iya boye abinda aka mishi ba, Amma da ya fahimci Aamil na bukatar iyayen su, sai ya hada kayan shi, ya bar musu gidan.

.... Duk da haka bai bar dukiyar su bai barshi haka ba, asalima ya tsaya duk da baya zama a kasuwa ya zuba idanun shi sosai akai har sauran kayan shi da suke kano.

Ganin baya nan ya sa kowa amincewa Aamil ne dan sun san Aamil ne ya tab'a gudu ga auren shi, kuma uwa uba rashin ganin Allison yasa suka kara yarda da cewa Ai shine Aamil.

.... Har yanzun babu wanda yasan dalilin Aamil na wannan renin hankali, kawai sun dauka dagaske yana son Sidrah ne, dan haka suka kuma diban jiki suka nufi Hadeja, an karb'e su da mutunci, amma sun rasa darajar su tunda Yan uwan Alhaji Ma'aruf suka zauna suka gasa mishi magana, da ciwon zuciyar shi ya so tashi, amma Aamil ya kafe ya nace, yana rokon su. Shi

idan na Sidrah ba mutuwa zai yi.

Shi kuma Baba Haliru, yana kallon su, amma bai ce musu kome ba.
"Ba zaka iya mutuwa akan soyayyar Sidrah ba, ka dai fadi haka ne dan mu baka ita, sannan ka tafi ka nimota duk inda ka same ta, ta amince da soyayyarka shi kenan."

..... Da wannan maganar suka dawo, dan haka ya tattara kayan shi, Iyayen suka hana shi tafiya.

Haka yayi ta mita tare da karamar hauka, suka danne shi. Da nuna mishi lallai suna bukatar shi kodan Cigaban kasuwancin mahaifinsu. Haka mara mutunci ya zauna ya kuma mike kafa yayi ta labta Iskancin shi son rashi.

Kuma da yayi hakuri da soyayyar da zasu mishi sai ta ninka da Allison, amma yayi karfa karfa, ya kwace yankin soyayyar mahaifanshi shi kaɗai.

---
"Zan kuwa ci uban kowa anan, ba zaku  gaya min ina kudin suke ba?"
Cike da mamaki suke kallon shi, kafin suka mishi.
"Yallabai kai ne kace kar mu kuskura mu bawa wani kome kuma ai Bama barin kudi a shago yana yawa ake kaiwa banki, wanda yake shagon bai wuce dubu saba'in ba.."

Dalla mishi mari Aamil yayi sannan ya tafi inda kudin yake ya bude ya kwashe tass, sannan ya bar musu shagon. Yana dirka musu ashariya.

Bayan tafiyar shi, Allison ya shigo musu, ganin yadda suke gunaguni ya sanya shi jin babu dad'i, dan haka ya daka musu tsawa, take kowa ya shiga hankalin shi.
"Akan me zanci zarafin ku? Ni na hana a dinga fitar da kuɗi daga shagon nan, idan zaku tafi gida, ga wancan asusun nan zaku cire kudin abin hawan ku! Ko ba haka muka yi da ku ba?"

"Eh Yallabai?" Suka bashi amsa.
Fidda laptop din shi yayi cikin nutsuwa, ya ajiye musu tare da kunna shi, sannan.ya shiga bude musu companies din shi nashi na kanshi, jikin su ne yayi masifar sanyi, sannan ya bude musu kudin shigar shi a duk kwanan duniya, miliyoyin dollas suke shiga asusun shi. Kashe laptop ɗin yayi sannan yace musu.

"Ni d'an kasuwa ne? Baka wasa da kasuwanci, hatta kudin da zan b'arnatan ina lissafin shi."

Takowa yayi har tsakiyar su, yace musu.
"Idan nace zan kashe kudi nan. Toh kudin shine kudin da ake biyan ma'aikata Kamfanonina.

Wancan da yazo ya amshi kudin Aamil ne! Ni kuma Aalim. Dan haka ganin cewa zakuna samun matsala da kasancewar mu, toh ga wannan alamar, idan nazo zan kawo muku nanbobbin yawanku, ku kuma zaku fadi cikon ni, wannan ya zama sirri tsakanin mu, idan ya

faɗa kunnen shi, kune zaku wahala, bani ba, domin ni ina gab da barin kasar baki daya, dalili me girma ne ya rike ni. Idan na samu zan bar muku kasar,.ina da nawa rayuwar a wani gurin, sanan.kudin ku, na sake muku tun d'azun, tayu bankunar kune basu baku ba, ina me kara baku hakuri da abinda ya faru, na tsaikon da aka samu, idan na samu lokaci zan na zuwa, idan damar haka ya samu, don Allah kuyi hakuri da abinda yake muku, don Allah kuyi mishi Uzuri kuyi hakuri ba halin shi bane"

"Babu kome yallabai, amma gaskiya kamar ku tayi yawa, gabaki daya, bamu iya banbanta ku," murmushi yayi sannan yace musu.
"Hussain dina ne, nine Hassan din shi."
"Mun gode Sosai yallabai"

"Zan koma, ina ga jibi kayan zasu iso, Khabiru naji sakonka, kazo muje.". Cikin farin ciki, Khabiru ya bishi, sunyi magana sosai..haka ya masifar musu dad'i. Sannan yace mishi.
"Ranar juma'a, kaje an hada kome ma kayan auren, abinda babu zaka ga albashinka ninkin uku ne, kasamu Ghali. Zan mishi magana idan an tashi bikin zai naka kayan abinci. Allah ya saka ayi a sa'a."

Kamar ya fasa kuka, dan murna addu'o'i kuwa Allison yasha shi.. dukkan su ma'aikatan shi sai da ya kara musu albashi sabida tsaikon da aka samu, sunyi murna sunyi godiya, tare da jinjina babbar zuciya irin na Aalim.

......

Yana barin shagon, ya nufi inda motar shi yake, domin dawowar Shi Aamil ya hana shi daukar motar shi, a cikin motoccin da yake sayarwa ya saka aka turo mishi. Wata Toyota me shegen kyau.

Gidan bakin Abban shi anan ya koma da zama, yana shiga dakin dan yasan ya rufe, sai ganin Aamil yayi yana zaune. Murmushi yayi sannan ya shiga d'akin. Ya ajiye laptop din shi.

Yana ajiyewa Aamil ya ɗauka, yana kunnawa hoton Sidrah ya bayyana, murmushi yayi sannan ya shafi fuskarta, yace.

"Kana sa'a, duk matan da kake tare dasu, sun haɗu." Yayi maganar cikin shakiyanci. Sannan yace mishi.
"Ka zare hannunka akan Dukiyar nan"
"Idan naki fa?"
"Toh kuwa zan nuna maka yadda nake." Murmushi yayi sannan yace mishi.
"Dama ya kake?"
"Ruwa biyu!"
"Ai kamar ya?"

"Zan iya sawa a b'atar da kai ne! Kuma ka tafi kenan, babu labarin ka."
"Duk sabida me?"

"Saboda me kake tambayana? Sabida ka tare min Sa'a ta! Ka hana ni sakewa da dukiyar Mom da Abba!"

Murmushi yayi sannan yace mishi.
"Zauna sai muyi tsayayyar magana."

"Ba zan zauna ba." Ya faɗa da karfi.
"Toh shi kenan! Kayi duk abinda yayi maka. Nayi imani da Allah, baka isa ka min kome ba sai da Yardan Ubangiji, dan haka dukiyar da kake ihu akai ni bai dame ni ba. Baya gaba na.

Aamil ka bude idanunka, wallahi dukiyar bata gaba na, Amma kayi min Alqawarin uku zaka cika min ni kuma zan bar maka kome."

"Wasu irin alqawari zan cika maka!"

Ajiyar zuciya ya sauke sannan yace mishi.
"Zan bar maka Iyayen mu, zan bar maka dukiyar mu, zan bar maka garin dan ka kula dasu. Ina rokon ka, don Allah ka bar min Sidrah!"

Wani kallon banza ya sakewa Aalim, sannan ya gyada kai cikin rashin mutunci, yace mishi.
"Wallahi ba zan bar maka Sidrah ba, kai ni fa sai na rabata da abinda kake kulafinci samu, wallahi ba zan amshi alqawarin ka ba,ka Cigaba da zama Sidrah ce sai na tab'a gurin da baka son na tab'a,.sai naji banbancin bakar Mace da baturiya, dan haka zaka gama haukarka, amma tabbas sai nayi yadda nake so da ita..malam zaka bani katinan bakin Abba ko sai na kaddamar maka."

Ciro Atm din Abban su yayi tare da wurga mishi yayi, ya mike zai fita yace mishi.

"Ko ban aureta ba, wallahi sai na mata cin da sai ta rasa inda zata cusa rayuwar ta, zan mata cin da ko ganin d'a namiji tayi sai ta rufe idanunta, kayi fatar kar na ganta, domin kuwa sai ta ji tsoron Allah idan bata ji daga ranar zata fara."

Bai mishi magana ba, sai ma kauda kanshi da yayi, haka Aamil ya fita, Aalim ya bi bayan shi da tausayin yadda rayuwar Hussain din shi ya koma, tausayin shi ya hana shi jin haushinsa. Dan haka ya mike tare da shiga ban daki yayi alolar azhar.

Bayan ya gabatar da sallar, ya jima yana nazarin, yadda zai bullowa Aamil, ba son Sidrah yake ba, kwaɗayin ta yake ji,shi kuma ba jikin Sidrah bace a gaban shi, itace farin cikin shi. Ya jima yana sakawa da kuncewa, har dare. Salla ce ke d'aga shi.

***
Yau wata biyu kenan da faruwar samuwar, dan haka Hajiya Uwani, tasa Aamil yayiwa Mahaifiyar shi, magana akan ta dawo d'akinta, aikuwa ta tuma tsalle tace sai Alben ya dawo ba

zata iya auren Alhaji Ma'aruf sai da Shawaran Alben, wato Aamil.

Haushi ya kama shi, kamar ya ce mata shine Alben, amma haka ya mata alqawarin zai nimo shi. Koda ya zo gurin Aalim gargad'i ya buga mishi tare da mishi mugun kashedin kar yayi kuskura ya b'ata musu shagali. Murmushi Aalim yayi sannan yace mishi.
"Toh ranka shi dad'e Yarima."
Dariya abun ya bashi, dan ya fuskanci rashin hankali a tare da dan uwan nashi, dan haka koda suka isa, nan aka shiga tambayar waye Aamil waye Bakon.

Kuma wani tashin hankalin da ya kuma dawowa gidan, shine Aamil ya fasa kofar store, ya kuma Barsu ana wasa da abincin,

Koda Ummi tayi mishi magana, yace a bari kawai babu amfanin rufewa, satar da Aalim ya dakatar na abinci, ya dawo kamar me.  Dan haka gidan an dawo da kome domin Ya Hindatu ta same shi da korafin ya taimaka ya bude abincin, da kuma yadda ake da. Dake banza domin ya nuna musu ya janye daga kudirin shi na farko, dan haka suyi kome kamar da kafin ya rufe. Kuma  bai san abinda Aalim yayi ba, kawai ya saka aka Cigaba da abinda ake, sannan su kansu basu san. Takamamen waye Aamil waye Allison ba, ganin shi wannan shima kusan dukkan abinda wancan yake banbancin su yaki bayyana, sai da Ummi ta rutsa shi ne, ya fada mata gaskiya shine Aamil, amma idan ta kuskura tayi magana, tabbas zai sanya a kashe Aalim, Kuma tunda ya fadi haka sai ta barshi, tare da rokon don Allah karya mishi kome, zata yi shiru.

Matar tayi nisa, dan haka ta sami Yayarta itace Nurse Salamatu, ta gaya mata. Halin da ake ciki a cikin gidan, dan haka tace mata.
"Matukar kika yi magana rayuwar wancan yana cikin damuwa,me zai hana muyi ta sawa ana musu saukar Alqur'ani, sune suka gurɓata shi, shi yasa da naga zai zama mugun iri a cikin al'umma na nemi ki shiga rayuwar shi,  a yanzun ma bana raba daya biyun akwai wanda yake amfani dashi ne,"

Dan haka suka fara sanyawa ba'a musu, sauka. Da addu'o'in a makarantar tsangaya, tare da niman Allah ya kawo sauki da mafita, ya kuma shirya musu Aamil,
.
Yana jin su yayi shiru, har aka bashi damar yayi magana da Maman,
"Alben! Kayi hakuri, abin da kayi baka kyauta ba, amma nasan mahaifinka zai baka dama ka samu wata matar ka aura, kaji abinda suke bukata me ka gani dan nasan kai ma kasha wahala a hannun su."

Shiru yayi sannan yace mata.
"Mom auren ki dashi , alqhairi ne..dan haka amince muma zamu samu nutsuwa idan kina tare dashi, amma ba zaki zauna a gidan nan ba, idan na gama gini na, zaki koma can, Allison ya baki gurin shi ki zauna shi ya koma daya gefen Abba inda yake saukar bakin shi, tunda naga yana sabon gini a cikin gidan, sai ki zauna a sabon, ko anan."

Wani irin tausayi ya bata, yadda ya daura kan shi akan cinyarta, suna haka Aamil ya shigo, shima yayi haka, suka kallon juna, murmushi suka saukewa juna, shi Murmushin Aalim na takaici ne, shi kuma na Aamil na samun nasarar. Anan ya shiga wani surutun shirme tare da sake narkewa.

"Mom yaushe zaki koma hadeja akan Sidrah!" Murmushi tayi sannan tace mishi.
"Ai zan samu lokaci naje da kaina, tunda Alben ya janyo mana jagwal, dole naje na roke su, su baka ita, yarinyar ma karama ce fa! Me zaku yi da premature. Akwai yan mata kuduba su kyakyawa.."

Mik'ewa yayi tare da cewa.
"Mom shi so babu ruwan shi da launin fata, yarena addina, abinda so ya sani yana iya shiga zukatar mabanbanta mutane, tare da musu dashe a cikin zuciyar su.

Mom So daban, sha'awa daban, soyayyar gaskiya bata taɓa barin ma'abota yinta, bata iya rabuwa cikin sauki, Mom ana mutuwa dan ciwo da hatsarin, amma ƙalilan suke mutuwa domin so. Dayawa suna rataye kansu, sabida bakin ciki, kalilin suke rataye kansu domin so. Hmm. Allah yana ji yana kuma ganin Mu."

Daga haka ya bar gidan ma, baki daya.. idan ya cigaba da zama ranshi b'aci zai cigaba da yi, domin Aamil ba zai barshi yayi rayuwar cikin salama ba.

***

Abuja..
Mika mata ipad yayi, tare da zuba mata ido, tana kallon hotunan su, kallon shi tayi sannan tace.
"Na kasa fahimtar Waye Aamil waye bakon."

"Mai budadden idanun shine Aamil, wanda idan shi basu cika buduwa ba Allison."
Kurb'an ruwan cikin glass cup yayi sannan yace mata.
"Wannan duk biyun na hada su, yanzun suna jin haushin junan su. Duk da Allison bai damu ba, amma ina son ki da Aamil shi yasa nake kara shirya target dina akan su.

Shi yasa dalilina nayi oral sex dake kenan, kuma na hadaki having sex da kowani mutum, sabida kuskuren da zaki iya samu. Aamil ya saba mu'amala da mata, Allison kuwa bai damu da mace ba, sai Yarinyar nan ki tura hoton su, zaki ganta!"
. tura hoton tayi sannan picture din Sidrah ya bayyana, wani irin abu taji ya tsaya mata a rai tace mishi.
"Na santa, kuma nasan lokacin da aka yi bikin su."

Amsar ipad din yayi ya shanye ruwan, sannan ya kuma kalleta yace mata.
"Indai haka ne, toh so nake ki shirya dakyau domin zan fara aikina akan su jibi idan Allah ya kai mu. Karki yarda ki kuma barin Arianah ta saka hannunta a gaban ku, domin ina son ki auri Aamil, tunanin shi baya bashi dai dai, Allison kuwa yasan mu'amala da mutane, kodan

kasuwanci shi ya koya mishi harka da mutane.

Ki nutsu da kyau, ki fara niman maganin gyara sosai, ki tabbatar da ko dinki ne anyi miki, burina ki fada rayuwar Aamil yadda zai addabi dan uwan shi ya bar mishi dukiyar, daga nan zan karasa aikina.

Ke mace ce, sauran ya haɗa da kissa da makirci zaki kara kwarewa akai, sauran zan gaya miki yadda zaki yi. Idan nace zan gaya miki abinda nayi zaki sha mamaki, dan haka ki tabbatar kin min yadda nace."

Kudi ya zuba mata, sannan ya nufa hanyar fita. Nan ta shiga niman wacce tasan inda ake gyaran jiki. Aikuwa Arianah ce ta sama mata inda za a mata. Cikin kwanaki ƙalilan.

**

Hadeja..

Kallon yayen dan Sahiya tayi da gaske yarinyar taki zaman lafiya da mijinta karshe da sheke auren ta fito, burinta Aamil. Da basu san mutuwar auren Sidrah ba, tunda Baba Haliru bai gaya musu ba, sai yan uwan shi maza, suma ya rike su, kar su fidda maganar.

Lokaci da Alhaji Ma'aruf yazo da maganar a maida auren kan Allison. A nan suka san aurenta ya mutu, ai kuwa Sahiyah sai da tayi rawa, dan murna. Dan haka tana zaune sai uban hada man da zai kara mata haske take, kafarta coca hannunta da fuskarta fanta, tayi wani shegen ja kamar tsada,

Har wani irin rawan kai take, ita zata auri Aamil tunda aikin su ya faɗa kan Sidrah. Yan gidan kuwa rashin mutunci take musu.

Kallon yaron tayi da yayi dagaje dagaje da kunu, ta mike tana fadin

"Ai Yaro shakurmin ka, idan na auri Aamil ka daina shan kunu, sai dai kasha shayi me kauri, da soyayyen kwai da burodi. Haka yan bakin ciki zasu ganmu su bar mu."

... Dariya suka yi ita da Lantana, tana cewa.

"Wato dai dole mu kara d'amara, tunda mun kusan kammalawa mu koma cikin barni"

... Dariya me cike da jin dadi, suke har zuwa wani lokaci, suka cigaba da abin suke kullawa.

*Dutse,

Zama yayi tare da zama hotonta, kawai yana zanawa ne amma zuciyar shi yana cigaba da kawowa mishi shawarar yadda zai fuskanci kalubale daga gare ta, domin ya fahimci ta dauki zafi ainun kan shi, kuma bai san yadda zai kare kan shi ba, murmushin bakin ciki yayi sannan ya kurawa hoton ido, tana zaune a zaman gado, ta haɗa kanta da kafarta, tayi shiru, hawaye na zuba daga idanunta.

Murmushi yayi sannan yace.

"Alkawari na miki, amma ban tabbatar ba ko zan iya cikawa, Sidrah ki yafe min laifina, nasan

nayi Kuskure babu wanda baya aikatawa.

Ina sonki! Har kullum, kece muradina, Ya Allah ka bani Sidrah badan na isa ba, ko na kai na same ba, sai dan kasancewata ni ba komin kome bane, ni ba kowa bane, Ya Allah nayi tawassali da sunayenka kyawawa tsarkaka, masu daraja, Ya Allah bani da gata bani da kowa sai Dan uwana da iyayen mu, ya Allah kasa su zame min komin kome na, su zame min gatan gata na, Ya Allah kai ka jarabce ni da kaunar Sidrah, Ya Allah kai ne mafi sanin sirrin boye da na sarari, Ya Ubangiji ka fidda mana gaskiyar ka kuma bayyana mana gaskiyar kome."
Tsiwar da wayar shi take ya sa shi dauka, Abba ya gani da sauri ya saka a kunnen shi. "Toh"
Da sauri ya fita, yaje ya dauki motar shi ya nufi gidan su.

----
Shiru duk gidan akayi, Abban su ya kuma mai-maita tambayar farko da yayi musu.
"Waye Allison!"
D'aga Hannu Aamil yayi,.haka ma Aalim.

Shiru yayi cike da mamaki, ya kuma zuba musu ido, yana son banbance su.
"Waye Aamil?"
Duk suka ki d'aga Hannu,(🤣)

"Toh wai meye nufinku. Hauwa zoki taya nie!"

Tana zuwa ta kama hannun Aamil tace.
"Ga Allison nan!"
"A'a Mom ni ne d'anki Allison!"
"A'a karya yake ni ne Allison."

Take suka jefa kowa cikin tashan hankali, ture Aalim, Aamil yayi yace.
"Munafuki ni ne Allison?"
"Karya kake nine Allison"
"Kai banza Ni ne Allison."

"Ka daina haka nine Allison..."

🙄🙄🙄🤔 Don Allah idan kun gano Allison din gaskiya kuyi min magana nima na rude Alqur'an...
Paid Before read...
#Mai_Dambu
[11/19, 9:26 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Conciliation

Tashin hankali gaba daya gidan, babu wanda bai rud'e,ba domin Aamil ya gama rud'a kowa, mik'ewa Abba yayi, ya fita. Domin ba zai iya da kayan haushi.
Number Baba Haliru ya kira, bayan sun gaisa tare da jajjantawa juna abinda ya faru, har

Abba yake tambayar shi Sidrah, nan ya gaya mishi ai bata nan ta, yayi yayi ya gaya mishi. Inda take , dakyar dai ya gaya mishi tana kwara, gurin Atiku amma don Allah don son shi da Annabi, kar ya gayawa yaran shi, domin karsu kuma cilla rayuwar ta cikin damuwa, da haka ya amince, suka yi sallama,

Number Atiku ya kira, dakyar ya dauka, shima din dan yana girmama Alhaji Ma'aruf ne, dan yau aikin da yake cikin abinci a jikin shi, shi ya nima sa, duk da bai kawo zai sami aikin ba, amma da kawowa Alhaji Ma'aruf, yace yaje nan da sati biyu zai kira shi, cikin Yardan Ubangiji satin biyun na cika sai gashi ya kira shi ya nima mishi aikin wanda idan shine yace zai nima da kan shi ba zai samu ba, dan guri me waye kasani.

.... Cikin kunya ya gaishe shi, duk da yana jin haushin sa, akan abinda ya Faru da sidrah
" Atiku don Allah taimake ni idan Sidrah tana kusa ka bata."

"Toh Baba,"
Yana ji ya kira Sidrah, kafin ya mika mata wayar,
"Sidrah!"
"Na'am Abba"
"Masha Allah, kina lafiya ko?"
Ya tambaye ta,
"Alhamdulillahi."
Shiru yayi ya rasa yadda zai, kafin yace mata,
"Don Allah ki taimake ni, kamar yadda Allah ya taimake ki, don Allah taya zamu gane Aamil da Allison."

Shiru tayi, kafin ta ce mishi.
"Kowa Ni d'an Adam, yana da buri, na wasu manyan buri ne, wasu kuma nasu kananun buri ne, sau dayawa mukan amshi abinda bamu so mukan amshi shi hannu bibbiyu, wasun mu, idan ka basu gudun shi suke da za'a gwada basu wani abun zasu fi kowa farin ciki koda kuwa abin bai kai na farkon inganci ba.

Dayawa bamu duba darajar abu muke kin shi, bamu duba illar abu muke karb'an shi, amma da zaka nima musu wani abu me kyau da k'awa, ba mamaki ka fahimci abinda nake nufi."

"Allah yayi miki albarka, ya kuma baki hakurin abinda muka miki don Allah kiyi hakuri!"

"A'a Abba Wallahi babu kome ya wuce, ai naka ne zai maka laifi kayi hakuri dashi bare ma kayi dashi balle naka, don haka babu wani abu da nake ji akan haka, kawai ya wuce."
Nan yayi ta saka mata albarka, har ta kashe wayar domin Abba Mutum ne,

Fitowa yayi ya sami, ana fada kamar kaji, sai da Mom ta shiga tsakanin su, a hankali ya tako zuwa gaban su. Yace musu.

"Zuwa dare ku same ni."

Daga haka suka suka fita, matukar zasu hadu toh babu makawa, sai sun raba halin su. Dan haka bai wani ji Dar ba, ya fita inda suke zama da abokan shi. Suka zauna. Anan yake labarta musu abinda ke faruwa a gidan shi.

Cikin halin damuwa, Alhaji Abubakar yace.
" Amma ga wani shawara! Tunda ita Sidrah ta gaya maka haka, toh me zai hana ka nemi daya a cikin su ka hada shi da auren Yar gidan Ahmad, kaga sai dayan su ya hakura ya rike Sidrah"

"Kai Haba, abar batun Nadrah, ku nima mu.."
"Ahmed ko baka son hada zuri'a dani ne? Tun lokacin da aka sami matsalar can ka hana Yarka zuwa gidana na.".
"A'a ba haka bane, amma Allah ya tabbatar da Alkhairi."

Nan Alhaji Abubakar ya kuma nuna musu fa'idar hadin da zasu yi, anyi hira sosai. Sannan suka tashi.

Bayan sallar isha ne, Alhaji Ma'aruf ya kira yaran shi, tare da musu tambaya na karshe.
"Waye Aamil, waye Allison?"
Duk suka yi shiru, kafin ya kuma magana, suka yi shiru, can yace musu.
"Toh tunda kai kace kai kace kaine Allison shi ya ce shine Allison, toh kai da kace kaine Allison ka barwa Aamil Sidrah, ga wata nan nasan ba zaka ki amincewa da ita ba."

Amsar hoton Aalim yayi cikin nutsuwa, ya kalle ta, ya ajiye mishi hoton sannan yace.
"Kayi hakuri Bazan iya aurenta ba, Sidrah ce mafarkina."

Daukar Hoton Aamil yayi tare da mata wani irin kallo, ya wani sake murmushi sannan yace.

"Abba dama akwai irin wandanan photo copy, din a duniya don Allah dubi Yarinya sai kace wacce akayi ta da d'anyen madara, ni gaskiya na bar maka yar baka dunarka, Ni dai Nadrah tayi min."

Cikin takaici, Abban shi ya wurga mishi throw na kujeran da yake kai tare da cewa mishi.
" Allah ya shirya ka, badan mu ba. maza ka bashi hakuri."

Dariya yayi tare da daura kanshi a bisa kafadar Aalim, tace mishi.
"Kayi hakuri! Kaje ga Sidrah, nima na sami tawa"

Girgiza kai yayi sannan yace mishi,
"Tace kar na nime ta!"
"Kai ba namiji bane ko dai har yanzun ɗan daudu ne?"
Buge mishi hannu yayi, sannan ya kauda kanshi, tare da cewa.

" Ko daya, kawai bana son na cigaba da sanya ta a damuwa ne!"
"No is time to find your love!"

Girgiza mishi kai yayi sannan yace mishi.
"A gurin wasu ni jarumi ne, a gaban Sidrah ne raggo ne, bani da iko da kaina, sai yadda tayi dani "

"Tab duk kaunar da nakewa mace ba zan yadda ta mai dani mace yar uwarta ba, zan dai biye mata amma ban juyar da tunani."

"Hmm!"
Da haka suka yiwa Abba godiya sannan yace musu.
"Toh yanzun ya za ayi, kai Aamil kazo ka b'ata mana kome,. Gyaran gidan da aka yi ka lalata mana, kasa ya kowa yana abinda ya gadama, ya dauke shi wata biyu yana gyara mana cikin gidan nan fa, sai ka gyara kafin na saka wando kafa daya da kai."

Dariya yayi sannan yace musu.
"Oho ya gyara mana!"
"Allison!" Kallon Abban su yayi sannan yace mishi,
"Aalim! Abba."
"Toh haka yayi, Allah yayi muku albarka, ku sassanta tashin  hankali babu dad'i don Allah karku kullaci junanku, Aalim kai ne Babba, karka kullaci Aamil, kayi mishi Uzuri, duk laifin da zai maka kayi hakuri dashi, Allah zai baka lada, kai kuma Aamil ka girmama dan uwanka, karka bari duniya ta shiga tsakanin ku, ban zauna dashi can ba, amma na fahimci shi mutum ne mai dadin mu'amala da mutane.

Sai dai shi.mutum ne mai matukar kokarin nima, kayi koyi da halin shi, kai ma ka kafa kanka, karka dogara da abinda mahaifiyar ku ta tara.
Kai ma ka zama kamar shi gurin niman na kanshi, yanzun yau kwana biyu da Mahaifiyar ku take gaya min yadda yake niman na kanshi sai da na jinjina mishi. Dan haka ka kara da irin halin shi."

Haka yayi ta musu nasiha, amma daga karshe ya saka Aalim a gaba yace yaje ya kuma niman auren Sidrah Insha Allah zai samu.

"Toh Abba!"
Lokaci da suka mike, sai da yaji sun burge shi, yadda suke hira har da Dariya, nan suna shirya yadda zasu yi da Mom din sune, dakin Hajiya Uwani suka shiga, suka samu tayi bakuwa har da Mom a falon.
"Ikon Allah! Toh wan nene kika tafi dashi wan neme kika samu anan?"
Kallon juna suka yi, sanan suka sauke murmushi, Aamil yace.
"Ni ne aka tafi dani!"
Da Hausa, Aalim yace.

"Ni ne aka bashi!"
" Ko dai kai ne dan Bature?" Dariya suka yi nan suka gaishe ta, sannan suka shiga hirar. Duk na irin wahalar da mahaifiyar su tasha ne. Sunkuyar da kai Aalim yayi tare da cewa.
"Indai gidan nan ne zasu aikata, domin ba daraja ce dasu ba."

Shiru Aamil yayi yana nazarin Yadda zai gabatar da kanshi, shi kadai sai wani murmushi yake, shi dayan shi. Har dai suka gama hira ya bar dakin ma, shima Aalim ya bar gidan.
.... Kwana biyu tsakani, ya tattara ya bar dutse, ya nufi hadeja. Tunda ya isa babu wanda yace mishi cikanka, sai Sahiyah itace keta hidima dashi.

Har su Baba Haliru suka dawo, yana gidan, da dare yayi ya ki tafiya, karshe dakin kofar gida aka bashi ya kwanta, bayi iya barci ba, sai dai ya saka maganin sauro....

**
Ilorin..
Kallon juna muka yi da Saratu, tace min.
"Ko zaki bani sako idan na isa garin dutse na kai mishi."

Girgiza mata kai nayi, sannan na had'iye kukan da yazo min, nace mata.
"Ba mutunci bane na nime shi, tunda na yarda ni mace ce, toh Tabbas dole ya biyo ni zai zo nima na, da kafar shi. Bana son mutumin  ya Atiku yake son na tsaya dashi."

Rike hannun muka yi, kwalla na zubo min daga Idanuna.
"Kiyi hakuri."
Girgiza kai nayi, sannan nace mata.
"Allison! Ina son shi."
Na janye hannu na, tare da kallon zoben hannuna, wasu kwalla na zuba min.
"Da yau ban amshi zoben shi ba, da nayi asara mafi girma a rayuwata,  Gashi nan Allah ya dube ni da idanun rahama, ya dawo min da zoben shi. Wannan shi ne kaddarar mu."

"Insha Allah, kome zai zo miki da sauki Allah yana sane dake"
_don Allah kuyi hakuri_🙏🏽
[11/20, 10:51 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Pardon.

.... "Yaushe? Na gaji."
"Rufe min baƙi tayi tare da girgiza min kai, tana faɗin .
"Insha Allah nace, ba dan Sarkin garinku ba, dalla Malama, ni tafiya Zanyi kuma dole ki iya harshen ki babu kintsi, kamata yayi. Zuwa Yanzun kin dauki darasin rayuwa, ba sai wani ya koya miki yadda zaki kula da wasu abubuwan ba.

Tun baki kai haka ba kike fuskarta rayuwa ba, Yanzun kuwa babu abinda damuwar wasu zata ja miki sai daraja, gaskiya zan baki shawara, idan Allison yazo ki amshi alamarin shi dan wallahi kafin ki sami madadin shi zaki wahala, mutumin da ya soki ba tare da ya, ke wai me ke

laifin Allison?

.... Laifin shi dan bai gaya miki shine Allison din ba ko? Toh wallahi kiji tsoron Allah, domin ni dai banga laifin shi ba, yana sonki yana Kaunar ki, karki yarda ki zama wacce bata san ƙaddara ba mana, ai rayuwa bata da amfani idan baka more shi a tare da wanda kake so ba, ki duba magana ta, da kyau duk inda ake niman mutumin kirki ya kai gurin, sai dai idan zuciyar ki bata Allah da Annabi bace."

Take jikina yayi mugun sanyi, domin kuwa, ban tab'a daukar haka a matsayin wani abu ba, kawai na dauki karan tsana na daurawa Ya Allison ne, lumshe idanuna nayi, tare da juya mata baya, nace mata.
"Me yasa lokacin da yazo bai gaya min gaskiya ba, ai da yau bana jin haushin sa, sai ya kama ya rufe ni"

...."amma wallahi da ace a sahun mutanen farko kika zo tabbas za a sha fama dake kafin ki amshi musulinci, banza kawai ya yaudare ki sai me? Wata baka munmuna irin ki, har wani abun damuwa ce, duk wanda zai zo rayuwarki zai zo ne sabida girmanki na mace, wawuya sakarya, sai ki zauna har sai yazo ya baki hakuri."

Kallonta nayi tare da zuba mata ido, kwalla na zubo min. Kaɗai kai nayi tare da Cigaba da shafa mai ina share kwalla da suke zuba min, wato ni bani da gata anyi min laifi kuma an hanani magana, dan haka na shiga kuka, kamar wacce aka min shegen duka, ina yi ina saka kayana.

"Kinga Sidrah! Ban gaya miki haka dan ya baki haushi ba, amma yana da kyau ki fahimci wallahi yana sonki! Sosai shima bai da yadda ya iya ne yasa shi miki shi, amma Uzuri yana da dad'i yanzun magana na gaya miki kina kuka, toh shi ki duba yadda zai ji maganar da kika gaya mishi, sau tari mukan amshi laifin da bamu ne muka kirkiro shi ba..

. Kuma mu amshe shi da hannu bibbiyu, sabida babu yadda muka iya, kuma a zauna lafiya.

"Ban tab'a sanin d'a namiji ba, amma sabida su Sahiyah gani ake na tab'a sanin namiji, dalilin da yasa Baba yace na dawo nan da zama kenan, yanzun zan je nayi musu kwana biyu ne, na dawo sabida gaskiya ina kewar gida."

Kura mata ido nayi, cike da mamaki tace min.
"Kema yaki barin ki zauna a can ne sabida auren sauran ya mutu, idan na ki ya mutu kika shiga gidan kema zaki bi sahun su ne.

Ki buɗe idanunki, wallahi zaki iya aikata kuskure."

Wani irin mutuwar jiki naji, ina kallon ta, duk abinda ya faɗa babu karya a cikin shi, gaskiya ce zalla, sai dai mutum yaki dan rad'in kan shi.

"Toh amma baki ji abinda ya Atiku yace bane?  Ya sama min miji, ogan shi ya ganni ranar da muka je musu jajje."
Na fada a hankali, rike hannuna tayi, tare da kallona, yadda na sunkuyar da kaina, murmushi tayi sannan tace min.
"Babu dole a rayuwar duniya fa, idan ya miki magana kice ke gurin Allison zaki koma meye a cikin Idanu ban da ruwa. Shi kenan, an gama matukar kika dauke kanki daga Allison Toh billahil azim, kin rasa namijin da zai yi tattalinki, ya ririta ki ya nunawa duniya ke matar shi ce. Wannan kawai zan gaya miki domin ni na fisonki da baturen ƙi."

Sosa kai nayi, sannan na zame dan kwali na nace mata.
"Taimaka min kiyi min kitso tunda gobe zaki ware."

"Bani ciki da Iskanci, ba zan miki ba, kiyi duk abinda yayi miki. wannan shegen gaggautsar gashin ki mara dadin nan kana tab'awa hannunka yana yanke wa shine zan kitsa miki shi."

Warware shi nayi tare da narke mata, tsaki tayi tare da dauko wurya, ta shiga kitse min shi, murmushi nayi sannan nace mata.
"Lokacin muna tare, da kanshi yake wanke min gashin ya kuma busar, zuwa na Dubai na shiga sayan mayukan gyaran gashi ina wankewa tare da gyara shi."

"Hmm! Kuma gashi har yanzun a tsaye kamar nonon maza." Maketa nayi tare da cewa.
"Ke kan kin shiga uku, kin iya sake batu marasa dad'in ji."

"Nayi din, idan an damu a min aure." Girgiza kai nayi tare da cewa.
"Yar banza auren wani abun daɗin ne, ki shiga damuwar mutane ta ishe ki, idan kuma kika samu namiji ya addabi rayuwar ki da fitina."

Dariya tayi sannan tace min.
"Ke washare walle, na rantse ranar da kuka kai ni, a kwai biki bidiri bire dede, domin sai na."

"Dan Allah ki bar maganar haka, kiyi hakuri ba a, bin gaggawa bane indai namiji ne."

Dariya tayi sannan tace min.
" Ke babu wani abu fa, domin an gaya min yadda.."
Make mata cinya nayi sakamakon jin Aunty Mariya matar Ya Atiku zata shigo dakin mu.

"Yan mata wai hayaniyar me ake yi ne haka?" Mikewa muka yi muna kade jikin mu, sabida gashi.
"Sidrah ina son gashin nan naki, wallahi ban shi baki kirin fa," ta faɗa tana shafa kitson.

"Mu dai kar a zubar mana da gashi, ina dalili. Mata idan an kwana biyu zaki fara fashi da reza idan gashi yayi miki , ki aske na kan mutane." Inji Saratu.

Dariya ta saka tare da cewa.
" Bani da lokacin ki, sabida ni bazan kula me jar gashi ba, da baki irin na Sidrah nake magana "
D'aga kai tayi tare da saka hannunta baƙin ta, tace mata.
"Ranki shi dad'e Gimbiya, daga yau ne fa idan na tafi san nan da sati Uku, zaki ganni Wallahi muna nan zaki zo nima na, ba dai Ni kika gayawa magana mara daraja ba?"

Cikin zolaya nace mata .
"Toh ke taki tana da daraja ce? Ban da rigima kayi laifi idan aka maka kaji babu dad'i."

"Sidrah Munfi kusa, domin tsakanin mu babu rata, ina hadeja ina Dutse, ko dan nasha shayi da soyayyen kwai, zan zo gidan ki, ita kuma sai kin kwana kin wuni a bisa doron titi. Ni magana ta tana da daraja."

Nan muka yita dariya ana wasa da juna, muka zauna aka kuma baje hira, anan Saratu take kuma mai maita min abin da take gaya min, itama kuma Aunty Mariya ta goyi bayan idan Allison ya dawo ba koma mishi.

Haka suka yi ta bani shawara akan yadda zan kuma rike shi hannu bibbiyu, nan na tuna musu da cewa.
"Ya zanyi da Ya Atiku?"

"Dole ya barki ki zaɓi abokin rayuwarki, ba shi zai zauna miki ba, na tab'a ganin karfin hali barawo da sallama."

Inji Aunty Mariya, shiru nayi dan ni kam ban san me zance ba, domin su dai da suka ga zasu iya magana na Barsu suyi ta yi, amma ba zan iya hana shi abinda ya ga ya dace dani ba.

Har kusan azhar, sannan muka fito, daura abincin rana, Allah ya taimaka bamu gama ba, sai karfe biyu, muna gamawa. Yana shigowa da ogan shi, har falon inda muka gyara tsaf.

......ina daki zaune dan ko wanka banyi ba, Aunty Mariya ta shigo fuskarta a daure, ta sani na dauki hijab, muka fito. Falon ta kai ni, inda mutumin yake, shiru ne ya gifta tsakanin mu, kafin ya fara magana.
"Suna na ASP Adawi Mu'awiyah Dass. Da fatan Yayanki ya gabatar da ni kafin nazo?"

Sake sunkuyar da kaina nayi, tare da jin kuka na zuwa min, a hankali kwalla yake zuba min, na d'ago kaina na kalle shi sannan nace mishi.
"Kayi hakuri! Har yanzun ina son shi, don Allah karka raba tsakanin mu dashi, na sani yana can yana nima na, don Allah ka bar mu, mu kasance a tabbatacce inuwa d'aya."

.. murmushi yayi sannan yace min.
"Gaskiya kiyi hakuri! Nima ina son mace irinki, ki rabu dashi na shirya miki duniyar da zaki ji

dad'i."

Girgiza kai nayi cikin kuka, tare da cewa.
"Shi duniyar shi ya tsallaka yazo gare ni, rayuwar shi ya bari ya zo gare ni, na hada ka da Allah ka rabu da ni, ni shi nake so ba wani namiji ba.

Don Allah kayi hakuri ka bar mu, mu rayu da junar mu, sabida shine abokin rayuwar ta."

"Ina da mata biyu, yara bakwai. Babbar Y'ata sa'arki ce, dan haka kiyi nazarin abinda zan shiryawa rayuwarki, zan baki duk wata kulawa zan kuma miki duk abinda kike so."

Ba zaka iya ba, shi ya faɗa ya cika, bana tunanin akwai wanda zai iya tattalina, domin ya bani ilimi nisanta ni yayi daga gare shi, duk abinda zaka bani ba zai tab'a zama dai-dai da wanda ya bani ba.

Ina matuƙar buƙatarsa a tare dani don Allah ka rabu dani, ka ɗauke ni a matsayin Yarka!"

"Ba zan haramtawa kaina abinda nake so ba, wallahi ba zan iya hana zuciyata mallakar mace da tayi min ba, karki damu, zan iya maneji da son da nake miki please ki amshi soyayata."
"Ba zan amsa ba kuma ban amsa ba, duk abinda yayi maka ka aikata ba zai dame ni ba, ina son shi kuma ina da yakinin zan rayu saboda shine, ruhina da gangan jikina mallakar shi ce, don Allah karka sani na rena ka."

Duk yadda naso dan akuyar ya fahimta ya kasa, asalima sai min yanga yake tare da lashe bakin shi, yana min wani irin kallo daga sama har kasa, sabida yaga nama, da yake shirin daka mishi wawa.  Fir naki kula shi daga karshe na bar falon, ana aure dan a samu masalaha ce ni rawa auren domin ya biya bukatar shi ya Atiku ya bada ni sabida Asp zai shigar da sunan shi cikin manyan yan sanda da za a tura karatun karo ilimi kasar waje.

Wannan masifar ya faru ne sakamakon wani fita da muka yi da Saratu, zuwa kasuwan cikin Barrack din, tunda mayye ya ganin sanye da doguwar riga na yafa gyalen shi, tun daga ranar ya takura min, dake ya fahimci raunin Ya Atiku, shine yayi amfani da wannan tunanin yake ta niman biyar bukatar shi.

Hmm, tunda na bar falon, ya kira ya Atiku, zai tafi ya raka shi, a hanyar fitar sune yake gaya masa yadda muka yi, aikuwa Ya Atiku yazo yayi ta faɗa, har yans cewa kwadayin duniya tasa naki amincewa da Auren Asp, ina hango abinda su Ya Aamil suke da shi, idan ba haka ba. Akan me zan damu kaina da komawa rayuwar su, dan ya taimake ni, ai ga Saratu bai damu da ita ba kamar yadda ya damu dani ba.

Shine wato bari na kunya tashi a gaban mutumin kirki irin Asp. Nayi kuka nayi dana sanin abinda na gayawa Asp, dan haka  na rasa yadda zan yi da kaina. Haka suka gama Maganar

suka fita shima Yaji haushina, ban san me ya faru ba, sai dai naji kamar hayaniya a falo, ina lekowa naga Saratu tana kuka. Tare da cewa.
" Toh an taba yin haka dole ne?

Tace mijinta take so, kuma ka nace lallai sai wancan bushashen mutumin Allah na tuba ana taba shi ba za a rasa shi da wani abu ba. Don Allah ka barta ta koma ga mijinta, idan ka tilasta mata zata zauna da shi amma ka sani zaka iya lalata mata farin cikin ta ne, ni ban ga amfanin takura mata ba.

Bayan wanda Innar mu tayi mata kai ma zaka mata, idan duniya da gaskiya kace ya hakura mana zaka zo ka takurawa marainiya dan kunsan ita kadai ce zata baku abinda kuke bukata, wallahi zan gayawa Baba."

..... Zuwa nayi na janyo hannunta, sannan muka nufi daki tana kuka, tare da cewa.
"Sake ni, wallahi ba zaka zauna da wani namiji ba sai Allison, babu namijin da ya dace dake sai shi. Akan me zan bari a baki abinda baki so, wallahi na rantse ba zaki zauna dashi ba, yaje can ya gama niman matan shi, maye kawai daga ganin mace hankalin shi ya tashi."

.yadda take shiga ba nan take fita ba, gashi tana kuka, Ni kaina kuka nake sosai, sabida rashin yadda zanyi kamar na bita mu koma gida, haka muka wuni ko abincin kasa ci muka yi. Sai dare, tana son kiran Baba ta gaya mishi na hanata, sabida babu amfanin haka. Nasan ƙaddarar mu ce, shi yasa ban kuma magana ba. Washi gari da zata tafi ni ce na rakata, har tasha mun sha kuka, idanun mu yayi fulu fulu, sama tun jiya muke kukan har yau.

..... "Insha Allah zan hada ki dashi ki kwantar da hankalinki, Sidrah da Insha Allah zan turo miki shi."

Haka muka rabu, da alkawarin zamu sake magana a waya. Tun da na dawo na koma wata shiru shiru, da kyar nake iya dogon magana da Aunty Mariya, idan ma ta kama dole zaki samu bata tsayi, Ya Allison ya gama gina min Son shi a Birnin zuciyata, kuma na na zauna na gyara gidan da kaunar shi. Ina zaune aka turo kirana, lokacin da na fita wannan nanataccen mayen ne,.mutum ya nace sai kace talauci.

Haka ya gama surutun shi, sannan ya mika min sabuwar waya a kwalinta, spark hot 6.
Kallon wayar nayi sannan na ki amsa nace.
"Kayi hakuri. Ina bukata zan tambaya a gurin yaya na, ka."
Takowa yayi warin sigari ya dake ni, har sai da na yatsina fuska.
"Ki amsa, ban tab'a bada kyauta anki karba ba, sabida haka amshi."

Kallon shi nayi sannan na sake murmushi, nace mishi.
"Ban tab'a k'arban kyautar wani ba, sai na mijina dan haka kaje da kyautar shi, kaga zoben shi. Wich mean, har yau muna tare da juna. Dan haka kayi tafiyar ka."

"Yes Wedding ring, lallai mijinki nan yana sonki zobe me tsada da kima haka, mu gani"

Girgiza mishi kai nai sannan nace mishi.
"Duk wani abu idan nashi ne bana wasa dashi balle zoben auren mu."

"Ok kenan, dan ya amshi virginity dinki shine kike rike da zoben shi, baki san akwai zaratan mazan da zasu iya cika miki marar ki da zazzafar ruwan jikin su ba, daga cikin su ina ina daya gani..ki yarda da abin nake fada miki. Ni zan iya cika miki gabanki ba tare da kin nemi karin namiji ba "

Lallai mutumin nan bai da kunya, me ya mai dani? Wato sakarya. Kallon shi nayi daga sama har kasa nace mishi.
"Allah yayi min tsari da kai! Ni mijina mutum ne da yasan darajar kanshi dani ma, idan yayi maka ka bar kofar gidan nan.idan bai maka ba, zaka iya Cigaba da tsayuwa amma ko fatalata ba zaka iya samun a matsayin matar da zaka aura ba balle ni me ita,.ba kai ba hatta wanda yake tunanin ni Sidrah Mrs Allison na fi karfin ka har abada."

Yaji mugun.haushi dan haka na juya na barshi a gurin, ba dare ba balle ya danne ni, rana ce banza falfala hamago, ya bani haushi Sosai.

.......
A hankali lokacin yana tafiya tunda muka yi magana da Saratu ban kuma jinta ba. Har kusan wata uku da tafiyarta gashi ya Atiku yana shirin gabatar da Adawi Mu'awiyah Dass a Hadeja.

***
Kasancewar shigowar damina, garin Hadeja tana fama da tumbatsar ambaliyar ruwa,.dan haka idan aka yi ruwa har shagon da yake kwana.. koda Saratu ta dawo, ta ganshi zata gaya mishi inda nake Baba ya mata fada tare da yunkurin sai ya mata mugun duka, haka yasa take jin ciwon hanata magana.

... Duk wanda ya san Aalim a baya sai ya masifar firgita domin lokaci guda ya lalace ga uban gashin da ya tara, gashi bayi da lafiya, sanyi ta shige shi.
Yau anyi wani ruwa wanda ya tab'a har gonar da yake bin Baba Haliru aiki, saura kiris da ruwa ta tafi dashi, domin bai iya ruwa ba, haka matasan unguwar da yake suka tsamo shi sabida suna tare a gonar..aka dawo dashi gidan.

Cikin damuwa aka kira Abban shi, washi gari suka iso, kan shi a sunkuye Mom tayi ta fada amma yaki cewa kome, gashi kana ganin shi kaga wanda sanyi ya shige shi.
"Aalim kazo muje gida ka hakura da Sidrah!"
"Mom bazan iya ba, idan zan iya tabbas da nayi, wallahi ba zan iya hakura da ita ba, kiyi hakuri ita nake so."

"Wai meye Sidrah tafi sauran matan?" Ta faɗa a tsawa ce har Abba yana rike ta, hawaye na

zuba a idanun ta.
"Mom kuyi hakuri! Wallahi matukar kika ce na biyo ku, tabbas gawata zaku kai gida, ban san yaushe ta gama dani ba, sai dai nasan ina gab da rasa rayuwata, matukar na rasata, wallahi ko ban mutu ba, nasan ba zaku more ni ba. Don Allah kuje kawai ina nan,. ina jiranta."

Yadda yayi magana sai da ya ƙarya mata zuciya, dan haka basu nemi ganin kowa ba, suka bar shi a gidan,.Saratu na jin su. Ta kira Number Aunty Mariya,.tana dauka tace mata.
"Don Allah ki bawa Sidrah."

"Gashi kayi magana da ita, na gaji da ganin ka cikin damuwa, babu dad'i itama tana can tana jiranka, tana sonka sosai."

Amsar wayar yayi tare da sakawa a kunne.
"Baby Love!"....🤔🤔 Romeo da juliet..
#Mai_Dambu...
[11/21, 7:12 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Favor

"Sidrahtul!"
"Na'am! Ya Allison,"
Wani tare yaji, zunzurutun yadda takira sunan shi.
"Aalim! Zaki ce min, ki kira Ni da Aalim"

"Ya Aalim!"
"Hmm" nan suka yi shiru, kafin ya kuma ce mata.
"Hmm! Sake kiranta da "Sidrah!"
"Ya Aalim!"
"Kina ina?"
"Uhum,uhum karka ce zaka zo, ka."
"Ki gaya min kina ina ne?"
Ya cire wayar da sauri a kunnen shi tare da cire Number dinta, yace mata.
"Ina jinki kina ina?"
"Karka ce zaka zo."
"Zan zo kina ina ne? Ki gaya min."
Kashe wayar tayi, sannan ya kalli Saratu.
"Tana Ilorin, a police barrack"

Tsabar murna rungume ta yayi tare da sake murmushin jin dadi, ya a cikin bagwaren hausan shi yace mata.
"Ki gaya min ke kina?"
"Babu kome, ni dai don Allah karka wulakanta Sidrah, bata da kowa sai kai don Allah ka riketa da Amana, wallahi bata da fitina."
"An gama, nagode"
Ya juya da sauri zuwa inda motar shi take, ya kuma dawowa ya kwashi kayan shi, ya fita da

sauri. Ya kuma dawowa ya rungume ta, tare da d'aga sama yana dariya, kunya ya hana ta cewa kome, har ya tafi a hankali tace.
"Ubangiji ga Marainiya nan Ya Allah kasanya Aalim ya zame mata gata, ya Allah karka bari wani ya shiga rayuwar su, Ubangiji duk wanda ya nemi shiga rayuwarsu ka kawo karshen Labarin shi.

Ya Allah na roke ka badan mu ba."
"Amin uwar yan tsari ni na shirya abinda ya dace ke kuma ku wargaza min ko?"
. "A'a Baban mu, wannan fa ba adalci bane, ni wallahi ba za ayi haka dani ba, yarinya tana son mutumin nan kuma kun wani karfa karfa zaku hana, yuwar kome, wallahi mutum zai iya mutuwa akan wannan al'amarin. Na dai fita hakkin bayin Allah na huta.

.... Haka kawai an shiga hakkin su, toh na gaya mishi sai dai yau kayi min duka dan wallahi na na lalata kome."

Kasa magana yayi ya zuba mata ido, girgiza kai yayi shi bai tab'a ganin mutum mara tsoron takife irin Saratu ba, sam bata san tsoro ba, asalin yar daba ce san bata gudun abinda zai je ya dawo.
"Allah ya shirya ki!"
"Amin Ya Allah, kai ma ka fahimci abinda nake nufi ba? Ai shi wannan al'amarin mutum zai iya bakuntar lahira, ni kuwa bana son dan tsohon mu ya mutu, gwara kaga aurena na haifa maka jikoki kaga kenan babu wanda zai."

"Ke tafi ki bani guri da sakarcin nan, tun kina aikin lissafi zaki shiga na shirme,. Allah ya kawo miki ɗauki,"

Haka tayi wucewarta, ta bar shi tana shiga gidan ta sami Sahiyah,.suka hada fura da nono. Ya sha bar bade.
" Da alamu dai wa Bature zaku kaiwa wannan jike jiken?"

"Sakarya mara zuciya, dalla matsa mana!" Inji Sahiyah,.
Fashewa tayi da dariya, sannan tace..
"Ai kuwa mijin Sidrah ya tafi dauko matar shi, maza a cigaba da hada aikin."

"Amma dai wannan yarinyar anyi ja'ira."
"Innar mu"
Suran Muciya Lantana tayi ta bita da gudu, ta fice tana dariya.

**NAD
"Gaskiya ba zan iya bada Nadrah ga wannan gidan ba, sabida basu san inda ke musu ciwo ba, ba zan iya ba, sokuwa ce. Duk yadda kayi da ita haka zata faru.

.... Yarinyata karamar ƙwaƙwalwa gareta, ina tsoron Allah ina tsoron wannan gidan, don Allah

kuyi hakuri da zumuncin nan don Allah ba dan ni ba" inji Hajiya Ubaidah ta faɗa cikin kuka da tashin hankali.

Lumshe idanun shi yayi cikin nutsuwa, sannan ya buɗe su, tare da furzar da iskar bakin shi. "Kiyi hakuri! Ba zan iya hana Ma'aruf kome daga gare ni ba, bana jin zan iya."

Sunkuyar da kai tayi, tare da sake kuka tasan tunda ya fadi haka, babu wanda ya isa ya hana ayi auren sai Allah. Dan haka ta cigaba da kuka, a hankali ya rungume ta, yana buga bayan ta..

** Daga Hadeja, ya tawo dutse. Ya kuma shiryawa, washi gari ya bar garin ya nufi Ilorin, dake jirgi ya bi, karfe goma sha biyu na rana, ya sauka a garin. Hotel din da ya kama a g.r.a sai da ya fara ajiye kayan shi, ya huta, wajen karfe hudu na yamma da rabi ya dauki motar hotel din, ya nufi police barrack. Da taimakon Sheikh google. Ya isa har barrack din. Tunda ya shigo. A hankali yake bin block din bai gane ba, haka yayi ta yawo.

Wajen biyar da rabi, yara sun taso daga islamiyya, tana rungume da Alqur'ani, a hankali take takawa, kamar ba zata taka kasa ba, fuskarta sanye da niffab. Unifoam din jikinta, ruwan hanta. A hankali yake bin bayanta. Yana jin ko a cikin miliyoyin mutane ya ganta zai iya ganeta balle kuka a cikin su da basu wuce dari ba, kamar yadda take me sanyin haka kome nata yake mai sanyi, haka tafiyarta ma a sanyayye take. Ajiyar zuciya ya sauke lokacin da yasha gabanta. Cak tayi tsaya kafin ta cigaba da tafiyar ta, sake Binta yayi da motar ya tsare mata hanyar fita. Kallon motar tayi a hankali ya sauke gilashin motar ya kalleta kadan yace mata..
"Shigo muje!"
Wani irin faduwar gaba naji lokacin da na ganshi tsaye a gaba na, tare da sunkuyar da kaina, kafin na kauda kai nayi tare da cigaba da tafiya.
"Kizo muje ko nazo na dauke ki!"

Cak na tsaya, ya fito daga motar, yace.
"Wallahi zan dauke ki!"

A sanyayye na juya tare da shiga
Motar na zauna, na juyar da kaina, a tunanina zai tambaye ni gidan da zai kai Ni ne, sai naga ta juya da kan motar, ya bar cikin Barrack din..
"Dalilin da yasa nace maka karka zo kenan, domin nayi imani sai ka jefa ni matsala. Meye nayi maka ai nace karka zo meye na zuwa?"
Me tambaye shi tare da kallon inda yaƙe.

"Sabida ba zan iya hakura da ke ba, shi sani zuwa." Ya fada min yana barin cikin barrack din.

"Don Allah ka mai dani bana son tashin hankalin, kaji ka barni na zauna lafiya." Na fada Mishi kamar zanyi kuka.

Kamar yadda nayi maganar haka shima ya kalle ni yace.
"Don Allah ki barni naje na leka wannan abu guda biyun"

Buge hannun shi nayi tare da hararar shi.
"Kai baka tsoron tashin hankali ne? Ni bana son damuwa wallahi." Na fada a raunane.
"Waye ya gaya miki ina tsoron tashin hankali, ai tun daga ranar da na ganki na shirya wa tashin hankali, kawai na ajiye shine a gefe saboda ba zai hanani abinda na saka a gaba na ba, don Allah ki share wannan batun."

... Duk yadda naso fahimtar dashi yadda zai janyo mana fitina yaki fahimta, kashe hotel din da ya sauka ya kai ni, kin fita nayi, ina zaune a cikin motar sai da ya zago zai dauke ni. Na dakatar da shi.

A sanyayye na fita ina bin bayan shi, kai na a kasa. Har muka isa dakin da ya kama, ina shiga yana jingina da kofar, ya zuba min ido. Bude min hannu yayi. Na kasa motsi,
"Baby Love, wato kin girma baki yi miss dina ba, Ni kuma na gama missing dinki, please hug me."

Kai na a kasa, na rasa yadda zan yi, sake jin muryan shi naji,.ya kuma maimaita abinda yace,
Da sauri na isa gare shi, tare da fadawa kirjin shi.
"Haka bai bada armashi ba! Sake ni tunda ba zaki min yadda kike min ba, Nagode zo mu tafi na mai daki inda na dauko ki"

... A hankali ya janye ni daga jikin shi, fuskar shi a daure.
"Toh ya kake so nayi maka? Kasan babu aure."

"Nasan babu auren muje na mai daki."

Komawa bakin gadon nayi na zauna tare da fashe mishi da kuka, lumshe idanunshi yayi cikin nutsuwa, sannan ya bude shi kai na.
"Zo ki gaya min tsoron waye kike ji, da kika manta da Allah? Zo nace miki"

... Da akwai tazara a tsakanin mu, dan haka ina tashi da gudu na isa tare da rungume shi,
"Yes that's my Baby Love, yanzun naji yadda nake ji a baya, yanzun na fahimci abinda kike shi. Waye yake damunki? Waye ya hanaki sukuni?"

. Ya tambaye ni, tare da k'amk'ame ni, ina kuka ina kuka shiga jikin shi.
"Ina sonki Baby Love, ina sonki sosai, kaunarki a jikina yake. Bar kukan nan haka."
"Ina ma hakan Ya Aalim, nima ina sonka ka tafi dani, Ya Aalim mu tafi gida, kar su nime ni zasu min faɗa."

. D'ago kan shi yayi tare da niman fuskana, ya haɗa bakin shi da nawa, da sauri na rike

harshen shi, kallon cikin kwaryar idanuna yayi, tare da matse ni kaɗan. A ranshi yana faɗin.
"Baby kinyi missing dina amma kunya tasa kin dage na mai dake gida."

A hankali yake takawa har bakin gadon, ya ajiye ni, shima ya zauna, kifa kaina nayi a gefen kafad'arshi nayi, tare da sunkuyar da kaina, ina sauke ajiyar zuciya.
"Baby Love, naji kin kara girma? Bari na ga kayana da ya tsulewa wasu idanu."
Boye fuskana nayi ina dariya, a sannu ya cire hijab din, sannan ya kura min ido, hannun shi ya kai bayana na, nayi maza na kalle shi.
"Don Allah karka jagorance ni aikata laifukan da bazan iya yafewa kaina ba."

"Ba zan tab'a aikata abinda zai kawo mana nakasu a rayuwar da muke faffutikar shiryawa ba. Ki yarda dani." Ya faɗa min haka,

Yana zuge min zip din rigar, idanun shi ya dauka kan kirjina, da sauri ya rufe tare da mik'ewa ina gyara zaman rigana.
"Shagali! Kice akwai ranar da zan kwana ina tab'e tab'e, wai Allah Nagode maka, yadda ka karawa Baby Love dina lafiya ta kuma girma, zo nan na rufe miki zip ɗin"
Juya mishi baya nayi, ina kunkuni.
"Wai na rantse na gama kai kwaleluwar hakuri, wallahi ko a mana aure ko kuma na sace ki mu gudu a daura mana aure. Dan na rantse ki koyi hakuri dan akan ki zan Baje tuzurcina, Yawwa na dai gaya miki, gwara tun wuri ki koyawa kanki yadda zaki karbe ni hannu bibbiyu."

Share shi nayi na dauki hijab dina, tare da cewa.
"Don Allah muje!"
Janyo ni yayi jikin shi muka fada gadon, yana kallon fuskana, tare da shafa bakina, yana faɗin.

"Baby Love, don Allah kizo mu koma gida. Ina sonki ban dauko ki nan dan na miki wani abu ba, ma kawo ki ne dan na ganki kuma na baki hakuri da abinda ya faru.

.... Nasan nayi laifi ko? Na yarda nayi laifi amma baby matakin da kika dauka yayi min tsauri, kalle ni dan Maraya, amma na kasa zama. A kasa tsaye, Baby bani da lafiya. Amma gani a gabanki na kuma zo domin ki, please kome ya wuce."

Hannun shi na rike tare da kwantar da kaina, na kuma lumshe idanuna nayi..
"Baby baki ce kome ba?"
Murza zoben shi nayi cikin nutsuwa, tare da cewa.
"Ya Aalim! Ka daina bani Hakuri, nima nayi maka rashin kunya tunda ban fahimci waye kai ba."

Rufe min baƙi yayi da hannun shi..
"Ni don Allah bar haka."

Mikewa nayi ina gyara zaman hijab dina.
"Zan koma gida shida ga har da kwata. Kuma"

"Muje!"
Ya mike tare da rike hannuna, muka fito, har gurin motar shi. A hankali muke tafiya, kafin mu isa gida yayi min sayayya, sannan muka nufi barrack.

......
Tun daga lokacin da suka ga bata dawo ba, aka kuma duba makarantar aka ce tafi to, ran Atiku ya b'aci sosai. Har yake gayawa Asp, nan aka zuba Yan sanda a bakin kofar shigowa barrack din.

Da suka zo shiga, aka ganta nan suka bashi damar shiga cikin barrack din. Har kofar gida na nuna mishi, Ya Atiku da Asp suna tsaye.
Ta fito rike da Alqur'aninta, shima ya fito, rike da laidojin da yayi mata sayayya, takowar Ya Atiku ya sani komawa bayan Ya Aalim.
"Zo ki wuce!"
"Don Allah kayi hakuri."
"Nace kizo ki wuce."
"Ai tace kayi hakuri, kuma ko a lahira wani na cin albarkacin wani, baby Love zoki wuce."

Amsar Alqur'anin yayi ya saka a cikin wani laida, sannan ya mika min kayan.
"Ba zata shigar min dashi gidana ba."

Kallon shi Aalim yayi.
"Zata shigar da shi mana, kuma ka saka ido ka gani, wuce muje." Cikin zafin kai ya tawo zai kwace kayan ya zubda.

"Kai karka damu kanka, ka daina Ove acting, Sidrah shige gida." A hankali na wuce cikin gida.
"Ki kula akwai kome a cikin kayan."

Ina shiga cikin gidan ya juya zai tafi suka rike mishi wuyar rigar shi, juyawa yayi sannan yace musu.
"Ku sake min rigana, idan kuka min wani abu, kai tsaye duniya zata fahimci girman Soyayyar da nake mata, kafin nan da awa daya. Zancen zai zama na manyan dan haka, a bani bar ni na koma. Gobe zan zo na dauki Sidrah mu koma gida. Karka damu amma ka tuna karka rike wanin Allah, dan ba zai biya maka bukatar da Allah zai biya maka ba."

Yana gama fadar haka yaja motar shi ya bar su tsaye.
"Me baturen nan take nufi? Ko ka manta abinda kake bukata ne? Ka bar ni na saka a gyara mishi gurin zama a daren nan"

"Ita zan iya lankwasa ta, shi kuma ba zan iya ba, koda nayi wani abu zan ji kunya daga baya."
"Amma kasan ina sonta?"

"Karka damu yallabai yau zan yi magana da mutanen gida."

Daga haka suka yi sallama, yana shigowa gida, ya samu ina sallar, zama yayi har na idar.
"Wato ban isa nace miki ga abinda zaki yi bako? Me yasa ban isa dake ba? Shine da yazo kika bishi gaki ishashiya ko?"

"Yaya don Allah ka bar ni dashi, ka bar min rayuwa na huta ni shine nake so, don Allah karka shiga tsakanin mu.

Allah ya gani ina son Ya Aalim, idan aka matsamin na auri wani wallahi guduwa zanyi!"

Na fada cikin kuka.
"Gaskiya ka kyaleta tayi rayuwarta da wanda take so, ina dalili me yasa baka nima mishi Saratu ba? Sai ita da bata da kowa bata da wanda zai tsaya mata sai shi.

...idan kayi haka baka yiwa kanka Adalci ba, sabida maraicinta, a rayuwar ta mijin da zai kula da ita take nima ba wanda zai hana rayuwar ta sukuni ba, don Allah ka kabar yarinyar ta.."
"Kece dama kuke zugata? Kece kike mata pamfo karta bi abinda nake so?"

... "Duk yadda ka dauka haka ne, Sidrah bar kuka gobe zaki bar garin nan na kira Baba na gaya mishi yace ki koma gida, zai yi magana da Aalim din, ku tawo tare."

Sunkuyar da kaina nayi, ina share kwalla.
Haka suka fita suka kwaure da fada, karshe naji sun yi shiru, ashe waya yake, ita kuma tazo muka hada kayana, a daren Ranar. Na raba abubuwan da muka zo dashi na bata, wanda zai lalace na cinye. Wanda kuma zai kai da safe na bari sabida na san ba mamaki tafiyar safiya zamu yi.

Dakyar nayi barci, dake ban bude ledar da na saka Alqur'ani ba, sai da asuba. Naga sabuwar Iphone pro 11ne, shiru nayi,ina juya wayar tare da kallon yadda yake. Sakawa nayi a cikin hand bag dina, na shiga nayi wanka da alola, nazo na gabatar da sallar nafilla kafin na daura sallar asuba.
Ina idarwa naji dirin mota a kofar gidan, yana buga kofar gidan, Ya Atiku ya bude mishi ban san me ya faru ba, naji kuma sun kaure da hira, a hankali na shirya cikin atamfar English Koriya me ratsin fari da baki riga da zani, na dauki farin mayafi hijab na saka sannan na fito, mika min kofi Aunty Mariya tayi, kunun gyada tayi na garin gero. Gashi ta zuba tsabar gero. Komawa daki nayi ina sha ina lumshe idanuna, sabida dad'i da gardin gyad'a. Ina gamawa ta zuba min dankalin turawa da tasoya, a wani rabo. Sannan na fito ina dariya nace mata..
"Allah na koshi da kunun!"
"Kanwata kodai ganin Lover."

"Kai ina!"
Haka tai ta tsokana ta,ina dariya. Ina fitowa falon na gaishe da Yaya, sannan na sunkuyar da

kaina, ina wasa da zoben hannuna.
"Baby Love, good Morning!"
Wani irin kunya ce ta kamani nace mishi..
"Lafiya!"

Mik'ewa yayi rike da wani flast, ga mug din da ya sha kunun,.ya kalli matar Ya Atiku.
"Madam da fatan kin koya mata irin wannan abincin, dan ina son shi sosai."

Dariya tayi sannan tace mishi.
"Gwana ce a girki bata bukatar koyarwar ta, amma nasan zata iya abinda yafi wannan dad'i."

Jan kumatuna yayi sannan yace.
"Kar kanki ya fashe ki fara jin girman kai dan ance ke na.."

Dariya duk suka saka, ya wani b'ata fuska tare da cewa.
"Allah sirikina, ni fa dan nayi rigima da mace na zai hanani ta girka min abinda zan cika cikina ba, domin bana son almubazzaranci, fadar mu daban abincin mu daban."

Dariya suka kuma saka mishi murmushi nayi sannan muka fito dashi, juyawa yayi ya amshi jakar hannuna, ya fita dashi. Sannan ya kuma dawowa ya amshi hand bag dina, muka fito gaba daya, har gurin motar da ya kawo shi muka shiga, daga nan muka yi musu sallama.

Tunda muka nufi hanyar airport, yake kallona tare da jan iska da hancin shi.
"Karki kuma saka wannan turaren sai a gidana."

"Toh!"
"Baby Love! Kinyi kyau fa?"
"Kai ma haka,"
"Baby Love!"
"Na'am!"
"Baby Love!"
Kallon shi nayi tare da cewa.
"Ba gani ba!"
"Ji nake kamar na boye ki"
"Zaka ma fito dani!"
"Baby Love!"
"Don Allah kayi hakuri da kiran nan"
"Ai ranar farkon mu, haka zan baki labarina, tare da kiran sunanki. Washi gari kuma"

Kafta min ido yayi, wani kunya ta kamani, ban san lokacin da na juya mishi baya ba, domin na fahimci babu digon kunyar a tare dashi, haka yayi ta jana da hira, ga kuma driven motar yana jin mu, saukinta kasa kasa yake maganar idan ba haka ba, toh da anji kunya.

..  kuma shi ba kunyar ce ta ishe shi ba, dan haka yayita b'aro min yadda zai yi shagalin shi.... Sorry.....🤣🙄🤔 Yacin kwamens dinku yayi kasa.... Mu jone da 5 read more
[11/21, 8:48 PM] Anum Muhammad Bello❤️: #The Tranquility
Sorry for The typing error
Hannun shi a cikin nawa, muka nufi airport, har aka sauke min kayana, muka zo wuccewa aka hana shi shiga, Sabida ya dauko flast, na karfe yana ganin haka ya mika musu suka duba suka ga kunu ce, sannan aka bashi ya wuce. Bayan ya shige. Muka zauna jiran jirgin da zai sauka a kano, daga nan mu wuce dutse ina jin yana waya da wani yaron shi nafi'u.
Tunda muka shiga jirgin ya riko hannuna, kaina a kafad'arshi.
"Da alamu baki yi barci ba? Baby Love ki kwantar da hankalinki, Insha Allah lokaci na zuba a jikina zaki kwana."

Zare hannuna nayi tare da jiyar da kaina, sanin belt yayi tare da kallona yana cewa.
"Kin san Allah! Zaki daina fita ne idan akayi bikin mu, domin gaskiya akanki ina da kazamin kishi. Sannan ina da zafi akan mata na, don Allah ki daina saka farin hijab, pink, da purple. Da mint color,  green da light blue.

Sabida yana fito min da botirina waje, wallahi muna shigowa na ga wasu maza suna kallonki, Ni nayi kamar zuciyata zata fashe please taimake ni ki daina shigar kayan da zasu na zagina."

Kwantar da kaina nayi a kafad'arshi, tare da damke hannun shi, ina kallon zoben mu.
"Babu wani a rayuwata sai kai, me yasa kake shiru yardar da nayi maka, ban hanaka kishi ba. Don Allah karka zama me kazamin kishi, gudun kar ya za me mana kalubale don Allah."

Daura kanshi yayi a kaina tare da cewa.
"Insha Allah,.idanuna basu ganin da zuciyata suke ganinki bana tunanin haka zai kawo mana matsala, Insha Allah ni dake har abada."

"Amin!" Nace a sanyayye, domin na soma jin barci, a hankali muka bar zancen na lumshe idanuna, tare da mai da kaina kafad'arshi, ina sauke numfashi. Idan tare dashi na kanji kwarin gwiwa, saboda ina jin shi kamar garkuwa ne a gare ni,  shi yasa naji zafin abin da yayi min na rasa wani duk wani kwarin gwiwa ta, lokacin da Bama tare a yanzun kuwa ina jin shi sosai a raina.

Ban san lokacin da muka isa ba, sai dai ya tab'a ni akan na farka mun iso, a hankali na bude idanuna tare da kallon mutane na barin jirgin. Murmushi nayi tare da mik'ewa na dauki yar jakata, muna fita shima ya dauki babbar jakar.

Muna fitowa waje, muka sami nafi'u, na jiran mu daga nan muka shiga motar bayan ya gaishe da Ya Aalim, muna tafiya yana kallon yadda nake ta hamma, mai da min kaina yayi kan kafad'arshi, na cigaba da barci.

Dake motar ta musamman ce har muka iso garin dutse, sai da naji yana cewa.

" Ka kai mu gida, gobe zamu wuce Hadeja."

"A'ah kai ni hadeja wallahi Baba zai min faɗa."
"Zai mana fada dai ko? Dan bana son ayi miki ke ɗaya, muje ki gaida Mom da.."
"Don Allah! Ka kai ni gida babu kima a haka zasu ga rashin kamewa na,"
"Mu wuce hadeja!"

Ya faɗa tare da rike hannuna, muna tafiya amma na lura kamar bai ji dadin yadda nayi mishi ba, sai na kwantar da kai na da murya na, na shiga bashi hakuri. Tare da gaya mishi muhimmancin kamun kai. Tare da nuna mishi haka da zai yi ya sabawa Al'adar Hausawa. Zasu na min kallon mara kamun kai.

Can kuma naji yace.
"Kuma haka ne fa? Muje."
Haka ya kai ni gida, kafin mu isa ya saya min kayan ciye ciye, wayata kuwa ya cika min da kuɗi, ya gyara min kome har muka isa gidan, Da gudu Saratu ta fito lokacin da aka ce gamu nan, rungume juna muka yi, sannan muka shiga cikin gidan na manta dashi har mun kusan shegewa yace min.
"Ina zan baza miki shanyar, kafin ya bushe."
Kunshe dariya nayi na dawo gaban shi tare da sunkuyar da kaina.
"Don Allah bani Little hug"
Kallon yadda mutane suke zuba mana ido ya sani shigewa da gudu cikin gidan tare da sake dariya, cusa hannun shi yayi cikin gashin kanshi tare da yamutsawa, ya sake murmushi ya ɗan kalle ni. Girgiza kai yayi tare da lashe bushashen bakin shi yayi wucewar shi mota bayan ya bawa yara kayana.

Tunda na shiga gidan, ake zuwa kallona, haka nabi kofa kofa ina ina gaishe su, a shake suke amsa min, basa gabana..ina shiga shashin mu, na gaida Sahiyah wacce bata nan aka je aka kirata nazo. Kallon tsoro take min daga sama har kasa, Inna Lantana kuwa bakinta sai cewa yake.
"Sannu Hajiya Sidrah."

Zama nayi a taburman da Saratu ta shimfid'a min, na zauna muna kuma gaisawa. Tace min.
"Bari a kawo miki abinci."
"A'a barshi akwai chips a take away, bani na ci."
Miko min jakar tayi, ta kawo min ruwa na fara ci, kuma hira. Kar'ar wayar dake jakata yayi na ciro.
"Baby Love! Na manta kunu na a jakarki kamar na dawo na dauka."

"Hhh! Man yanzun zai shige cikin babban birnin cikina!" Na gaya mishi haka,

"Kina nufin shanye wa zaki yi?"

"Ga zahiri!"
"Baby duk ranar da kika shiga hannuna, zan nuna miki rashin kirki fa."
"Ai dama baka da kirki ne? Toh Man idan ka kamani, na san kyautar da zan maka, bye ina cin abinci ne!"
Na kashe wayar ina dariya, sai bina suke da kallo, murmushi nayi sannan na cigaba da cin abincin, yana daga cikin dalilin da Yasaka naso abincin da yasaya min.
Akwai wani abun da yake damun mutane, da zaran na zauna na ci abincin da aka kawo min ko na gidan, sai ya zamin gori.

Shi yasa da ya fara saya min kamar su, chocolat da waffer Ban hana shi ba, sabida nice ya taimaka, muna gama cin Abincin, Har zuwa lokacin ba ayi wanke wanke ba, fitowa nayi na gabatar da alola, sannan na koma nayi sallah, ina idarwa na Kwanta muna hira da Saratu take bani labarin abinda su Inna Lantana suke shiryawa akan My Man.

Dariya ta bani, nayi ta yi ina kallonta. Domin ban tsammaci zan ji haka ba kawai na zuba mata ido. Sannan nace mata.
"Ya Aalim bai min Alqawarin zama dani, Ni daya ba. Amma nasan idan kika ga ya zaune da mata biyu toh ki kaddara haka Ubangiji ya ƙaddara mana."

Shiru nayi kafin na kuma gyara kwanciya ta, ina jinjina qarfin halin su, kawai na share na cigaba da barcina.
**Dutse
"Wai ni! Hajiya taya zamu zuba ido sai Abinda Yaran Hauwa suka bawa mutane, me suka mai damu ne? Na gaji da abinda Alhaji yake, kome ya tattara ya bawa Aalim da Aamil!"

"Hmm! Ina kallon shi dai! Karki damu, Zamu dauki mataki akan su baki daya. Bari mu gama samun damar shiga jikin su, na gaji sun mai da min da yara bayi, sai yadda."shiru suka yi sakamakon shigowar Aalim gidan, kallon su yayi yaga sunata aikin su. Har ya shiga gurin Ummi ya gaisheta. Sannan ya leka dakin Hajiya, bata mishi magana ba, dan ta zaci Aamil ne d'azun suka gama fada dashi ya fita yana mita, kallon shi tayi sannan ta buga tsaki yace mishi.

"Sakarai! Sha-sha-sha."
Table baki yayi sannan ya fita ya bar mata d'akin, bayan ya dire mata ledar kilishi ya fita abinshi. Sai da ta bude ledar ta b'allo kilishin ta wurga a baki, sannan ta gyada kai tana faɗin.

"Duk abinda zaku yi ba zai sani son uwarku ba, dan banza Jikar mangofak." Jin motsin Ya Hindatu ya sa ta boye laidar tana b'ata rai.

Daga dakin gurin Mom ya shiga ya same ta, zaune ita da Aamil zama yayi yana kallon furar da Aamil yake sha, yace mishi.
"Bani nasha!"
Mika mishi yayi tare da fara sha.
"Bakin ka da magana ko dai Sidrah ta dawo hadeja ne?"

"Ban da haka zaka ganshi ne ba ya zabi can da nan ba"

" A'a Mom! Taya zanyi laifi kuma naki amsar laifina, kawai dai ina son na amshi laifina ne, kuma mun dawo ban jima ba da na kaita gida na dawo nan!"

"Don Allah ka taimake ni, har yau banje gidan su Nadrah ba, ban san me zan gaya mata ba, wannan shine lokacin da zan fara soyayya. Kuma ya kamata ya zama me ma'ana, kamar kai da Sidrah." Inji Aamil

"Ina babu inda zani, dan daudu fa? Yau kai ne kake niman taimakon dan daudu. Jarumi yaje ya nimawa kan shi soyayya ba dai da taimako na ba" inji Aalim.

"Don Allah taimaka Jarumin Sidrah, taimakawa dan kaninka Husain dinka, idan na kuma tsokanarka." Inji Aamil,

Shiru yayi kamar baya gurin sai da Mom ta saka baki, kafin ya kalle shi.
"Shi kenan, zan je Amma dole ni zan tuka motar. Kai na ma fasa jaka nimo jarumi irin ka, ya raka ka."

"Don Allah kayi hakuri!"
"Gaskiya ba zanje ba, ka nimo wanda ba lurasari  ba." Ya faɗa tare da kurb'an  furar shi.
"Yawwa Abba don Allah ka saka baki ya raka ni!"

"A'a nima ina bayan shi baka ga yadda yayi fadar niman soyayyar shi ba, toh kai me zai hana ka gwada sa'arka!" Inji Abban su.

"Abba! Soyayya bata da Jarumin ta, Asalinta ragone. Bata da karfi, haka nima nake a kome zan iya nuna ikona da karfina akai ban da soyayya, da zaran naji sunan Nadrah zuciyata bugawa take. Don Allah kace ya rakani."

Dariya ne ya kama su, tare da nuna shi. Dakyar suka lallaba Aalim ya amince ya raka shi. Tun da suka amince sannan ya mike, tare da cewa..
"Kayi maza ka shirya, amma ka samu kaya irin nawa domin mu rikita ta."

Gyada mishi kai yayi tare da cewa.
"Eh zan saka tare da kome irin naka, kome zai zama d'aya."

Murmushi yayi sannan yace.
"Karka damu twins."
Rungume juna  suka yi, cikin wani irin kaunar junan su.
**
Guess housa.
"Don Allah ka rage min wallahi marata ta cika dam, kamar zata fashe ka taimaka min don

Allah!"

Girgiza mata kai yayi sanan ya dauki wani kwaya ya bata a lemo tasha, sannan yace mata. "Dole kiyi hakuri! Na fison ki fara da mijinki, kafin mu bude shafin mu. Bana son haduwa na dake"

Gyda Nadrah tayi tare da rike mararta kwalla na zuba mata, bai tab'a ta ba....

Kuyi hakuri 🙏🏽🤭
[11/22, 8:31 PM] Anum Muhammad Bello❤️: The Clash.

Shiryawa suka yi cikin kananan kaya, Aamil ya saka Black jeans da Whiter sleeve shirt. Sanann ya daura jacket black, ya gyara gashin shi ya kwanta, asalin shirga Aalim kenan.

Shi kuma Aalim, yayi shigar Aamil, inda yayi pop da gashin sa, tare da gyara shi. Sannan ya sanya kaftani da wata farin material na maza, wacce aka mata bankole. Cream wandon kuma brown. Sannan ya dauki hular zanna bukar ya coka agaban goshin sa, sannan ya dauki wata vanne ya yafa a wuyar shi tare da manna wata sunglass blue black, tare da gyara zaman hular shi suka fito.

(OMG.... Ina Candy taga Crushing guys, Aamil ko Aamil, Ango na gaba dai ba dai Na Sidrah Yaya Aamil, Na gaishe da Angon Nadrah Yaya Abdus Samad, Na gaida Mazajen Mom da Ummu! Shalelen Abba😎😍😘😠naji wata tace kirarin yayi mata😏)

.... Banbanci takalmin su, Aamil Cover shoe ya saka, yayi da Aalim ya saka Saddle,.haka suka fito tsakar gidan, babu wanda ya iya iya banbance su, saboda kamar da fito tsakanin su, sannan Uwa Uba, suna sanye da shigar da kowanne su yake yi.

A hankali suka fito Aamil ya cillawa Aalim key motar shi, suka fita daga harabar gidan bayansu shiga motar, suka nufi gidan su Nadrah. A hankali Aalim yake jan motar, kamar mai koyar motar. Kallon wayar shi yake wanda yake blank, murmushi yayi bayan ya hango alamar shigowar sakon Sidrah.

_I truly miss you and it's sad that all I can do every time I feeling the loneliness is to stare at your photos and then smile at the funny memories we share_

Murmushi ya sake tare da lumshe idanun shi, ya dafa kirjin shi, da gayya ya sake kan motar. "Dan girman Ubangiji ka rufa min asiri, rike kan motar kaji."

Murmushi ya sake tare da gyara zaman shi, sannan ya kuma bawa motar wuta, ya kashe ido daya wa Aamil.
"She sent love message for me! Baby Love!"

"Mara mutunci, shine bari ka zuba ni a rami, koma gefen hanya, dan na lura farfadiyar soyayya ta kama la, don Allah sauke mu, na amshi tukin." Inji Aamil,

Murmushi Yayi tare da jan motar a guje, har ya isa gidan yana wani lumshe idanun shi sauri yake ya bata amsa.

(Wato akafin ayi aure! Ji ake kamar a cinye juna da soyayya After marriage sai kaji kamar za a cinye juna da rigima 🤣)

Suna shiga gidan ya jingina da jikin kujeran ya shiga maimaita sakon, ya fi sau goma. Kafin ya fara niman wani wanda yasan kunya kawai ya isheta.

*Never knew I could feel like this, like I never saw the sky before. Want to lose myself in your kiss, everyday I love you more and more.*

Yana tura mata ya sake murmushi, yana jiran sakonta, ya kuma ga bata turo mishi ba, shine yayi kundublar kiranta.
"Baby Love!"
"Hmm!"
"Babu magana ne?"
"Hmm!"
"Kawai dan nace kiss shine bakinki ya mutu, toh baby love. Idan kuma ranar da kika zo a matar da nake aure fa?"

Kashe wayar tayi, ya fashe da dariya tare da dukan motar, kallon mahaukaci Aamil yayi mishi, tab'e baki yayi sannan yace mishi.
"Kazo gyara min soyayyata ne ko kazo kashe min ita ne?"

"Bani da lokacin ka, kawai mu tafi. Dan naga budurwan taka, mulki take ji, da baza ta fito ba." Aalim ya fada tare da kallon kofar shiga cikin gidan, bude motar Aamil yayi tare da zuwa ya bude na Aalim, yace mishi.
"Maza fito"
"Toh Ubana! Gata nan ma ai,"
"Don Allah!?"
"Waiga mana,"
"A'a kunya nake ji"
Zaro idanu Aalim yayi cikin baƙin ciki yace.
"Allah ya isa wa kunya, ka cutar da kunya."

Wani murmuasawa yayi tare da rike hannun mota, shi kuwa Aalim ya zuba mata ido, har ta shigo motar, tana murmushi cike da kunya.
"Ina wuni Ya Aamil?"
"Lafiya!"

Kallon Aamil tayi sannan tace mishi.
"Ya Aalim ina wuni? Ya baby Sidrah?"

"Lafiya lau! Ya kike?"
"Alhamdulillah!"
"Masha Allah!"
Duk bata fahimci da Aamil take ba, dan haka ita tunaninta da Aalim ne.
"Ko zamu shiga daga ciki ne!"
Juyawa yayi tare da kallon Aamil, d'age mishi gira yayi shi kuma ta saka hannu a baki alamar yaji kunya, fitowa yayi suka nufi cikin gidan.
Duk da Alhaji Abubakar ya mata bayani akan su, gabaki daya ta rude, ta kasa fahimtar Waye Aamil waye Allison, kara kallon su tayi suka tafiya suna dariya tare da hira cikin jin dadi, juyawa tai cikin nutsuwa, tana murmushin mugunta, yadda zata tarwatsa wannan yanayina, sai ta lalata wannan farin cikin da wannan soyayyar da take gani a kwarya idanun su, sai ta mai dashi mafi girman k'iyayyar da aba tab'a samun masu irin shi ba.

Yarda da ke tsakaninsu sai ta mai da shi, cin amanar juna, sai ta mai da kowannen su abokan gaban juna, yadda kowa sai ya tsorata da yanayin su. Ta rantse da Allah, sai ta taimakawa Alhaji Abubakar ya lalata kome nasu. Sannan ta koma mallake kowannen su, yadda zata fasa Sidrah a ruwan sanyi. Yadda aka hanata auren Aalim, haka take son ta wayi gari taji ta hana Sidrah kwanciyar hankali a rayuwar aurenta.

"Ke ki kula zaki buge." Da sauri ta kalli gabanta tana sauke ajiyar zuciya. Cike da mamaki, taya akayi ta kusan bugawa da karfin settlight, haka.
"Nagode! Ba karamin ciwo zanji ba." Ta faɗa tana kallon Aamil, hankalin Aalim yana ga wayar shi. Yace.
"A duk lokacin da ka shirya alamomin tarar damuwa, sai Allah ya makantar da ganinka, gaki ga sahibi mai buzu buzu!"

Kallon shi Aamil yayi cikin damuwa, kar ya bata mishi tafiyar shi, har cikin gidan su. Takai su. Inda ta ajiye su a falon Daddy, sannan ta kuma fita ta shiga kawo musu abinda zasu ci.

Kallon juna suka yi shida Aalim ya nuna mishi abincin da ido, girgiza kai yayi tare da cewa.
"A'a!"
Bayan ta gama ta zauna daga nesa dasu. Kallon ta Aalim yayi sannan yace mata.
"Ya karatu?"
"Mun kusan gamawa, Insha ALLAH."

"Hmm!" Inji Aamil, duk sai ya diririce,rike hannun shi Aalim yayi tare da jinjina mishi kai, Alamun karka damu..

Rike d'an uwan yayi alamar yayi mata magana shine.
"Hmm! Ni kam na kasa banbance ku! Waye Ya Aamil? Waye kuma Ya Aalim?"

Mikewa Aalim yayi lokacin da wayar shi take kara, ya saka a kunne yace.
"Baby Love! Ina zuwa!"
Ya fita ya basu guri, ganin yadda Aamil din yake ta sake murmushi yasata fahimtar shine.

Shi kam baban soyayya, yana fita ban da hira da babyn shi babu abinda yake, ya ma manta inda yake asalima, ji yaƙe kamar dan aka wanzar da ranar, sai ji kake turanci yana tashi, a sanyayye. Kusan ma shine mai hirar. A bangaren Sidrah bin shi kawai take da eh ko a'a, har dai suka yi dogon hira, fitowar Aamil da Nadrah yasa shi kashe wayar tare da tura mata sakon.
_Being with you feels so perfect. I've never felt anything like this before in my life, ever! I love you!_

har ya ajiye wayar dan Aamil ya fitowa da Nadrah abinda ya kawo mata, sai yaji karar sakon Sidrah.
*I never knew life could be so beautiful until I met you. I love you.*

Kamar ya fasa ihu, da yaga sakonta, ya karanta yafi sau goma, ya karanta ya kuma karantarwa, sai da Aamil ya fauce wayar, yana kallon shi.
"Ko ka tambaye ni? Ya muka yi da ita?"

"Da naga kun fito da farin ciki ya sani fahimtar  ko kun gama ne" ya faɗa a sanyayye,
Juyar da kai yayi tare da kallon wajen motar, lokacin da Aalim ke barin gidan.
"Tace zata aure ni ne bisa umarnin Iyaye amma Mom ɗinta bata son auren,.kuma tana goyan bayan mahaifiyar ta, amma ba zata iya bijirewa mahaifinta ba!"

Taka motar yayi tare da kashe motar, ya fita daga cikin motar, bai saurari Aamil ba ya rufe motar yadda ba zai iya fita ba.

Ya shige cikin gidan, tare da sallama. Fitowa Hajiya Ubaidah tayi tana kallon shi, tana faɗin.
"Aamil, shigo mana!"
"Aalim ne! Nazo gurinku ne ke da Nadrah"
"Ok mu shiga daga ciki."

Shiga yayi suka zauna a falon, kawo mishi abin sha akayi ya girgiza kai tare da cewa.
"Ya ishe ni!"

Sai da ya nutsu, tare da kai hannun shi biyu ya hade a fuskar shi, kafin yace mata.
"Ni ne Hassan din Aamil! Shakikin shi! Abokin Haihuwar shi. Tagwayen shi! Yan biyun shi."
Shiru yayi tare da lumshe idanun shi, tare da kai hannun shi bayan ya ja wani irin iska.
"Wani lokaci muna tare da abinda mu so, amma bamu fahimtar k'iyayyar shi, sai wani al'amari ya faru.

Yau nazo ne badan kai na ba, badan na isa ba, ba dan ni da Hussain kowa bane, mun zo

niman soyayyar Yarki tare da niman sa Albarkanki! Ba dan kome ba, sai dan kina da ikon ki hanata karban Aamil a matsayin abokin rayuwarta kuma haka ya zauna dai dai, ke uwa ce nasani kina gudun halin Aamil da ma mutanen gidan mu, Hajiya na rantse da Allah, Wanda Babu wani abin bautawa da gaskiya sai shi musu bazan tab'a barin ayi da ita ba.

Balle kuma d'an uwana ba zai tab'a cutar da Yarki ba, Hajiya Yarki gata nan, Insha Allah ba zan tab'a barin wani ya cutar da ita balle ya sami damar koyi da wani ba, ki tuna Yaron da ya taso babu tausayawar uwa babu. Dumin uwa a tare dashi taya zai fahimci goben shi?

.... Ina da yakinin Nadrah zata iya kawo wani sauyi da baki ba zai iya fahimtar haka ba, ki bawa Kanina dan uwana Yarki na miki alkawarin  da Yardan Ubangiji ba zata zubda kwalla na bakin cikin dan uwana ba, zai rike ta da amana, idan wani abu zai fito toh wallahi sai dai daga wani gurin na dai daga gurin shi ba, na yarda da dan uwana."

Sannan ya zuba gwiwar shi a ƙasa tare da rokon Hajiya Ubaidah ta saka baki akan Soyayyar Nadrah da Aamil.

Jikinta ne yayi mugun sanyi, tana ji a wani gurin bata tab'a sanin cewa yarta zata kawo wanda zai nemi a bawa dan uwan shi aurenta ba. Mikewa yayi sannan ya isa bakin kofa.

"Shi rayuwar aure babu tilastawa, ganin damar kane ka zauna da abokin tarayyarka, ganin damar kane kace baka yi, amma kafin a sami namijin da zai miki so irin na Aamil sai Kinyi da gaske, kafin ki samu siriki irin Aamil zaki sha wahala."

Daga haka yayi ficewar shi, ya barsu cikin nazari, tabbas wannan zance da yayi gaskiya ne, amma ita bata son damuwar da zata lalata zumuncin da aka gina shi shekaru da dama, kallon Nadrah tayi sannan tace mata.
"Me kika gani da abinda ya nima?"
"Mommy duk abinda kike ce shi kenan, yadda take maganar zaka dauka ta Allah ce, nan kuwa kamar ta tashi ta buga tsalle da ihu ne.

"Shi kenan, jeki zamu yi magana da Daddy dinki." Gyada kai tayi tare da barin falon ta shiga daki, saka key tayi sannan tace.
"Wow! Zan ci uban kowa daya bayan daya. Sai na buwaye ku!"

.......
Yana fita ya same Aamil ya buga tagumi, shiga motar yayi bai ce mishi kome, ba.

"Kasan Yarinyar ka ta fahimci cewa ba kai ne ba, ka bar wayar ta kira ban dauka ba, ya dame ni shine na dauka, amma yarinyar nan ina dauka tace min.
"Ina me wayar?"
Sai kashe kiran nayi ga uban sakon da tayi ta turo maka"

Amsar wayar yayi tare da duba sakwanin.

*Being with you is like having every single one of my wishes come true Dashing man♥*

Murmushi yayi sannan ya tura mata da wannan.
_I'll lend you my shoulder for you to cry on, my ears to listen to, my hand for you to hold, my feet to walk with you, but I can't lend you my heart coz it already belongs to you. Killer queen_
Kuyi maneji...
#Mai_Dambu...
[11/23, 9:27 AM] Anum Muhammad Bello❤️: The Engagement.

Yana lura da Aalim yaki yace mishi kome akan abinda ya shiga yayi a cikin gidan, sai ma kara share batun yayi.

Shima a nashi ra'ayin ba zai gayawa Aamil abinda ya faru ba, ya san halin shi yanzun sai ya iya haukace musu, shi kuma abinda baya so kenan, dan haka ya share zancen kamar bai san Aamil din yana son ji daga gare shi ba,

Matsalar su, kowannen su zai ba zai iya jure damuwan dan uwan shi ba, musamman Aalim baya kaunar abinda zai b'atawa Aamil rai, asalima tattalin farin cikin shi yake, shi yasa yaji zafin abinda Nadrah tace, kuma yayi alƙawarin matukar bata yarda da shi ba,sai ya nimo mishi wacce ta fita haɗuwa.
*
Bayan kwana biyu da zuwan su gidan su Nadrah, suka kuma shiryawa suna hira kamar yadda suka yi a wancan lokacin, suka nufi Hadeja. Da misalin ƙarfe biyar na yammacin ranar.

Har cikin gidan suka shiga, tare da gaida mutanen gidan, tana jin shi, suna magana da Baba Haliru amma taki ko lekowa, haka suka fita waje, a cikin dakin kuwa shiryawa take, a nutse tare da gyara jikinta.

Farin hoda ta shafa, tare da murza mai a giranta, sannan ta saka kwalli a idanunta, bata shafa wani lip stick ba, kawai ta shafa glossslip, tana gamawa ta dauko wata Arabia gown Golden, ta saka tare da gyara daurin igiyar shi a bayan ta.

Tana gamawa ta dauki turb baki na karamiski ta saka, sannan ta nade kanta da mayafi bayan ta gama, sannan ta dauko plat shoe ta saka, sannan ta juya ta kalli Saratu, sake baki tayi tace mata.
"Wallahi ban da kece sai nace ba Sidrah da na sani bace a gaba na, kin koma kalar larabawa."

Murmushi nayi sannan nace mata.
"Zo muje don Allah!"

A hankali ta mike tare da murza turarruka na, sannan ta dauki tiren kayan sha da muka hada musu tare da pepper fish, muka fito dasu. Dan har kasuwa muka shiga inda muka sayo kayan da zamu yi amfani da shi, muna fitowa na hango su shi yana cikin motar, Ya Aamil yana tsaye.

Kallon Saratu nayi nace mata.
"Zaki iya gane su?"
"A'a wallahi, wannan yanayin ba zan iya fahimtar kome ba."
Muna zuwa na wuce shi, na zubawa ya Aalim ido.
"Fito!"
Nace mishi, ai kuwa yana fitowa. Na ganni yar cakwai a gaban shi, baya nayi da hannu na, na rike su tare da dan juyawa ina niman yadda zan rena mishi hankali, irin abin nan da yara suke, idan suna son abu. Su kai hannun su bayan su, suna dan moving kaɗan kaɗan.
"Ya Aalim! Koma abinka!"

Har ya shige zai zauna nace mishi.
"A'a ba nan ba nan!"
Kallona yayi, sannan yace.
"Ina?"
Bayan mota na nuna mishi, tare da d'age mishi gira. Gyada kai yayi sannan ya fita, ya shiga bayan motar, yana kallona.

Har ya shiga bayan, sannan na amshi abin da muka kawo na saka a gurin shi, na kalli Ya Aamil, nace mishi.
"Shiga ku ci abincin kazamai!"
Na fadi haka kaina a sunkuye, ina wasa da hannuna.

Shiru yayi sannan yace min.
"Toh Matar Hassan!"
Da sauri na d'ago kai na, murmushi yayi min sannan ya shiga motar. Mu kuma muka juya na turawa ya Aalim sakon idan kun gama ka min magana,

Tunda suka shiga motar, kamshi kifin ya cika musu hanci, murmushi suka yi bayan sun kalli juna, suka fara ci. Baka jin kome. Sai karan spoon, ana kwashe girkin Yar kwaila.
"Allison! Allah yasa mata na ta iya girki irin Sidrah! Da na warke, domin ko waje bazan fito ba, kai Sallah ma zan koma yi ne a cikin gidana."

"Toh Mr Alben, maza kwashi garan bakar mace!" Suka kwashe da dariya, suna gamawa. Suka fito tare da wanke bakin su da hannun su, Aalim yace.
"Baby Love! Kinci na biya wannan girkin domin na ji dadin shi."

"Gaskiya girkin ya hadu ba laifi." Tura mata sako yayi da cewa.
_You are the only girl in the whole world who can love me like my lover, support me like my friend and motivate me like my boss. I love you. Strawberry_

Yana turawa ya zubawa kofar gidan idanu.
Karar sakon da yaji tare da dubawa wanda yayi dai-dai da fitowar ta.
*Be I richer or poorer, till death takes us apart, I will give you great portions of my soul and my

heart. My tiger toes*

Kura min ido yayi, sannan ya nad'e hannun shi a kirji, cikin nutsuwa na isa gare shi tare da sunkuyar da kaina.
"My Sugar puss!" Da sauri na d'ago kaina, tare da rufe fuskana ina dariya cike da kunya. Takowa yayi gabana yana faɗin.
"Na rantse da Allah, sai na mai dake mara kunya, sai na sanya ki kin zama tantiriyar mara kunya, yadda babu wanda ya isa ya shigo gidan mu, ki ji kunyar shi matukar ba Ummi da Mom ko Abba bane, sai ko Twin bro, ke Candybar dina ce, dan haka. Ki daina jin kunyar sunanyen da zan kira ki dashi. Sabida ni bani da sauki akan abinda nake so."

Takowa yayi gabana, tare da tare ni da ido. "Bani da kunya akanki, kuma na san zaki yi hakuri da ni, saboda zan zama mayyenki. I promise to stand by your side forever and forever. I promise to love you just this way till my last breath. I love you a lot."

Sunkuyar da kaina nayi na rasa wani irin dace nayi ne a rayuwata, ya Aalim yana min son da ban san iya kar shi ba, a sanyayye nace Mishi.
"I didn't find you first, nor did you find me first. God found both of us first for each other."

"Don Allah ku gama, romeo da juliet,.ina son zan tafi gurin Hot chocolate dina!"inji Aamil, ya faɗa tare da lekowa, saboda yadda suke amayar da soyayyar su,dan Mantawa suke da kowa.

"Ok Moe zamu tafi!" Murmushi nayi sannan nace mishi.
"Toh Mr. Muscleman nagode da zuwan ka."

"ko my Hummingbird! Thank You da sunanye masu dad'i da kike bani my Little dove."

Kunyar shi ta sani kamo habbar gyale na, ina murmushi. Juyawa yayi bayan motar ya shiga fitar min da wasu jakkuna, tare da kawo min gabana, yayi kasa da bakin shi dai dai kunne na, yace min.
"Akwai wasu kaya na musamman, ki addana mi su. Shine ma first night din mu, ki gwada du amma. Idan basu yi ba ki turo min sakon zan saka wasu a kayan lefen da zasu kawo miki."

"Amma naga akwai na wancan auren babu abinda nayi dasu, kayan kwalliyar ma, sun dauko lalacewa." Na fada mishi,. Yadda yake kallon bakina ya sani rufewa tare da sake dariya ina kallon shi. Cizon lips d'inshi yayi tare da cewa.
"Wookie idan na kamaki zaki yi kukan jini ban kyale ki ba"

Rike kunne nayi tare da narka fuskana nace mishi.
"Am sorry my Ice Man! Ba zan kuma ba."
.juyawa yayi yana faɗin..
"Ki jira ranar da ba zanji rokon ki ba, ba zan saurari kukanki ba, zan cigaba da.." da sauri na kwashi kayan na kule cikin gidan, ai kuwa ya fashe da dariya Mugu kawai.

Har na shiga dakin mu, Sahiyah da Inna Lantana suna tsaye kaman wasu Status. Saratu na mikawa kayan na fito, ina tsaye gashi unguwar babu mutane, da sassarfa na isa tare da rungume shi, matse ni yayi cikin nutsuwa tare da saka bakin shi kunne na, yana fadin.
"I miss your warm body, Baby Love. Ina kewar ki sosai my Baby face, you Are Lovey dovey. Barbie doll."
"Thank You, Sugah boogah."
"My Amazing,"
"Nagode Baby boy! Sake ni kar mutane su fara fitowa a ganmu haka na shiga uku."

A hankali ya sauke ki tare da cewa.
"Ok! My Honey badger. Zamu tafi sai an kwana biyu!"
Gyada mishi kai nayi sannan nace mishi.
"Munyi sallama na uku kenan, Dragonfly!"

"Na goma ma zamu yi! My Jamster!"
Sanin ba zai tab'a barina yayi tafiyar shi ba, ya sani juyawa na bar shi a gurin, Allah sarki Ya Aamil, sai ya zama kamar bako a cikin mu, domin a zahirance salon soyayyar su ya kayatar da shi, duk wannan abin da suke yi yana jin zai iya, amma matslar shi nace ba zata yi ta rena mishi hankali har haka ba. Har Aalim ya shigo suka fara tafiya murmushi yake cikin jin dadi tare da bin wayar shi da ido, yana kallon sakonin ta da suke shigo mishi.
A smile will always remain in life,

till the time you are with me,

I would feel so special,

because you will be to see

that I so love you in life!..

Murmushi yayi sannan ya tura mata da cewa.
*Love maybe only a four letter word. But it is more powerful than anything in the world. It can alone make you the happiest person in the world, or the saddest.*
"Don Allah ka ajiye wayar nan, ka koya min yadda nima zan dauke zuciyarta da zafaffan kalamai."

Murmushi yayi tare da dafe kirjin shi, yace mishi.
"Banbancin mu, a zahiri ƙalilan ce, amma a fagen soyayya kowa da abinda yake so. Dan haka kaji a ranka zaka ka iya abinda ma bazan iya ba."
"Gani nake kamar ba zan iya ba " ya faɗa a sanyayye,
"No dan uwa, zaka iya mana ni na taso a duniyar da ake Baje hajar soyayya ce, kuma kome kyan abu zaka samu sun iya ririta shi, da soyayya. Na fito a inda namiji yake raka matar shi

asibiti ne, kaji a ranka duk abinda zaka yi sadaukarwa ce ga soyayyarka."
. Cikin jin dadi Aamil yake gyada mishi kai.
**
Sati biyu tsakanin, Iyayen suka shiga al'amarin, kuma kowani ɓangare, sun amince da junan su. Dan haka, suka saka bikin Soon. Bayan an musu baiko. Yayar Maman Sidrah Binta ita tazo ta dauketa. Suka nufi Kano da ita, kafin ta fara mata gyaran jiki sai da takaita asibiti aka duba ko tana da infection, ana cewa babu.
.. ta dauke ta zuwa gurin wata Yar leboness, Hajiya Raziya. Matar har ajiye amare take. Dan haka bikin an saka shi nan da wata uku. Aka ajiye Sidrah a gurinta.. ga masu bukata cantack Zahrah 07035133148.... Littafina na kuɗi 🙏🏽
#Mai_Dambu...
[11/24, 10:25 AM] Anum Muhammad Bello❤️: My twins brother.

Gyara sosai ake min, wanda ya shiga cikin jikina sosai, duk inda na zauna kamshi yaƙe kama gurin, a hankali na fara samun yawan bukatar shi a raina, amma cikin ikon Allah dake ban damu da abin ba, sai gashi bai cika damuna ba. Haka zai ta kirana wai muyi video call, wani lokaci na dauka, ya zuba min ido yana kallona.

... Wani lokaci kuma yayi ta murmushi yayi cewa.
"Luv puppies! Kin hadu kuma kin kara kyau! Meye ake baki ne?"
"Babu abinda suke bani Budduh"
" da gaske Pooboo?"
"Dagaske nake Booboo!"
"That's my Bubbies!" Dariya nayi nace mishi.
"You are my Sugar puff!"
"My pumpkim! Ki shirya da kyau"
Shiru nayi tare da cewa.
"Toh Baby puff, zan cigaba da shirya."
Haka muke sallama, sau dari idan ya kirani da suna, baya kuma maimaita, sai dai ya kirani da wani sunan, shi yasa nima na mai da hankali gurin niman romantic Nick names,kuma na samu. Dan haka yadda bakin shi baya gajiya haka nima nawa baya gajiya.

---
A hankali ya gama juya wayar hannun shi, tun d'azun yake kiranta, bata d'aga wayar ba. Asalima ya kai awa daya a kofar gidan su.

Yana cikin motar shi, yaji dirin mota, a bakin get din. A hankali ta bude kofar shiga harabar gidan tayi tozali da motar shi, had'iye yawu tayi tayi sannan ta ja kafarta tare da nufa inda motar shi take ta bude motar tare da cewa.
"Kayi hakuri!"
Murmushi yayi sannan yace mata.
"Karki damu, zauna."
Shiru ne ya gifta tsakanin su, kafin yace mata.

"Me kike bukata na hidimar."
"Babu kome, sai dai zan haɗaka da Kawata ko zata fini sanin abinda ake bukata na bikin."

"Toh ba damuwa!" Ya mika mata wayar shi, ta saka Number Arianah. Sannan ta mika mishi, garin karba ya rike har da hannunta, kallon juna suka yi na wasu lokuta, kafin suka janye hannun su.
"Har ga Allah Aamil so yake mata har cikin ruhin shi, wani irin mahaukaciyar soyayya yake mata, wanda koda za a fita a gaya mishi wacece ita, ba zai tab'a kyale ta ba, sabida yana sonta ne da pure heart, baya jin zai iya daukar kasadar rabuwa da ita.

Ganinta yake itace dai-dai dashi a wannan lokacin, baya kuma tunanin akwai dalilin da zai saya a raba shi da ita ba. Nadrah mace ce har mace matsalarta kazamin burin da mugun rayuwar da ta saka kanta ciki ne.

Kuma ko iyayenta da Kawayenta musamman Arianah bata san abinda take aikatawa ba, ta dai san labarin harkalla da suke da Alhaji Abubakar ba, yanzun ma dawowarta daga gurin shi ta fito, taje ya tsotse ta, shine ta dawo amma dake burat ne a ranta kawai fuska tayi amma ranta bawai yaso lasar da yayi mata bane.

Kallon ta yayi cikin nutsuwa, sannan yace mata.
"Toh zan iya tafiya!"
Kallon shi tayi, tana me cizon lips dinta, sannan ta gyada mishi kai. A sanyayye ta juya zata fita, ya rike hannunta tare da fisgo yayi kirjin shi tare da tsare ta da idanun shi yana mata wani irin sassayar kallo me cike da wani irin kaunar mara iya.

Ba zai ce ga lokacin da ya fada soyayyar ta ba,but ya riga da yayi mishi mugun kamu, a hankali ya yake jan fuskarta into him face, yaga yadda ta lumshe idanunta, she luk glam and sunshine! Wani banzan kallo yayi mata cikin wani irin karsashi yace mata.
"My Tootsie! Can i kiss You!"

Wani uban kamshin berry taji ya bugu noise dinta sai da ta lumshe idanunta, tare da sunkuyar da kanta, sumbatar goshinta yayi tare da d'ago kan ta a karkace ya bata wani banzan ya bata a lip ɗinta na kasa, ga baki daya jikinta ya mutu,kafin ta ankare ya kuma sucking lip din a sanyayye, bude idanunta yayi tare da kallon cikin idanun shi,a hankali ta sake mishi jiki, a sannu a hankali yake bite lips dinta, tare da bata sani butterfly kiss.

Kamo hannunta yayi tare da kaiwa fuskar shi, kafin yayi breaking kiss din, yana kallon yadda take sauke wani irin breath, a haukace kamar wacce tayi gudun fanfalaki. Sake kiss din neck ɗinta yayi cikin wani irin kwarewa. Sai da tayi huging d'inshi tight, kamar zata shige jikin shi, kafin ya saka hannun shi ya janye ta daga jikin shi tare da juyar da kanshi yana sake wani cutie smile.
"Ok Honey bun zan tafi" a wani lalace ta kalle shi tare da narka da fuskata..kamar zata tsalla ihu take ji sabida shi totally unexpected sunan da ta kirata dashi. Sai wani iyayi take ta rasa inda

kanta yake, yau take jin ina friends dinta suke suga yadda ake riritata, tare da kiranta da romantic names.

"Zan tafi!"
"Thank you my Paami"
"Thank for wat? Or for de kiss."

Da sauri ta buɗe motar ta fita,.jikinta na wani irin sanyi, ta bar gurin shi, murmushi yayi sannan ya shafa wuyar shi wayar shi ya ɗauka ya manta bai amshi Number ta ba, kallon ta yayi tana kusa da shiga cikin gidan su. Ya fita yace mata.
"Hey!"
A hankali ta juya, murmushi yayi mata sanan ya rufe motar ya nufi gurinta, sai lokacin taga shigar jikin shi, wasu irin dressing yayi na daukar hankali. Yadda yake takun shi zaka rantse Basarake ne Malam Aamil. (🤣🤭 Dalibin Baban Soyayya!)
Yana isa ya mika mata wayar shi tare da tsareta da idanun shi.
"Digital"
Amsar wayar shi tayi ta zuba mishi Number ta, sannan ta kira yaji wayar ta shiga, zata mika mishi ya rike hannunta, suna kallon juna.
"Thanks Baby flower"
Murmushi tayi sannan ta janye hannunta, ta nufi cikin gidan. Jikinta na kara sanyi. Tana jin shi Kamar kyauta ne a rayuwar ta, bata tab'a ganin wanda ya hadu da wacece bai san wacece iya ba,ya gigice sai Aamil gaba daya bai damu da yasan wacece ita ba, kawai the only thing da ya sani shine yana sonta. Tunda ta shiga dakinta ta kwanta rub da ciki.

Tana jin wani karsashi kiss din da yayi mata, tare da jin wani irin yanayi na musamman, kara narkewa tayi a gadon tare da lumshe idanunta, tana kuma jin yadda yayi huging ɗinta, tana jin hannun shi a jikinta yana kuma yawo kamar yanzun abin yake faruwa. Kara karar wayarta tayi tana dubawa taga number shi dan ma bata yi saving ba, had'iye yawun tayi tana kuma jin shaukin son kasancewa dashi. Cikin wani irin kasalalliyar murya me mugun jan hankali da mai da wata irin Fitina ta dauka.

"Quake! Hmm, babu wata matsala?"
"Hmm! Ya Aamil! Ka koma lafiya?"
"Gani a cikin gidan ku, baki bani damar tafiya ba!"
Kamar yana gabanta ta fito da sauri, yana saman motar shi rike da wayar shi, ya dubawa kofar fitowar ta, idanun shi na kan ta. Dira yayi daga saman motar, ya tako gabanta.
"Baby flower baki ce na tafi ba,.shi yasa na zauna jiran ki"

Dafe goshin ta, tayi sannan tace Mishi.
"Ban san yadda ka ɗauke ni ba, but son da kake min yayi yawa. Please ka rage kar ya zam.."

A gigice ya isa gaban ta, tare da riko hannun ta.
"Nadrah, kece mace na farko da na fara so! How zan iya rage sonki. I promise You babu wanda

ya isa ya wulakanta min ke! Zan soki sama da yadda nake son kowa. Please accept my love"

"Zan soka, amma sai naga yadda.."
"Please! Karki ce haka kizo ni. Tun yanzun ki gaya min me kike so? Gaya min abinda zan miki. Na shirya miki duniyar ki, na Kawata miki rayuwarki, don Allah ki amshi soyayya ta."

Cikin wani irin jan aji, ta tab'e bakinta,sannan tace mishi.
"Sugar boy! Karka damu ina tare da kai,any more."
Allah sarki abu daya yake bukata daga gare ta, kuma ta fahimci haka, so take ta gano weakpoint shi, a fahimtar ta son da yake mata shine abinda son ji, by now ta kuma ji dan haka, ba tare da ya fahimci abinda ke ranta ba, tace mishi.
"Ina sonka nima! Amma kayi min Alqawarin ba zaka tab'a sauraron wani ba, idan kuma zaka iya sauraron koda twin brother dinka ne kawai kaje na fasa au.."

Rufe mata bakinta yayi, tare da girgiza mata kai, yana kallon Beautiful face ɗinta, lumshe idanunshi yayi sannan yace mata.
"Bayan Abba, Mommy, Ummi, Twin bro. Shine ma haf. Please karki ce kin fasa aurena, karki shiga tsakanin abokin haihuwa ta, don Allah karki hada soyayyarki da tashi, bawai dan bana sonki ba, d'an uwana shine farin cikina. Kuma nima nice farin cikin shi." Wani irin numfashi ya sauke tare da kallonta, kafin ya cigaba da cewa.
"I love you, fiye da yadda kike tsammani, but my twin brother, zan iya samun mata sama dake, amma bazan iya samun sama da Bro dina ba. Zan tafi nagode sosai. Akwai wasu matan a duniya wasu ma yau za a.haife su wasu kuma an haife su, wasu kuma an samar da cikin su, Zan iya hakura da kome ban da mutumin da yasha duka sabida ni, banda mutumin da aka rufe shi sabida Ni, ki gaya min mutumin da ya tsallake rijiya da baya, sabida zan iya janye soyayyar shi ne? Ke zan sami madadinki, shifa? Thank You."

Ya juya zai tafi tace Mishi.
"Kayi hakuri! Nima ina sonka da kuma twin brother." Bai kulata ba yayi tafiyar shi, har cikin motar shi ya shiga, tare da kallonta, sannan ya sake mata murmushi, ya karkata hancin motar yayi tare da ficcewa daga cikin gidan. Shiru tayi tare da yin wani iri da face ɗinta, tana kallon yadda yake jan motar, ba tare da ya kuma kallonta ko ta madubin motar Ba.

B'ata rai tayi tare da kallon wayarta, sannan ta kuma turawa Alhaji Abubakar abinda suka yi da Aamil, take ya turo mata da cewa.
*Karki damu! Ki amince mishi*
Tab'e baki tayi tare da juyawa cikin gidan su.
...... A hankali ya sauka daga saman titin ya kifa kanshi a sitiyerin, yana wani irin jin kamar ya fasa ihu, idanun shi sunyi jajjur, duk yadda yaso yaja motar ya kasa, dole ya dauki wayar shi ya turawa Aalim sako,

*Kazo bazan iya tuki ba, jikina babu karfi please!*
Kiran shi yayi cikin damuwa, ya tambaye shi.

"Kana ina?"
Ajiyar zuciya ya sauke tare da jin wani irin abu, ya gaya mishi hanyar da yaƙe, bayan kamar minti goma, ya iso gurin. Yana zuwa ya bude inda yake tare da kallon shi, rike mishi hannu Yayi tare da cewa.
"Fito ka shiga baya!"
A hankali ya fito, sannan ya. Mika mishi hannu, ya shigar dashi baya. Kallon shi yayi ta madubin motar, yadda yayi shiru tare da lumshe idanun shi.
"Me ya haɗaka da Nadrah?"
"Babu kome! Kawai bana jin dadi ne"
"Twins bana son karya! Ba halin ka bane, twins me ya faru?"
Girgiza mishi kai yayi tare da cewa.
"Babu kome zazzaɓi nake ji, zaka gaya min ba kenan sai naje na ci Ubanta, "
hannun shi ya kai kafad'ar Aalim, alama yana calm din shi.
"Toh meye ya faru?"
"Wallahi kirjina ne yake ciwo!"
"Are you sure?"

"Eh da gaske nake!"
Kawai yaji shine amma bai yarda ba, dan Uban Nadrah sai yaci Ubanta, a daren nan. Dan itace matsalar Aamil, dan haka da mugun gudu ya kai Aamil gida, har part din su ya kai shi, yana kallon tsarin ginin da Abba yake musu, kome nasu iri daya ne. A gefen gidan. Sannan ya shiga cikin gidan, ya rasa yadda zai yi da Abba ne, amma da ya bar gidan. Daga shi har Sidrah halin su daya, basu son tashin hankali.

.... Haka ya gama, kallon ko ina sannan ya fita tare da shiga motar shi ya bar gidan. Bai tsaya a ko ina ba, sai gidan su Nadrah. A hauka ce ya shiga cikin gidan.

Ko parking me kyau bai tsaya yayi ba, ya fice daga motar ya nufi cikin gidan.
"Nadrah!!!" Ya kwala mata kira tare da shiga har falon gidan, da sauri ta fito.

"Wallahi kika sake wani abu ya sami Alben! Sai na juye dukiyana baki daya na rufe wanda ya tsaya miki, sakarya wacce bata san me kaunarta ba. Ce miki akayi kowa gidahumi ne? Dan yace yana sonki sai ki kashe shi.

.idan baki kaunar shi bana sonka Aamil Finally! Kin zauna kina azabtar da shi kamar kin sami danki, ban da ina jin kunyar Iyayen mu da wallahi baki isa ki samu shiga a cikin gidan mu ba, tunda kin san baki son shi ki rabu dashi ki je can kiyi rayuwar ki, idan..."
Daga haka ya juya ko sauraron Alhaji Ahmed bai yi ba, ya bar musu gidan.

"Kina son Aamil ki baki son shi?" Alhaji Ahmed ya daka mata tsawa.
"Ina son shi Daddy! Uban me yayi miki da kike son jefa shi cikin damuwa?" Cikin tsananin tsoro tace.
"Babu kawai dai na yi mishi wasa n."

"Ki min shiru, wallahi karki sake ki lalata min zumuncin da daura tun shekaru da yawa, karki lalata min amintar da take jingine tsawon shekaru, tunda baki son shi akwai yar Muhmood kanina Mansura, zan bashi ita kije kici bakin halinki.

Kina niman kashe ni da rayuwata, kina janyo min magana,.kin saka mutane na min kallon na barki kina abinda kika gadama, toh baki isa ba. Wallahi bakin isa ba. Na rantse ba zaki tab'a min kimata ba, haba don Allah meye yayi miki da zafi haka ne? Wallahi ko kina so ko baki auren nan sai inyi ko dana shine abinda zan aikata daga shi sai mutuwata sai anyi. Mutuniyar banza kawai."

Daga haka ya kade babban rigar shi ya bar falon ranshi yayi mugun b'aci, dan yasan tunda Aalim yazo a haukace yasan ta tab'a mishi dan uwane. Ya yarda da girman Soyayyar da sukewa juna, musamman Aalim din yadda yake masifar kaunar Aamil.

Dan bai da magana sai na Aamil, ko abu zai saya sai ya turawa Aamil ya gani, idan yace bai mishi ba, koda shi yayi mishi zai hakura, akan Sidrah ne kaɗai baya iya hada sahun data Aamil, amma lokaci guda yarinya tana niman hada musu kashi, akan me dole yayiwa tufkan hanci kafin ya warware dashi, yadda Alhaji Ma'aruf ya rufa musu asiri a duniya waye zai iya musu.

Mutumin da abin duniyar shi bai rufe mishi ido ba, shine yar banza zata ja mishi kwarewar mutuncin shi a kasa warwas. Ya rasa inda zai cusa kanshi.

Kallon ta Hajiya Ubaidah tayi, tare da cewa.
"Ni kam tsoro kike bani! Gani nake akwai abinda kike aikatawa ba a tare da sanin mu ba, Nadrah meye laifin mu? Nasan nice nace bana son ki shiga cikin gidan su, amma irin soyayyar da nagani a idanun Aamil ranar da ya shigo na fahimci ya sadaukar da duk wani abinda yake sabida ke! Ya bar wa dan uwan shi yarinyar da yaki sabida ke! Amma dake kedin gidahuma ce, kin zauna kina musu abinda ranki yake so.

Me kike bukata? Me kike nima? Idan mata ne wallahi daga cikin ƙasar nan har zuwa wajen kasar, zai samu wacce tafiki kina cutar dashi sabida Kinga Allah yayi miki kyau ko? Toh ki sani shi din Ruwa biyu ne! Bahaushe ne sirke da jinin turawa, me yasa? Me kike nima? Yaron da ya gaji din bun Arzikin kakan shi, kike wulakantawa.? Meye kika fi sauran matar? Wawuya sakarya kawai, wallahi duk ranar da wani abu ya faru. Ki ji a ranki mun yafe ki, ki je can ki karata da wanda suke giya miki baya, idan ma Arianah ce zan kirata naci kaniyarta."

A gurin suka barta, tana share kwalla. Wato ita ba a damu da ita, sai Aamil ai ita zuciyarta ba Aamil take muradi ba, Aalim yake bukata, shi take ji zata iya karba a matsayin mijinta, ba brother din shi ba, akan me za a bata abinda bata so?

. Ita Aalim take so? Ba Aamil ba, a duba zuciyarta da rayuwarta daga haduwar Farko ta fadawa soyayyar shi karan iska a bata Aamil mutumin da take da yakinin ba wani sonta yaƙe ba, Amma Aalim fa? Baya sonta amma tayi imani zai jiyar da ita dadin da babu wani namiji da

ya iya bayarwa sai shi. Insha Allah dole ta wargaza tsakanin su. Yadda ita ce zata mamaye zuciyar su.

Tare da kwalafa, rai akan Aalim ta kuma sha alwashin ko ana muzuru ana shawo, sai taji dadin da yake tare da Aalim, taya ma zata amshi Aamil, ga wanda ya taso cikin turawa, yasan yadda suke tattalin mace da ririta mace, wannan fa? Bai iya kome ba sai tsabar tsageranci (🤣🤣🤣🙄🤔 🤦🏾‍♀️ Mommy Sayyid How market?) Da rashin hakuri. Ta san da Aalim ne zai iya hakuri da ita, kuma zai nuna mata soyayya a gaban Uban kowa, ita kuma dan an tsane ta, an bata made in Naija (😝😜🤣😆) haka kawai ina ba zata iya ba, wallahi ita ko zata mutu, sai ka ride din Aalim, sai taji yadda Underpants din shi yake. Sai ta lashe Lollipop din shi, tayi tsotse crown din shi, ba zata tab'a barin wannan mafarkinta ya rushe ba koda zata rasa kome da kowa nata. Ta ajiye a ranta sai ta ji yadda yake.

...daga haka ta mike tare da barin falon ta koma dakin, tana kuma aiyanawa a ranta, a shirye take ta rabu da kowa, akan Aalim koda zata rasa rayuwarta, sai taji abinda yake tanadawa Sidrah."

**

Coffee Mom ta haɗa Mishi. ta mikawa Aalim, da hanzari ya amsa. Zai mika Mishi kiran Sidrah ya shigo mishi, ya katse ya isa gaban Aamil ya fara bashi.

Da cokali, yana amsa. Kawai tuno yadda yayi ta gaya mishi magana yayi, Aalim kyauta ne a gare shi, idan babu Aalim a rayuwar shi tabbas sai ya tafka asara, kwalla ne ya zubo Mishi, cikin wani irin shakuwar da ya wanzu a tsakanin su. Kiran Sidrah ya kuma shigowa ya katse. Na uku ba shigowa ya dauka cikin zafin rai yace Mata.
"Ke wacce irin mutum ce mara hankali, kin kira na kashe kin kuma na kashe ba zai saka ki fahimci ina cikin damuwa bane."

"Kayi hakuri, Baby boy ba zan kuma ba Insha Allah. Ubangiji ya huci zuciyarka, kayi hakuri kayi baby ba zan kuma ba, ka gaida min Twin bro da Mommy da Ummi." Ta karshe Maganar cikin kuka. Kashe wayar yayi dan yasan ba zata tab'a kashe kiran shi ba.
Cillar da wayar yayi, ya debi ruwan coffee ya kai bakin Aamil ya buge hannun shi.
"Meye laifin Sidrah? Meye tayi maka? Don Allah karka yi Hurting yarinayar da ta baka rayuwarta, a hannunka. Am suffer for love, me yasa kake bukatar wata ta shiga irin rayuwar da nake ciki?"
"You can Understand!"
"Bazan tab'a fahimta ba! Ba zan gane kome ba, karka kuma cutar da Sidrah! Don Allah karka kuma cin zarafin ta, babu dad'i wallahi naji zafin haka, karka kuma twins. Don Allah. Please my twins brother"
Ya rike hannun shi, tare da kallon shi.
"Kirata don Allah!"
Amsar kofin tea din yayi Mommy tana kallon su, sun rayu a mabanbantan duniya, amma soyayyar mahaifar su, tana like a zuciyar su, wannan wacce irin kauna sukewa junar su.

Daukar wayar yayi ya shiga kiran Sidrah.
"My pumpkim!"
Cikin muryan kuka tace..
"Har ka huce! Honey stick!" Murmushi yayi sannan yace mata.
"Silly lady na huce! Am sorry!"
"No karka bani hakuri nice nayi rashin hankali, kayi hakuri ba zan kuma ba."
Duk sai yaji babu dad'i, ba shi ba hatta Aamil sai yaji sun bashi tausayi, sabida shi gashi dan uwan shi sun sami matsala da yarinyar da suke soyayya. Kuma ba dan kome ba, sai dan Nadrah, itace yarinyar da ya fara so, kuma gashi tana niman kai shi kasa. Dan haka Insha Allah ba zai kuma d'aga hankalin shi akan ta ba, duk abinda zai faru zai barwa zuciyar shi, domin dan uwan shi ya sami damar Kasancewa da tashi abar Kaunar, baya son yayi abinda zai kuntatta rayuwar dan uwan shi. Shi yasa ya hakura da nashi farin cikin domin nashi. Wanan itace adalcin da zaiyiwa Aalim, domin idan ba haka ba, sai ta jefa shi cikin kunci da damuwa, yana cikin tunanin yaga Aalim ya mike tare da barin falon, ya nufi can backyard din, bishi yayi da ido, sannan ya mai da kan Mommy yana cewa..
"Mommy! Allison ya dace da mace ta gari, yarinyar da ya daura bisa tsarin shi, kinga shi zai iya sarrafa tare da lakwasata, ya kuma biyar da ita yadda yake bukata bata damu ba, amma Ni farkon tafiya har na fadi, bani da sa'a, bani da yancin samun yadda nake so."
Matsowa tayi kusa da shi, tare da rike hannun shi, suna kallon juna tace Mishi.
"Alben, kai ma soyayyarka tana nan tana zuwa gare ka, akwai lokaci, idan tazo maka zaka manta da kayi irin wannan rayuwar."
Haka tayi ta rarrashin sa, tare da cewa. Zata shirya mishi tafiya shi da Allison...
ga masu bukata cantack Zahrah 07035133148.... Littafina na kuɗi 🙏🏼
#Mai_Dambu..
[11/24, 7:52 PM] Anum Muhammad Bello❤️: The trip.

Rashin daidaito yasaka ana tunanin dakatar da bikin Aamil, duk da abin yaso shafan dangatar da take tsakanin manyan Aminan guda uku, abin da ya fusata Alhaji Ahmed yazo gida yayi ta faɗa, kamar zai daki Nadrah karshe yace mata.
"Nagode sosai! Sakayyar da zaki min kenan?"
Murmushi yayi me mugun ciwo, sannan yace mata.
"Allah ya shirya min ke!" Da ciwo ace dan da ka haifa ya fi karfin ka, kuma baka iya sarrafa shi yadda kake so.

Koda ya shiga dakin shi, kasa jurewa yayi ya dinga zubda kwalla, abinda ya fusata mahaifiyarta kenan, ta shiga kitchen tare da dauko Muciya, tayi ta muka mata, sai da ta targada mata hannun, tana kuka tace.
"Me muka rage ki dashi? Waye yake hure miki kunne? Me muka miki haka?" Kukan da uwar take yasata tsorata, sosai.
Hajiya Ubaidah tace.
"Kin bani kunya, nan aka aurar da Sidrah, yarinyar nan ko tashin hankali bata haifarwa kowa ba, asalima nunawa tayi an haifeta ne domin ta musu biyayya.

Ke da kika taso a cikin mu, cikin gatar ki. Yau kece kike nuna mana iyakar mu, mun gode sosai. Mun fahimci abinda kike son fahimtar damu, na rashin miki adalci. Mun gode, kodan Kinga kece kawai muka haifa shi yasa kike tozarta mu. Idan muka mutu da bakin cikin ki, sai ki zubda ruwa a kasa kisha."

Wannan abun yayi mugun d'aga mata hankali, dan haka tayi ta kuka tana rokwanso su yafe mata, suka share ta babu wanda ya kuma mata magana asalima share batun ta suka yi tare da barinta tayi abinda take so.

....
.....
Tsakanin mu da Ya Aalim, idan ya kira. Idan kuma bai kira ba sai na ajiye shi a gefe, asalima tsoron kar na mishi laifi nake, domin na lura kamar akwai abinda ake mishi na jin haushi, idan yaji haushin sa, sai ya nemi ya sauke min Bala'i, dan haka na daina kiran shi a waya, sabida halin da Aamil yake ciki yasa shi zama masifaffen dole.

.. ba tare da sanin Aamil ba, suka shirya mishi tafiya yawon bude ido, a manyan biranen duniya, a cikin su kuwa har da Wuhan.(🤣😆) Daga cikin su har da wasu guraren a califonia, sannan sai doha da kuma sweden. A nahiyar Afirka kuwa Egypt. Bai sani ba, haka suka gama shirya mai kome. Tare da da yaran Hajiya Uwani, daga nan zasu yi Umrah tafiyar da Aalim ya shirya musu har da Sidrah da Nadrah. Duk da tana rashin mutunci haka bai hana a shirya tafiyar da ita ba, dama Aalim yana da passport Sidrah. Dan haka yayi mata kome, Nadrah kuwa Ummi da Mommy ne suka je gidan su aka basu nata, dan tafiyar har da Iyaye duk da ba jimawa, zasu yi ba ba zasu wuce sati huɗu ba.

Dan Aalim yana shirya musu tafiya honey moon, dan haka ba zasu jima da dawowa  ba za ayi bikin su.

......
Lumshe idanuna nayi sakamakon manyan kalaman da Mr Luv, ya cika min kunne da manyan al'amura. A hankali na sauke ajiyar zuciya tare da cewa.
"Mr. Cutie! Nifa ba zan sami zuwa tafiyar nan ba, sabida bana son damuwa."
"Waye kike tunanin zai sanya ki damuwa?"
"Kawai mu hakura da tafiyar, bayan bi.."
"Kice min ba zaki ba kawai, kin san tafiyar ba dan kaina bane dan uwana ne, amma kike gaya min magana akai? Ok yayi kyau."

Kashe wayar yayi na gyara kwanciya ta, sannan na rike wayar na ma rasa me zan gaya mishi kawai na tura mishi sakon ban hakuri.
_You are as sweet as honey. You are as bright as the sun. If you accept my apology, you'll be my number ._

Shiru har yanzun bai kuma turo min kome ba,.
Sake tura mishi wani sakon, nayi tare jiran amsar shi.
_For old time's sake, accept my apology. I want to be with you again, don't keep me away.😭🙏🏽😢_

*Ok ya wuce amma tunda Ni nake shirin zama shugaba, a daina min gardama!*

Murmushi na tura mishi. Addu'a da godiyar saukowa da ya. Sannan na kashe wayar. Gaskiya Ya Aalim shima masifaffe ne, ana ganin na Ya Aamil ne shima rigima ce a ran shi. Dan haka nake lallaba shi kamar tsohuwar mota.

... Domin a zahirance bayi da Hayaniya amma a bad'ili, masifaffen mutum ne, baka tab'a fahimtar haka sai ka zauna dasu. Amma dan hargagi da fada Ya Aamil ne, shi kuma wannan a tsanake yake soyaka yana bar bada yaji ba tare da ya damu ba.

.....
Kallona Inna Binto tayi sannan tace min.
"Ki kame kanki, karki yarda kina shige mishi, dukda tafiyar taku da manyan amma don Allah ki tayani rike mutuncinki.

Ban yarda ku keb'ence ba, karki yarda don Allah ki rufa min asiri a kai ki lafiya, kinji karki yarda ku keb'ence. Don Allah na roke ki karki yarda ya miki wani abu."

Cikin hauka irin nawa nace mata.
"Toh Innah meye ne a cikin dan ya nime nazo muyi hira."
Buge min baki tayi  tare da zabga min harara, goshinta ta dafe tana faɗin.
"Toh ciki zai miki kuma yace ba nashi ba, wallahi kika yarda ya kebe dake, wallahi sai kin kusan mutuwa yar banza me shegen idanu a tsarka. Wuce da kugun ki nan kamar na sauro."

Tura baki nayi ina jin zafin yadda ta gama kwashe min albarka, sannan ta kuma kara min da nasiha, tare da Addu'ar Allah ya tsare ni.

Share batun ta nayi, nace Amin amma Innah bata so tafiyar ba, sai dai dake sunyi waya da Ummi take gaya mata zamu tsaya ayi mana gyaran jiki a Saudiya ne shi yasa. Akwai wasu yan tunisia sun iya gyaran jiki na fitan hankalin.
Amma maganar gaskiya, a tsorace nake da maganar da Innah tayi min, domin kuwa zama nayi ina nazarin abinda ya faru lokacin su Sahiyah har zuwa lokacin da ya Kuskure ni a Dubai. Take wani munafikin tsoron shi ya kamani, a take wani lalataccen tunani yazo min, kamar zanyi kuka nace.
"Shi kenan! Yanzun ko hannuna ya tab'a cikin zanyi? Toh wallahi bazan yarda da abinda zai sani ya tab'a hannuna ba, kawai yayi min abu ya cuce ni."

Ita Innah tayi min iyaka dashi ne sabida kar na saki jiki wani abu ya faru, amma ni yadda na

dauki Al'amarin ba sauki fa,  dan hk nayi ya shirya yadda zamuyi dashi dan kar ya min ciki!(Mumu girl 😏🤣) ai kuwa nasha alwashin ko hannuna bazan barshi ya rike ba, balle kuma ya tab'a min bakina, kawai zan mu Cigaba da yin hot luv da text amma no more kiss da hug...

*** Shirya mata wasu mahaukatan kaya Ariana take, duk da tafiyar tasan cewa da Manyan kuma babu inda za ayi wannan shigar banzan, sai kallon juna suke, tare da Arianah tace mata.

"Bab ni dai karki manta ki sayo min joystick na roba, shine bukata na dake."

"Shegiya mayya me zaki yi da kayan maza? Keda kika ce ko a kafa aka daukar miki namiji zaki guje shi, ki dai ji tsoron Allah." Inji Nadrah,

"Tunda ba tsoron Ubanki zan ji ba ai da sauki."

"Bana son Iskanci meye Ubana yayi miki? Karki kuma."

"Kina son Uban naki kike watsi da maganar su,kingani nan wallahi idan Abbana ya nima min namiji ya bani na aura da gudu zan aure shi. Ba dan kome ba sai dan nasan ba zasu tab'a bani abinda zai cuce ni ba.

.... Amma ke Allah ya baki iyaye na gari burin su, ki auri mutumin kirki, amma kike watsi da bukatar su. Tabdijam, kina da aiki a gaban ki. Wallahi bari na gaya miki, irin wannan abinda kike musu, kina ji kina gani koda anyi auren ita wancan da bata da fitinar zasu kambama al'amarin ta, dan haka kiyi ƙoƙarin ganin kin sassanta dashi, Wallahi kodan Albarkacin zumuncin da iyayenku suke ai kyaso shi."

Lokaci guda jikinta yayi mugun sanyi, tare da cewa.

"Insha Allah, zan farantawa Iyayena."

Sun jima suna hira kafin suka, kuma fada shaidancin su, jakuna kawai.

***

Rana bata karya sai dai uwar d'iya taji kunya, a yau muka shirya barin ƙasar, tunda suka iso kano, yake kirana. Kamar makaho. A hankali nayi musu kwantaccen gidan mu, koda suka zo,na kai su cikin gidan su Mommy da Ummi. Shi kam kamar zai cinye ni. Duk inda na wulga sai ya bini da ido, karshe a falon waje, ya riko ni. Tare da saka hannun shi duk biyu a k'uguna. Kallon shi nayi cikin sauri kirjina na bugawa.

"Baby kin kara girma, kin kara zama big girl! Babu kome naki ya zama na musamman, Please kiss me."

Leka hanyar waje nayi naga babu me shigowa, kara tsayi nayi tare da riko fuskar shi, sai da na bari ya sakankance,.kawai na zabga mishi cizo, wanda ya saka shi sake ni da sauri.

....na koma cikin gidan da gudu, ina dariya sam na manta da cewa gidan akwai baki.

"Nayi maganinka gobe ma ka kuma, sai na maka abinda yafi haka, dani kake zancen!"

Na aika mishi da gwalo."

Murmushi yayi sannan ya gyada kan shi, can ya rufe idon shi daya tare da yarfe hannun shi, yana jin kamar wani abu ya faɗa mishi a cikin idon, da sauri na isa gare shi ya janyo ni falon, kafin na ankara ya matse ni tare da hade bakin mu, make shi nake tare da ture shi, shigowar Ya Aamil, shi da Nadrah yasa suka yi turus. Wani irin kunya ce ta kamani ban san lokacin da na fashe da kuka ba, dole ya sake ni yana kallon fuskana. Ganin yadda nake juya bayana tare da mannewa a bango..

Takowa yayi gabana, tare da riko hannuna.
"Kiyi hakuri, toh me nayi miki kuma."
Cikin danyen yarinta nace mishi.
"Shi kenan, abinda ake gudu ya faru, Innah tace ciki zaka min gashi ka samun yawun bakinka a bakina, na shiga uku na lalace."

Dafe goshin sa yayi cike da nadamar abinda ya aikata, ji yaƙe kamar ya kurma ihu, Aamil kuwa me zai yi ban da dariya, dan shi abin yayi mishi mugun dad'i, rabon shi da yayi dariya har ya manta. Wani irin kallon tsana Nadrah take min, ni kuwa na wani lafe a jikin bango ina share kwalla, a hankali ya juyo yana kallona, tare da zuba min ido.

"Toh naji dawo min da yawuna, ba zaki samu cikin ba, tunda kin dawo min dashi. Kallon shi nayi tare da cewa.
"Da gaske?"
"Eh da gaske mana, maza dawo min da abuna, shi kenan."
Kasa nayi da muryana nace mishi.
"Toh amma da mutane!"
"Ai toh shikenan, ki bari idan mun tafi sai na biyaki, sannan idan min fara jin amai da tashin zuciya ki gaya min sai nayi maza na kwace cikina, dan kar wani abu ya faru."
Da wannan dabarar ya mantar dani zancen. Kallon Nadrah nayi naga tana min wani irin kallo,sunkuyar da kaina nayi tare da cusa kaina kirjin shi, ina cewa.."zan shiga cikin gidan."
Kafin ya bani amsa, tuni zakara ya bani sa'a, ina fita tana jan tsaki. Dukkan su sunji amma babu wanda ya kulata. Suma cikin gidan suna shiga, can kuma suka sake fitowa, aka nufi airport. Tunda suka dauki hanya. Nayi shiru, kaina a sunkuye ba kamar Nadrah da suke hira da Mommy ba. Duk da ina kusa da ita amma kunyarta ya hanani cewa kome, suna lura da yadda Nadrah take hantara na, karshe Ummi ta canza mana gurin zama da Aashiq...
😏😏😏
#Mai_Dambu
[11/25, 9:00 AM] Anum Muhammad Bello❤️: The Encounter

Ita a tuninan ta, ban tab'a hawa jirgi ba. Sai ta ga cikin kwanciyar hankali, muke hira da Ummu, har muka shiga jirgin. Zan zauna kenan ya mika min wata takarda kallon takardan nayi naga an saka first Class, murmushin jin dadi nayi sanan kalli Ummu nace mata.
"Bari na koma can!"

"Ina?"inji Nadrah,

"VIP!" Ummi ta bata amsa, bin bayan mu tayi da idanu tana jin wani irin b'acin rai, tare da cewa. Kenan an kawo tane a nuna mata iyakarta a wannan tafiyar, tana ganin har Aamil suka tafi abinsu.

Shima yanzun shareta yake, ta rasa yadda zata yi da shi. Cikin jin haushi ta zubawa window Idanu, har jirgin ya tashi kamar zata yi hauka.

Tunda muka hadu mu uku, ake hira, duk hiran ba wani abu bane sai sanya Aamil cikin nishadi, kuma haka yayi mishi dad'i. Kallon shi Ya Aalim yayi sannan yace mishi.
"Me yasa ka ki bawa Nadrah daman zuwa tare da mu?"

"Kawai naga bata da wani amfani a zuwan ne," ya faɗa a sanyayye, sabida ya lura da yadda hankalinta yake wani guri na daban.

...
Madinatul Munawarah suka sauka, tare da fara gudanar da Ibadar Umrah, daga nan suka nufi Makka, tunda muka isa ban cika ganin Ya Aalim ba, yana yawan zuwa jami'ar da take da'yifa,.kasa hakuri nayi na tambayi Ummi ina Ya Aalim yake zuwa?

"Zai gabatar da Jarabar shi ne domin yana karatu da jami'ar ta online, bai da lokacin mu yanzun sabida shi samu zauna na tsawon sati biyu."

"Allah ya bashi Sa'a ya kuma bashi abinda yake nima, Allah sarki Habibi!" Juyawa tayi tare da zuba min ido, da sauri na kauda kai na, dan sai da na fadi haka kunya ta kamani, karshe ma guduwa nayi tana murmushi tace.
"Ja'ira, da kin tsaya mana!"

Ganin yadda muke damuwa da juna, ya sanya take jin koda anyi bikin ba lallai bane, a iya samun wanda zai shiga tsakani ba, sabida, yadda muka fahimci junar mu.

...
Rashin Ya Aalim ya sanya Ya Aamil komawa yanayin shi, dan haka ya gayawa Nadrah ai Aamil yayi tafiya, ni kuma da na san da haka sai na share su tunda ba Aalim bane, da wannan yanayin ya janyo hankalin ta gare shi, wani lokaci idan ta ganni dan ta bani haushi sai tayi ta mishi wasu abubuwan.

Shima kuma ya fahimci hankalinta yana ga D'an uwan shi ne, sai yayi kokarin ganin ya sami dan uwan suna waya dashi inda ya gaya mishi abinda yake faruwa, ranshi ya b'aci dan haka ya kirani ya gaya min,.toh me zance?

Dan haka na zuba musu ido, haka ya saka ya Aamil yawan zama cikin kaɗaice, har Allah Allah yake Aalim ya dawo.

Kamar Ya Aalim ya fahimci yana cikin kadaice ko nace yaji haka a tare dashi ya sani nake yawan zuwa muna hira dashi a bakin hotel din,  haka ba karamin d'agawa Nadrah hankali yayi ba dan ta zata Ya Aalim ne, bayan Aamil ne, ganin haka ta shiga min rashin mutunci, tare da ɗaukar shi suna fita yawo, idan ta zauna dashi ban da kushe ni babu abinda take.

"Ya Aalim me zaka yi da Sidrah! Munmuna ce fa? Ga mata dayawa birjin irina, sai wata Ugly girl, ban da an saka baikona da Aamil da nace ka fasa auren Sidrah ka aure ni, zan baka."

Cike da mamaki yake kallon ta, sannan yace mata.
"Meye laifin Soyayyar da Aamil yake miki?"

Tab'e bakinta tayi sannan tace mishi.
"Dabi'un shi da halayyar shi na yan Arewa ne? Kuma kasan kai ba ka taso a cikin arewa ba, sannan baka san wata rayuwa bayan ta kasar Turai ba, da wannan nake kin auren shi but da zai canza maybe zan zauna dashi a haka!"

Tausayi kanshi ne ya kama shi, dan haka koda ya tafi dakin ka'aba, bai bar gurin ba sai da ya fashe da kuka, saboda wani irin mugun so yake mata, wanda bai tab'a jin zai iyawa wata mace bayan Nadrah ba.

Yayi fatar Allah ya amshi rayuwar shi da tashin hankalin da take dabda jefa shi, domin yana tsoron karta raba shi da d'an uwan shi, abokin Haihuwar shi, su biyu ne tak wa Mommy, taya zai iya kallon haka. Yawan Ibadar da yake da rashin zama cikin mutane ya sanya ya fara samun saukin damuwar shi.

Sai dai ya ki gayawa twins brother halin da yake ciki, shi kuma da yaji jikin shi na bashi akwai matsala ya kira Sidrah, ya balbale ta da faɗa. Dan haka ta fita tana niman shi. A can bakin swimming pool ta same shi yana kallon ruwan, zama tayi kadan daga kusada dashi tace mishi.
"Barka da hutawa!"

"Sidrah Barka dai! Ya kike?" Ya tambaye ni, murmushi nayi sannan nace mishi "Alhamdulillahi."
"Akwai wani damuwa ne?"
Girgiza mishi kai nayi sannan nace mishi.
"Ya Aalim ne yake son magana da kai!"
Na mika mishi wayar. Yana amsa kiran na shigowa, cikin fada yace.
"Har yanzun baki kai mishi wayar ba, meye nufinki?"

"Mr kyam-kyam, ba ita bace Ni ne!"
.mik'ewa nayi na basu guri, suka shiga hirar su.
A hanyar komawa ta muka hadu da wani Balarabe, sai kace mayye, dan haka ya shiga bina. Dakyar na samu damar rabuwa dashi. Duk akan idanun Nadrah, abinda ya bata mamaki yadda bamu zama da Aalim, a tunaninta fa.

Tunda ta ga balaraben ya jarabu da bina, dan haka ta shiga bibiyar mu, ni kuma ba wani abu nake na jan halin shi ba, kawai dai jaraba ce.

Dan haka da yamma muke tafiya Masalaci,  bamu dawowa Sai karfe tara. Yau ban sami zuwa ba. Sabida hutun salla da nake zama shiru ya dame ni. Sai na fito bakin masaukin mu na zauna, anan ne Balaraben ya kuma dawowa ina ganin shi na koma cikin hotel din da gudu.

Dake kowa yana harkokin gaban shi ne babu wanda ya damu da wani shi yasa basu fahimci dalilina na shigowa da sauri me hade da gudu ba.
Haka mutumin nan ya biyo ni,.ina rufe kofar yana turowa da mugun karfi, dariya ya fashe dashi tare da cewa.
"Kin gama gudunki? Gashi nan na biyo ki ai."

Kuka ne ya kwace min, ban san me zancewa Mutane ba. Dan haka da mugun sauri na rarumi wata kwalbar Flower na jefa mishi, cikin mugunta ya karaso tare da kai min duka a cikina. Wani irin dunkule min yayi lokacin guda, yayi masifar tauri. Kasa kuka nayi tare da kallon shi, sake kai kafar shi yayi zai dake ni. Nace mishi.
"Had'a da Allah karka kashe ni?"
Durkusawa yayi a gaba na, ya saka hannun shi biyu ya yaga rigar jikina, tare da tsinka bra din dake kirjina, wani irin kuka ne ya kwace min, na kai musu duka tare da tokare shi da kafana.

Wani irin naushi ya sauke min, a tsakanin cibiya na zuwa mara na, wanda ya sanya ni daukewar wuta, na lokaci guda. Tare da sake wata irin kara, na zube a gurin. Rike da cikina.

Hannun shi ya kai tun daga kirjina har zuwa kan cikina, tare da matsa Boons dina cikin jin dadi, wayar shi kirar iphone, ya ciro, tare da ajiyewa yana daukar mu video.
"Ya Allah! Ya Allah! Ya Allah, na kiraka Ya Allah ka amsa min, Ubangiji ka amsa min, Ya Allah karka bashi damar keta alfarmata, Ya Allah Nagode maka." Na fada cikin kuka,me ban tausayi, gabaki daya ya rud'e kawai akan kirjina bai kuma zarewa ba, sai da ya saka hannu zai taba pant dina ne, na fashe da kuka, tare da ja a kwancen.

..ina kuka ina rokon shi haka ya zare pant din wanda yayi dai-dai da zubar jini kaca-kaca a inda nake kwancen. Kifa min mari yayi sai da hancina ya fashe, ya shiga dukana, juyar dani yayi zai bi bayana. aka buga kofar da mugun ƙarfi. Sabida kukan da nake ya tsannanta, da sauri ya dauki wayar shi ya adana videon tare da boyeta sannan ya nufi kofar bayan ya tsallake ni,  yana bude kofar ya hadu da Ya Aamil da Nadrah, kallon juna suka yi, tare da Aamil. Ya kuma jiyo sautin kuka na. Leka d'akin yayi da sauri ya rintsa idanun shi, tare da dafe goshin sa, idanun shi sunyi jajjur, take dabi'ar shi ta baya ta dawo mishi lokaci guda.

Matar da Dan uwan shi yake tanadawa wani yazo ya lalata musu alfarmarta, wani irin naushi ya kai mishi sai da guy din ya zube kasa warwas, ya kuma cigaba da dukar shi, tunda ya fahimci zai iya tona mishi asiri, da sauri ya samu ya mike tare da komawa dakin ya bude kofar.

"Zoka dake Ni! Ba kai mara mutunci ba, zoka dake ni, idan ka isa kuma anan na dauki hoton abinda muka yi, sai na sake a duniya."

..."Aalim maganar gaskiya ka barshi ya tafi, ita kuma sidrah ka rabu da ita, idan ba haka ba baka san inda abun zai tsaya ba."

Cikin hargagi ya ture ta yana fadin.
"Ni ba Aalim bane, saura kwana uku ya dawo ya tafi exam, idan ban kare matar da zai aura ba meye nayi? Meye amfani na? Meye laifin yarinyar da bata ji ba."

Murmushi tayi sannan tace.
"Toh ka kyale shi, tunda mijinta bai sani ba, ko baka tsoron ni da na gani na gaya mishi wacece zai aura?"

Bakin shi sake, yana kallon ta. A hankali ta kalli gayen sannan tace mishi .
"Zaka iya tafiya?" Kafin ta kuma kallon Aamil tace.
"Nasha mamaki da naga baku zama da Sidrah, a hankali na fahimci kai ne Aamil Aalim baya nan, kuma na kuma tabbatar da haka ne ta hanyar daukar wayar Sidrah juya naga sakoninta da Aalim, shine ka ninke ni bai-bai.

Ga dai Sidrah! Mutuncinta zaka kare ko na d'an uwanka? Ni dai a ganina, ka mai da hankali gurin tsayawa a matsayin ka, ita kuma yarinyar zata iya daukar nauyin tafiyar, idan kuma wani yayi min katsalandar dakatar dani, zan sake video."

Cikin sanyin jiki yace mata.
"Me kike bukata?"
"Ina son ka! Kuma zan zauna da kai, shine kawai nake bukata, ita kuma Sidrah a rufe zancen wani abu. Amma bana son damuwa, kuma bana son shishigi a cikin lamarina"

Allah sarki abu biyu, Son dan uwan shi, tare da makauniyar soyayyar da yake mata, ya amince. Ta sanya shi a gaba ya shiga dakin ya gyarawa Sidrah kayanta, tare da taimaka mata, yana zubda hawayen bakin ciki tare da kauda kanshi har ya taimaka mata, dan tace ba zata tab'a saka hannunta a jikin sidrah ba.

Yana gamawa ya dauko ni muka nufi asibitin, lokacin su Ummi sun dawo. Suke tambayar ta ina muke. Budar bakinta tace.
"Ina nasani tunda Aalim ya bar garin nan, Aamil da sidrah suka hade kansu, nayi magana ya gaya min maganar da ta sani kuka, shi yasa na daina shiga harkan kowa. Dan na fahimci cin amana ta yawaita, yarinyar da dan uwan ka yake so zaka na."

"Ke bana son hauka, ko mutuwa dayan su yayi zai yi wuya daya ya auri matar d'aya balle kuma bana fatar haka. Ki iya bakinki bana son rashin hankali."
.  Inji Ummi, Tana kuma jin tsanar Nadrah tare da jin ina ma ba yar Aminiyarta bane?

---

Baki kallon shi, haka shima yaki kallona, bini bini yana goge fuskar shi haka nima, kuka nake sosai. Iya cin zarafina anyi shi, ban san me nayi musu ba. Har likita ya gama dubani ya kalli Aamil yace mishi.
"Kayi hakuri zamu mata wani bincike. Sabida buguwar tayi."

Dan haka suka kuma kai ne wani daki aka saka ni cikin wani na'ura, ana duba ni..yana waje cike da damuwa ga wayata a hannun shi Dan uwan shi yana kira na, ya kasa d'agawa. Hawayen takaici da yake saukar a idanun shi kawai ya isa ya tabbatar maka da cewa yana cikin bakin ciki sosai. Haka ya ke kallon sakonnin da Aalim yake turowa na damuwa da kewa ce.
_Without you, am a loner in the crowds. I miss you, and miss you real bad_ wani irin kuka ne ya zo mishi ya fita waje yayi sosai yana tir da makauniyar soyayyar da yakewa Nadrah mara amfani.

Da yana da iko da zuciyar shi, tabbas da zai cire ta ya wurga ko zai huta, duk wannan abin yana faruwa ne sabida Burin shi na kaunar kyalkyali banza, gashi nan bata amfane shi da kome ba, sai bakin ciki. Tunda ya hadu da Nadrah ya fahimci bai da sa'a duk wanda ya rabe shi sai ta cutar da shi.

Gashi nan tana shirin lalata mishi amintar dake tsakanin su da dan uwansa, Soyayyar da sukewa junar su, kifa fuskar shi yayi a tafin hannun shi, yana sauke sheshrkar kuka, rabon shi da yayi kuka tun yana yaro, ganin wulakancin da aikawa sidrah ya sanya jin tsanar kome a ranshi, tausayin yarinyar tare da jin ina ma da ya amsheta tun lokacin baya da yau babu wanda ya isa ya tab'a alfarmarta, amma ina zanen kaddarar su bata bashi damar zuwa ga abincin ruhin d'an uwan shi ba.

Bata tab'a kai zuciyar shi ga abinda dan uwan shi yake bukata ba. Koda zai rage daga shi sai Sidrah ba zai tab'a aurar ta ba.

Ba zai tab'a kusantar ajiyar dan uwansu ba, koda kuwa zata halatta mishi ya hakura da ita har abada, balle baya fatar wani abu ya tab'a rayuwar dan uwan shi, zai iya daukar kome, amma banda fushin dan uwan shi. Ya Allah Ya furta a hankali lokacin da ya kara jin wayar yana kara, dubawa yayi yaga.
*Sugah boogah* hawaye ne ya zubo mishi ya kashe wayar baki daya dan babu amfanin barin yana kiran ta, kuma bai dauka ba. Haka ya zauna a gurin akala ta kai awa daya da rabi kafin ya mike ya koma cikin asibitin har zuwa lokacin basu fito da ita ba.

..... Koda suka sani a cikin gurin suna bincike, tare da wasu mata likitocin. Yanayin kallon da suke min ya sani fahimtar akwai matsala ina kallon suka shiga min wasu gwaje gwajen kimiyya har suka fito dani, suka  kwantar dani, aka Cigaba da dube dube su. Suna tattaunawa dan sun bawa tattaunawan muhimmanci,  zuwa wani lokaci suka kuma kiran wasu likitocin. Aka shiga aiki cikin damuwa da tashin hankali. Suna cikin haka ciwon cikin me mugun ciwo, kamar ba zan

rayu ba. Haka nake juyi. Allurai suka min, tare da saka min ruwa. Suka mai dani dakin. Gwajin ganin yadda nake zubda jini yasa daya daga cikin su komawa gefe tana kuka. Tare da dafe goshinta. Iya kokari sunyi kamar zasu cire ciwon a jikina su mai da tasu.

Har kusan karfe biyu na dare sannan suka fito daga cikin dakin, aka turani zuwa dakin da zan zauna.
"Kai ne ka kawo ta?"
Suka tambaye shi, d'ago kumburrun idanun shi yayi ya gyada kai.

"Ok biyo mu Office." Jikin shi na rawa ya bisu. Suna shiga suka nuna mishi gurin zama, a hankali ya zauna. Sannan aka turo mishi wasu takardun masu mugun yawa, kamar Document.

Shiru suka yi na wani lokaci, kafin suka ce mishi....
😏🤔🙄 Jiya da na baku 3.5k tsallake shi kukayi yau kuma 2.5k.

Na dare kuma 500 Words 🤣😜

ga masu bukata cantack Zahrah 07035133148.... Littafina na kuɗi 🙏🏼
#Mai_Dambu..
[11/25, 8:12 PM] Anum Muhammad Bello❤️: The secret

Zama yayi a dararre, kamar wanda ya aikata mugun laifi tare da nutsuwa, yadda kasan yana gaban alkali, haka ya nutsu dakyar yake fidda numfashi, sabida tsoron abinda ya faru da Sidrah.
"Abinda muka gani kuma yake shirin faruwa da, da farko muna me tuna maka yarda da ƙaddara, wannan al'amarin da ya sameta bayana nufin ba zata kuma samun kyakkyawan sakamako bane a rayuwarta, dan karka ga yadda Allah ya jarabce ta kace ba zaka iya zama da ita ba.

Muna baka hakuri ka kuma hakuri da ita, wallahi babu wanda ya isa ya kaucewa kaddarar shi, yarinyar da ka kawo. Ba zata kuma Haihuwa ba,  sai abinda Ubangiji yayi sabida shi yake da Ikon ya wanzar da ikon shi." Wani irin kuka yake yi me mugun cin rai.

Bai gama jin abinda zasu ce ba ya mike tare da cewa.
"Ina Sidrah take?"
"Ka nutsu mu maka bayani!"
"No need, kawai ku nuna min inda take."

Ya fita a hankali, yana tafiya kamar wanda yasha abun mayye,  fitowa suka yi aka nuna mishi dakin da take, a hankali da bi bango Ya isa dakin da take barci, gefen bakin ta a fashe, a sanyayye ya isa gaban ta, me yasa sai da kome ya faru, yake jin yafi kowa laifi akan abinda ya faru da Sidrah?

Me yasa yake jin shine ya haifar da kome?
Da ace yau ya amshi auren Sidrah da haka bai faru da ita ba, wata irin zuciya yake dashi mara amfani? Yau tana kuka ne saboda shine yayi kuskurin shigowa da ita cikin rayuwar su, da wancan lokacin ya yiwa zuciyar shi adalci, da haka bai faru ba.

Gashi garin faffutikar niman yancin ya shafi kowa, hatta yarinyar da take cikin maraici, itama laifin shi ya shafe ta, a hankali ya isa bakin gadon, ya tsaya yana kallon sirrintaccen kyan da Allah yayi mata, wanda bai tab'a kawowa tana dashi ba.

Wasu irin kwalla yake zubdawa tare da kallon ta, abinda ya faru d'azun yana dawowa Ƙwaƙwalwar shi daki daki, tiryan tiryan. Rintsa idanun shi yayi tare da buga kanshi da bango baya kaunar dukkan abinda zai zauna a ƙwaƙwalwar shi, baya son kome ya samu muhalli a cikin Ƙwaƙwalwar shi, dan haka ya fita da sauri dan ya san matukar ya cigaba da kallon ta, kome zai zauna a kan shi. Kome zai zauna a inda ba zai tab'a yiwa ba. Ofishin likitocin nan ya koma suka kuma mishi bayani wanda ya sanya shi kuma riris, shi kenan Sidrah ba zata tab'a haihuwa ba kenan.

A hankali ya fito, bayan sun rubuta mishi maganin da zata Sha..ya kawo dakin, dake babu me me kwana a gurin majinya ci tasa shi dawowa gida, tun a bakin hotel din ya fara ruwan bala'i, tare da masifa har office din MD na hotel aka je, abin mamaki koda aka duba record na cctv ya nuna babu abinda ya faru.

Komawa daki yayi tare da cewa kowa ya shirya su bar hotel din tunda jibi Aalim zai zo, daga nan ya gaya musu halin da Sidrah take ciki na rashin lafiya

"Wani irin ciwo ne haka? Daga!"
A fusace ya shake wuyar ta, idanun shi jajjur.
"Karki tab'a fushina!"
Nuna mishi wayar ta tayi, tare da murmushi, wurga da ita yayi gefe.

.. .sannan ya dauko kayan shi suka tattara suka bar hotel din, suka kama wani, daga nan Mommy da Ummi suka nufi asibitin, sun same ta har zuwa lokacin tana barci ne. Gashi tayi wani irin rama. Haka suka gama dubata sannan suka dawo masauki kowa da abinda yake rayawar a ranshi.

Babu wanda ya sami barci, dan tun bayan sake musuluntar da Mommy tayi, take yawan sallar dare,,. Dan wasan kusan daren sun raya shine da bautawa Allah. Ya kawo musu mafita. Da asuba suka nufi masalacin, ana idar da sallah. Ko zama bai yi ba ya nufi asibitin.

A lokacin ya samu ta farka, Idanunta lumshe, tana dai kukan zuci ne tare da zubda kwalla, a hankali ya iso gabanta, ya zauna a kujeran da ke kallonta, yayi shiru.
"Nasan kina jina! Nima ina jin ciwon abinda ya faru."
"Toh meye a ciki? Meye ya faru, it's all about Destiny! Idan ban amshi kaddarata ba,

sunana jahila! Idan na amshi kaddarata ba, ban isa na kira kaina da musulma ba, tun ban kai haka ba nake ganin kaddarorrin rayuwa, kuma Alhamdulillahi Nagodewa Allah da ya jarabce ni ta wannan hanyar.

Ya kuma bani ikon cinye jarabawar, idan nayi hakuri shi zai kara min, ya kuma karamin ya kuma bani har sai na kasa gode mishi. Tunda abinda mutumin yaso bai samu ba, babu amfanin d'aga hankalin. Nagode da bani kulawa!"

Kawai ji yayi kamar yanayin da yake ciki yana karar ninkuwa sama da yadda yake ji baya, ji yaƙe yarinyar ta isa a sanyata a kowani mataki na rayuwa. yarinya karama tana da halayyar magabatan mutane, tana da hakuri irinta manyan bayin Allah, takawwar da ta nuna tare da tawakkali yasan yashi kara kambamata  a zuciyar shi. Katse shirun da ya wanzun a tsakanin su yayi ta hanyar cewa.

"Ban san yadda zan gaya miki ba, amma sun ce kin sami matsala.."
"A wani kaulin shiru tare da binne sirri itace abu mafi muhimmanci da daraja, matukar aka boye domin halin rayuwa toh Ubangiji zai iya mai da shi Alkhairi. Shiru a ajiye sirri wata damar bawa wasu mutanen su rayu cikin salama ce, bayyana shi tamkar musanya farin ciki da bakin ciki ne, don Allah karka gaya min abinda shekaruna da hankalina ba zasu dauka ba.

... Na yafe jin kome, don Allah ka tafi." Ta gaya mishi tare da share kwalla da take son zubo mata, tana kuma ambaton Allah, hakuri da dangana shi ne take jin  suna maye gurbin kukan da raunin da take dashi. Dan haka ta Cigaba da cewa.
"Ya Allah! Na kiraka ka amsa min, Ya Allah kamar yadda ban san kome ba, kamar yadda ban san kowa ba, Ubangiji nayi tawasalli da sunayen ka kyawawa. Ubangiji bani da ayyukan da zan kira su kyawawa, domin kullum cikin kuskuren nake, Allah tuba da rahama nakane, tausayi da jin kai naka ne, Ya Rabbi Alamin, ga Marainiya nan tana niman jin kai dinka, Ubangiji ka sanya Abokin rayuwa ta ya zama me min Uzuri har karshen rayuwata. Ya Allah ka sanya mishi me min adalci har karshen rayuwata, Ya Allah ka yayyafe min ruwan sanyi a rayuwata. Ubangiji idan nayi kuka kamar na rena yinka ne, amma idan nayi farin ciki tare da gode maka, shine abun da zanyi naji sauƙin zuciyata. Alhamdulillahi Nagodewa Allah duk halin da nake ciki."

Ta faɗa tana jan shasheka. Amma taki zubda kwalla, shashekar ce take sosai, har su Ummi suka shigo, shashekar take, bata iya musu magana ba. Tunda Ummi ta fito mata da brush tayi, sannan ta mike ta shiga wanka. Ta fito sanye da doguwar rigar atamfar.

Ta zauna ta baza gashin nan, sannan ta mishi wani irin sauri, a saman shi, wato Zahrah Buhari. Ga kuma gashin da suka zagaye bayanta. Har zuwa kirjinta tayi kyau sosai. Fuskarta kawai zaka kalla  ka fahimci akwai damuwa a kwance kan shi.

Tea take sha, dan da taki sake jikinta, lokacin da Aamil yake dakin, yana fita ta fara tura tea ɗin, tana ci tana tunanin Aalim idanunta ne suka cika da kwalla, kasar wayar ta gani a hankali ta zaro tare da kunna wayar. Tana kunna wayar, sakonin Aalim yana shigowa, budewa

tayi tana kokarin danne kwallar ta, ta tura mishi sakon.
_Eight letters, three words, one regret. I miss you._

A gigice ya kirani, ina dauka yana sauke ajiyar zuciya.
"Dessybaby ina kika shiga? Me ya sami wayarki, tun jiya!"

"Kazo! Don Allah ka dawo, don Allah ka dawo kaji."
"Baby me nene? Gaya min!"
"kawai kazo!"
"Toh shikenan!.gani nan a hanya"
Kashe wayar nayi, dai-dai shigowar Nadrah, tana bina da wani irin kallo. Kauda kai nayi tare da share kwalla. Murmusa min tayi sannan tace min.
"Ya jikinki?"
"Da sauki?"
Bata kuma cewa kome ba, nima kuma haka, sai dai da zaran mun hada ido, zata kashe min ido. A hankali ake hira, har kusan karfe ɗaya saura sannan suka tafi masallaci. Har kusan karfe biyu, ina zaune ban kwanta ba, dan bana jin barci, damuwa ce take son sani a gaba tare da tuna abinda ya faru.

... Sai karfe hudu suka dawo, ina barci, suka same ni. Can na farka na gaishe su, sai lokacin suke tambayana abinda ya faru. Kasa magana nayi,.kaina a sunkuye, kwalla na zuba min.

... Duk dakin ya dauki shiru, domin kaina a sunkuye, kamshin turaren da ya cika dakin ne ya sani sauke ajiyar zuciya, me haɗe da kuka, na sauka da gudu na rungume shi, tare da k'amk'ame shi.
Rungume ni yayi da sauri Aamil ya bar dakin, ina kuka tare da cewa.
"Karka tafi ka bar ni, don Allah ka zauna dani, ka zauna dani har abada,.karka kayi nisa dani, Ya Aalim karka tafi ka zauna dani."

Rungume ni yayi tare da sumbatar wuyana, a hankali su Ummi suka bar dakin, rufe kofar yayi tare da kai ni bakin gado, yana kallona.
"Dessybaby! Meke faruwa? Na tambayi Aamil yace min babu kome, ke kuma gaki asibitin?"

"Ciwon ciki ne,. lokacin da abin ya faru suna masalaci har na fadi na bugu, Amma da dauki tunda ina jin ko zuwa dare zasu sallame ni!"

Kallon fuskana yake, tare da cewa.
"Duk a faduwar kika ji wannan ciwon?"
"Eh ko baka yarda dani bane?"
"Kawai ina jin kamar sum one attack You!" A rud'e na kalle kofar tare da rasa bakin magana ban san lokacin da na sake kuka ba, na shiga niman hanyar da zan kashe maganar ganin yadda na birkice nace ya mai dani gida.

Rike hannuna yayi tare da cewa.
"Wallahi duk ranar da na kuskura na kama wani ya tab'a min ke? Domin if you want to no me touche my Woman, na rantse da Allah, zan kashe."

Rufe mishi baki nayi, tare da sake wani irin kuka.
"Karka fada haka, domin!"
"Iya gaskiyar kenan, duk wanda yake son sani na, ya taba min Matana, toh ba makawa, zan aka aikata kome."

.. shafa fuskana yayi cikin nutsuwa, yana faɗin.
"Karki damu ai sai an tab'a ki!"
Da gaske yaƙe fa, abin tausayi. A hankali ya gama mitar shi yaje ya amso min sallama, a sannu nake tafiya sabida jin da nake cikina zuwa bayana a daure, muna fita ban san ya akayi ba, kawai na tafi zan zame, kawai sai jin muryan Ya Aamil muka yi kamar zai fasa makogaron shi, yayi wani mugun tawowa, kafin ya tare ni, Ya Aalim ya riga shi. Ya d'ago ni tare da manna ni a kirjin shi. Ajiyar zuciya na sauke ina me rike rigar shi. Cikin sanyin jiki Aamil ya koma inda motar da zata mai damu masaukin mu, ya bude min inda zan zauna, a madadin haka. Nadrah ce ta zauna tare da b'ata rai. "Fita a gurin Sidrah."

"Malam ba dai surar da ka gani bane yasa kake jin sha'awan ta ba?"
"Meye haka?"
"Kai ka sani,"
"Don Allah ki taimaka min, mu rufe sirrin nan."
"Au bai sani ba? Toh zan rufe amma ka fita hanyar ta, idan ka Cigaba da shiga huruminta zan yi magana kuma zan fidda sirrin boye,babu abinda ya dame ni. Kai nawa ne, Sidrah na Aalim ce magana ya kare."
........🤣🤣🤣 Ina son Action dinki Nadrah... Fire dem..
[11/26, 5:59 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Be with me.

Koda wasa ban d'aga hankalina ba, sai ma zubawa Action ɗinta ido nayi naga yadda zata yi da sauri Ya Aalim yaje ya fita da ita, zuwa gurin gyaran ciwon.. sake janyon tinah yayi yana kallon inda nake, ya kuma hade bakin su, cikin jin dadi yake kallon na da wutsiyar ido. Ture Tinah yayi ya dauki kwalbar giya ya d'aga sai da ya shanye tass.

Ya kuma ɗaukar wani kwalbar ya shanye, idanun shi a kaina.
Tashi nayi tare da, barin gurin, a hankali ya taso zuwa gurin d'an uwan shi, wanda ya shigo kenan.
"Kasan me? Ban tab'a ganin abin da ya min kyau a duniya sama da ita ba! Ta daki zuciyata lokaci guda!

Ta gama da rayuwata, I love her! She is Queen of my kingdom! I love her! Me yasa tuntuni ban fahimci darajar ta ba, sai da na rasata.

Yau ina son kowa yasan yadda nake sonta, Ina sonki..."

Faduwa yayi a jikin Aalim, "please be with me"

....
Haka ya shiga barci, abin ya bawa Aalim mamakin, ga Nadrah da aka fitar da ita, gurin gyaran ciwonta, a hankali ya fito da Aamil zuwa waje ya nufi inda. Nadrah take, yana zuwa tayi wani irin kafin ya tambaye ta, ta fadi, da sauri ya rike ta, lura da yayi tana son ya dauke ta, ya sashi riko hannunta a cikin motar da ya kawo mu.

Phantom, ya shigar da ita bayan inda Aamil yake, Ni kuma ina gaban motar, kallon juna muka yi tare da murmushi, janyo hannuna yayi tare da daurawa akan motar muka shiga tuki. Muna hira jifa jifa.

... Har muka iso gida, kallona yayi tare da cewa.
"Ki taimakawa Nadrah, zan dauki Twins broda."

"Meke damunta da zan dauke ta?"na tambaye shi, hade giran shi yayi cikin nutsuwa sannan yace min.
"Nace ki riketa karki yarda kice zaki juyani, kece a kasa dani."
"Kayi hakuri!"
Na fada zan fita, ya riko hannuna. Kallon me ye nayi mishi.
"Daga magana har zaki fita wata ga masifaffe zai fara."
Gyara zama nayi tare da cewa.
"Toh ka bani izinin fita!"
"Zaki iya tafiya;"

A hankali na bude motar, na iso inda take zan kamata, ta ki, sai da ta fito kawai ta fadi tare da sake kara, nad'e hannun nayi a kirji ina kallon ikon Allah.

"Sidrah!" Ya daka min tsawa, kallon shi nayi, cikin masifa yayo kaina zai mare ni ne ko meye ne, sai ganin Aamil muka yi ya shiga tsakiyar mu, yana kallon Aalim, yana tangadi, tare da cewa.
"Wato dan baka da mutunci zaka daki Mace me daraja irin Sisisisidrah, toh wallahi ba zaka tab'a ba matukar ina raye.

Ba zan tab'a barin hawayen bakin ciki ya sauka.a idanunta ba. Kai ko kaine ka tab'a ta sai na... Karka ce zan ji tausayin ka, harbeka zanyi indai akan tane, sannan wancan Yarinyar ita ta jefa rayuwata a cikin wannan yanayin.

Itace bata bani kulawar da ya dace ba, kai kuma da ka sami me kula da kai zaka zauna kana biyewa makircin ta.

Badan kome ba nake magana baz sai dan zan iya ji maka cicicicicicwo"

Daga hakan ya shiga kwara amai, sannan ya koma zai zube dan uwan ya rungume shi.

Juyawa yayi tare da cewa..
"You are wonderful lady! You deserved every thing " daga haka sai barci, har ya fara ya kuma farkawa, da haka muka shiga gidan, kunya ce ta kama Nadrah. Koda muka shiga kowa dakin shi ya wuce.

---
Kwanakin da suka biyo baya, duk babu dad'i, dan tsakanina da Nadrah yana tsami, har ya kai zata d'aga hannu ta dake ni, Allah ya taimaka Aalim yazo ya shiga tsakanin mu, a can bayan gidan akwai wani katon swimming pool, ban cika shiga ruwa ba, amma idan ina cikin damuwa, ina yawan zuwa gurin na zauna. Daga nesa ta hango ni, ina zaune ni daya na, kafaffuna a cikin ruwan, kaina a sunkuye.

Swim din yana da zurfi gaskiya, dan haka tana zuwa abinda yayi shine kawai tura Ni, sannan tabar gurin, shi kuma Ya Aamil ya dauko kwalbar giya zai sha idan zuciyar shi ta cunkushe ƙwaƙwalwar shi ta dame shi da tunani, sai kawai ya dauki kwalbar ya zago baya ya sha, sai ya kwanta a kujeran hutu, dan can na kwanakin baya Ummi tayi mishi fada sosai, toh tunda ya fahimci haka sai ya zago yafara sha.  Daga nesa ya hango hannuna, ina niman wanda zai ciro ni. Dan sai nutsewa nake, wurga da kwalbar yayi da gudu ya tawo, yana zuwa ya faɗa cikin ruwan lokacin har na nutse cikin ruwan, bina yayi yana kallon fuskana.
Shafa fuskana yayi a hankali ya furta..
"Me yasa ba zaki kasance dani ba? Sidrah! Me yasa na rasa ki bayan nasan kina da daraja, please be with me!"

A hankali ya matso tare da d'ago kaina, ya rungume fuska na ya haɗa da nashi, duk da zuciyar shi tana tunatar dashi abinda yake shirin aikatawa kuskure ne babba, haka bai sanya shi ya daina ba, sai da ya haɗa bakin mu, ya shiga huro iskar bakin shi yana hura min, a hankali tare da doke ruwan hancina.

D'ago tai yayi tare da fito da ita sama, ya d'aga ta kenan sai ga Nadrah. Dariya take sanan ta iso gurin, tana kallon shi.
Kafin ya fito daga ruwan ta saka kafarta ta kuma shure Sidrah ta faɗa  cikin ruwan.
"Ke dakikiyar ina ce?"

Da sauri ya kuma komawa, yana d'agota, ya goyeta tare da fito da ita ta kwantar da ita, a hankali ya tsaya, yana kallonta, kamar wanda aka jefo Aalim, sai gashi nan, yana zuwa abinda ya fara yi shine matse cikin ta, sai da tayi ta fitar da ruwan da tasha, kafin ya kuma matse ta ruwan suka fita sosai, a hankali ta bude idanunta, ta mika mishi hannu, rike hannun yayi tare da aka wa a kan fuskar shi.
"Baby Love! Taya kika fada ruwan?"
Lumshe idanunta tayi tare da cewa.
"Sanyi!".

Daukarta yayi zuwa cikin gidan, gurin su Ummin. Nan aka Mommy ta kira Family Dr din su yazo ya shiga dubata.

---

Tunda ya koma daki, yayi shiru. Shigowar Nadrah, tare da zuba mishi ido, a hankali ta isa gare shi.
"Kana wuce iyakarka! Na soma gajiya da abinda kake min."
Bai mata magana ba, dan yanzun bata da abinda zata mishi barazana, kawai ta kyale shi ne.

Haka suka yi ta rigima, karshe ya fincikota, suka fada gado. Kallon shi tayi sannan tace mishi.
"Sake ni, bana son Iskanci."
"Me zan miki kawai na miki haka ne dan na huta da surutunki" daga haka ya ture ta, daga gadon ta fado ƙasa.

...... Ni kuwa sai da na kwana uku ina jin kunne na kamar wani ana buga min ganga a cikin shi. Sannan na ware, kamar bani ba. Ina zaune naga sakon Ya Aalim, da sauri na fito ina zuwa dakin abinda na fara gani, katon zanen hoto na a falon ya dage sai zanawa yake, murmushi dauke a fuskana na isa falon naga kowa yana yaba hoton, ina zuwa na kalli yadda nake cikin hoton dariya nayi har da wani Flower crown. Nayi kyau.

Kwantar da kaina nayi a bayan shi nace mishi.
"Ina sonka!" Tarin Ya Aamil muka ji alamar ya kware, tari sosai ture ni yayi ya nufi gurin d'an uwan shi, sai da yaga ya daina tafin sannan ya dawo yana kallona yace min.
"Sorry baby bana son ganin twins brother cikin damuwa ne!"
Juyawa nayi na kalli Aamil din wanda yake ta aiki da laptop.
Wato idan na fahimci abinda wadannan mutanen suke nufi, nice basu kaunar na alakantu da Aalim.

Babu shiru na birkice musu akan lallai sai an dawo dani gida, kai har abincin na daina ci. Ganin haka ya shiga nutsuwar shi, ya dawo jikina, ina dalili zasu Rabani da abinda abinda nake so.

...... Sati huɗu muka wuce tunisia a can aka mana gyaran jiki na wani irin kyau muka yi,.a cikin sati biyu muka dawo Egypt. Anan aka mana orden kayan walima da kuma kayan da zamu saka ranar liyaffa, sannan muna dauko hanyar naija. Tunda muka dauko hanyar gida, naga Ya Aamil sai shige min yake, karshe a airport na tsayar mishi tare da gaya mishi maganar da sai da yayi ta dukar bango, na kuma tabbatar mishi koda wani kaddara zata fado wallahi ba zan tab'a auren shi ba.

Dan haka yaje ya sami kyakyawan mace da yake bukata kar ya kuma dawowa gare ni, ai ko babu kome ana barin halas domin kunya, dan haka kar ya kuma damuna,.idan ya kuma zan mishi abinda ba zai ji dad.

Ganin da ya kawo min naki amsa, dan dole ya hakura, da min magana har muka iso kano da kaya nikiniki.

Sannan suka wuce, Bayan tafiyar su naga wani sako tare da cewa.
```Anyone can love rose
but no one loves a leaf that adds beauty to it

moral: don't love someone who is beautiful,
but love the one who makes ur life beautiful.```

Banza nayi da sakon ban kuma bi takai ba, tunda muka dawo, ake shirya shiryen bikin, dan haka kwana na biyar muna nufi Hadeja.

---

"Bani s card din da na baka,. kafin ka tawo daga Saudiya."
Babu musu Alhaji Abubakar ya ciro mata tare da mika mata, murmushi tayi sannan ta saka a wata wayarta sungsum, ta shiga har inda ta ajiye video din ta kunna, Alhaji Abubakar da wata mata, nuna mishi hoton tayi a firgice ya mike tare da cewa.
"Ke bana son tashin hankali a ina kika samu wannan videon"

Baya tayi da wayar sannan tace mishi.
"Ji kishin kishin, zaka fita takarar dan majalisar dattawa shine na dauke ka, kai da Matar driven ka, wanda ka biya musu Umrah, gaskiya Alaji ka iya cin mace, but karka damu, nayi haka ne domin na maka gargad'i da babban murya kar na kuskura naji labarin ka a cikin gidan aurena.

Ka zauna ni zan biyo ka, idan kuwa ka kuskura ka shiga cikin lamarina."

Takowa tayi gaban shi ta kamo jalbaban shi, sai da ya zabura. Kashe mishi ido tayi cikin kwarewa da iyawa, tace.
"Kaciya zan kuma maka, idan ka nutsu kuwa, sati Uku da aurena zan nime ka dan naga har yanzun da sauran ka" daga haka ta bar shi tsaye har ta kai bakin kofar tace mishi.
"Kayi nazarin idan na sake wannan a kafar sadarwa na zamani ya zaka ji? Karka yarda na fusata."

Daga haka tabar gidan abinta, ta gama da tsohon banza.

**Hidimar da ake, ba na wasa bane, musamman iyayen Nadrah, sun zo sun mata jere da wuri, ni kuma Mommy da Ummin sun min dan tun a cairon suka saya min kayan daki, wancan kuma aka barwa Mommy, domin idan aka daura auren mu tare da nata da Abba ne.

Haka akayi ta shiri sosai, kamar yau za a fara aure a gidan, kasan cewar za'ayi bikin har da na Harira da Kuma Hasnah.
```

Dan haka ta kowanne fanni babu b'ata lokaci..
.....
Tunda muka dawo aka dame ni da turo sakon, wallahi bai tab'a burgeni ba, asalima ana turowa zan goge.
Na kuma mai da hankalina, akan shirin da mike, Saratu an kawo sadakin dan haka da ita za a hada bikin

Domin sun kawo kome nasu, Allah sarki mun je ana raba anko har mun hadu da Angon, kafin mu dawo sai ce mana akayi wai barin mu bakin kasuwa mota ta buge shi....
#Mai_Dambu
[11/27, 2:41 PM] Anum Muhammad Bello❤️: No matter....

Abun tausayi koda muna isa asibitin an hanamu gashin haka tayi ta kuka, karshe aka lallabata muka dawo gida. Sai dai ta koma kamar taɓaɓɓiya haka tayi ta surutu, karshe sai suma take sakamakon janye auren da dangin Rulwani suka yi.
Duk rashin imaninka idan kaga halin da take ciki sai ka zubda kwalla.

Dan kusan nice a kusa da ita, haka zata yi ta kuka, ina bata hakuri,.karshe dai sai da aka ririta wani rikici da sunan nice sanadin fasa aurenta. Wannan abun ya matuƙar min ciwo.

Ranar sunga bala'i da rashin kunya, abin har samun su yayi dama haka nake da masifa, nake kallon su. Kamar zan cinye su sanye haka nake kallon kowa nayi fushi sosai domin karshe na fita na bar musu gidan baki daya dan ina cigaba da zama raina b'aci zai kuma na zane kowacce mata.

Gidan kawuna yakubu na koma na zauna, a da ne nake tsoron zuwa sabida kar a min magana a Yanzun kuwa ko takan kowa banayi, takaina nake dan haka ban damu da duk abinda zai faru sai dai ya faru.

---
"Kin tabbatar Arianah abin zai yi amfani?"
"Akan me zan cuce ki, Nima wata yar dakin mu ta bani labarin shi, kawai ni kuma na nimo miki shi."

Murmusa mata tayi sannan ta rike abun da kyau, yadda zata kuma ci Uban kowa hankalinta kwancen, sannan ta cigaba da cewa.
"Lallai zan yi abinda nayi niyya! Domin sai na hana kowa sukuni, sai na gaggari kowa."

Haka suka ci-gaba da kulla duk wani sharrin su, tare da tabbatar da abinda zasu aikatawa..

** Duk yadda ya so cireta a ranshi abun ya faskara, asalima sai yawan mafarkin abinda ya faru yake matukar zai kwanta zai ganshi yana maida mata kayanta, idanun shi a rufe ita yake

gani.

"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun Ya Allah, na tuba karka barni cikin masu son kai da son zuciya. Ubangiji ka rufa min asiri ka cire min soyayyar matar da Dan uwan zai aura." Yana wannan addu'a yana risgar kuka tare da niman yafiyar Ubangiji.

...... Ko jiya da yamma Nadrah da Kawayenta sun zo gidan, suka gama zaga part din su. Inda taga kamar anyi son kai domin kuwa gani take shashin su Sidrah ya fi nasu. Dan haka ta kira Aamil da yazo suka dan keb'ence.
"Ni baka fahimci wani abu ba? Kalli yanda aka gyara part su Sidrah bane?"

Kallon gidan tayi sosai, kafin ya mai da kanta, yace mata.
"Sai akayi yayya?"
"Toh naga baka fahimci abinda yake faruwa ba, amma kayi hakuri."

Daga haka ya bar mata gurin, dan shi yaki Kawata gidan kome na cikin gidan da wajen duk iri daya ne, kawai banbancin su yadda aka Kawata part din su Aalim ne.

Kawai shi bai wani damu da yayi murnan buki ba, amma duk wani kayan shagali da abubuwan bukata, duk Aalim ne yayi musu.

Bin bayan shi tayi da harara tana fadin.
"Ka kusan shiga hannu na!"

Haka ta biyo bayan shi, tana kallon yadda take tafiya a sanyayye, tsayawa yayi a harabar gidan sakamakon shigowar Aalim.

Da sauri Aalim ya fita, daga motar. Yana fitowa ya isa gare shi yaja hannun shi, suka shiga falon bakin Abba. Zama suka yi tare da fuskarta juna.

"Twins meke faruwa?"
"Wallahi ban sani ba!" Aamil ya faɗa a sanyayye idanun shi yana cika da kwalla.
"Kamar kana boye min wani abu?" Inji Aalim,
"Bestie! Tabbas rayuwar bata da wani abu da zaka yi alfahari dashi kamar yarda da ƙaddara!

Twin nayi Kuskure, amma don Allah kayi hakuri karka juya mata baya"

Ya fada a hankali tare da goge kwallar da yake son sauka yace.
"Babu wnada ya fi karfin ƙaddara, duk abinda ka gani a duniya yana da sila, duk abinda yake faruwa ni ne musabbanin shi.

.... Wallahi ina ji kamar zuciya zata buga, ina da Damuwa sosai, na rasa yadda zanyi dashi, Amma idan na tuna ina tare da kai sai naji ina da yakinin zaka fahimci abinda nake nufi."

"Toh Allah ya kawo mana mafita amma ka rage damuwa." Inji Aalim,

"Zan rage amma kayi hakuri, ka kuma yafe mana." Daga haka ya mike tare da barin d'akin. Shima Aalim ya nufi gidan su.

Inda ya hadu da Nadrah, da Kawayen ta. Kauda kai yayi cikin nutsuwa ya shiga cikin gidan. Yana shiga wani irin zazzaɓi ya rufe shi, dakin da aka tanadar mishi ya shige, ya kwanta har da lullubewa yayi da bargo.

..... Har aka yi sallar magarib da isha, yana kwance wasa wasa. Sai gashi har zuwa karfe biyu na dare yana jin jikin shi kamar ana mishi lugude. Sai wajen karfe uku ya samu ya shiga ban daki yayi alola tare da wanka yazo yayi Sallah, yana idarwa ya kuma rarrafawa ya haura gado.

Wasa wasa, sai da ya kwana ya wuni babu wanda ya san yana kwance ba lafiya ba sai da ya kuma kwana babu shi babu labarin shi anan ne fa, aka shiga niman shi daga karshe aka gano yana kwance na lafiya, Aamil ne ya taimaka mishi suka nufi asibitin gashi bikin saura kwana biyar.

......
Kullum na kira wayar sai naji ance a kashe gashi bani Number kowa a cikin gidan, dan haka na rasa yadda zanyi, na dai zuba idanu naga ta inda kiran shi zai shigo min.

Kullum idanuna yana kan wayata, idan naji tayi kara zan duba, har ya kusan tab'a min zuciya, domin haka kawai naji zazzaɓi yana rufe ni.

Kamar jaraba idan ban tura sakon biyar shi ba, toh zan kira ya kai sau bakwai wani lokacin ma zan kira yafi sau goma,

Har Mutanen gidan kawuna yakubu sun fahimci ina cikin damuwa sosai, sabida yadda nake raba idanuna akan shi, har dariya suke min wai ai na zaucce eh na zaucce akan Aalim. Ana saura kwana uku na kira wayar yana shiga muka sauke ajiyar zuciya a tare dashi.
"Ina kashi gane?"
."bashi bane, twins brother ne!"
"Toh sanu, ina mijina yake?"
"Yaushe aka daura auren?"
"Wannan ba matslar ka bace ta muce, idan ba zaka bashi wayar ba ka kashe kawai karka kuma kunnawa."

"Toh boss lady! Amma kin san yadda muke da shi mijin naki, boss lady?"

Kashe wayar nayi tare da Cigaba da abinda nake.. kusan wunin yau nayi shine cikin jin haushi, da na kuma kiran shi Aamil ya dauka, tare da cewa.

"Boss lady! Ga angonki nan bai da lafiya ne, ya hanani na gaya miki, shine kika kira tare da tsagalgale ni"

Kamar yana gaba na, na murguda mishi baki na tare da cewa.
"Wannan matsalarka ce ba tawa ba, don Allah ka bashi muyi magana."

Kasa kasa yace min.
"Toh fitilar Tagwaye!"
Kashe wayar nayi can ya kirani, ina jin muryan Aalim na shiga zuba mishi shagwaɓa tare da rikici kala kala. Kuka kuwa bori nayi ta mishi tare da fitina kala kala, shi kanshi abin dariya ya bashi sabida yadda nake kokarin sanya shi farin ciki.
.....
Lokaci da Aamil ya mika mishi, fita yayi gaban shi yana faduwa, tare da jin zafin a zuciyar shi, a duk lokacin da zai ji Aalim da Sidrah suna keb'ence toh ji yaƙe kamar zuciyarshi zata fita daga kirjin shi.

Wani irin ciwo yake ji, kuma a sanin shi bai soma jin haka ba, sai ranar da ya shirya Sidrah, a ranar ne ya fahimci yana mata makauniyar soyayyar, yana jin matuƙar bai same ta ba, har abada ba zai kuma samun wata bayan ita ba, Sai Yanzun yake kara fahimtar dalilin son Nadrah ba kome bane yaja haka sai masifar kaunar abu me kyau.

Bai tab'a niman Alkhairi ba a rayuwar shi sai dai Allah ya bashi abinda yake so gashi dai ya same Nadrah ana gab da auren su amma kuma ya kasa fahimtar kome akan ta, sai ma wahala da take bashi, a Yanzun kuma idan ya fito da halin da yake ciki bai san wani yanayi dan uwan shi zai shiga ba, ajiyar zuciya ya sauke tare da niman Ubangiji ya bashi dangana akan Sidrah dan yasan ya haramta mishi,

Dan haka cikin tsarkaken niyya, ya fara addu'o'in. Har ya shiga addu'o'in yake dan bai shirya cutar da dan uwan shi ba.
Alhamdulillah an sallami Aalim, amma kuma bai da lafiya gaskiya b'oyewa yaƙe, ta cikin jikin shi yake fahimtar akwai matsala, duk yadda yaso b'oyewa Aamil sai da ya takura mishi ya ce babu kome, amma akwai matsala babba sosai. Amma yana kan zuwa asibiti a b'oye...
..... A cikin kwanaki biyu, har azumi yayi tare da sallah dare, walaha, da nafilla dub bayan sallar farillan, ban da Isha da magbri. Shi Ubangiji gwani ne gaggara misali, lokaci guda ya zare mishi damuwar da yake damun shi, tare da sanya mishi juriya da hakuri.

Haka ya kuma kawo nutsuwa da hankali a tare dashi, ana gobe daurin auren, suka nufi gurin Sidrah. Da kayan fitar bikinta, murna da tayi ba iyaka, dan haka ko da zasu tafi sai da tayi ta rigima. Shi kuwa Aamil dariya suke bashi. Dan a Yanzun ya fahimci Babu abinda ke dawainiyya dashi sai sha'awa, Alhamdulillahi a Yanzun kallon Kanwar shi yake mata.

. Cikin sanyin jiki ta fito fuskarta a kumbure, da sauri Sidrah ta nufe, tare da cewa.
"Sis lafiya?"

"Hmm! Na gaji da zaman daki ne nazo nan!"

"Toh muje ku gaida dasu Ya Aalim." Tabe baki tayi tare da cewa.
"Ba zanje ba ki karasa kice ina gaishe shi, banda wancan me idanu a tsakar ka din nan." Ta zabgawa Aamil harara.

Sannan ta juya zuwa cikin gidan abinda, Sidrah na komawa tace musu.
"Tana gaishe ku."
"Ba zamu amsa ba, me yasa bata iso ba?"

"Ayya mijin da zata aura ne yayi hatsari, shine aka fasa auren."
"Ai shine take harara ta? Ni na buge mata shi ne da zata harare ni? Da na kamata sai na karya kafarta da shegen idanunta irinta tsaka, sai shegen siririntaka kamar fol."

"Ai kuwa itama cewa tayi bata son ganinka."
"Kutt ina wasa da yarinyar nan ne? Sai na shiga cikin gidan na mata rashin mutunci,"
Ya shiga kokuwa zai fita. Kawai sai ga ta nan kuma ta kuma fitowa.

Shima ana danne shi kawai ya ture Hannun Aalim, yaje yasha gabanta. Tare da tsayawa.
,"Ke Ni kike harara?"
"Eh na harare ka, sai me? Kasan yadda nake jin haushin ka, kuwa? Toh b'ace min a hanya kafin na baka mamaki."

"Ke ni kikewa rashin mutunci?"
"Toh uban Uwata sai kar na maka dalla bani hanya."

Make bakinta yayi da sauri ta rike bakin tare da d'ago kai tana kallon shi, shiga tsakanin su muka yi.
"Wallahi sai na rama, sai na maka rashin mutunci a gaban kowa sai kaji kunya ehhe "
. "Twin bro sake ni, na ci kaniyar yarinyar nan."
"Toh me ta maka?"
"Baka ga yadda take harara na ba? Baka ga yadda take min rashin mutunci ba?"
"Wallahi ban gani ba!"
"Toh karka gani, sai na zaneta."
Sosai ya fusata fa, itama Saratu haka karshe tafiya suka yi ran kowa a b'ace,
"Toh meye yayi miki?"
"Haushi ya bani? Kawai na tsane shine."
Ikon Allah, shima kuma haka ce ta faru bai san kome ba sai tsanarta.

.....
Al'amarin biki kuwa, an shirya za a fara daura auren Aamil sannan azo a daura na Aalim, haka kuwa aka shirya.

Ranar Asabar, aka fara daura auren Nadrah da Aamil, akan sadakin dubu dari cif.

Bayan an gama suka kuma dibo jiki, zuwa Hadeja, aka daura na Aalim da Sidrah, akan sadaki dubu dari da hamsin, sannan aka dauko amarya, sabida dinner da zasu yi anan.
#Mai_Dambu.
[11/28, 1:34 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Sickness

Tunda Suka dauko hanya wani irin zazzaɓi ya rufe shi, sake jikin shi yayi a jikin Aamil. Yana rawan sanyi. Kafin wani lokaci ya fara kwara amai. A gaggauce aka wuce dashi asibitin. Inda aka yi mishi karin ruwa, da allurai basu dawo ba sai karfe bakwai na dare ana shirya dinner.

Kamar ba za ayi ba, amma yace.
"A'a za ayi fa! Bikinka ne fa dole ayi shagali, dan haka nima zan je."

Daurewa kawai yake amma idan kaji yadda yake fidda huci a jikin shi, sai ka dube shi toh wai a haka basu ga kome da ke damun shi ba.. shi da Yake jin ciwon yasan halin da yake ciki, dan haka suka shirya aka nufi gurin taron da yake harabar gidan.

Lokacin da muka iso, gurin mu ma, anan suka ce kowaccen mu ta duba mijinta, kasancewar shigar su kome nasu iri daya ne, ita aka fara bawa dama, koda ta zo a gaban Aalim ta tsaya, sannan aka bani damar nazo, ina zuwa yaje kusa da ita, nace mata.
"Shekaru biyar ba wasa ba, a cikin wannan yanayin na fahimci waye nake so, dan haka ga Aamil can, wannan abincin Ruhina ne shi."

Cikin mamaki ta kalli Aamil tare da isa gurin shi. Ko kallo bata ishe shi ba, domin ya gama cika da ita, a sanyayye na isa kusa da Aalim, tare da zama a jikin shi, kamar dama ni yake jira kawai ya zube a jikina.

A razane na saka salati, Aamil ne ya tawo inda yake, tare da saka shi a kafad'a shi da Ghali. Muka nufi cikin gidan, abin da ya sanya aka fasa dinner din kenan.

Daga cikin gidan aka nufi asibiti da ita, tunda suka fita nake kuka, kamar rai na zai fita. Tsoro ya gama kama ni, abinda ya faru da Saratu ne ya fado min, mik'ewa nayi zanyi magana ban san ya aka yi ba, sai ji nayi bana gani bana jin kowa.

Kai na ya min wani irin dumm, ban kuma sanin abinda yake faruwa ba, sai washi gari da naji Inna Sabuwa tana cewa.
"Sannu Sidrah, Allah ya baki lafiya tare da mijinki." A hankali na bude idanuna tare da mik'ewa, na zauna ina kallon su. Tare da tuno abinda ya faru. Idanu na ne, suka shiga cikowa da kwalla.
"Ina yake?"
"Ki kwantar da hankalin ki, kinji Babu abinda zai same shi."

Inji Ummi, da ta shigo rike da kayan abinci, a hankali na kalli hannuna da ake cire min abin karin

ruwa. Sauka nayi zan nufi ban daki na zube ina haki. Da sauri suka yo kaina, tare da d'aga ni. Saratu ta kai ni ban daki nayi alola nazo na gabatar da sallar asuba, tunda na idar nake addu'a. Ina kuka sabida tausayin rayuwar mu.

Saratu da zata rarrashi ni, itama kuka take karshe dai mai da ita gida aka yi, Ni kuma Mommy da Ummi suka zauna a jikina, wani irin kulawa suke bani, cikin so da kauna.

... A can dakin da yake kwance kuwa, drs ne hudu akan shi, bai san waye akan shi ba, duk iya bincike anyi amma babu wani abun da suka gani, sai dai lura da suka yi da kankancewar alauran shi, abin da ya basu mamaki kenan. Suka kuma mai da hankalin su akan bincike.

Babu wani abu, kawai dai yanayin zazzaɓin da yake fama dashi ne. Dan haka basu wani dauki ciwon da zafi ba, dan sun gano matsalar da ga zazzaɓi ne.

..... Wunin yau babu wanda ya min wani zance akan shi sai ma kulawar da ake bani, dan haka koda likitocin suka musu bayani, hankalin kowa ya tashi, musamman Aamil wanda yake jin kamar zuciyarshi zata diro kasa.

A hankali ya shiga cikin dakin, yana kallon shi yadda yake ta barcin shi. Idan bai yi karya ba, zai iya cewa banbancin shi da Aalim shi yana kwance ne, amma shi ma yana masifar jin ciwon a jikin shi. Sau uku ana gwada shi daga jiya zuwa yau sai da yasha magani. Amma haka bai dame shi ba, kamar bakin labarin da suka gaya mishi.

Kwalla ne ya cika mishi idanu, zama yayi tare da rike hannun shi, yana fadin.
"Alhassan! Meke damun ka? Don Allah tashi kai ka min alƙawarin zama tayi tare,.kuma alkawarin da kayi hada Zuri'ar mu, dan karsu rabu kamar yadda bamu rabu ba.

Don Allah karka min haka. Don Allah ka tashi dan rayuwar Sidrah, kaji don Allah karka mai da ita marainiya, tana cikin damuwa karka mai da ita mara galihu, katashi d'an uwana. Don Allah Allison karka tafi kabar mu, muna bukatar ka."

Idan kaji yadda yake magana sai tausayin shi ya cika mata zuciya, haka ya zauna a jikin shi tare da riko hannun shi, a gefen fuskar shi. Har aka zo aka fitar dashi.

.... Gida aka mai da Aamil, tare da sashi ya kwanta. Ko zai samu damar hutawa dan jiya bai sami barci ba, yana kwance gabaki daya jikin shi ya dauki zazzaɓi, Nadrah tashigo. Kwanciya tayi a bayan shi, tare da sakalo hannun ta, bayan shi.

Tunda yaji ta a jikin shi ya matsa ta sake shiga jikin shi, duk yadda yaso kauce mata tare da nuna mata bai da lafiya, mayya sai da ta kai shi matakin da ya kasa fahimtar kome, sai gashi ya sabule rigar ta, tare da zubawa boons ɗinta idanu, tare da had'iye yawu. Ya shiga lasar su kamar ya samu Lillipop. Shan su yake tare da matse su.

Ga baki daya ya fita hayacin shi, bai san lokacin da ya farmata ba, wani irin sarrafa yake a nitse tare da kwarewa, yake bin ta. Gaba daya ya gama saka ranshin tare da kwalafa rai zai samu abinda yake kallon zai tara, daga waje a rufe ba laifi amma yawan saka hannu ya budar da cikin haka ya zura, Hakimar shi.

Cikin wani irin yanayi, ya dauke wuta, haba dole rashin kunyarta yayi yawa, ashe ta kwashe duk wani darajar ta a waje ne, haka yayi ta mata mata roughly sex. Cire tausayi yayi ya mata wani irin wasan ci, dan tun yana ganin yadda take jin dad'i.

Har takai da kanshi ya fahimci, yadda take niman yakince shi daga jikin ta, sosai yake bata wuta, kuma da karfi, sai da yaga baki daya bata iya fahimtar kome sannan ya janye daga jikin ta. Yana faɗin,

"Jaka dabba, ki sani a ranki wallahi sai nayi aure har yanzun ban huce ba, wallahi sai na auro wacce dare daya da zanyi da ita sai ya zame miki daren mafi muni a rayuwar ki, wawuya kawai."

Dake bata kunya a rayuwarta sai ce mishi tayi .
"Eh naji amma kai da ka samu na taimake ka, har shine zaka zage ni. An gaya maka."

Abinda ya fusata shi kenan, bai san lokacin da ya cakumo rigar ta, ya shiga zane ta. Yana kwallon da ita. Sosai ya mata duka, sannan ya rufeta a toilet, ya fita ya bar gidan baki daya.

Tabbas alhakin yaran mutane ne ya kama shi, Shi kan shi bazai iya cewa ga yawan yan mata da ya kwantar dasu ya kuma raba su da kimar su ba, dukda wasu yan mata har gida suke biyo shi.

Bai tab'a kama mace da karfin tsiya ya biya bukatar shi ba, "Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun Ya Allah, na tuba. Ashe haka abin yake da ciwo" ya faɗa a sanyayye. Lokacin da ya dawo asibitin ya samu ana bani abinci dakyar ina kuka. Tare da rokwansu, akai ni dakin da Aalim yake.

"Tashi muje." Da sauri na sauka muka nufi waje.
"Don Allah kayi sauri."

Mamaki ya cika mishi rai, har suka isa d'akin, wani irin ajiyar zuciya ta sauke tare da isa gaban shi. Tana kuka, tare da fadawa kirjin shi, tana kallon fuskar shi tana faɗin.
"Don Allah,ka tashi kaji, don Allah ka tashi kaji, wallahi ba zan iya rayuwa babu kai ba. Duk mazan duniya nan kallon mata nake musu, wallahi bana son kowa sai kai, ka tashi ka taimakawa maraicina. Karka tafi kaji ina sonka nima mutuwa zanyi don Allah karka min haka"

Yadda take wannan surutun cikin kuka da tashin hankali, sai ka tausaya mata, yadda take kuka kamar zata shiɗe.

Duk ta fita hayacinta, idan ka ganta zaka ji zuciyarka ta karaya, yayi yayi ta fita taki, haka ta zauna a jikin shi, karshe hayewa gadon tayi ta kwanta a kirji shi. Har barci yayi gaba da ita. A haka tana barcin hawaye na zuba  daga idanun ta, duk likitan da ya shigo ya gansu, sai yasan akwai soyayya me ƙarfi sabida yadda ta nanne a jikin shi, haka da Iyayen suka shigo ganin halin da suke ciki yasa suka fita tare da jin a ransu dole a hakuri da wannan auren duk son da sukewa juna dole su hakura.

Lokacin da iyaye maza suka haɗu, tattaunawa suka yi, inda Suka tsayar da shawara akan a raba Sidrah da Aalim, Baban Nadrah yace.
"Ba za a kashe ba! Abinda zaku fahimta, auren su kulalle ne, koda kuwa muna so ko bamu so za ayi a shi.

Sidrah da Aalim, suna matukar kaunar juna. Zai yi wuya su iya rabuwa da juna, amadadin haka kasara rayuwar su zaku yi, dukda dalilin da yasa zaku yi raba auren babba ne, amma abun dubawa shin ita  yarinyar zata iya yarda ta  zauna dashi a haka, kafin ya samu lafiya.

Idan kuwa tace zata zauna, toh ban ga dalilin da zaku raba musu aure ba, ku Barsu idan tasan darajar abin da ake son raba auren domin shi, toh anan sai ku raba. "

"Ahmed! Ba zaka gane bane. Yau da gobe ya wuce wasa, mace ba kamar namiji bace, tafi namiji karfin sha'awa, kuma yarinya ce wacce take ganiyar balagarta, idan muka duba tana da hakki akan shi, sannan abin tausayin hatta kafaffuna shi ba zasu iya sarrafuwa ba, jiya likitan yake gaya min, yace yaki gayawa Alhussain ne sabida kar hankalin shi ya tashi.

Alhassan ya sami matsala daga cinyar shi zuwa azzabarin shi ba zai iya daukar nauyin mace ba, kamar Sidrah bada take lokacin ta, don Allah ku bar na raba auren ta samu wani." Inji Abban su.

Shiru yan uwan Abban sukayi tare da zurfaffa tunanin. Kafin Baba Mamman yace.
"Yanzun abinda nake ganin, mu dan kara hakuri a sallame shi sai a tambayi Sidran aji zata iya zama dashi a haka ko zata rabu dashi, idan tace zata zauna shikenan. Sai ta Cigaba da karatunta, idan kuma tace a'a ba zata zauna ba, shikenan sai a warware auren."

Da wannan Shawaran aka ajiye maganan sabida sunfi karfin Abban ne.

---

Nadrah kan, mantawa da ita Aamil yayi, tare da zama asibiti, sau uku yana son shiga dakin idan yaga yadda Sidrah take kwance a jikin Aalim, sai ya koma.

Kamar wanda yake wata duniya, haka yaji iska tare da damshi a kirjin shi, a hankali yake buɗe idanun shi wanda suka kasance sun mishi nauyi, sake shaƙar kamshin turaren jikinta yayi ya tabbatar mishi da ita ce ba wata ba. Murmushi yayi lokacin da abubuwan da suka faru ya

shiga dawo mishi, matse ta yayi tare da sauke ajiye zuciya.

Shafa kanta yayi sannan cikin kasalalliyar murya yace.
"Sidrahtul!"
"Mmm!" Tace mishi tare da gyara kwanciyar ta a jikin shi, tana kuma lumshe idanun ta, sake kiran sunanta yayi da dacewa.
"Soda pop, tashi idan wani ya shigo fa"
Ita duk a tunaninta mafarki take, dan haka ta kuma k'amk'ame shi tare da rike rigar shi, wanda take mishi kallon bargo ne,
"Allah bazan tashi ba, domin mafarki ne!"

A sanyayye ya d'agota, tare da hura mata iskar bakin shi.

Tar ta bude idanunta, sake k'amk'ame shi tayi tare da fasa ihu tana fadin.
"Alhamdulillahi Allah nagode maka, wallahi ya tashi, wayyo Allah na!"
Ta dira a gadon, tare da fitowa ta manta babu hijab, murna yasa tafito tana gayawa su Ummi.
"Wannan wani irin Shashanci ne, ina hijab dinki, kin mata."

Inji Inna Sabuwa, da gudu ta koma dakin tare da yafa hijab din.
"Sam bana tunanin raba Sidrah da Aalim zai zaama mafita, su Alhaji su duba Alamarin, wallahi suna son junan su." Inji Inna Binto.

"Eh toh amma a musulunce ma, an bata damar ta zauna ko kuma ta rabu dashi, idan muka duba yarinya ce karama, dan har yanzun bata wuce sha bakwai.  Dan haka tana da ikon zaban abokin rayuwa, sannan matsalar Aalim Babba ce, daga cinyar shi ta sami matsala, har zuwa mazantakar shi.

Kunga kenan akwai shiga hakkin, dan haka nima ina bayan su a raba auren."

Inji Ummi, kamar wanda aka wurgo shi yace.
"Babu wanda zai raba auren nan, wallahi sai Allah karku shiga tsakanin su, wallahi duk wanda naji ya shiga wannan al'amarin sai na hukuntashi."

"Aifa sai kayi aure zai rabu, dan babu inda aka tab'a tauye hakkin akan dalilin son rai, matukar tace ba zata zauna ba, mutumin banza...😏🤔🙄 Da Alamun dai aure zai fashe..
#Mai_Dambu
[11/28, 8:34 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Sacrifice.
"Don Allah. Abba karka shiga wannan lamari, wallahi Allah yasan abinda ya shirya a zamansu, karku raba wannan tsakanin."

"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun! Wayyo Allah na,.kuzo ya fad'i."
Na fada da karfi, ina kuma rike hannun shi, da sauri suka shigo dakin  Aamil ne ya d'ago shi, tare da ajiye shi a bakin gadon. Muryan shi na rawa yace masa.

" Ba dai bana tafiya ba? Kana nufin ba zanyi amfani ba kenan?"
Ture Aalim nayi tare da rungume shi, ina faɗin.
"Babu abinda ya faru da kai, karka sani kuka, ina tare dakai."

Janye ni, Abba yayi yana kallon fuskana yadda yake zubda kwalla, ya rasa yadda zayi a rayuwar shi. Ya zai yi da Sidrah? Ya zai yi da Aalim? Kowannen su yana bukatar d'an uwan shi. Dan haka ya fita dani, ina ihun tare da kiran Aalim.

"Karka bari a fita dani, don Allah kace Abba ya barni, nasan zaka samu sauki." Bai iya cewa kome ba. Ya Cigaba da kallona har Abba ya fita da Ni, ya kai ni gurin yan gida,

"Rabi tafi da ita gida! An gama shirin fita dashi."
"Wayyo Allah na! Wallahi ba zanje ko ina ba, don Allah karku raba mu."

Da karfi na kwace kaina, na ka dakin, da gudu na kuma fadawa kanshi, ina kuka tare da cewa.
"Ice Man! Ba zan iya tafiya ba, shigowar da Abba yayi na biyu ne, Aamil ya tsaya a gaban shi.

"Lokacin da ya amshi aurenta, a farko bai gujeta ta kamar yadda nayi mata, ya zauna da ita har ya tabbatar ta zama mutum, a yanzun da yake nima wani a kusa dashi, kama yayi ta zame mishi garkuwa, a cikin wannan yanayin ya kamata ya fahimci wacece ita,. A wannan lokacin ya kamata. Idan har baturiya irin mahaifiyar mu, attajira irinta, Macen da ake mata yakinin tana cikin manyan mata masu ƙarfin arzikin U.S, zata biyo bakin fata ta b'ata shekara uku da kai.

.toh meye Sidrah ba zata Mishi ba? Meye ba zata iya ba. Har yanzun bata kai matakin da zata bukaci wani abu ba. Kabar su kamar yadda kowa ya faɗa, wani alamarin sai Ubangiji. Yana sane da ita."

Jikin shi ne yayi sanyi musamman yadda Aamil yake rokon shi tare da fidda shi waje, sake k'amk'ame shi nayi sai lokacin ya rungume ni, tare da cewa.
"Baby flower! Zaki iya zama dani?" Sake k'amk'ame shi nayi tare da cusa kaina a jikin shi. Ina shashekar kuka, a hankali yake shafa bayana. Har nayi shiru, kafin ya kuma janye ni lokacin da Aamil ya shigo da keken masara lafiya. Yana isowa yayi gyaran muryan.

Janye jiki nayi, sannan yace.
"Bari na rike ka, sai ka sauka akan wheel chair din"
"A'a barshi ni zan iya." Na ce mishi, tare da kai hannuna na shiga kokuwar, saukar dashi. Amma abun ya gaggara. Dariya suka saka tare da kallona, cikin jin haushi na kuma kai hannuna zan dauke shi, ya d'an mike k'adan sannan ya zauna. A kujeran yana murmushi.
"Ba zan tab'a lamunta na ganki fadi na, duk inda nasara take toh zai na nima miki shi."

Murmushi nayi sannan nake bayan keken, na shiga turawa. "Daga nan zamu wuce kano ne, domin zamu kai ka Germany ne a can zaka ga likitan kashi."

"Amma ba zan iya tafiya babu baby Love ba, kuma kai ma kasan ba zata zauna ba. Zata yi ta musu rikici ne."

"A'a bata da international passport fa!"  Inji Aamil,
"Tana dashi yana cikin jakata, ka duba mata,"
"A'a twins brother ta zauna kawai babu wani dadewa da zamu yi!"

Wani irin fuskar mage nayi mishi tare da idanuna da suka cika kwalla, na wani narke mishi idanuna yana kan shi. Shima sai da ya ji babu dad'i, kawai yace min.
"Bar min kallo da wannan Mayun  idanunki irin na wancan bagidajiyar yar uwar taki."

"Babu damuwa tunda ka amince, shi kenan. My Hugster muje ko, yanzun kai ne baby ni ce kai!" Na fada mishi tare da tura kenan da yake kai, kamar ba nice na gama ihu ba, dan haka muka nufi gida. Idan ya kwashi kayana, tare da wasu abubuwa na Aalim, sannan muka shiga yin sallama da mutanen gidan, kafin shi kuma ya shiga ya bude Nadrah wacce ta gallabaice a cikin ban daki, wuni guda.
.    Haka ya riko gashin kanta, ya wurgata a falonta, tare da taka mata kafa.
"Ki sani zan tafi na raka d'an uwana, dan haka wallahi na dawo sai na gyara miki zama."

Daga haka ya shure ta da kafa, ya dauki kayan shi ya bar gidan, yana nufar cikin gidan ya samu Hajiya kakar su tana zage Sidrah.
"Toh yar baka duna, kalwa uwar miji, tattabara uwar son aure, kar aje a kwaso mana kayan tsiya, dan haka a nutsu a zauna gurin namiji ɗaya, dan ban ga amfanin tafiya dake ba, baliga da kuma wani baligin, zamanin da cin amanar juna yayi yawa, a fake da jinya ana lashe Wani zumar a ge..."

"Sam kin kasa fahimtar shekarun ki, kin kasa rike kimarki, kin saka tashin hankali da damuwar su a ranki, toh yayi miki kyau wallahi na kuma ganin kin tsare Sidrah kina gaya mata magana, zan gaya miki wanda sai jininki ya haura, tsuhuwar kawai."

Daga haka ya bar gidan, tare da saka Sidrah a gaba suka fita, suna shiga mota, ta faɗa jikin Aalim, tare da tura fuskarta cikin jikin, tana sauke ajiyar zuciya. Shafa bayan ta yake a nutse tana kuma kifa kanta a kirjin shi.
"Sidrah!"
"Kyaleta an gaya mata magana ne! Kuma na fanshe mata.". Daga haka suka ja motar, suka bar gidan. Babu halin Abba ya bisu.

Tun kafin su bar garin ma ta fara barci, gyara mata kwanciya yayi a jikin shi, suna isa Kano, ya saka Aamil lallai ya saya mata rigar sanyi sabida lokacin dusar ƙanƙara ne, kuma yasan ƙasar sosai. Aikuwa ya zab'a mata manyan masu kyau irin na mata, sannan ya kawo mishi ya bata.

Karfe biyar suka bar ƙasar, yana manne da ita, a duk lokacin da take tare dashi yana manta cewa shi bai da lafiya, tare da jin ta har cikin ranshi, shi yasa bai ji kome akan ciwon ba, dan yasan itace kwarin gwiwar shi.

Sake saka hannun shi yayi ya rungume ta, a hankali yana shafa bayan ta, har dare yayi.
**Dutse
"Arianah! Kina ganin wulakancin da Aamil yayi min, ya kwanta dani, kuma yayi min mugun duka, dubi jikina! Ya farfasa min jiki kamar wacce bata da galihu."

Shiru tayi sannan tace mata.
"Akan me?"
Ta shigo dakin dauke da cup, dan har zuwa lokacin Nadrah na kwancen, mika mata tea tayi tana murmushi, tace mata.
"Kin san tare da lolah muke!"
"Shegiya! Mata maza tana ina? Kice ta shigo!"

"Lolah!" Da sauri wata farar mace ta shigo, dariya suka fasa, tare da shewa, suka tafa. Wato lolah yar daudu ce, ko nace dan daudu! Yana da halittar maza da mata, kuma a haka suke shedancin su dashi. Dan haka daga shi har Arianah da ita kanta suna da kyakyawan alaka.

Duk wanda yasan Bob risky, toh ba sai na gaya maka yadda lolah yake ba, sabida iya yadda wancan yake haka wannan yaƙe.

.... A hankali ta kai hannun ta, tare da jan duvet din tana dariya, kurb'an tea Nadrah tayi sannan tace mata.
"Lolah! Ya kwana biyu, tunda kika bi wannan Baturen sai yanzun shegiya kinyi kudi, kin mata damu."

Shafa cinyar Nadrah tayi sanan ta sake murmushi tare da kai hannun ta bakinta tana wani irin lasar shi, tace.
" Nady! Sabida ke nazo. Ina alkawarin mu?" Tana Magana kamar yadda goggagun yan bariki suke yi, kafin ta kuma kai hannunta wuyar Nadrah tana faɗin.
"Amma mijin nan naki wani irin dakikin jakine, dubi yadda ya zane min beautiful body."

"Kinga bari don Allah bana so."
Kallon juna suka yi da Arianah. Sannan suka sake murmushi.
"Toh ba damuwa! Tashi muje Arianah."

Mik'ewa suka yi zasu fita tace musu.
"Please idan kun fita ku rufe min kofar dakin gidan."

Cike da mamaki suka kalleta , murmushi suka yi sannan suka fita. Basu bar unguwar ba, dan sun san zata iya fitowa niman su.

Tana gama shan tea din, ta kwanta tare da matse pillow, tana sauke ajiyar zuciya, ganin yadda take cike da desire yasata lallubar number Alhaji Abubakar, sannan ta gaya mishi gata nan zuwa.

Da sauri ta saka kayan da Kawayen ta suka yi iri daya na anko, sannan ta fito daidai ana sallah, tana fita ta sami wani me abin hawa ya kawo mutane, ta gaya mishi gidan bakin Alhaji Abubakar.

Suna Binta har gidan, suna ganin tashiga, Lolah ta koma da motar bayan gidan ta haura ta kantanga, ta sauka sannan Arianah ma, suna shiga suka hango ta, ta wangale kamar an bude kofar shiga cikin gidan. Shi kuma tsohon banza yana faman cinyeta.

Asalin Binta yake kamar zai zuketa, kafin suka kuma shiga masha'ar su. Kamar yadda suka saba can baya, dan haka bata bar gidan ba sai da lokacin sallah magarib yayi sannan ya fita daga gidan, tare da jin ta sauka.

-- murmushi Ariana tayi sannan tace.
"Taya zamu gama aikata laifukan ace lokaci guda ta same Mr Perfect! Ina ba zai yiwu ba, dole ta rabu dashi, kuma ko bata so sai na tsaya iya tsayuwata, nayi waje da ita."

---
Bamu sauka ka ba, sai ƙarfe goma na safen Laraba, ina jin yana shafa fuska na, yace min.
"Yan mata! Yar magen Ya Aalim da Aamil, tashi mun iso."

"Ni wallahi ban gaji ba da barcin ka barni na karasa sai na tashi." Na fada mishi tare da tura bakina.

"Dalla malam tashi, zan zane ki ne. Ni ba Aalim bane dan haka tashi ko nazo gurin." Inji Aamil.

Cikin tsiwa na juya tare da murguda mishi baki, nace mishi.
"Ina ruwanka damu, ni bana son shishigi. Ban ce ka baro matar ka a can ba da zaka sauke min haushin kaza huce a dami."

Tsaki ja, yana faɗin.
"Ku zauna a gurin."
"Tigeress! Sannu da rashin kunya. Bana son haka, d'an uwana ne fa."

Kwalkwal nayi da idanuna, dan dole ya gyara min gashi na tare da gyara zaman mayafina. A hankali na cmbude mishi keken shi ya zauna, asibitin hadeja suka samu saya, a hankali ya haura sannan. Na turo shi muna zo fita anan naga Aamil yana jiran mu, da sauri ya ido tare da rike kujerar, ya shiga sauko dashi a hankali yana kallon shi, har ya sauko dashi, sannan ya bar

Sidrah ta Cigaba da tukashi.

Har suka shiga cikin arrival din, kallon yadda dusar ƙanƙara ya mamaye ko ina take, sai yanzun ta fahimci dalilin saka mata kayan sanyi da yayi,har tana mita, akan me zata saka kayan sanyi.

Suna shiga gurin, ya shiga cicike musu takardun su, ita kuma tana rike da hannun Aalim, har Aamil din ya gama sannan suka dan zauna kadan sabida sanyin yana mugun shiga jikin su, kallon Sidrah yayi yaga tana goge Hannun ta, da juna tare da hura iska me zafi.
"Baby! Zo nan" da sauri ta isa gare shi, ya bude mata hannu, ta shiga jikin shi, shafa fuskarta yake tare da cewa.
"Ana sanyi anan, Kinga london suma suna da sanyi sosai, and u.s suma haka, toh a haka ma sai kiji tsoron zama kasar russian, sabida suma sanyin su ya b'aci.

Baby, lokacin nan aka fi shan ruwa zafi, And Nima a wannan lokacin nake fatan Alkhairi Da Yar baby na, dan naga jikinki akwai wani irin yanayi na musamman. Baby Love."
*Ana ciwon ma ba za a huta ba 😏🤔🙄😜*
#Mai_Dambu
[11/29, 11:50 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Good News.
"Mmm, lallai kuwa. Ni sake ni tsoro kake bani, ka ga bari na tashi a jikinka, dan nasan yanzun sai ka iya."

Na fada da sauri ina mik'ewa a jikin, sake matse ni yayi a jikin shi, yana kallon fuskana, tare da cewa.
"Karki damu, ai muna gaban jama'a, kuma ina tattalinki."

"Hmm! Shine kake wani irin magana."matse bakina yayi tare da cewa.
"Wannan bakin da bai da birki sai na cinye shi."
"Toh sake ni!"
"Idan naki fa?"
Eh toh ba sai na cije ka ba!"
"Da gaske zaki iya!"
Tura baki nayi tare da cewa,
"Toh ka sake ni mana."
"Lallai zanyi maganin wannan bakin naki!"
Rufewa nayi da hannu na, ina raba idanu, tab'e baki yayi alamun ba yanzun ba, har zuwa lokacin ina jikin shi.

Zuwan Aamil ya sani mikewa muka fita bayan ya dauki kayan mu, Ni kuma na shiga tura keken shi, muna tafiya muna hira, tare da nuna min wasu guraren yana gaya min, har motar hotel din da suna kama yazo,

Tunda muka shiga ya kuma janyo ni jikin shi, muna kallon juna, kai hannun shi yayi cikin

Idanu na, na rufe da sauri.
"Matsoraciya!"

"Eh naji"
Mun isa wani babban hotel, me mugun kyau, dake lokacin christmas ne, sunyi decorations din gaban hotel din da kayan fada father chrismas! Muna shiga cikin hotel din Aamil shi yayi kome, sannan aka kwashe kayan mu, tare da kai kai mu dakin da zamu zauna.

Muna shiga abinda muka fara, ban daki na kai shi, tare da taimaka mishi ya cire kayan shi, ina ganin ya rage boxes ɗin shi, na juya zan fita, da karfi ya dawo dani.

"Haba ai sai kin cika ladar ki, dama zaki biyo ni baki min aiki bane, comman bude ido ki taimaka min na cire boxes ɗina."

"Toh wallahi ba zan kalle ka ba,.kuma ka rufe idanunka kai ma."
"Idan naki fa?"
"Sai na fita!"
"Lallai kuwa!"
Cire rigar sanyin jikina yayi tare da cewa.
"Kema zaki ji yadda nake ji."
Rike hannun shi nayi, ya janyo ni jikin shi ya shiga cire min kayan, tare da cewa.
"Haka zaki ganin kamar yadda zan ganki!"
"Uhmm! Karka cire min."

Zare rigar jikina tare da balle pin din bra dina ya sani kallon, shi.
"Karki damu, kallon ki zanyi ba wani zan miki ba"
D'ago ni yayi, tare da kallon kirjina. Da sauri na rufe, amma dake yana shirye da abinda yayi niyya sai ji nayi ya sauke min pant dina. Kuka na saka mishi tare da durkusawa, murmushi yayi tare da cewa.
"Wai! Yan mata irin wannan koshin."
Buge hannun shi nayi, tare da cewa.
"Ni bana son haka, wallahi ni bana son abin da kake min, ka wani tashi kallona kamar wani abu. Toh babu kyau."

"Inji wani algungunmin yace babu kyau mijin aure ya kalli matar shi, zo nan wannan zan miki. Idan kuma kika bari na kamaki nayi da karfi."

"Me zaka yi da karfi!"
Shafa fuskar shi yayi, sannan yace.
"Kome ma, domin kuwa sai nayi."
A hankali nayi ta matsawa da tub din wankan, na juya mishi baya na shiga. Shima kuma matsowa yayi ya dafa a hankali ya shiga cikin ruwan. Takura kai na nayi a cikin ruwan yana shiga ya janyo ni jikin shi, tare da saka kan shi a kafad'ana, a sannu yake yawo da hannun shi,

har ya iso kirjina. Wani irin abu naji yana yawo a kaina kamar wani guguwa, sake narke mishi nayi tare da lumshe idanu na.

Sake matse ni, yayi da jikin shi. Bakin shi a kunne na, yana cizon su, cikin wani irin yanayi da Ni kai na ban san lokacin da na biye mishi ba, juyar dani yayi tare da sumbatar goshina, sannan ya sauko hancina. Kafin ya iso bakina.

Rike hannun shi nayi gam, tare da kara shigewa jikin shi nayi, haka na cusa hannuna cikin gashin kanshi, mun jima a haka. Sake bakina yayi ya gangara zuwa wuyana, a daidai kirjina ne na dauke wuta baki daya..ba zan iya cewa ga asalin ƙasar da nake ba, amma wallahi Ya Aalim ya kai ni class din da ban tab'a daukar darasin shi ba.
....
Dakyar muka fito, Bayan mun yi alola shi yaja mu Sallah, muna idarwa yasa Aamil ya kawo mana abinci, dake har zuwa lokacin jikina a mace yake, ban iya cin abincin ba, na sauya kayana tare da niman masu nauyi zan saka, sai ganin shi nayi ya wurgo min wata riga, sannan ya danna room heater.

"Saka shi, ina son na ganki cikin su."
D'aga rigar nayi fari ne tass, kuma idan na saka kamar ana kallon ko mi nawa ne, dunkule shi nayi tare da cewa.
"A'a! Ba zan saka ba"
"Kika ce ba zaki saka ba!"
Kallon shi nayi tare da kuma auna mizanin maganar da nayi.

"A'a zan saka."
Na fada mishi, sabida naji ni kaina maganar bata min ba, balle shi.
Daukar rigar nayi na saka, bayan na kashe wutar dakin, ina gamawa yace min.
"Kunna min wuta naganki dan ni ba munafiki bane."
Kasa nayi da kaina sannan na kuna wutar, murmushi ya sake. Tare da zuba min ido.
Bakin gadon ya haura sannan ya zauna yace min.
"Kashe min wutar, kizo nan"

Kashe wutar nayi na haura gadon, na kwanta a gefen shi, da dan nisa, matsowa yayi ya janyo ni saman shi.
"Har kin manta lokacin da muke kwanciya haka! Kin manta lokacin da baki iya barci inda ba a jikina ba. Yau an wayi gari guduna kike"

K'amk'ame shi nayi, tare da sauke mishi kukan sakalci, tunda ba a yi min kome ba, shafa bayana yake a nitse, tun ina kukan har na daina nayi shiru. Har barci yayi gaba dani,,. shima kuma barcin yayi tare da matse ni a hankali.

-- Shiga da ficce Aamil yake tunda ya iso bai zauna ba, haka ya nufi asibitin ya shiga

niman ganin likitan, tare da nima inda zai biya kome sannan ya yi booking, sabida likitan ba kullum yake ganin mutane ba.

Tun safe da ya fita, bai dawo ba sai la'asar, yana dawowa ya canza layin kasar sannan ya kira Abba suka gaida yake gaya mishi ya gama musu kome, sai nan da wata sati zasu ga likitan, addu'o'in yayi musu sannan suka yi sallama.har zai kashe wayar yake gaya mishi, ai an daura musu aure da Mommy, wani irin murna yayi tayi mishi tare da musu fatan Alkhairi.
.....
Bayan ya gama, ne ya kunna data.
Ya shiga duba sakon ni, a hankali ya ga sakon wata tace mishi.
_Hey_
Banza yayi da ita, tare da duba wani sakon da ya gani a tweeter.

Sake turo mishi magana tayi tare da cewa.
_mijin Nadrah ko?_

Budewa sakon yayi, yaga zata mata mishi rai, kawai yayi blocking din ta yayi sannan ya sauka abin shi. Gallary  ya shiga tare da kallon hotunar da ya dauki Saratu, ranar da suka tawo da Sidrah.
Abinda ya faru a ranar ya bashi dariya, kuma ya sanya shi ba zai tab'a mantawa da abun ba.
Tawowa yayi bayan an kawo Nadrah, zai shiga cikin gidan, ita kuma ta fito zata duba Khairat, bisa rashin sani kawai ta gware shi, yin baya tayi zata fadi, yayi maza ya kai hannu. Shi k'ugun ta, tsabar ta razana sai da ta kamo rigarshi idanun ta a rufe.

Kallon fuskarta yake, cikin wani irin yanayi na fisgar shi, bude ido tayi cikin mamaki, suna kallon juna.
"Hannunka a kutirina!"
Fuska yayi kamar bai ji me tace ba yace.
"Dama ba abinda kike bukata ba kenan, karamar jarababbiya."
Sake rigar shi tayi tare da cewa.
"Toh babban jarababbe sake ni na tsaya da kafana."
Sake ta kuwa yayi ta fadi kasa, cikin jin haushi tace mishi.
"Ji min mugu, zaka kasara ni ne?  Wallahi ni ba irin wancan tsadar nace dan na fita kwarin kashi."....

*_Don  Allah kuyi hakuri zai Zainab bata da lafiya yau ma kawai nayi ne dan kar na shiga hakkinku ne!_*
[11/30, 8:18 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Consequent.
Banza yayi da ita tare da barinta a kasa, ta mike tana faɗin.
"Dama kayi kama da mugu, dake zuciyarka babu Alkhairi sai Sharri shine bari ka karya min kutiti mugu..."

Yadda ya juyo kanta yasata had'iye sauran maganar ta, tare da cewa.

"Wallahi karka iso inda nake, idan ba haka ba sai ka karya ma!"
Takowa yake gashi babu kowa a gurin, amma a haka bakinta bai mutu ba.
"Karka matso ni ba yar iska bane! Idan ka tab'a ni sai na."
Yadda ya matseta a jikin bango Ya saka tayi shiru tare da yake tana faɗin.
"Toh ai nasan kai mutumin kirki ne, kuma ko wani yace baka da kirki sai inda karfina ya kare. Kuma ai kai yaya na ne."
Yadda tayi maganar yasa shi sake wani karamin murmushi cikin mugunta ta take mata kafarta. Zaro idanu tayi waje,'.

"Allah sai ya saka min, bakin mugu."
D'ago kanta yayi, yana murmushi yayi sannan yace mata.
"Baki da tsoro ko?"

"Inji wa? Ni din banza, baka ganka dani bane, ai zaren ba kalar yadin bane, idan ka kyale ni Allah zai maka albarka, idan kuma ka min wani abu, toh ba makawa, abinda nake ji a kanka toh zan iya karyawa." Ta faɗa a hankali tana matsawa daga bangon, shi kam dariya taba shi. Yarinya sai ka ce Radio.

Riko hannun ta yayi tare da dawo da ita gaban shi, yana kallon cikin idanun ta.
"Baki da kunya, kuma kina da baki. Toh zan rama rashin mutunci da kika min,"

Kai fuskar shi yayi tare da yi kamar zai yi kiss ɗin ta. Kawai ta yi maza ta janye fuskarta gefe, tare da rintsa idanun ta. Hannun shi ya kai k'ugunta, tayi maza ta kalle shi bakin ta yana rawa.

"Ni ba yar iska bace,"
"Waye dan iska?"
"Ban ce kome ba, kawai idan ka barni na tafi."
"Toh me kike ƙaryata wa akaina?" Ya tambaye ta,
"Toh yadda ka matse ni, taya zan iya samun damar gaya maka abinda muke fada a kan ka."

Janyewa yayi tare da matsawa, tattaro rigar ta tayi ta arta a guje, tana kaiwa bakin kofar shiga tace.
"Toh wallahi ba komai ba ne, kai babban mugu ne, baban mugaye,."

Murmushi yayi sannan ya tare da ɗaukar ta hoto, har da mishi alamar tsokana da harshen tare da gwalo, tayi ta mishi abinda zai ji haushi, tana gamawa ta juya tare da barin gurin.

Murmushi yayi bayan ya kuma shafa hotunar ta, a kasar hoton ya rubuta, Sarah. Yarinyar ta dauki hankalin shi sosai, gata da kayan haushi, amma kuma tana da hankali.

Kunna laptop ɗin shi yayi tare da kunna ta, a hankali ya saka cable tare da haɗawa da wayar shi, ya shiga tura hotunarta yana murmushi ƙwayar idanunta yayi zooming din shi. Dariya

yayi har sai da hakoran shi suka bayyana, sannan yace.
"My Empress! Sarauniyar rikici. Uwar yan baƙi."

Haka yayi ta kallon hotunar karshe yaja bargon ya kwanta.
**Dutse.
Tun da aka yi sallar la'asar aka daura auren Mommy da Abba, bayan an gama daurawa ne, Hajiya Surayyah ta shiga cikin gidan, inda Mommy take da Ummi sai Latifah. Suna hira.

"Hauwa! Kenan kin kuma dawowa gidan Ma'aruf a karo na biyu, tare da kwarin gwiwa. Na san dai ba haihu zaki kuma ba, sannan ban da abin kunya Yaranki basu jima da aure ba kema kin dibo jiki zaki.Kin zo kin tsayawa an daura auren ko? Hmmm toh wallahi ki zauna zaki ga abinda idanunki "

"Dad'i na dake baki da hankali, ban da jahilci.  Toh kije kiyi duk abinda zaki yi ki je kiyi mara mutunci kawai." Inji Ummi,

Tun daga ranar suka shiga takun tsaka sosai, haka da ta fara ya janyo musu sanadin da aka daina wasu abubuwan a cikin gidan, domin kuwa abinda Aalim yayi lokacin da lafiyar shi.

Akai Mommy ta daura aikin shi, abubuwan da ake kashewa a kasuwa ta zuba ido a kai tare da bawa Ghali matsayin Aalim. Kuma ana samun yadda ake samun saboda yasan kasuwancin.

---berlin
Yau likitan da zai ga Aalim ya iso, ya shiga duba takardun, sannan aka shigo mishi da Aalim.

*Idan kana son ganin farin cikin ta, da karta fuskanci wata matsala, sai ka kawar da d'an uwan ka! Idan yana raye toh ba makawa ba zaka tab'a ganin ta sami farin ciki ba. Idan ba haka ba laifin dan uwanka zai iya shafar ta.*

Zaro idanu yayi cikin damuwa da tashin hankali, tare da jin mutuwar jiki, maganar da Alh Abubakar yayi mishi yana kuma dawo mishi, lumshe idanunshi yayi tare da kwanciyar shi, bai tattara takardun ba, har ya fara barci, kamar wanda aka tashe shi ya tashi zaune ya tattara takardun ya zuba a cikin locker din ya rufe, sannan ya kwanta cikin bakin ciki da tsanar Aalim, yana kuma dawo mishi zuciyar shi. Ya raba shi da kome yana can yana rayuwar jin dadi.

Toh shima sai ya raba shi da kome dan yaji yadda yake ji. Dole ya nuna mishi kalamar nan ta bahaushe.
*Ruwa biyu! ka sayi daya ka samu daya kyauta.*

..... A can kuwa, suna ta shirin murnan Birthday din shi amma shi bai iya tabuka kome ba, gabaki daya baya kaunar abinda zai iya juyar musu da duniyar su.

Baya a son su rabu, baya kuma kaunar su kasance ruwa biyu, wanda duk wanda zai amfane su, ya zame musu masu kyau koda zasu saya su saye su a cikin aminci ba wai su sayi daya su sami daya mara daraja a kyauta ba, duk wanda za a gwada ya zame musu masu kyau da daraja, yana son su kasance guri guda, su zauna a waje daya. Su zama ruwa daya ba, ruwa biyu ba. Baya son wanin su ya fidda wani abu daga gare su.

Anyan lokacin bayyanar Ruwa biyu bai zo ba.... Toh ni dai nace yanzun aka fara... Kuka,bakin ciki, cin amana, kyashi, hassada, sharri, rayuwa da mutuwa.... Mu hadu daga nan har yanzu inda alkalamina zata tsaya a zanen kaddarar su..... Hahaha... Kar a kira sunana 🤭🤣🙏🏽🤔 walle labarin nan nada tsayi don Allah mu lallaba juna ko mu samu a gama shi Insha Allah 30 december Insha Allah
#Mai_Dambu
[12/6, 1:27 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Hankalin shi a tashe idan ya kuma tuna d'an uwan shi da iyayen su, sai yaji tsoron kar wani abu ya same shi, babu shiri ya fara hada kayan su, dukda ba wani daukar lokaci suka yi da zuwa ba dan wata biyu kacal duka kenan da zuwan su.

Aikin da ya bari yake son kammalawa, toh ga tashin hankali da ya fara fuskanta, da abokin haihuwar shi, dan haka ya tattaro, kallon shi tayi cikin damuwa tace mishi.
"Hero, ina zamu yanzun haka?"
"Ba zamu koma gida ne"
Ya fada a takaice,
"Toh amma ai bamu gama kwanakin da ka diba mana ba, kuma naga kana da aiki dayawa a gaban ka, ko wani abu ya faru ne!"

"Ban sani ba, kome sai kin sani ne, kome sai na gaya miki ne, idan ba zaki koma gida ba, kalas amma ba ki saka ni a gaba da tambaya na, wacece ke?" Ya daka mata tsawa, a tsora ce tayi baya, tana me girgiza mishi kai, bakin ta yana rawa tace mishi.
" Allah ya baka hakuri."
Fitar da kayanta ya fara, tare da watsi dashi, cikin tashin hankali ta rike hannun shi tare da cewa.

"Kayi hakuri! Wallahi ba zan kuma ba, don Allah kayi hakuri." Ta fadi haka hawaye na zuba daga idanun ta,kwace hannun shi yayi tare da ture ta, ta zube a kasa ya cigaba da hada kayan,

"Ki fita min daga nan, bana son damuwa!" Da sauri ta fita waje. Zuciyarta na wani irin bugawa, kuka ne ya kwace mata, tunda yayi mata haka ta fahimci rikicin shi akan d'an uwan shi ne, dan haka ta yi mishi uzuri, yana fitowa yayi gaba da kayan su, da sauri ta koma ta dauko hand bag dinta, da gudu ta iso. Shiga motar tayi tare da sauke ajiyer zuciya.

Gyara zama tayi aka rufe motar, matsawa jikin shi tayi tare da kwantar da kanta a kafad'arshi, "kayi hakuri ba zan kuma ba"
Ta faɗa a sanyayye,tana me sake sassanyar kuka, a hankali dai dai kunnen shi, lumshe idanunshi yayi sannan ya bude akan ta, sumbatar kanta yayi tare da cewa.
"Ya isa!"
Sake shigewa jikin shi tayi, tana me tsannanta kukan ta, kai hannun shi yayi bayanta, yana dan dukar bayanta, ganin taki shiru ya sanya shi tura hannun shi cikin rigarta, tare da shafo boons ɗinta, cikin wani irin kulawa, wanda ya sanya ta yin shiru tare da rike rigar shi, a hankali yake shafawa, lokaci guda ya sanya ta, sake wasu Tagwayen nishi. Ganin tana shirin fita hayacinta. Ya sanya shi sumbatar goshinta, sanan yace mata.

"Bana son ganinki cikin damuwa, idan kika ga nayi abu, karki dame ni, akan d'an uwana, zamu yita samun matsala, bana son haka bana son kina shiga cikin wannan lamari. Tsakani na dake babu wata matsala, tsakanina da d'an uwana, kuma shine nake fuskarta damu, bana son kina kina min magana idan kika ga haka ya faru."

Cikin sauri take gyada mishi kai tare da cewa.
"Insha Allah, ba zan kuma ba."

Haka yayi ta zuba mata sharadi akan dan uwanshi, tare da gargad'i me zafi, har suka isa airport.
**
Dutse.
Tsakani da Allah, Aamil ya dauke kanshi daga al'amarin iyayen su. Ya dauki fushi babu gairi babu dalili. Sosai yake jin haushin kowa, babu wanda ya fahimci halin da yake ciki, sai matar shi ita kuma zuga shi take bana wasa ba, har take gaya mishi ya kwashi rabon shi domin ai dukiyar su ce.

Dan haka ya fara wasa da dukiyar tare da sake mata yadda take so, a cikin kwana biyu ya saya mata motar da taci uban na Sidrah. Kuma dan b'atar basira, a Kano ya sayo motar gurin sayar da motar Aalim.

Abban shi yana zaune ya ga fitar kudin, har kusan miliyan tamanin da bakwai, kiran shi yayi dakyar ya dauka. Yace mishi .
"Lafiya naga kudi yafita?".
"Eh na sayawa mata na mota ne!"
Shiru Abba yayi bai kuma cewa kome ba.

.... A cikin wannan yanayin Aalim suka iso, yazo ya ga irin b'arna da Aamil yayi, dan haka ya dawo basu hadu ba, sabida Aamil yayi tafiya da matar shi. Dan haka bai wani yi magana ba, sai ma maida hankali da yayi kan maida abinda Aamil din ya b'ata, bai wani damu ba.

Wato dai Nadrah saka Aamil tayi a gaba, suka bar kasar suma. Inda ya kwashi kudin na fitar hankali, suka nufi Dubai. Haka yayi ta kashe musu kudi da yar shi da matar shi, haka suka bata watanin har uku.

Anan kuwa Aalim ya nimawa Sidrah wata makaranta da ake extra moral, tana zuwa babu b'ata lokaci.kuma tana fahimtar abinda ake musu.

Ranar wata Jumma'a ta dawo, ta samu su Nadrah sun dawo, cikin murna ta isa har bakin kofar, ta kai hannun ta zata buɗe kofar taji abinda Nadrah suke tattaunawa da kawarta.

"Na samu ya dai na kula d'an uwan shi, yanzun abu daya ya rage shegiyar yarinyar itace next target dina,idan kuma na tashi toh haka ba zai mata dad'i ba."

Da sauri na bar kofar, jikina a sanyayye. Duk sai naji na damu da kaina. Haka na shiga mana aikin gida, har zuwa wani lokaci abinda take fada yana yawo a kaina zuwa kunnen na.
....
Mika mishi hannu yayi, cikin farin ciki zasu yi musabaha, amma Aamil yaki amsa, cike da mamaki yace mishi.
"Me yasa? Ko nayi maka laifi ne!"
Tsaki yaja sannan ya canza gurin zaman shi, duk sai yaji kome yazo mishi banbara kwai, dan haka ya mai da hannun shi tare da dunkule shi, kan shi a sunkuye.

Bayan sallar juma'a, ya mike tare da nufar inda yaƙe, amma wani ikon Allah, ko da ya isa, Aamil ya ki kula shi karshe ma barin gurin yayi ya nufi inda motar shi take ya shiga, tare da bude Aalim da kura.

Duk sai jikin shi yayi mugun sanyi, haka ya shiga motar shi, ya iso gida a dame, yana ganin motar dan uwan yaje har kofar gidan shi, yayi sallama cikin wani shaidanun shiga ta bude kofar dauke kan shi yayi tare da barin kofar gidan ma, ina zaune sanye da wata body hook, me hannun vest, sai top da nasaka me kamar jacket, lemon green tare da jeans legis, wandon shi Blue.

Kai na sanye da hular karen miski, bude kofar da yayi na zuba mishi ido, a hankali na mike na amshi daddumar da ya dawo da ita daga masalaci, na riko hannun shi, muka nufi cikin dakin shi,.na hada mishi ruwan wanka.
Koda ya fito, ina tsaye tare da nima mishi kayan sawa, rungume ni yayi ta baya, kan shi a kafadata. A hankali yake goga hancin shi, hannun shi biyu suna matsa dukiyar Fulaninta, kamar yadda yake so haka take biye mishi. Karshe dai sai da ta kai ta itace ta ja linzamin shi, har ta kai da ya samu nutsuwar zuciya.

Tana kanshi, ita take, Zungure shi (🤣) haba jama'a, hannun shi duk biyu a k'ugunta, sai kara mata kwarin gwiwa yake ta hanyar d'agata yana shigar ta , sosai. Tare da sauke wasu irin nishin dadi, yarinya zata haukar shi, ta san kan namiji, gashi a ruwan sanyi tana cinye shi tass.

"Baby karki sauka aka kaina, ci gaba da sukwana na, haka nake so yar aljanna ta, yawwa baby love. Yawwa abincin Ruhina, wayyo my soul, maza ita sassukata, maza zungure ni, Mamacita. ki cinye duk abinda ya rage daga gare ni."

duk wannan abin da suke, Akan Idanun Nadrah, tare da matar kafarta, abin mamaki ita duk Iskancinta bata tab'a cin namiji ba, amma yau taga yadda yarinya karama take juya namiji kamar mota a saman gado, abun mamaki wato har Sidrah tayi hankalin da zata iya juya Aalim a saman gado ba tare da ta nunawa duniya, ita kwararriiya ce ba..yarinyar da ta dauka ba zata iya kome ba, yau itace a saman mutumin da take mafarkin itace akan shi. Jinjina kai take kawai, tana jin lallai dole ta kunyata Sidrah idan suka shiga cikin gidan, dan tasan dole zata shiga. Da wannan tunanin ta bar window, din tare da jin lallai sai ta saka Aamil yayi.mata irin wannan cin.

Ya kuma ji dadin haka, domin rungume ta yayi tare da matsa bom-bom ɗinta, kanshi a kafad'arta, yana sauke ajiyar zuciya yace.
"Nagode sosai, naji dadin haka, idan zaki iya ki cigaba da taimakona a duk lokacin.da na"

Sumbatar kirjin shi tayi tare da lumshe idanunta, dan ta gaji matuƙa, gyara mata kwanciya yayi suka shiga hira, a hankali barci ya dauke ta, bata farka ba sai da la'asar, suka yi wanka tare shi ya tafi masalaci, bayan ya idar da sallah, ya shiga rabawa mutane kyautar da ya saba.

Kallon shi Aamil yayi sannan yace mishi.
"Wannan abin da kake shine ake kira riya, idan da gaske alkhairi zaka aikata kabi kowa gidan shi, bawai dan niman suna ba ka shiga rabawa mutane yan abinda bai taka kara ya karya ba, kai ga mutumin kirki."

Bai kalle shi ba ya fita, tare da tsayawa a kofar cikin gidan, Aamil na fitowa ya ce mishi.
"Wai meye nayi maka ka tsane ni ne?"

Cikin masifa ya wuce, ya kuma tare shi lallai sai ya gaya mishi abinda yayi mishi, bai kula shi ba, Aalim ya rike hannun shi tare da tambayar shi a karo na uku, kawai Aamil ya rufe shi da duka, dai-dai fitowar Sidrah, da gudu tazo tare da ture Aamil akan Aalim,

"Kai wani irin mugu ne? Meye yayi maka zaka illata shi, sai kace ba jinin ka ba." Ta fadi haka tare da rungume mijinta, tana zubda kwallar bakin ciki..
"Ki ja mishi kunne, ya fita harkata idan ba haka ba, mutuwar shi a hannuna take."
A razane Mommy da ta iso gurin ta kifa mishi mari, ta kuma marin shi, zata yi na uku, Aalim yace mata.
"A'a Mom! Barshi abin alfahari ne a gare ni, gawata ta sauka akan hannun shi, haka kawai ba zai tsane ni ba. Don Allah ku rike shi ba zan kuma mishi kome ba, idan laifi na maka ba zan kuma ba."
Abin tausayi, haka yake rokon Aamil yayi hakuri, amma haka ya wuce cike da fushi, yana shiga cikin gidan shi, Nadrah tace mishi.
"Da na gaya maka basu kaunarka kora na kayi amma gashi sabida shi ana dukar ka"

Nan ya kuma hawa, ya zauna sabon k'iyayyar dan uwan shi yana kuma hawa, zuciyar shi. Haka ba karamin rura wutar rikicin yayi ba.

A hankali kowa na gidan ya san irin k'iyayyar da Aamil yakewa Aalim, wanda ta kai ya bar ma zuwa kasuwa, kuma bai hana yaje ya kwashi kudin na hauka ba, haka zai zauna da Ghali yana kallon shi tare da gaya mishi abin da yake damun shi akan dan uwan shi.

Gashi ya hana Sidrah magana, dan dole ta zuba mishi ido, sanadin wannan abun har ya fara wani irin rashin lafiya, a tsaye, kafin wani ya farga Sidrah ce ta fara fahimtar haka, shi ne ta sami Ummi suka kai shi asibiti, gwajin farko aka ci jinin shi yayi mugun hawa, itace ta zauna a jikin shi.

Kwanan shi biyu, aka sallame shi. Suka dawo gida. Yana shan magani. Ranar kasa b'oye halin da take ciki tayi..
"Tunda yace ba zai yi da kai ba, dole kai sai kayi dashi ne? Ko ya zama tilas ne sai ka zauna dashi, idan wani abu ya same ka ma zaka ce min, bani da Uwa bani da uba. Bani da kowa a zaga ye na, sai kai.

Kai kuma kana shirin rabani da kanka, idan ka mutu shi kenan na tashi mara amfani a ko ina, don Allah ka rayu dani mana, Insha Allah zaku dai dai, amma sawa kanka damu ni kake cuta ba kowa ba.".ganin yadda take kuka yasanya shi kulata tare da ajiye kome ya rungume rayuwar su.

Tunda babu wanda ya isa ketare kaddarar shi, ya kuma yi kokarin ganin sun daidaita da dan uwan shi....
** Bayan shekara biyu..
(🤔🤣🤓 Mrs Aliyu! Ke bakuwa ce a karanta book dina, tsofin members sun san da haka, duk da ban san yadda zan muku bayanin ba, ina ganin ku bata labarin da ciwo a rayuwata matar so, matar malam, Ina da buri, masarautan Jordan. Yar gidan yadiko, kwarkwarah! Toh duk wanda ya san wannan zai iya fahimtar dake alkalamina! Ban iya ba har yanzun koyo nake! Idan babu Nadrah da Abubakar! Taya zaka ayi d'abi'ar mutane biyu ya bayyana kan shi. Dole Idan zaki yi tsare da dawakai ki tabbatar dokin ki yana koshe, kuma baya tare da ƙishirwa. Ta hana ka ne zaka iya zaburar shi. Labarin yanayin shi kusan yanayin rayuwar mu ne, ban ce true event bane, amma yana iya faruwa a duniyar mu, domin fadi ne da ita..kusan wannan kalmar itace na fada a Kwarkwarah wasu suka yi ta yawo dani, dan haka labarin dai kusan yanayin mune,🙏🏼😎)
[12/6, 7:09 PM] Anum Muhammad Bello❤️: A cikin shekara biyu, rayuwar da muke a cikin gidan babu dad'i Sai godiyar Ubangiji, gashi sun sani a gaba da gorin haihuwa,.haka zan zauna nayi kuka, har nagodewa, a cikin shekaru nayi jarabawa sau biyu ina rasa English da Maths dalilin haka ya ce ya gaji da kashe kudi bana tausayin shi, naki na maida hankali nayi abinda ya dace, dan haka zai bai dani daga Ss3 nayi jarabawar da kyau.

Janan yarinyar ta makale min, sabida shigar ta, gurin Mommy muna haduwa da ita, dan haka take kirana da Mami. Uwarta kuma Aunty.

Tunda uwar ta fahimci cewa Ni yarta take kira da Mami, sai da ta mata shegen duka. Tare da jan kunnenta karta kuma kirana Mami.

Bana shiga cikin gidan, sabida na fahimci akwai renin hankali, idan na shiga sai naji ana bada labarin yadda muke rayuwar auren mu, kawai sai na daina shiga domin sunce yawan sex ne ya hanani daukar ciki.. naso na saka haka a raina amma sai ban damu ba, na barshi akan duk abinda ya faru da mutum daga Allah ne.

Shi yasa na daina shiga cikin mutane, tare da mai da hankali na kan abinda da yake gaba na, na karatu. Bana shiga harkan kowa, tare da kame kaina, dan na fahimci sun rena kansu.

Sai na bar shiga harkan su.

Mijina mutum ne mai zuciya dan haka ya bani kudi me yawa, na fara kasuwanci, Makarantar da nake akwai malamai da yan mata, dan haka idan aka tashi break nakan bi Office da Class na musu tallar kaya a waya ta, da fari sun hada ni da Principle, ta nime ni, tana gama min fada na juya zan ta sai kuma na ce mata.
"Mah nawa zan baki sai ki barni na cigaba da, kin gane ai"

Yadda nayi mata maganar sai ya baka dariya, zare ido tayi. Sannan ta leka waje taga babu kowa, dan haka ta yafito ni. Saka bakinta tayi ta gaya min yadda zan bata.
.aikuwa na kira shi na gaya mishi, ce min yayi na amso mishi Acct ɗin ta, na tura mishi.

Ko minti biyar me kyau bayi ba, kudin ya shigo. Daga nan dai na toshe bakin ta, tunda na shiga kawo kaya, bana bashi. Dan yace min kowanne kar na bashi bashi.

Kaya ne, takalma da Hijabai da mayafai. Idan suka tambaye ni bashi nace musu. Mijina ya hanani bada bashi sai suyi ta kallona suna min dariya, wai nayi karama da aure, murmushi nake musu sannan nace.
"Amma banyi karama da aikata masha'a ba ko? Me yasa kuke rena mace karama me aure? Da yau Iskanci zanyi sai ace yarinya karama ta lalace, bayan kune kuka lalata ni, Ina da miji yanzun shekarar uku da wani abu."

Daga haka na kwashi kayana, so irin wadannan kananun abubuwan baya damu.
......
Ana hidimar sunan matar Bala, na shiga gidan bayan na dawo makaranta, sai da na gaida Mommy sannan na shiga gurin su Ummi, nan ma na samu da mutane a gidan, bayan na shiga ciki ne na dan ji wasu mata na cewa.
"Eh itace mana, baki ga yadda ta girma ba, ga abokan auren su duk sun tara yara, ita kuma ina ga lokacin ne da saura."

Duk sai naji kamar an sake min halitta, dan haka na fito daga gidan na shiga gidan sunan. Da sallama na shiga, hannuna rike da kayan da na kawo.

"Juya kin shigo ne?"
Maganar ya dake ni ba iya ni ba, hatta wasu manyan mata da suke zaune a tsakar gidan sai da suka kalle mu. Suna mamakin. Abinda Nadrah tace min. Murmushi nayi sannan nace mata.
"Toh uwar haihuwa, na shigo ko babu kaso nane a gidan?"
"Fada da ihu ki kara da tsalle, kowa yasan irin haihuwa aka auri baki ga cikin na biyu bane?"
"Gaskiya kan na gani, naga ba rawa kika yi ba, kuma ba kokari kika yi ba, asalima ganin damar shi ce ya baki ya hanani. Dan haka masu gindin haihuwa Allah ya baku cikin duniya."

"Oho! Juya haka dai zaki kare rayuwarki babu ciki babu d'a sai dai a yita kashi." Lumshe idanuna nayi sannan nace mata.

"Bani kikewa gori ba, bani kike gayawa magana ba. Yana jin mu kuma yana ganin mu, idan yaso sai ya dauke dukka wanda kike alfahari dasu ya ga yadda zaki yi.

Tayu Ni Ubangiji ya fahimci cewa bani haihuwar masifa ce shi yasa ya hanani, ya ajiye min madadin shi, ku kuma da ya baku, yaga zaku iya ne ya baku dan haka ba haihuwar bace Matsala, yanzun duniya ta cigaba da ilimin Technology, idan ina son dubu zan samu, amma ba damuwata bace na same su. Na fison ya bani ban san da shi ba.

A wannan lokacin da tarbiyya yake tsada, hakkin ya'ya yake bibiyar iyayen su, wallahi dan Ubangiji bai bani ba, ba zance akan me ya hanani. Tunda ya bani lafiya da numfashi, kome ya kare bani da haufi akan haka, ina da mijin da yake sona a haka meye damuwata dan ban haihu ba.

Ko shima yace haihuwar yake bukata, Alhamdulillah ya karo wacce ta cika mishi gida da y'aya, kune da san Barka, ni bana niman rabon wani, rabona ya ishe ni."

Daga haka na wuce dakin me jegon na gaida mutanen ciki, wata mata ta mika min ruwa nasha. Dai dai shigowar Ummi, tana zuwa na kalle ta, kuka ne yake zuwa min. Mikewa nayi na mikawa Raliyah kayan ta mika min babyn, daukar nayi. A hankali hawayen da nake dannewa ya sauko a kan fuskana ya d'aga a fuskar yarinyar, sai da ta bude idanunta. Da sauri na mikawa uwar yar zan fita. Kakar Raliyah tace min.
"Toh meye kuma? Kukan me zaki yi? Bayan kina da Allah waye kike da shi bayan nan.

Yana sane dake kuma zai baki kema, idan d'an adam bai mutu ba, kar ya cire rai da rahaman Ubangijin shi."

Gyada kai nayi, Ummi ta riko hannuna. Tunda muka nufi cikin gidan, na samu sabon tashin hankali, ashe wai takawa karana ne..wai nace yarta zata mutu,kuma cikin jikinta ba zata haifa ba.

Na kasa cewa kome, karshe da Abba ya tambaye ni, bani da zab'i nace mishi.
"Eh na fada amma bazan kuma ba"
Nan yayi ta min faɗa, wai irin wannan maganar zai iya ja min masifa, sannan aka bata hakuri. Nima na bata, ba zance ya kare ba. Na dawo gida, yadda ake ji da Nadrah yanzun ya wuce misali. Musamman wannan cikin nata, da akayi scan aka tabbatar musu yan biyu ne.

Tuni kan su ya fashe, Mommy ma da taji abinda ya faru, kamar zata cinye ni d'anye babu wanda ya damu yayi mata fada, sai ni.

Ban san waye ya gaya mishi ba, amma yana shigowa ya shake ni yana zare min ido.
"Wallahi kika sake wani abu ya sami matar kanina sai na baki mamaki, ina ƙoƙarin daidaita da dan uwana, zaki kuma birkita min shi, da kike alfaharin na auri wata mace bar damun kanki aure zanyi kuma ki shirya muje Asibiti wallahi na gano kece da matsala zaki gane baki da

hankali.

Sakarya kawai, wacce bata damu da kowa ba, sai kanta."

Saratu nakira na kasa kuka, kawai sai ajiyar zuciya nake yi, dan haka na shiga daki na wanke fuskana, na saka hijab muka fito. Tunda muka isa asibitin, ko inda nake bai kalla ba. Ya shiga muka sami likitan, aka fara min gwaji sannan aka shiga na shi, duk kusan lokaci guda aka mana.

Sannan aka sallame mu akan gobe mu dawo, lokacin da muka fito ko inda nake bai kalla ba, asalima b'ata rai yayi sannan muka nufi gida. Tun daga bakin get na hango Aamil. Tsoron su dukkan su biyun ya kamani, muna shiga ko tsayawa ba muyi ba, ya bude inda nake zaune. Ya watsa min takardun.

"Kince mata na da yarinya na zasu rasa rayukansu! Toh ba zan ce miki kome ba, amma idan baki manta ba, shekaru uku da suka wuce, wannan takardun sune shaidan na zaki tab'a haihuwa ba.

Sabida idan zai fitar da kwan halittar jikinki sun farfashe sakamakon gayen da kika dauko ya kwana dake? Ba zan tsawaita miki baya ba, amma wallahi wani abu ya shiga tsakanin wannan furicin ki. Maybe zaki gama rayuwarki a gidan yari.

Kai kuma mr rich man, da alamu baka san wacece kake aure ba ko?"

Kan shi a sunkuye, daga Ni har shi babu wanda ya iya cewa cikanka. Har ya gama tijarar shi ya bar gurin.
"Nagode!"
Yace min, daga haka ya fice ya barni a motar, tunda na shiga dakina. Na zauna a bakin gadon. Ashe kuka rahama ce, na kasa fahimtar wata duniya aka haife ni.
Wacce duniya nake rayuwa, a wacce duniya zan mutu? Wannan sune yanayin da na tsinci kaina, haka nayi sallah na kwanta a gurin, har washi gari ban leka waje ba. Ina zaune rike da Alqur'ani ya d'aga labulen, kallon yayi tare da watsi mun takardun asibitin.

A hankali na dauka, tare da dubawa. Ban fahimci kome ba, kawai na nad'e su ne na ajiye zan kai Ummi ta duba min, ina cikin damuwa sosai. Dan haka ban kuma ko zuwa makaranta ba, kawai na ajiye kome na fuskanci rayuwa ta, kuma ina kan fusakarta rayuwar.

Mijina ya tubure min, aure zai kara, babu sani na. Dan haka na kame kaina fiyye da da, na nutsu na kuma rike maraicina, sai yanzun na fahimci wani abu. Ashe akwai mutanen da zaman. Da nake da mijina lafiya yake samun su, basu iya b'oyewa ba, sai da aka fara wannan rikicin.

Ban tab'a d'aga ido na kalle shi dan zai kara aure ba, kuma a haka zai zo ya kwashi awa daya a kaina, ba tare da ya ce min cikanki ba. Wannan abin yafi kome cikin rai, haka zanyi kuka nayi

danasanin mara iyaka.

Ranar da ya ishe ni, yazo na mike zan tafi ban daki ya janyo ni da karfi, yana me zare min ido.
Cire hannun shi nayi, nace mishi.."baka bani tsoro! Baka da wani abun da zai bani tsoro. Ni damuwata kawai ka rabu dani, a da ina kallon idan na rabu da kai nayi asara, by now bana da wani asara. Kasan duk abinda zaka min bai kai wanda na gani ba. A rayuwata ba, akan idanuna aka yanka iyayena dan haka bana jin akwai abinda zai bani tsoro.

Haihuwa kake bukata toh kace kayi ta yi mana, na hanaka ne? Sai rashin mutunci, amma baka iya rike bukatar ka, ka rabu dani. Kaje matar da zaka aura ta baka abinda na hana yau."

Fada da karfi ina kuka, cire hannun shi yayi, na zata zuciya yayi ashe sau mutumin bai da ita, domin da karfin ya biya bukatar shi, bai tab'a min irin abinda yayi min yau ba, domin kome da karfi yake, wai na b'ata mishi rai.

Babu inda baya ciwo a jikina, dan haka na kwanta na yita juyi, karshe Saratu na kira ina kuka, tace min.
"Ki bar gidan mana, dole ne sai kin zauna."
Kashe wayar nayi dan bazan iya yaji ba. Haka na wuni da ciwon jiki. Washi gari ma haka, tunda na fahimci yana son lalata min gaba ne, sai na daina mishi rashin kunya, dan haka sai yazo ya gama bance mishi ko me ba.

A haka muka dauki wata daya ana niman na biyu gashi har zuwa lokacin basu daidaita da dan uwan shi ba, nima kuma bana jin dadin zama da shi. Dan haka na yanke shawarar bari na same shi da kaina, ko zai taimaka su daidaita idan yazo nima mu shirya na gaji da wannan wulakancin da yake min.
Dan haka da rahama na shirya ba shiga gidan kasancewar naji dawowar shi gida.
"Assalamun Alaikum!"
Bude kofar yayi tayi tare da amsawa tana kallona.
"Lafiya?"
"Nazo gurin Baban Janan ne!"
"Toh shigo!"
Tace min, na shiga jikina a mace, sabida yadda ta sake murmushi tare da nuna min kofar.
"Zauna bari na taso shi."ta fad'a, kitchen ta nufa, bata jima ba ta fito min da Five a live, da kuma ruwa, ajiye min tayi na girgiza mata kai nace.
"Wallahi na koshi."
"A'a sai kin sha da! Ba zaki zo baki sha kome ba."
Karban lemon nayi na sha....😎😝😜🤣 Yesssso
#Mai_Dambu
[12/7, 10:10 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Ahirin uku.
Nan ta zauna tana tambayana ina bata amsa, har na ajiye kofin na zuba mata ido, kafin na duba wayar hannuna. Naga uku da wani abu,. Hamma nayi tare da kallonta nace mata.

"Don Allah kiyi min magana da Baban Janan, zan koma na kwanta a gida."

Toh tace min tare da tashi da katon cikin ta, ta nufi hanyar dakin su,.ina zaune a gurin har zuwa wani lokaci, ban kuma sanin me ya faru ba, domin nasan na d'an jingina da kujeranta kawai.

---

Tunda ya taso daga kasuwa, burin shi ya tawo ya sauke gajiyar shi, kwana biyu yana jin Sidrah tana shan wani abu, domin ya fahimci bayan ni'imar da Allah yayi mata, toh akwai wani abu da yake kara mata dad'i da dumi, kuma baya gajiya da ita, ya fara fahimtar haka ne yau kwana bakwai da suke gabata, dan haka yake sauri domin ya cimma ta, domin Allah ya gani ba zai iya rabuwa da ita ba kamar yadda take gaya mishi tunda ya gaji da ita ya sallame ta Kawai itama ta gaji.

Koda ya dawo wayar shi ya shiga jin sakon na tashigo mishi, dubawa yayi tare da bude video, a hankali abubuwan da suke faruwa da matar auren shi, ya sanya shi taka birki sai da ya daki bangon gidan, cikin tsannanin b'acin rai, ya fito sabida a kasar videon ance mishi ka bincika irin cin amanar da mutanen da kayar da dasu suke maka.

Da sauri ya duba cikin gidan shi, bata nan, ya kuma duba gidan Mommy bata nan, wucewa yazo yi yaga takalminta a kofar gidan Dan uwan shi, jikin shi a sanyayye ya isa tare da bude kofar shiga, bra ɗinta wanda yafi so ta saka mishi ya gani, fari tass. Sai da ya kuma dubawa yaga pant dinta a bakin kofar shiga dakin Aamil, a hankali ya tura kofar. Sai ya fasa.

A cikin dakin kuwa Aamil da Sidrah ne kwance ya juya Bayan shi, abinda ya dawo dashi gida ciwon kai, yana kwance yaji numfashin mutum a bayan shi juyawa yayi, kamshin turaren Aalim daki hanci shi, ya zata mafarki yake, dan haka ya kuma komawa dan ya zata kodan yadda ya damu da d'an uwan shi ne yasa yake mafarkin yana tare da shi, a hankali ya bude kofar tare da kunna wutar dakin. Matar shi da dan uwan shi ya gani a kwance.

Gado daya, farkawa Aamil yayi tare da janye bargon. Kawai yaga Sidrah akwance babu kaya. Da sauri ya maida mata bargon,jikin shi na rawa.

Kallon juna suka yi tare da sunkuyar da kai.
"Don Allah karka bari shaidan ya samu galaba akanka Wallahi ban san lokacin da ta shigo min ba,"

Juyawa yayi zai fita, suka yi kicibis da Nadrah, rungume da yarta.
"Me ka shigo min a gida na?!".
Kallon juna suka yi sannan ya kauda kan shi tare da barin gurin, ya koma falo ya zauna dafe goshinsa yayi yana mishi wani irin sarawa.

Da azama ta bude kofar, ganin Aamil da Sidrah ya sata fasa ihu sai da tayi uku yadda kowa zai ji, sannan ta fashe da kuka. Tana shigowa ta rufe Sidrah da duka.wanda ya sanya dole ta

farka daga barci, mikawa tayi kanta na sarawa, ta ji babu kaya a jikinta. Ga Nadrah tana kuka. Cikin wani irin tsoro ta rufe jikinta har kanta, sannan ta fashe da kuka, me mugun cin rai. Waye zai fidda ta. Dan haka ta shiga niman kayanta bayan sun fita daga dakin.

Ta saka kayanta, a hankali ta fito lokacin matan gidan sun taru, ganin ta ya jefa zukatar mutane da yawa a cikin wasi wasi. Dan haka suka zuba mata ido,. Aalim wasu abubuwa guda Biyu da suka faru daga jiya zuwa yau ya janyo shi fadawa cikin wannan halin dimuwa. Na farko juya sunyi fada da Sidrah tace mishi.
_nayi imani da ya Aamil ne da tuntuni ya manta da. Abinda ya faru, domin shi fada gareshi ba riko ba_..
Shi kuma garin yaji haushi yace mata.
"Dani da Aamil waye yake aurenki m?"

_ban sani ba amma ya bar maka sudinshi ne._
"Toh fita kije yayi miki cikin ai tunda Ni na gaza."

_Saurin me kake yi, har haihuwa sai nayi da shi_

D'ago rinannun kuma jajjanyen idanun shi, ya kafa kanta, ji yaƙe yau tafi ko yaushe muni a gare shi, sannan ya janye idanun shi daga kanta ya mai da kan Dan uwan shi, wanda suka gama sa'in'sa a kasuwa dazun nan take gaya mishi.

"Na rantse da Allah, duk matsayin da ta kata ka, sai na taka, ba kana tutiya Allah ya baka kome ba, zan taka kome. Wallahi matukar ina raye sai na taka duk abinda ka taka, sai na yi duk abinda kayi wanda ya gaza bawa matar shi farin rayuwa."

Kallon mutanen da suka shigo, suna jiran karin bayani, yayi tare da nuna musu hanyar fita, ba musu suka fita. Yaje ya rufe kofar sannan ya kalli nadrah.
"Kin tarawa Uban Yaranki mutane, sabida yayi laifi. Tabbas duk zafin da kiji bai kai wanda nake ji ba, duk ciwon da zaki ji bai kai wanda nake ji ba.

Dan haka tsakanin mu, zamu bar wannan al'amarin, matuƙar ya fita, kimar mijinki da naki ne zai zuba, mata na kuwa zan iya sallamarta, amma shi fa? Duk inda kika shiga sai an nuna mijinki da matar d'an uwanshi a gado daya, dan ki bar abin, idan aka tambaye ki, ki gaya musu sata ta miki, wannan yafi kome muni, ita zata kunyata"

Daga haka ya bar gidan, da sauri na bi bayan shi, a filin waje na rungume bayan shi, ina sauke ajiyar zuciya. Kasa tafiya yayi yana tsaye cak, a hankali ya janye ni daga jikin shi. Ya nufi gidan mu.

Ina zuwa bakin kofar ya rufe min kofar, nayi bugun duniyar nan ina kuka tare da rokon shi, ya bude min zan gaya mishi gaskiya.

....
"Me ya faru? Ban san kome ba"
Cikin kukan munafunci ta kalle shi.
"Wallahi kai ne baka san Sidrah ba, amma tayi nisa. Ta rena iyawar mijinta ne bayan itace bata haihuwa, shine tazo ka raba makwancin d'an uwan ka. Tana burin haihuwa! Shi yasa ta buge da zuwa gare ka."

Cikin mamaki yake kallonta, kafin yayi shiru yace.
"Shine ɗan hada husuma ta haɗa ni da d'an uwana, tazo ta kwanta a bayana, lallai yarinyar nan makira ce."

Da sauri ya fita, ta sake wani irin murmushi. Tana kallon shi cikin nutsuwa ganin yadda ya amshi batun ta yasata kwashewa da dariya.

Yana fita, ya sami Sidrah a bakin kofar, tana kwara amai mik'ewa tayi ta kuma cigaba da cewa.
"Ni na amince ka kai ni duk inda zaka kai ni amma karka juya min baya, wallahi ban yi abinda kake tsammani..."

Wani irin amai ne ya kwace mata, tana yi tana jan numfashi. Aman da yake fita hanci da baƙi. Ga baki daya ta fita hayacinta.

"Don Allah ka rufa min asiri, ka bude min kofa. Wallahi hukuncin yayin min tsauri. Don Allah ka duba maraicina, bani da kowa bayan kai, naji na amsa nayi laifi. Amma kayi min afuwa, don Allah kayi hakuri ba zan kuma ba,.idan na kuma kayi min hukuncin da yafi wannan."

Gashi garin Damina, shi kanshi Aamil ganin halin da take ciki, ya matukar karya mishi zuciya, abinda yayi niyya take ya rasa. Hadarin da ya hadu, kafin kace me ruwa ya kwarara da tsawa me mugun karfi, ya sanya kowa zubawa kofar idanun. Amma bai sanya Aalim bude kofar ba, haka aka fara ruwa taba zaune a gurin gashi har da ƙanƙara, bai sa taji a ranta ta tashi ba. Haka suke zuba a kanta tare da kwale ta, amma bata d'ago ba..

Tawowa yayi ya daki kofar da ƙarfi,
"Kai dan gidan Uban waye da za a maka laifi ba ka yafe ba, mugu Azzalumin macuci, sai da ka gama kashe rayuwarta akan ka zaka juya mata ba, anyi abinda kake zargi lusari dan daudu kawai.

Wanda bai da fadar kanshi sai na mace, karka bude kuma sai na  kuma aikata abinda kake zargi. Idan yaso kayi hanging kanka a cikin gidan mugu mara Imani."

Bude kofar yayi idanun shi sunfi kowani lokaci rinewa, yaba fitowa bai b'ata lokaci ba, ya rufe Aamil da duka, bai yi yunkurin maido mishi ba, asalima ya fahimci hakan ne zai sanya shi ya samu sassauci, dukar shi yake tare da kuka.

"Meye nayi muku? Idan Kana bukatar Sidrah sake ta zanyi ka aureta, ba ka same ku a wannan halin ba.

Na rabu da kome da kowa idan akan Sidrah ne da kai me yasa baku fahimci yadda kuke a zuciyata ba, me yasa baku min adalci ba.

Ashe kun jima kuna cutar dani, ban sani ba, kun dadde kuna azabtar da ni ban sani ba, dama kasan ba zata haihu ba, ka boye min ban maka magana ba, kasan tana bin wasu mazan baka gaya min ba, ashe har kai ma kana da alaka da mata na, ban sani ba.

Kaje da Sidrah na yafe maka, kuje can na yafe muku, ni da baku kaunar zan tafi na barku kuyi rayuwar ku, amma ku sani wata rana zaku nime ni, daga haka ya koma cikin gidan ya shiga kwaso kayan shi yana zubawa a motar, haka ya gama kwasar kayan shi. Yazo gaban Sidrah ya durkusa, tare da ɗaukar hannunta ya saka a kirjin shi.
"Kinji yadda yake bugawa?"
"Naji amma me yasa bata min uzuri ba? Me yasa bata dube ni da adalci ba? Kome nayi ban cancanci wulakantanwa ba, zaka tafi ka bar ni ko? Amma ka sani game da abinda ya faru, kasan ba zaka iya taimakawa rayuwata ba me yasa a wannan ranar ka rabani da kimata?

Kasan ba zaka iya yarda dani ba, me yasa ka rufe idanunka kayi ta koya min yadda zan fahimce ka, kai da aurena kayi ƙoƙarin raba ni da kimata me yasa lokacin baka yi tunanin cewa dole wata rana haka zai faru? Haka kuka sani amsa laifin da bana ba, haka ba amsa kuma na yarda, ka tab'a tambayar zuciyata me yake damuna?

Baka san bakin ciki ba, kawai abinda ka sani shine ka biya bukatar ka dani, me yasa baka tab'a tunanin wata rana haka zai zo ba?"

Amai ne ya zo mata kamar zata fidda kayan cikin ta, sannan ta kai hannunta kirjin shi a karo na biyu.
"Zaka tafi amma don Allah karka rabu dani."

A hankali ya mike bai ce kome ba, har ya juya zai tafi. Ya kuma dawowa gabanta, ya saka hannun shi dukka biyu ya dauketa, tare da kai ta gidan Mommy, ya ajiye ta. Sannan ya juya zai fita, ta rike hannun shi, tare da mik'ewa ta rungume shi ta baya, sai lokacin ta samu damar kuka.
"Me yasa ba zaka hakura ba? me yasa ba zaka zauna da ni ba? Wai wani irin laifi na maka da ba zaka yafe min ba?

Kayi hakuri mana, ka tafi dani duk inda zaka, zan zauna da kai haka."

Janye jikin shi yayi, ya fita daga gidan, zuɓewa tayi ta kama kakari babu amai sai kumallo, kwanciya tayi a gurin duk karfinta ya kare, karfin ruwan da ake tare da fitar shi ya d'aga hankalin mutanen gidan, har da Aamil wanda shima yabi bayan shi. Sai dai duk yadda ya nime shi bai

same shi ba.

... Sidrah kan asibiti aka dangana da ita, inda aka shiga mata karin ruwa, lokaci guda. Sai kusan karfe goma sha daya na dare, aka samu ta farka, da amai.

Dakyar suka tsayar da aman,

**

Labarin da suka ji yo yau gabaki daya yan gidan, wani irin hatsarin da aka yi, tsakanin wudil da Kano, wata tankar mai ta fashe ta kuma kama da wuta, dayawa wasu motocin sun fada a ruwa, daga cikin su har da Benz wacce take dauke da Lambar Jigawa 340Hdj. Mallakar shahararren attajirin dan kasuwan Amirkan nan, wato Dr Aalim Ma'aruf Adam Hadeja, har yanzun ba a sami wani labari baz dan ana ta ciro gawar mutane, Aamil da ya hauka ce a gurin lokacin da aka ciro motar Aalim ihu yake Abba na rike shi.

Sai Ghali da Ali da suke Bala da Faruq suna ta nutso a ruwan ana bincika gawar shi, sai Isah da Nasiru, suna duba gawarwakin da ake ta cirowa....

#Mai_Dambu😭🙏🏽😢

[12/7, 8:29 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Kwana aka yi ana binciken ruwan kafin aka samu wasu masunta da suka same shi a can , babu abinda ya dame shi, a gangan jikin shi, kan shi zuwa kafadar shi ne, aka samu katon sara. Wanda ban da ikon Allah ba zai kai labari ba.

Cikin tashin hankali aka nufi Kano dashi, ana ƙoƙarin ceto rayuwar shi, domin sarar keyar shi inda sarar da buguwar abu ya kumbura.

Jini aka nima, Aamil ya bada na shi, cikin abinda bai kai awa daya ba aka shiga dashi aiki. Sai dai abinda ya daure wa Aamil kai taya aka yi shi da yayi hatsari, kuma sara da buguwa akan shi, dan haka ya zubawa jikin Aalim ido, can wasu likitoci biyu suka zo zasu shiga ya bisu cikin dakin suna koran shi amma fir yaki kula su.

Zuwa yayi jikin Aalim ya shiga cire kayan shi, ganin shi a kife ya kuma sanya shi duba jikin shi anan ya ga sukar wuka a bayan shi, murmushi yayi sannan ya mai da ya rufe. Zuba musu ido yayi sannan ya fita, ko minti goma ba ayi ba, suka fito jikin su a mace, tare da mika musu takardun, sannan suka ce.

"A gaskiya majinya cin ku ba zai tashi ba, sai wani ikon Allah.

Kuyi hakuri bamu da abinda zamu iya mishi."

Shiga dakin Aamil yayi ya zuba mishi ido, ganin gefen idanun shi yana zubda kwalla, ya riko hannun shi.

"Kana son ka rayu ko? Insha Allah zaka rayu! Amma dole sakon mutuwarka ta isa inda ake bukata, dole ka mutu domin nimo suwaye a Inuwar mu."

Fita yayi ya nufi Office din likitan ya same shi, shiru likitan yayi tare da cewa.

"Amma kasan halin da yake ciki kuwa? Toh ya shiga coman ne, kuma ba lallai bane ya tashi,

koda zai tashi sai wani ikon Allah, sannan ka ce ayi karyan ya mutu."

"Haka nake nufi? Na sani watanin baya kafin wasu abubuwan su faru, yayi kokarin ganin ya turo min wasu sakonnin, sai dai samun sab'anin da muka yi ya sani kin fahimtar shi, yazo har gidana yana min bayanin wasu abubuwan da ya turo min, sai dai a washi gari bayan haka an sace min waya ta, domin ya kuma min magana akan wannan abun da ya turo min.

Toh nayi welcome back, jiya ya kuma turo min sakon, da safe sai dai ban san ya aka yi ba, wayar ta dauke baki daya sabida tsumata a ruwa da yarinya ta karama tayi.
Wannan sarar keyar shi, tare da sukar jikin shi, ya sani fahimtar akwai matsala, Dr ni tsohon dan daba ne, akwai sarar da idan na gani anyi shi ne kawai, akwai sarar da matukar ba gani anyi shine ɗan rufe hujja.

Dr Aalim baya cikin hatsarin da aka yi, gawar daga baya aka kawo shi rafin, ka duba sauran gawarwakin sun jima cikin ruwa, shi kuma ka duba raunin shi, da alamar bai wuce daga zuba zuwa kafin a dame shi ba aka yi shi, bari na mata a fakaice ni na san kan harbi, idan aka harbe shi tabbas zan iya fahimtar wanda yayi. Amma da aka yi da salon da na sani, na fahimci wani abu.

Kafin faruwan haka da Asuban jiya ya gaya min akwai laptop din shi, a cikin sif din matar shi, zai fita da ɗayar don Allah nayi kokarin saka ido akan, laptop din, bayan haka ya gaya min cewa. Ana bibiyar shi idan ni ne, don Allah na bari kar wasu suyi amfani da k'iyayyar mu.

Wallahi ban fahimci hakan ba, sai da naga sara a keyar shi wanda idan na fahimta dai dai, a matsayina na d'an sandan farin kaya, wuyar shi aka zo sarewa aka sami keyar shi.

Ya fahimci, akwai wanda yake bibiyar shi, aka suka mishi wuka anan bayan shi, ka duba hannun shi na dama zaka ga kamar sukar abu, kamar faduwa yayi a kan abu, da alamar ya dafa wani abu mai tsini ne, sakamakon sukar da aka mishi, ka duba gwiwar shi, akwai fitar kokon gwiwar, an duke kafar ne.

Idan nace zan kawo maka Hujjoji dayawa akan shi zaka sha mamaki, abinda na sani. Next target din su Sidrah ce, sabida itace kawai tasan abinda yake turo min, dan haka a yanzun zan baka katin bankin shi, kayi kome domin Allah, karka manta akwai rayuwar da take can tana tsumayen dawowar mijinta.

Dr ka dauki duk abinda yayi maka, don Allah rayuwar d'an uwana, nake rokon alfarma ya rayu. Nasan mutuwa ta Allah ce, amma shi bai deserved din mutuwa ba. Don Allah ka taimaka min."

A tare suka fito, inda suka kuma komawa dakin suka canza Aalim da wani gawa, sannan aka kai wani daki inda akawa gawan sutura, likitan ya sami Abba da bayanin mutuwar Aalim, mutuwar da ta kuma taso mishi hawan jinin shi.

Haka aka dawo dutse da gawar, aka sallaci gawar.

Sannan aka kai shi gidan shi na gaskiya.

Kowa jikin shi yayi sanyi, dan tun da suka ji labarin hatsarin hankalin mutane da Mommy ya tashi, duk suka manta da Sidrah a can asibiti.

Har dare, farkawa tayi cikin tsannanin jin yunwa ta farka, dai dai shigowar wata mata da sauri.
"Kece Sidrah Kamil Hadeja!"
Gyada mata kai tayi,. Kallon window dakin tayi, tare da cewa.
"Zaki bar asibitin nan, domin naga wasu mutane. Suna niman dakin da kike ki dira ta window."
A rikice ta kalli matar, wacce ta rufe kofar, sannan ta sanyata ta fita ta window.

"Toh ina zani?"
"Ban sani ba, kawai ki gudu." Haka ta juya tare da kallon bayan asibitin me cike da duhuwa, jin ana buga kofar, matar itama ta diro, dan ta fahimci Sidrah ba zata tab'a bin dajin bayan asibitin ba, ta finciko hannunta suka fara gudu. Cikin tashin hankali suka nausa cikin dajin.

Duk yadda Sidrah taso hutawa, matar ta hanata, sai da suka yi gudu tun suna jin ana binsu har suka daina jin sahun mutanen.

Tsayawa Sidrah tayi, tare da kwara amai, tare da rike cikin ta.
"Wayyo Allah na, don Allah ki barni na huta, cikina ciwo yake min."
"Zaki iya tashi, muna da saura." Tashi tayi cikin kuka tare da cewa.
"Cikina wallahi ciwo."
Dole yasa suka kuma Cigaba da tafiya, har suka iso bakin titi.
"Sidrah! Na gama aikina, wannan sakon kuma na mijinki ne.

Karki kuskura ki zauna a garin Jigawa, a wannan yanayin. Gashi laptop din shi ne, kece kika san kome akai, don Allah ki rike da muhimmanci, akwai Atm card, wannan kuma mukulin gidane yana garin Lagos. Don Allah karki bari wani abu ya faru da laptop din nan."

Gyada kai tayi, sannan ta juya tare da nufar titin, abin damuwar bata tunanin tunkarar Lagos, domin indai har wannan matar ta gaya mata, haka toh tabbas idan aka kamata zata iya gayawa wasu. Tana tsaye a bakin hanyar wata sharon tazo da gudu, tare ta tayi, dan taga mutane a cikin shi duk da dare ne, taga mafiya yawancin mutanen cikin motar maza ne, kallon motar tayi sai kuma tsoro ya kamata, ta kuma rungumo kayanta.

"Ina zaki?"
Wani irin kwalla ne ya zubo mata, tace.
"Ban sani ba, amma don Allah ina zaku?"
"Bauchi zamu wuce."
Ajiyar zuciya ta sauke, sannan tace.

"Ni ko ina na ma, zan je." Shiga motar tayi tare da zama, tana share kwalla, suna barin gurin, wasu bakaken mota biyu suna zuwa, inda suka fito ta cikin dajin nan. Babu alamar Sidrah nan sai dai hango motar da ta bar gurin.
A cikin kunshin kayan, ta ga kudi.
"Nawa ne kudin motar?"
"Dubu biyu!"
Kirga kudin tayi, sannan ta bashi, shiru tayi. Tana nazarin abinda ya faru, tabbas zasu biyo bayanta, idan ta kuskura ta isa bauchi zasu iya kamata, ba zata zauna a bauchi ba, zata nisa da bauchi yadda zasu gama bilayin su basu same ta ba.

Da wannan tunanin suka iso garin ningi, kawai ganin yanayinta garin tayi ya burge ta, dan haka tace a sauke ta a tasha, anan suka ajiye ta dake tashar da mutane, wani shagon me shayi ta tsaya, bayan ta sayi shayi. Tasha amma yaki zama, komawa gefe tayi tare da kame jikinta a cikin hijab din ta, hawaye na zuba mata. Shiru tayi tare da lumshe idanunta, wasu abubuwan na rayuwar su yana dawo mata,

Kewar mijinta da rashin da yana kara samun dama a zuciyarta, a hankali barci ya dauke ta, me cike da mafarkan, Nadrah tana Binta da gudu hannunta rike da wuka zata soka mata. Da sauri ta buɗe idanun ta akan wasu mutane da suka taru a na kallonta, da sauri ta tashi zaune ganin har gari ya fara wayewa, bakin masalaci taje ta debi ruwa, tayi alola. Sannan ta koma gefen na mata tayi sallah, ta jima tana addu'o'in, tare da niman kariya a duk inda mijinta yake, duba kayan ta fara, a hankali ta shiga buɗewa. Takardan da aka rubuta, password na bankin sai dubu goma sha takwas da yan canji, sai laptop din da wani greeting card...kuka ne ya kwace mata musamman da taga sakon jikin card din.
```Missing you is not in my hands,

as life is never planned,

my dear I miss you so much,

I miss your talks and your touch,

please come back and give me my life,

it's really getting tough to survive,

love you and miss you lots!```
Tayi kuka har ta godewa Allah.
*** Dutse.
Nasan zaki so sanin taya akayi haka ya faru.
Flashing back.
Tafiyar Aamil U.s daga Pagen da aka harbe shi sun zata Aalim ne.
Frank Breth, shahararren dan ta'adda da yake da alaka da yan yadda kayar baya na ISIS,
```

shi yake shigar musu da duk wani sirrin U.s....
🤓🤣🤔 Allah ni dai ina da baiwar datse labari....saura page kusan talatin da wani abu, mu lallaba mu gama,idan ba haka ba yadda nayi tsakiyar nan zan iya datsewa wallahi 🤭
#Mai_Dambu..
[12/8, 12:40 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Lokacin da ya Iso U.s an saka tukwanci ga duk wanda ya same shi, sannan kuma ana bukatar duk wanda zai kama shi ya kawo shi a raye.

Dan haka aka ranar kawowa Aalim hari, ana niman kashe shine, shi kuma ya buge mutumin, ba tare da ya sani ba, dan haka ya wuce, ganin mutumin yana mika mishi hannu, ya dawo ya dauke Shi,

Kallon Mutumin yayi sannan ya fahimci shine ake nima, dan haka ya turawa yan sanda sako, shine sukayi ta bin shi. Har inda suka fita wajen jahar, ya tsaya ya fidda musu shi.

Ana suka tambaye shi me yake so? Yace musu zai yi aiki da hukumar yan sanda, dan haka suka mika shi, a bisa sharadin dole ya fara aiki da CIA, a matsayin Spy, dole ya kashe mutanen da ake zargin su. Tun daga lokacin. Ya shiga kashe duk wani fitinanne a cikin garin, har sai da ya gama musu aikin su,sannan suka tura shi horon aikin yan sanda.

Na tsawon shakaru Biyar, inda ya kware a binciken sirri, koda ya gama suka bashi aiki, yayi musu na watanin ne sannan ya ajiye ya dawo gare wannan kenan.

(Wani lokaci ana iya aikata laifi ga wanda ya san yadda yake yi amma da zaran ya ki bayyana kanshi ba lallai bane ya fahimci waye me laifin! Babu wanda ya san gaibu, kuma koda yake ma'aikacin sirri bai san gaibu ba, dole sai da masaniya, abinda yake faruwa kuwa, duk yana cikin yanayin labarin ne,)

**DUTSE.
"Alhaji Abubakar! Yarinyar nan fa ciki ne da ita kuma ta gudu, matsalar shine Aalim ya tabbatar da ya turo mishi kudin da wasu bayanai na kamfanonin Aamil.

Ni abinda nake so, kawai ka nimo min laptop ɗin Aalim, shi kam, lokacin shi yayi. Matsalar bana son Aamil ya rigani samun Sidrah ne, domin duk wani bayanai da nake bukata suna cikin laptop ɗin, kuma a ranar da abin zai faru matar da suka kashe a dajin asibitin ai itace mutum na ƙarshe da suka yi magana da Aalim, kuma taki fad'ar kome."

"Toh amma ai yarinyar ban ga alamar tana gurin da muke tsammani ba, kuma kince Aamil bai da waya yanzun tunda kika lalata wayar shi." Inji Alhaji Abubakar,.

Shiru tayi sannan tace mishi.
"Amma ai suna can zasu nime ta, Ni kuma da haka zan amshi laptop din, sai na tattara kome na juye a cikin Acct ɗina, daga nan shima na saka a kashe min Shi sannan na bar kasar baki daya."

Gyada mata kai yayi, sannan suka fada masha'ar su.
**
Lokacin da Aamil ya tambaye Mommy Sidrah take gaya mishi cewa tana asibiti, da karamin ciki a jikinta na sati biyar da kwana biyu. Jikin shi na rawa ya nufi asibitin, Nan suka sami bata nan babu dalilinta.

Haka suka bazama niman ta, hankalin shi a tashe, haka suna yi ta bin hanyar da suka bi, koda suka fito inda aka kashe matar nan, gawarta suka samu. Dole suka dauke ta bayan sun kura an sanda, sabida bincike. Zunzurutun bakin ciki Aamil kamar ya fidda zuciyar shi waje ya huta.

Dan haka ko da ya dawo gida, Nadrah ya samu tana kuka domin har sun sami labarin b'atar Sidrah, ga kuma wani karin tashin hankali cikin da Sidrah take dashi.

Wannan yanayin al'amarin ya kwab'e, dan haka Ali da Faruq suka shiga barna a kasuwa, babu wanda ya fahimci haka, sai da suka durkusar da kome na kasuwancin da Aalim yayi raised din shi Up, sannan babu wanda ya san haka.

Ganin akwai abinda zai iya fallasa asirin su, yasa suka kona Officen din Aalim da na Aamil.

Sai dai sunyi baya ba zani, domin kudin da suka kwashe iya kacin shi bai wa wani yawa, dan kafin faruwan hakan Aamil ya kwashe duk kudin ya tura bankin da suke ajiyar kudin. Dan haka ya bar dan kalilin.

Jin zafin haka yasanya suka kona kome, ayi asara biyu.

Lokacin da wutar ta kama yana can hadeja, yana zuwa gidan Innar Sidrah aka ce mishi bata zo ba, amma kafin zuwan shi wasu mutane sun zo.
Shiru yayi sannan yace musu.
"Toh ba kome!"
Yana fita ya nufi Office din yan sanda, ya biya kudi masu yawa, akan lallai samu wasu yan sanda

Da zasu zauna suna jiran Sidrah ko zata dawo.
Koda ya dawo ya sami konewar shagunan su, shiru yayi yana nazarin abinda yake faruwa, kallon Abban shi yayi, tare da cewa.
"Toh meye sanadin haka?"
"Eh toh wuta aka kawo me ƙarfi! "
Shiru yayi sannan ya koma cikin gidan shi, yana shiga ya sami nadrah da katon cikin ta,. Bai mata magana ba, ya shiga ban daki bai iya cire kome ba, haka ya tsaya ruwa na zuba a kanshi.

Ruwan ne yake zuba akan shi yana me jin sanyin har cikin kanshi amma zafin da yake fuskar a

ranshi yafi haka.
Aalim
Sidrah + Kasuwa
Waye kuma next, tabbas akwai matsala waye yake mishi wannan abun da bai sani ba, lumshe idanun shi yayi yana kuma tuna abinda Aalim yace.
"Akwai matsala! Kuma kaki fahimtar abinda yake faruwa.

Don Allah Twin bro ka bude idanunka, wallahi ana bibiyar mu, sannan akwai sakonka kayi ƙoƙarin dubawa, Don Allah ka fahimce ni, wallahi bana jin dadin abinda yake faruwa"

Cikin izgilanci yace mishi..
"Me zan fahimta? Bayan ka ɗauke min kome nawa! Na Barka kana raye ne fa, kawai amma da naso karban abinda kake takama dashi zan sanya a b'atar min da kai. Kai da matar ka kun hana mun gidana zaman lafiya. Kullum sai kun d'aga min hankalin mata na.

Haihuwa idan kuka yi hakuri Allah zai baku amma kun wani saka mu a gaba kamar muke badawa."

Duk wani cin mutuncin da cin fuska yayi mishi, amma bai damu ba, haka yayi ta binshi yana bashi hakuri kuma bai ji a ranshi ya sauraren shi ba, sabida yadda yake ganin ya kwace mishi kome sabida shi mutumin kirki ne ya sanya kowa yana tare da shi, dan haka ya tafi ya barshi kar ya kuma damun shi.

Toh me yasa ya damu da sai ya saurare shi, abun ya fara damun shi, tabbas akwai wani abun da Aalim ne kawai ya sani, bai tab'a danasani mara amfani ba sai yau, bakar zuciyarshi ta hana shi fahimtar gaskiya, kullum cikin zargin dan uwan shi yake.

Koda ya kama shi da matar shi a daki bai ga k'iyayyar da shi yake mishi ba,ya san da cewa da shi ya kama Aalim da Nadrah, garin dutse sai ta tsaya da gindinta. Amma shi dan a zauna lafiya sai ya tafi ya bar musu garin, yau kwana uku kenan, amma ya rasa ta inda zai fara fidda gaskiyar meke faruwa da su.

Haka ya gama b'ata lokacin shi, sanan ya fito ya kwanta, tare da dauko tsuhuwar wayar shi yana ta kokarin ganin ta kunnu, haka ya ajiye ta, tare da dafe goshin sa, yasan duk ranar da gaskiya ta bayyana, zai ci Uban kowa a mutunnce. Da wannan tunanin ya kwanta, tare da lumshe idanun shi.

Yana son jin halin da Aalim yake ciki, amma ba zai yiwu ba, dole sai ya samu lafiya sannan zai iya samun damar tambayar shi.
**
Yawo take, a hankali tana niman inda zata cusa rayuwar ta,.gabaki daya kowa tsoro yake bata, shi yasa idan taga mutane suna yawan Binta da kallo take tsarguwa da kanta, tana niman yadda zata boye fuskar ta.

Ga yamma tayi gashi tana jin kamar karfinta ya kare, dan haka a hankali take tafiya, tare da niman guri tana hutawa, har ta kai bakin wani kofar gida, ta samu ana ta watsi da kayan wasu mutane, yana ta roko amma anki kula su, a hankali ta ta isa kofar gidan.
"Me ya faru don Allah."
"Kudin hayan yaki biya shine ake koran shi."
"Nawa ne kudin?"
"Dubu goma mana!" Ya bata amsa a dakile.
Kutsa kanta tayi har, inda me gidan yake tace mishi.
"Zan biya kudin!"
"Toh bani"
Kirga kudin tayi sannan ta mika mishi.
"Allah yayi miki albarka, yarinya sannu Nagode sosai."
Taya shi tayi ya kwashe kayan, bayan ya biya kuɗin, sannan suka shiga cikin gidan, a bakin kofar shiga cikin gidan, ta fara amai. Sabida kamshin shinkafar da taji.

Anan ta fara amai, dakyar ta samu ta shiga dakin matar mutumin, kallon ta matar mutumin tayi, tare da cewa.
"Malam itace wacce ta biya kudin?"
"Itace Yahanasu, gata ma ba lafiya ma." Fahimtar da tayi matar bata gani kuma tana son ta rike hannun Sidrah, matswa tayi kusa da matar, tare da mika mata hannu.

Rike hannun tayi, tana kifta idanunta, murmushi tayi sannan tace.
"Ciki ne da ita Malam, kuma d'anye ne sosai."

A razane na d'ago kaina, ina girgiza kai bakina yana rawa nace mishi.

"Ciki! Wallahi bana haihuwa, kuma bani da kome."
"Karki damu, ciki ne dake." Inji matar, kuka ne ya kwace min, na gaya musu gaskiya, tare da cewa "ba zan iya daukar ciki ba."

Ganin haka ya matar tace naje asibiti, tare da rakiyar mutumin muka je wani chemist gurin wata mata, ta duba ni ta tabbatar ina da cikin. Haka ta kuma tura mu, gurin scan. Muna zuwa muka bi layi,, yana zuwa kaina na biya kudin, bayan an gama min, me scan din yace.
"Cikin sati biyar da kwana shida, kuma gashi nan a cikin mahaifa."

A hankali na mike tare da goge cikina, ina kuma jin kaunar cikin da dukka zuciya ta, hannuna, na kai kan cikin ina rungume shi, hawaye na zuba min.
A hankali na shiga taryo abubuwan da suka faru, tun daga ranar da muka yi sa'in'sa, da, a ranar ta fara period ɗinta, dan har a daren ranar ya nime ta ya samu tana jinin, ya kyaleta.

Dake kwana uku take, tana gamawa shine ranar da ya gwada mata karfi, a cikin

kwanakin da suka biyo baya duk sai da ya samu nutsuwa da ita. Daga wannan kwanakin yayi tafiya na sati biyu. Har zuwa ranar da abin ya faru. Kuka take, tana faɗin.
"Babu amfanin gudun wuce sa'a, ba zan tafi ko ina ba, zan koma na haifa mishi jinin shi, idan sun zo su kashe ni."

Suka dawo, ta zauna tayi kuka a ranar har dare sun yi sunyi taci abinci taki karshe kunun tsamiya aka sayo mata, shine ya zauna a cikin ta. Haka suka kwana a dame, washi gari tana tashi suka ce P.O.S suka cire kuɗi sannan ta bawa mutumin sauran kuma ta shiga kasuwa ta sayi nikkab da doguwar riga, ta koma tasha, a nan ta nemi motar hadeja.

Sallama suka yi da Mutumin, suka dauki hanyar hadeja, karfe biyar na yamma suka isa, tayi laushi. Koda ta isa kofar gidan Innarta sabuwa. Ta zaune a bakin kofar gidan, takai awa daya kafin ta rarrafa ta shiga, aranta tana cewa.
"Idan haka cikin da ake gorin shi, toh Alhamdulillahi. Wannan ciwon kawai ya isa yasa mutum yace ya hakura da haihuwar. Allah na tuba"

"Innah!" Na kira sunanta, da sauri Khairat ta fito.
"La Sidrah!"
D'aga ni, Khairat tayi tare da cewa.
"Umma ki fito wallahi Sidrah ce bata da lafiya!" Suna fitowa suka d'agani zuwa d'akin ta, tunda na shiga nake amai, fita suka yi aka kira wani nurse tazo ta ce ruwa za a saka min, tare da min allurai.

Bayan fitan Baba ya kira Aamil ya gaya mishi, amma ban da lafiya, dan haka yace zai zo...
🤭🤔 Sorry Guys
#Mai_Dambu
[12/8, 7:58 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Tun daga ranar, na zama Allah sarki, zunzurutun laulayi bana cin kome kai sunan abinci aka furta amai nake balle kuma na ganshi a gabana, wayyo Allah na. Ji nake kamar mutuwa zanyi.

Sabida ni suka daina cin abinci a gabana, suka daina ambaton abinci, kullum zaka same ni makale da ruwa, shine abincina. Abin ya dame innah dan zama take tayi ta kuka, wai abubuwan sunyi min yawa, nayi karama da ɗaukar ƙaddarorin da nake fuakanta.

Wani lokaci haka zanta yawo da hannuna a saman cikin, ina son jin ta inda abin cikin yake, haka zan gama wahala na ban ji kome ba, ga uban yawu da yake cika min baki. Haka zan gama kakarin amai baya fita, wani lokaci Kuma nayi ta sha'awar abinci. Ana kawo min abincin zan nemi juye musu amai.

Sai da nayi sati Uku, ranar da yamma ina kwance, sai ga Saratu da Aamil, ganin shi da nayi ya fama min abinda ya faru,, wata daya da suka wuce. Nayi kuka har nagodewa Allah. Haka suka zuba min y'ay'an itacce a gabana, Khairat da Saratu suka gyara, aka zuba min a wani filet, kallon Innah nayi tare da cewa.

"Inna baki da Zuma ne?"
Jikin ta na rawa ta wuce daki ta dauko min, tare da bani na zuba, a hankali nake ci ina lumshe idanuna, tare da jin kewar Mijina. A hankali na kai hannuna kan cikina, ina sauke kuka a sanyayye.
"Kana jin labarin inda yake kuwa?"
Na tambaye shi tare za zuba mishi ido. Cikin karfin hali ya ce min.
"Alhamdulillahi, yana lafiya."
Kallon shi nayi sannan nace mishi.
"Toh kuna waya!"
Anan ne yayi jim kafin yace min.
"Eh amma ba sosai ba, sai dai yace min yana kewarki."

Ban san lokacin da nayita tura fruit ba, kafin wani lokaci na cinye sai cup, amai nake ji ya cewa Saratu. "Maza kije bayanta kiyi ta shafa bayan ba zata yi aman ba"

Haka kuwa tayi, karshe nayi gatsa. Kwanciya nayi a jikinta, a hankali suke hira sama sama, tun ina jin su har barci ya dauke ni.
"Wallahi yau na samu nutsuwa sosai, taci sosai tunda haka ne zan cigaba da saya mata tunda tana so."
"Amma Innah tafiya Zanyi da ita fa?" Ya katse mata hanzarin ta,
"Toh baka ganin cewa wani abu zai sami cikin?"

"Insha Allah babu abinda zai faru, ina tare da ita. Don Allah karku gaya mata kome." Mikewa yayi sannan ya fita bayan ya kalli Saratu, a kunya ce tabi bayan shi.
Tana isa soron gidan taji, an fincikota. A tsorace ta bude baki zata yi ihu,ya rufe mata da hannun shi, ya kai hannun shi duk biyu, ya rungume cikinta. Nan ita me ƙarfi zata kwace kanta.

"Zakanya! Zakinki a bayan ki." Ajiyar zuciya ta sauke tare da lumshe idanun ta, shafa fuskarta yayi tare da juyar da ita.
"Ba zaki gabatar dani bane?"
"Ayya wani ya rigaka!" Ta bashi amsar. Kamar wanda zai kai mata cizo yace.
"Taune kowani dan banza zanyi. Dan ke tawa ce"
"Allah ko? Yaushe ka fara lashe mutane!"
"Tun ranar da na fara haduwa dake!"
Ya fadi haka yana me hade fuskar su, kauda kai tayi tare da komawa gefe tace mishi.
"Zoka mai dani gida, kafin a sanyani a jerin marasa kamun kai."

Fita yayi tabi bayan shi, ya kaita har kofar gida sannan ya ciro abinda ya kawo mata ya mika mata dakyar ta amsa, sannan suka yi sallama, yace mata don Allah karta bari kowa yasan Sidrah ta zauna a garin.

---
Ina cikin barci naji ana ja min yatsar kafana, Innah ce. Tashi nayi na zauna sannan tace min.

"Zaki bi dan uwan mijinki ne, kuma ina ganin yanzun ya dawo,"

"Tsoro nake ji "
"Insha Allah babu abinda zai faru!." Ya faɗa yana tsaye a bakin kofar Shigowa. Haka ta shirya min kayana, tare da laptop din, muka nufi dutse, tunda muka fara tafiya na fara barci, bai ce min kome ba, sai kallon yadda na sauya baki daya.

Girgiza kai yayi, yana jin wani b'acin rai, abinda ya faru ranar ne ya dawo mishi.
A ranshi yace.
*Ina Nadrah ta tafi da har Sidrah zata shigo gidan? Taya za ace tana gidan Sidrah ta shigo dakin shi? Akwai wani a ƙasa*

*Haka kawai Sidrah ba zata bar mijinta tazo min ba, su da basu iya boye soyayyar su a gaban jama'a, shine zata zagayo mishi ina, haka ma ba zai yiwu ba, ko lokacin da yake rashin lafiya bata d'aga ido ta kalli wani namijin ba, sai shi? Akwai abinda aka rufe shi wanda kuma matukar ya gano masu hannu a ciki zai ci Uban su.*

**
Cikin tashin hankali ya juya tare da barin gidan bakin Alhaji Abubakar, jikin shi yana rawa, halie yake bayan ya shiga motar yacewa driven shi.
"Iliya! Mai dani gida yanzun, kai ni gurin Hauwa."

Numfashin sa, yana hawa da sauka. A hanya yayi kokarin kiran Alhaji Ahmed amma ya kasa magana, karshe Aamil ya kira.
"K..a...na ina.?"
"Yanzu mun kusan gidan gonar ka na hanyar Hadeja, Ni da Sidrah!"
Cikin wani irin fita numfashi yace mishi.
"Ita da mahaifiyarka, suna bukatar ka, ka ajiye ta a gidan gonar kazo ka dauki mahaifiyarka su bar ƙasar su koma can U.s da dama, kayi maza karka bari wani abu ya sami mutanen nan guda biyu, suna bukatar ka."

"Toh toh toh, Abba gani nan zuwa."
Ya faɗa da sauri yana kara gudun motar, buga motar yayi sai da ta farka yace mata.
"A ina passport dinki suke? Zan dauko Insha Allah yau zaku bar kasar."

A sanyayye tace mishi.
"Yana cikin drower Ya Aalim, na gurin gadon shi."
Koda ya isa gurin. Kawai ji yayi a ranshi bai gamsu da ya ajiye ta ba, dan haka ya juya tare da nufar barrack din sojojin ƙasa , ya ajiyeta sannan ya dawo ya nufi gari lokacin da ya nufi gidan su, ya samu anata kiciniyar kai Abban su Asibiti hankalin kowa yayi kan asibitin, dan haka ya shige har dakin Aalim ya shiga duba passport dinta, a hankali ya janyo wani drowa take wasu kaya suka zubo a gaban wani dan karamin locker ganin yayi har da murfi, abin mamaki yadda Aalim ya shirya wasu littattafai a gaban dan abun ba zaka tab'a kawowa wani abu bane, dan

haka bai bi takan shi ba ya shiga Niman passport dinta, bai samu ba duk sai da ya caje dakin, karshe ya dawo jikin locker din, anan ya samu tare da duk wani abinda ake rigima a kai,da wani wasika.

...dauka yayi tare da barin d'akin, ya koma d'akinta ya kwashi kayan ta, sannan ya fito nufar dakin Mommy yayi ya samu sun tafi asibitin,bin su yayi ya samu sunyi cirko cirko, kawai ya kamo hannunta tana juyawa ta gan shi, rufe mata baki yayi suka bar asibitin.

Yaje barrack ya dauki Sidrah dole ya koma gida ya dauko passport din Mommy, da wasu documents ɗinta, sannan suka bar garin, lokacin da ya nufi airport yaje ya saya musu kome na U.s, yace mata.
"Ina son zan amshi laptop din Aalim, sai dai kuma na samu wasu takardu a cikin gidan shi, idan na duba zan dawo yanzun nan."

Fita yayi a hankali, ya nufi waje cikin motar shi ya zauna tare da bude takardar.
```Assalamun Alaika! Dan uwan rabin jiki, naso ka saurare ni, kaki amma ba laifi nagode sosai a haka! Idan baka manta ba nace maka ka duba sakon da na turo maka,toh ba kome bane. Dama zan gaya make me ina tayaka murna zama daya daga cikin manyan Attajiran U.s da Afirka, a yanzun kudinka da kake samu a kamfanin ka sun haura adadin namu da na Mommy. Dan uwana wannan ba karamin dad'i yayi min ba, sai dai kuma tun ranar da na turo maka sakon, wallahi na daina samun barci me kyau. Asalima ce min ake domin ka rayu ko Sidrah ta rayu, na turo dukiyar nan taka. Dan uwana ina tsora ce fa, domin wallahi kullum sai sun gaya min zasu kashe ku ko ni. Toh ni kuma ba zan iya basu ko daya ba,indai akan dukiyarka ne sai dai ni da Sidrah mu mutu,tasan da haka. Dan uwana akwai abinda na rasa yadda zan gaya maka Amma ina fatar Allah ya nuna maka da idanun ka, wannan sune takardun shaida, da nayi printing din su, wannan na laptop din shine original din, zaka iya ajiye laptop din. A gurinka toh ni dai kayi hakuri ka daina fushi dani. Ka yafe min, amma duk abinda zai faru ina rokon Allah yasa kome ya faɗa hannunka hankalina zai kwanta domin duk abinda yake faruwa a yanzun duk sabida kayanka ne```

Cukwaikuye takardan yayi sannan yace.
"Lokacin cin abinci akanku ya kama! Na nimo ku!"
Murmushi ya sake, yana murza kan motar sannan ya koma cikin zama yayi tare da amsar laptop din ya kunna,.cire wayar shi yayi ya haɗa USB, ya shiga tura kome, yana gamawa ya mika mata abinta, yana tsaye har jirgin su ya tashi.
Lumshe idanun shi yayi sannan ya koma motar shi, ya shiga garin kano aka kuma mishi printing din takardun, yana dariya kasa kasa.

Ana gama mishi ya biya kudin, sannan ya kalli takardun masu shegen yawa, ya dawo gida abin shi, a daren ya kai kowanne inda yake bukatar idanun su gansu. A gajiye ya nufi asibitin ya samu ana niman Mommy, shima domin ya taya bera barna ya shiga taya su niman ta, har da karamin hauka, duk inda ake tsammani babu ita babu labarin ta, haka duk suka jigata.
🤭🤔😝🤣 Wallahi labarin nan dadi da gundura...
```

#Mai_Dambu
[12/9, 1:41 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Dake an hana kowa kusantar inda Abba yake, shi daya aka bari ya shiga, shima sabida Abban yace yana son ganin shi ne, ya samu damar shiga.

Yana shiga ya ja kujeran dake gaban gadon, a hankali ya zauna. Yana kallon Abban shi, wanda yake sanye da takunkumin numfashi, a hankali ya d'aga daga fuskar shi, yana kallon yadda Aamil din ya koma sabida tsananin damuwa, mika mishi hannu yayi.
Ya rike, cikin tausayin D'an shi yake kallon shi, sannan yace mishi.
"Am sorry!"
Da sauri Aamil ya kuma rike hannun Abban sosai. Jikin shi yana rawa.
"Kayi hakuri! Duk ni na janyo muku faruwar kome, da ace tun farko na saurari shawaran Ahmed da ban samu kaina a nan ba, sannan shima kuma bai san wata wainar ake toyawa ba.

Nasan nawa me sauki ne na shine dai ban san me zai ji ba, amma"

Shiru yayi sabida numfashin sa da yake kaiwa da komowa. Yana son yayi magana amma ya kasa dole yayi shiru hawaye na zuba mishi, yana rike da hannun Aamil, yana jinjina karfin cin amanar da aka mishi, tare da mutanen da ya yarda dasu. Karshe ciwon Abban ne ya tashi dole likitocin suka sa Aamil ya fita, aka cigaba da kulawa dashi.

Wannan abinda ya tsaya a ran Aamil, yadda Abban shi yake matse hannun shi. Idan ya fahimta akwai abinda yake son gaya mishi, amma babu bakin magana. Kuma yasan akwai abinda yake son gaya masa.

Dan haka ya zauna cikin nazari, fita yayi zuwa waje, dai dai ana kiran sallah farko, dan haka ya zauna ya gabatar da sallah,sannan ya komo gida. Lokacin da yazo yake tambayar Malam iliya ya zo ne.
"A'ah bai zo ba, sai dai yace gashi a baka."

Amsar key din motar yayi, tare da shiga cikin gidan shi, ya sami Nadrah tana bawa Janan abinci.
"Ya jikin Abban?"
"Da sauki, amma kuma akwai abinda yake son gaya min, kuma bai iya gaya min ba."

A firgice ta kalle shi, yada yake wasa da Janan ya hana shi fahimtar halin da ta shiga na rud'ewa.
"Yanzun haka Iliya ya dawo min da key motar kuma ina son ganin shi naji ina suke je da Abba? Domin."
Cikin rawan murya tace.
"Toh Allah yasa dai kome yazo cikin sauki."
"Amin Ya Allah!"
Ya fada tare da mik'ewa zai bar falon ta wurgo mishi wasu tambayoyi guda biyu.
"Ka sami yarinyar nan kuwa ita da Mommy?"

Cikin damuwa ya juya yana kallonta.
" Ban san inda suke ba, amma nasan Allah zai bayyana su."
"Amin Ya Allah!" Ta faɗa a takaice.
Tunda ya shiga cikin dakin shi, ya zauna shiru tare da gyara wasu abubuwan shi. Idanu ya zubawa madubin dakin shi. Yana son fahimtar, abinda ya banbanta su da Aalim.

Duk da kasancewar su, ruwa biyu. Haka ma halayyar su ya banbanta, Aalim bai son tashin hankali, yayinda shi kuma ya kasance dan takife. Aalim yana da kyawawa alaka da kowa, shi kuma babu asalima jarabarshi ya hana kowa kusantar shi.

Halayyar su ya banbanta, shi bai damu ba idan Aalim zai yi kome akan shi, amma shi Aalim bai da juriya idan yana fushi da shi. Duk yadda yaso su shirya fir yaki.

A iya fahimtar shi, zaman su a duniya daya ne yake da matsala, matukar zasu kasance tare toh har abada, ba zai tab'a gamsuwa da soyayyar da ake mishi ba.
**Washington DC.
A safiyar Laraba muka sauka tare da Mommy, tana rungume da Ni, dan tun a jirgi nake amai. Duk hankalin mutane ya tashi.

Motar asibiti ne ya zo daukar mu, dan haka suka wuce damu, tana rike da hannuna. Tunda muka isa aka shiga ƙoƙarin akaina, har kusan karfe ɗaya na rana, sannan suka fito. Likitan ya kalle ta, yana fadin.
"Laulayi ne, na matakin farko na cikin, amma da sauki fa."

Daga haka suka nufi Office dinta, suka shiga tattaunawa har suka gama, sannan yace mata zuwa yamma za a sallame ta.

A d'akina kuwa ina ta barci, me cike da mafarkin Mijina, ina kwance a jikin shi, a hannun shi akan cikina. Tare da shafawa yana faɗin.
"Sidrah!"
Rike rigar shi nayi, tare da kallon cikin idanun shi.
"Hmm! Yaushe zaka dawo gare ni, ina bukatar ka ba iya ni ba kowa ma na bukatar ka, don Allah karka mai dani mareniya mana, ina bukatar ka!"
Share min ruwan da ya digo daga gashin kanshi yayi tare da cewa.
"Ina bukatar ki nima! Ina kewarki Sosai, Sidrah ina."

Kallon juna suke tare da rungume juna muka yi.
"Toh ni kam, na gaji da rashin ka baka damu dani ba sai kanka"
"Na damu dake mana, kawai dai akwai wasu abubuwan"

Na bude baki zanyi magana, bude ido tayi lokacin da aka dafa goshinta, ta kurawa Mom idanu.
"Mommy! Ina ya Aalim yake?"

Shafa kanta tayi tare da sumbatar goshinta.
"Allah ya baki lafiya!"

Lumshe idanunta tayi, tare da jin kewar mijinta, kwalla ne ya cika mata idanu.
"Mommy, mijina!"

"Kiyi hakuri! Allah yana tare daku!" Ta rungume kanta, tare da shafa bayanta, kuka Sidrah take sosai. "Mommy kice yayi hakuri ba zan kuma ba, wallahi ban san me ya faru ba, Mommy kice yayi hakuri ya dawo gare ni muna bukatar shi da babyn mu."

"Allah yana tare daku, Insha Allah shi zai tsayawa Babyn ku." Kukan da Sidrah tayi babu iya, dan har aka sallame ta, tana jikin Mommy.

Suna waya da Aamil, sosai tare da turo mata wasu takardun Sidrah, akan ta fara karatun ta a gurin.

Sosai Mommy ta mai da hankali akanta, tare da kaita gurin shakatawa, tare da kai ta gidajen tarihin kasar, tare da bata labarin abubuwan al'ajabi.

**
LONDON.

Dr Salim Khan. Shine likitan da yake kan Aalim, tun kawo shi Asibitin, wasu daga cikin dalibai da suka zo daukar darasi yake musu bayanin doguwar suman da Aalim yayi, kallon shi wata yarinya take, cikin damuwa tace.
"Dr kuma ya dauki wata nawa kenan?"

"Bai wani jima ba dan sati Uku ne zuwa huɗu." Ya bata amsa.
"Toh Dr zai iya kaiwa yaushe kafin ya farka?" Ta kuma tambayar shi,
Shiru yayi kamar ba zai bata amsa ba, tare da rubuce rubuce.

Sannan ya ce mata.
"Zai iya kaiwa wata daya, biyu, kai shida shekara. Har inda Ubangiji ya gajerce mishi. Wahala"

A hankali ta tako kan shi, tare da shafa gashin kanshi, sannan tace.
"Dr kuma naga yana zubda kwalla ta gefen idanun shi."
"Yana bukatar ya rayu ne, yana da burin da zai cimma, yana da buri a ranshi. Shi yasa yake fatar ya mike domin tabbatar da burin shi."
Rubutu tai sannan ta d'ago kanta tana kallon Dr kamar zata fasa kuka tace mishi.
"Dr Salim don Allah ka barni ina kula dashi mana;"
"An rigada an dauki masu kula shi zaku iya tafiya."
Ba tare da cewa kome ba ta kifta idanunta, manyan dasu sai ga kwalla.
"Anyah ! Kin san Babanki ba zai yarda ki zama yar kula da lafiyar wani ba, sannan shima

dangin shi suna kula dashi."

Cikin tura baki tace mishi.
"Toh wallahi ba zan hakura ba, ni zan kula da ita, don Allah ka barni karkace a'a, kuma karka gayawa Abbi"

Kura mata ido yayi cikin sanyin jiki, kafin yace mata.
"Toh Anyah amma ba zaki zauna a jikin shi ba, zaki na zuwa kina duba shi."

Gyada mishi kai tayi sannan taje inda Aalim yake, ta kai hannunta ta shafa fuskar shi. Kafin ta bar dakin tare da sauran ɗalibai.

Anyah Abdul Malik! Shine cikakken sunanta, babanta babban minista ne a garin Lahore na kasar Pakistan, kuma itace yar karamar yar shi duk sauran yaran maza ne, Anyah duk yayunta guda hudu masu d'amara ne, domin biyu yan sanda ne biyu sojoji ne, suna mugun sonta, domin akanta mahaifiyar su ta rasu, shi yasa suka dauki soyayyar duniya suka daura mata.

Bayan rasuwar mahaifiyar su, Baban su ya kara aure inda ya auri wata yar Kashmir, anan matar ta daurawa Anyah k'iyayyar duniya, tana azabtar da Yarinyar. Ganin haka yasa Yayunta suka tattarota zuwa gurin yar uwan Mamansu mijinta yana nan a London yana aiki da ofishin jakadancin Pakistan da yake nan london.

Dr Salim Khan, kanin mijin Kanwar Maman Anyah ne, yana masifar kaunar Anyah amma bata tab'a sani ba, tana da nutsuwa da hankali, gata da mugun tsokana, tana da halin girma na taimakon mutane, gashi tana da ilmi babu abinda ta rasa. Sai rashin kulawar Mahaifin su.

Domin kuwa, bai damu da ita ba tun bayan auren matar shi, da kuma abinda ya faru, yasa shi fushi da ita, wai tana kawo mishi fitina da yaran shi suma sun tsane shi.

Sai dai tana yawan damuwa sosai, haka zata ganin haka yasa yan uwan ta suka tattarota zuwa london, duk da haka Mahaifinta bai fasa jin haushinta ba, kuma ya sha turo mata manema su zo niman aurenta, amma haka take koran su. Haka ya kuma fusata shi, har yake ganin gwara ya cire hannun shi a kanta.. tare da zigar matar shi.

Da farko tana yawan kuka, amma dake yayunta suna yawan kiranta kuma dr salim yana shige mata a hankali suka zama abokai. Har suke iya raba matsalolin su tare. Lokacin Dr Salim yana da buguwar shi yar garin Islambad mai suna Aania Abrad. Suna cikin soyayyar su. Shigowar Anyah rayuwar shi, ta raba shi da yarinyar ta hanyar nuna mata suna soyayya da Dr Salim.

A dalilin wannan al'amarin yaja suka yi ta rikici da yarinyar kamar me, karshe haka suka rabu da ita, a bayan ita rabuwar su ne, ya hadu da.
"Banafsha! Ita kan yar garin Bagalore ne, ita kan har anyi baikon su.. lokacin Anyah tana

Pakistan, ranar da taji labarin anyi baikon su. aikuwa kwana tayi suna fada da shi a waya,.kuma da zaran ya ajiye kiran ta balbale shi da masifa.

Yayanta Anouri ya kwace wayar tare da zuba mata ido.
"Anyah! Me yasa ba zaki rabu dashi yayi rayuwar shi ba, kinyi mishi adalci kenan? Idan kuma kuma son shi kike toh sai kiyi magana ba ki saka shi a gaba ba, da masifa."

Manyan idanunta ta d'aga tare da fashewa da kuka, sannan tace.
"Yanzun idan yayi budurwa. Mantawa yake dani,.naci abinci ko banci ba. A dare yakan leko d'akina sau uku, amma idan yayi budurwa ko damuwa bayayyi dani.

Haka zai ta rayuwar shi babu ni, yayi ta soyayya a gabana, ko damuwa dani bayi, nice nake damuwa dashi."

Sake baki Anouri yayi cikin takaici, Yarinyar da ko gama secondry bata yi ba, itace tasan darajar kulawa.
"Toh naji yayi laifi! Amma don Allah a barshi yayi rayuwar shi da matar da zai aura don Allah."

Tura baki tayi tare da cewa..
"Shi kenan."
Koda ta dawo, yarinyar nan bwts nutsu ba, haka take zuwa ma DR salim daki. Wani lokaci ya fito wanka,ta haye gadon shi. Yaji bude kofa amma bai kawo cewa akwai mutum a dakin ba, yana fitowa ya cillar da towel ɗin kan fuskarta, yayewa tayi ta baya, kawai idanun ta ya sauka akan shi Allah yaso yana zaune ne yana shafa mai, aikuwa ta fasa mishi ihu. Tare da dira a gadon, shi kan shi kunyar ce ta dame shi, dan haka ya tura mata sako ta same shi a bayan gidan.

Ita kuma tana rike da wayarta tana bawa kawarta Neeha labarin abinda ta gani a dakin Dr Salim.
_Allah Neeha nayi mugun gani 😭😢_

*Ladybug me kika gani?😜*
Dan emjin yana goge fuskar shi ta tura mata,
_🤧 Allah a bar batun wasa naga mugun abu_
*🤔🙄 Me kika gani haka? Don Allah gaya min 🙏🏽*

_Dr Salim na gani babu kaya a jikin shi😭😢_

*😳😲🤯🤫 Wayyo Allah na,don Allah goge kafin Amam ta gani tace na zama yar iska. Kin san tace min idan mace taga namiji babu kaya mutuwa zata yi domin wani.*

_😳😲 Wayyo Allah na, na mutu na lalace don Allah kome goge gashi nan ya turo min sako yau na leko abinda ya dame ni._

*Toh ni kan sai anjima tsoro kike bani*
Karfi da yaji, Tsoro ya hana Neeha bawa Kawarta shawaran Arziki."

Haka ta saka kayanta, ta fito wajen shi, ta makale a jikin bango. Kuka take a hankali, takowa yayi gabanta.

"Kayi hakuri ba zan kuma ba."

Jan kumatunta yayi sannan yace mata.

"Karki kuma shiga dakin mutane babu sallama, kinji ko? Ba zan miki kome ba, amma ki nutsu kuyi karatu, ince baki gayawa kowa ba."

Cike da tsoro ta ja da baya tana kame kame tare da gaya mishi ita bata gayawa kowa ba, kawai dai.

"Karki gayawa kowa! Ki nutsu akan karatunki."

Lokacin da wannan abun yake faru dukka bata wuce sha biyar ba, kuma take wannan shirmen.

Lokacin da suka aka fara shirin bikin shi da Yarinyar da yake so. Anyah ta taso da rashin lafiya, kamar zata mutu. Ana wannan yanayin tayi ta janyo mishi rikicin da ta turawa Banafsha hotunan ta da Dr salim.

Shi kanshi bai dauki hoton da wani abu ba, domin tayi shi ne ranar wani Diwali, dake Mahaifiyar su Dr Salim Yar kasar India ce, kuma sunyi shigar Sari fararre.

Kuma kowa yasan bikin Diwali bikin launika ne, dan haka ita da Dr sun bata juna da launin, ana ta daukar su hotuna asalin irin hotunar nan da ake kira Hotter.

Ta turawa budurwan shi, ana saura kadan daurin auren, aikuwa Yarinyar ta fito tare da mika mishi hotunar  Allah sarki bai kawo kome a ranshi ba ya gaya mata kome, a nan gurin ta fasa auren.

A ranar da abin ya faru, jikinta yayi mugun sanyi, domin rufe kofar dakin shi yayi tayi ta bugawa yaki bude mata. Anyah kamar zata yi hauka, karshe haka tayi ta bashi hakuri yaki kulata. Ya fita hanyar ta ma baki daya.

Lokacin da Abbas yazo yayanta baban kenan, Dr Salim ya bashi Shawaran a kaunata bodin school domin ya bashi labarin yadda tayi ta sheke mishi auren shi babu iyaka. Kuma ya gamsu da hakan domin tayi karatu a nutse aka kaita makarantar kwanan.

Lokacin da ta gama tayi hankali sosai, ta daina shirmen nan, shi kuma bayan tafiyar ta yaso ya gyara tsakanin shi da Banafsha amma fir taki, dan dole ya hakura tare da rungume hannu a kirji, dake Anyah tana da kwazo shi ya nima mata admission, anan jami'ar da yake aiki da Asibitin koyarwa su. Kuma suka dauke ta, shigar ta jami'a ya kuma sawa ta zama yarinya me aji, nan mutumin shima ya faɗa tarkon soyayarta.

Ya shiga kore mata samaruka, kullum sai sunyi fada da ita, tace mishi tunda ya rama ya barta, baya jin haka.

Ganin yadda yake makale da ita, yasa samaruka suka ja baya da ita..yanzun haka yana da shekaru talatin da biyar a duniya.
Ita kuma Ashirin da hudu, tana shekarunta na karshe a jami'a, kuma yaga Aalim ya burge ta, a daidai lokacin da Salim yake shirin gabatar mata da kanshi.

Sai ga Aalim yayi mishi overtaking 🤣🤧
Wannan labari ba dai Chakwakiyya ba wallahi 🤣😹
#Mai_Dambu
[12/10, 9:17 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Cikin takaici yake bin bayanta ta da ido, ga baki daya tana shirin birkita mishi lissafi, lumshe idanun shi yayi tare da ware su akan Aalim, tare da jin kishin sa, dan daga ganin shi. ANYAH TAKE niman sauya tsarin da suke shiryawa rayuwarsu, cikin rashin jin dadi ya gama duba Aalim ya fita daga dakin.
---
Dutse.
Kallon Alhaji Ma'aruf, Alhaji Ahmed yayi cikin damuwa tare da rike hannun shi yana me jin kamar kwalla zai zubo Mishi. Gashi nan suna kallon juna amma babu bakin magana, sai kwalla da yake zuba mishi.

"Ma'aruf ba zaka iya ko Rubutu ba?" Inji Alhaji Ahmed, tausayin abinda zai gayawa Alhaji Ahmed yake, shi da ya kasa rike tashin hankalin taya zai gayawa Alhaji Ahmed cewa yar shi da abokin su, suke cin amanar su?

Ta wani hanya zai fahimtar da Ahmed, Alhaji Abubakar ya ci amanar su. Shar shar yake kuka da idanun shi, tare da jin gwara ya mutu da abin a ranshi da ya gayawa Alhaji Ahmed, dan yayi imani da Allah kashe Nadrah zai yi. Mutumin da tuntunin su bai da wata manufa akan Amintar su.

Gwara Alhaji Abubakar shi yasan cewa shi yayi ta zuga mishi Aamil, ya dinga tura yaron cikin damuwa da nuna mishi baya kaunar shi, ya san Alhaji Abubakar baya kaunar alaƙar shi da d'an shi, amma bai kawo cin amanar juna zai kai har haka ba.
Ya zata idan kome ya lafa zai daina wannan abune.

Cikin mugun nufi gashi ya cutar da amintar su, ya lalata musu zamantakewar su. Yardan da suka yi da juna na shekaru ya lalata musu.

Sannan ya keta mishi haddin auren dan shi, a yanzun idan yayi magana sharri za a ce yayi, anya babu hannun su a cikin faruwar hatsarin Aalim? Da wannan damuwar jinin shi yayi mugun hawa, tare da fitar numfashi babu iyaka, dole aka kuma hana kowa shiga, domin matukar Samun lafiyar shi.

Lokacin da Alhaji Ahmed ya fito,ya sami Nadrah ta nutsu da Janan, suna zaune a gefe kallon Yarinayr yayi wacce hasken fatar uwarta kawai ta dauka, hatta tusar jakin da yake kasar haɓɓar Alhaji Abubakar, yarinyar tana dashi. A hankali yake kallon yatsun hannunta, sai da kirjin shi

yayi wani mugun bugawa, tare da jin kamar wani abu zai diro mishi.

A hankali ya d'ago zai mata magana, yaga yadda Take kuma jan Yar a jikinta, tare da bata abu a bakin ta, shiru yayi sannan ya fita bai bi ta kanta ba ma, ya fita daga asibitin.

---

*Baka tunanin Alhaji Ma'aruf yasan alaƙar mu kuwa? Domin yaki yarda yayi magana da kowa ko kuma ya kula kowa daga Dad dina sai Aamil*

Sako ya turo mata tare da cewa.
_Eh yazo gidan ranar! Kuma nasa an kashe driven da ya kawo shi! Domin na gani ta Cctv tv ya shigo gidan da driven shi,bai kai ga shigowa ba, ya tsaya a bakin kofar shiga ya juya ina zargin yaji abinda muke yi ne_

*Haba biri yayi kama da mutane, domin naga Dad dina, yana min kallon zargi, idan zai kawo mana matsala a sanya likitoci su gama dashi.*

"Nadrah!" Aamil ya kira sunanta, a firgice ta d'ago kanta, tare da sake wayar a kasa,da sauri ta mike tana kallon shi bakinta yana rawa tace.
"Aamil! Abban Janan."
Kallon mamaki yayi mata yadda yaga ta rud'e, ganin ta mike wayar ya kuma faduwa sai da ya tako har gurin ya dauka tare da mika mata, sannan yace mata.
"Kinzo da yarinya kin barta ta fita yawo idan aka dauke ta da, ni bana son sakarci idan kin san ba zata zauna a jikinki ba, toh ki koma gida kawai bana son ciwo. Kai."

Ya fada tare da mika mata yarinyar.
"Kayi hakuri!"
Bai kulata ba yabar ta a gurin, yana mamakin yadda ta rud'e.
Toh me ya rudar da ita? Toh ko akwai wani abu da take b'oyewa ne a wayarta,da yada bata son a gani? Toh me ye nata da firgita dan ya kira sunata, yaga ba wani abu yace ba.

Kawai ta rud'e har tana yarda wayarta, indai haka ne toh akwai matsala domin ba zai dauki wannan shirmen ba. Idan kuma akwai matsalar da yafi haka girma da? Wani shashi na zuciyar shi ya bashi amsa. Shiru yayi har ya bar cikin asibitin.

Daga nan hanyar garin Auyo ya dauka, tare da kutsa kai bai tsaya ba, sai a wani can daji inda ya saka aka gina mishi wani gida karami me shegen kyau. Yana shiga. Ya sami wasu amintattun yaran shi da suka yi aikin dana da su.
Dakin da aka ajiye Malama Iliya yayi ya shiga a cikin a hankali. Lokacin da ya shiga dakin dattijon yana zaune a dame.
"Sannu Baba?"
"Yawwa me guda Aalim?".
"Aamil dai!"

"Toh Allah Yallabai ai kamar kuta ɓaci."
Gyara zaman shi yayi sannan yace mishi.
"Ina son ka gaya min me ka sani da halin da Abban mu ya shiga?"

Shiru yayi sannan ya kuma d'aga kan shi ya kalli Aamil, komawa Aamil yayi ya zauna wani kujeran da yake .kallon malam iliya.
"Nasiru! Kunce shi yayi tafiyar shi. Amma kasani jiya ba dan mun kawo maka dauki ba, da sun kashe ka.

Amma zaka iya tafiya, tunda ka zabi haka."

A hankali ya mike ya bar gidan, ba tare da ya gaya musu kome ba, domin tsoro yake kar ya fadi gaskiya Aamil ya kashe shi. Bayan har kashe wani aka yi akan shine.
Cikin takaici Nasiru ya mike zai bishi.
"Dawo ka rabu dashi, ka rabu dashi karka damu, dole gaskiya zata yi halinta."

Daga nan suka bar gidan, tunda basu a da wani abin da zasu iya.

"Oga Aamil! Ko zaka tuntube me me gadin kune?" Inji Nasiru,
"Babu wanda zan tuntuba, sabida duk wanda abun ya shafa kashe shi ake,. Kai ma zan tura ka gurin su Mommy ne ka zauna da Sidrah, karka manta kai ne kawai kasan Aalim yana raye, zan tafi gurin shi amma sai na duba yanayin jikin Abba idan da sauki zan tafi idan babu sauki zan zauna har."

Wayar shine yayi kara, dubawa yayi yaga Ali. Da sauri ya dauka tare sakawa a kunnen shi " kazo"
Sannan ya kashe wayar, da sauri suka fita kowannen su ya shiga motar.

Koda suka isa ya samu asibitin a cike da yan uwan su, ana kuka koda basu gaya mishi ba, yasan abinda ya faru. Jikin shi a mace zuciyar shi na bugawa, ya tsaya a bakin kofar. Sannan ya shiga d'akin. Yaga yadda aka rufe gawar Abban su.

A hankali ya bude gawar, zuba mishi ido yayi tare da kallon yadda fuskar shi tayi, tare da kallon bakin kofar, a hankali ya mike tare da komawa other side, yana kallon kofar, saka hannun shi yayi a bakin shi. Hawaye na zuba mishi.
"Tabbas kashe ka aka yi."
Ya faɗa a sanyayye, sannan ta nufi inda hannun shi yake ya tab'a, bai jima da mutuwa ba, dan har lokacin jikin shi da dumi, share kwalla yayi sannan ya fito. Yana kallon yadda fuskokin mutanen suka shiga alhini, dan haka ya juya tare da komawa dakin. Ya gyara gawan sannan ya zauna a gaban Abban.

Yana addu'o'in, yana idarwa ya kuma fitowa sannan aka dauko makara aka shiga da shi, ana d'aga gawar aka saka, suka fita, wani takarda ya fado, dauka Aamil yayi sannan yabi bayan

su.

Mutuwar Abba ya shiga jikin shi amma bai nuna haka ba, domin yana ganin abubuwan da suka fara faruwa, bayan anyi jana'izar shi, akan kai shi gidan shi na gaskiya abinda aka fara yi shine lallai a raba gado, bai taba yarda da cewa basu kaunar shi sai lokacin domin ido da ido suka cewa Alkali kar a raba da Mommy a bata tumunin takaba.

A cikin asusun Abbana kuwa jiya suna zaune da Aamil ya ce mishi.
"Bani wayata!"
Mika mishi yayi, sannan ya dauka tare da buɗewa ya tura sauran kudin Mommy da suke hannun shi, sannan yace.
"Kayi hakuri! Ba zan iya gaya maka abinda ya na gani ba, amma ina rokonka alfarmar kayi aure, sannan akwai duwatsu Mahaifiyarka da yake d'akina, a bayan mirror din d'akina, nasan ta bani ne, amma don Allah ka cire guda biyu kabawa Uwani.

Sannan kanen ka, yaranta ku tsaya musu kai da Mahaifiyar ku,"

Rike hannun juna suka yi sannan Aamil yace.
"Abba. Aalim yana raye!"
Zaro idanu yayi cikin kaduwa, sannan yace mishi.
"Taya haka ya faru?"
"Haka ya faru ne sabida bana son a karasa shi, tunda aka dukiya ta ake abun."
Rike hannun shi yayi, sannan yace mishi.
"Allah yayi muku albarka, kuma karka yarda kanku ya rabu, sunyi kome ne dan su raba ku, don Allah kayi hakuri ka rike dan uwanka da Amana, shi yana kaunarka kai ne baka fahimci haka ba karka yarda da kowa sai shi don Allah yaran Rabi amanarku ce."

Da haka sun jima suna tattaunawa, sannan ya fita. Duk yadda Aamil yaso Abba ya gaya mishi me ya faru yaki magana, yana tambayar shi zai dauko mishi wani abu na daban, aure ne dai yace mishi yayi, kuma har yake gaya mishi yaje ya tuntube yar gidan Haliru, domin sunyi magana da Baban Saratu.

Cikin farin ciki ya bar asibitin, washi gari ma kafin rasuwar ya kuma jadadda Mishi maganar ya nemi auren Saratu. Dan har shima ya fito ya gayawa Abban cewa ai suna son juna da ita.
Abba yayi farin ciki, sosai sannan yayi mishi nasiha, bayanya fita ne suka sami Malam iliya,nan suka nimo shi.
....
Maganar Ali ne ya dawo dashi daga duniyar tunani.
"Amma ai bada Aalim za ayi rabon gado bako?"

Kallon Ali yayi sannan yace mishi.
"Baya ciki, amma kuma shashin da aka bawa kowa mallakar abinda Sidrah zata haifa ne, tunda matar shi tana da ciki, sannan kuma."

"Toh shine."
"Haba Ali! Me yasa baka da hankali ne?"
Inji Hajiya wacce tayi kuka har ta godewa Allah, domin duk zaman su da danta bai tab'a mata musu ba, gashi tana tsaka da hada kai a cuce shi sai gashi ya tafi ya bar mata duniyar ba.

Dan haka suka gama rabon su, tare da kasa kome, Aamil ya koma dakin Abban su, ya dauko abun da zai dauka sauran kuka ya barsu.
Sanin basu da hankali yasa Hajiya Uwani ta tattara har da yaranta suka bar gidan, sannan shi ya cigaba da zaman shi, yana aikin dake gaban shi, bayan addu'ar uku, wasu suka watse. A cikin masu tafiya ya samu Baba Haliru suka tattauna, har yake gaya mishi cewa.

"Mahaifinku mutumin kirki ne, ya nima maka auren Saratu, domin har da sadakin shi, ya bani. Sannan yace min yana tausayin duk ranar da ka fahimci matar da kake aure."

Da sauri ya d'ago kan shi.
"Baba ko ya gaya maka wani abu ne?"
Girgiza kai yayi tare da cewa.
"Bai gaya min kome ba, amma iya haka kawai ya gaya min."

Godiya yayi sannan yace mishi..
"Insha Allah, nan da sati Uku kawai a daura auren zan zo na tafi da ita Inda Sidrah take su zauna a can nan akwai wasu yan matsalolin da nake son magance ne."

Da wannan suka yi sallama, ya koma yana kallon Nadrah, kawai sai yaji kome yana dawo mishi, akan shi. Taya Sidrah ta shiga dakin shi? Sannan haka kawai ba ,ba zata tsalleke mijinta ba.

Maganar Aalim ya kuma dawo mishi.
_Ka saurare ni! Nayi imani akwai wanda yake cike ingiza ka_

_kai ne baka san wacece Sidrah ba!_
_Ka sami labarin inda su Mommy da Sidrah suke?_
_Anya Iyayen ku suna kaunar ka kuwa? Dube yadda suka damu da Aalim shine na gari ba kai ba! Basu kaunar ka, me yasa suka fifita shi? Me yasa kome sai shi? Me yasa kowa ya damu dashi basu damu da kai ba?_

_Sidrah tace sai ta kashe ni da yarinyata tare da cikin jikina_

_baka ga yadda mijin Sidrah yayi mata abu kaza ba_
_ni ba irin wannan irin kwanciyar nake so ba, ai Sidrah tace min mijinta yana yin kaza da kaza da ita?_

Me yasa Sidrah?....
🤔🤔🤔🤔
Alkur'an ya farfaɗo.....
[12/10, 8:53 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Idan ya fahimta duk abinda yake faruwa, duk sabida Sidrah tana auren Aalim ne ko toh sabida me? Dan shi bai ga wani abinda zai kai har a fara kome akayi mata sai anyiwa NADRAH.

Ya jima yana sakawa yana kuncewa, da dare ya kalle ta ta shirya cikin doguwar rigar barci, tare da juya mishi baya, ya lura tunda aka yi rabon gadon su take cika tana batsewa. Bai ji a ranshi yana son ayi rikici da ita ba, amma kuma haka kawai yaji ya dirsa zargin abinda yake faruwa a ranshi. Zato zunubi ne.

Amma yana zaton akwai abinda take b'oyewa bayan k'iyayyar Sidrah ba, dan haka baya tuninan rasuwar Abba ko yace kashe Abba da akayi. Lumshe idanun shi yayi tare da sake ajiyar zuciya, sannan ya zauna tare da janan.

A cikin kwanakin da suka biyo baya, abubuwa suna ta faruwa a cikin su kuwa har da fitowa da Alhaji Abubakar yayi yace yana bin Abban su miliyan talatin, dole aka d'aga wasu daga cikin kayan da aka raba aka sayar karshe a wulakance aka saya, tare da amsar wasu kudade, a cikin har da motar Sidrah da na Aalim, duk aka sayar aka Musu ciki..dan rashin mutunci, da aka zo sayarwa kamar ba zai tab'a motar Ba, sai da ya nemi Nadrah ta bashi motar ta, amma taki. Shine ya tab'a motocin duka biyu, sauran kudin ya zuba a cikin Acct ɗin Aalim.

A cikin sati Uku da suka zo aka daura auren shi da Saratu, amma bai gayawa Nadrah ba, domin yana da abinda ya saka a gaba, yana son ya kai Saratu can gurin Sidrah.

Yana cikin haka ya tafi gurin Aalim, yayi sati biyu ya dawo. Tare da gyara shagunan su, yayi odar kaya tare da zuba su a shagon, kudin Aalim ya tab'a, dan shi yana son yaje U.s ya tabbatar da kudin shi. Toh abubuwan da suka rike shi, domin Alhaji Abubakar ya fito mishi da rashin girmamawa.

Shi kuma dake karen bana ne, yake tsula mishi Iskanci, dan ido da ido Alhaji Abubakar yasa aka kama yaran Aalim, shi kuma dake tsohon dan jagaliya, (🤣🤓) ya kama dan iskan tsohon dan iska ya dake shi, tare da dukar shi da itaccen shebir, domin haka kawai yake jin haushin Alhaji Abubakar, dan idan ya tuna da yadda yayi ta tunzura shi yana kafta rashin mutunci, son shi, sai yaji kamar ya sare kan dan banza ya huta, dakyar Baban Nadrah ya kwace shi, cikin dariyar mugunta yace.

"Duka na kayi yau a gaban jama'a, Ni kuma na jima da ciwon da har abada ba zai cika ba, na maka mi kin da ba zai tab'a warkewa ba, zaka rayu da bakin cikina."

Abin da ya kuma fusata Aamil kenan yaja wani karfe, Baban Nadrah ya kwace tare da kifa mishi mari.

"Baka da hankali ne? Aminin mu zaka daka ashe zaka iya duka  Ubanka kenan, koni ai ko dan albarkaci amintar da yake tsakanin mu, zaka kyale shi tunda na rike shi."

"Toh munafiki, gwara shi kai ina ganin hawan jinin da kake ƙoƙarin inganta shi ya sauka shi zai kashe ka har lahira, kuma kai ma haka zaka ganni ka barni. Domin na maka abinda ba ka da yadda zaka yi dani." Haka ya haɗa su dukkan su biyun yayi musu cin mutuncin kare dangi. Sannan ya juya ya kad'a babban rigar shi, ya bar gurin su."

Zunzurutun abubuwan sun mishi yawa ya manta da wata Saratu,  wani abin da ya fara d'agowa shine zai farka cikin dare ya ga Nadrah zaune tana kallon shi, idan ya tambaye ta lafiya tace babu, a hankali ya shiga jnyewa daga gare ta, tare da kin cin abincin da ta girka, sabida yaji a ranshi akwai wani sharrin da take kulla mishi. Dan haka ya zubawa takunta idanu. Batun Alhaji Abubakar kuwa ya zuba mishi ido yana shirya yadda zai mishi takife baki daya.

***U.S
Bayan wata uku.

Wanda ya bawa cikin Sidrah damar shiga wata huɗu zuwa biyar, har gida ake zuwa mata kome bata fita ko nan da can,idan kuwa zata fita toh kuwa a cikin gidan ne.

Wani irin kulawa Mommy take bata, tare duk abinda take bukata. Kallon ta Mommy tayi tare da mika mata wani tap tace.
"Kwanan zasu yi lunch sabida kayan babys, duk unsex."

Shiru tayi tana kallon Mommy, da take zaune cikin zulumi, dan tun da ta sami labarin rasuwar Abba tayi sanyi sosai, dan har take cewa. Aamil ya dawo da Nadrah da yaranta nan, dake Allah ya saka mata son yaran, shi yasa take ganin ko zai dawo dasu. Ganin haka ya sashi ce mata sai dai ya dawo da Yaran Hajiya Uwani gurin, domin sune suka fi dacewa da zaman kusa da su. Tunda Nasiru yana nan tare dasu.  Yanzun ita damuwarta botsare mata da Sidrah take ayi akan lallai sai an gaya mata inda mijinta yake shine damuwarta,

"Daughter kici abinci mana." Mommy tace mata  cikin kulawa, cikin zubda kwalla tace..
"Ni bazan ci ba, ku gaya min ina Mijina yake? Idan kuma ya mutu ne ku gaya min mana."

"A'a bari na kira Miki Aamil."

Kiran layin shi tayi taji wayar a kashe, dai dai shigowar Nasiru da Saratu. Kallon ta Sidrah tayi tare da nuna ta da yatsa, zubur ta mike tare da kwasa da mugun gudu, Mommy na mata magana bata kulata ba, suka rungume juna suna kuka,  me cike da kewar juna.
"Sidrah! Kin manta da abin cikin ki ne, irin wannan gudun haka?"
"Ni wallahi na manta, kewa na gani." Gyaran murya yayi suka rabu leka shi tayi tare da zuba

mishi ido.
"Ina Annur yake?"
Ta faɗa tana me sake kuka sosai,  rab'a gefen su yayi, ta kuma shan kanshi tare da cewa.
"Don Allah idan nayi maka laifi ne kayi hakuri, ka kai ni gurin mijina."
"Toh idan baki daina shiga damuwa ba, Wallahi ba zan kai ki ba."

"Mommy kice a kawo min abincin zan ci yanzun nan!"
Abincin aka shiga jera abincin, tunda aka zuba mata ta fara ci, bata d'ago ba sai da ta cinye, shi kuma yana zaune kusa da Mommy kanshi akan kafad'arta, tana mishi fada.
" Kai ko kunya baka ji ba, ka zauna kana wani narkewa ina kuma Yaranka suka yi haka fa?"

"Mommy, ya cikin Sidrah? ince tana cin abinci? Bata da wani damuwa ko?" Ya jero mata tambayoyi,
"Toh Ni dai ban sani ba, sabida baku dauke ni aikin Nanny ba, idan kuma shi kuka dauka na sani."
"Daughter zo nan, ki rabu da damamnen mijinki, ya Nadrah da yaran?"
Tab'e bakin shi yayi sannan ya kalli inda Sidrah, take a hankali tana shan kankana.

"Ni ban masan halin da suke ciki ba, amma nasan ta kusan Haihuwa, kuma na bar mata kome."
"Amma banji dadin haka ba, domin ai ko babu kome matar kace, bai dace kana wofantar da ita ba, wai ma ka gaya mata kayi aure?" Mikewa yayi tare da kallon Saratu yace mata.
"Ke zo nan!"
Ya nufi hanyar dakin shi a sama, kunya ya hanata tashi sai da Mommy ta bar falon ta mike tare da cewa.
"Mamin baby bari naje gurin Zakina!"
"Hmm! Da alamu an raba reni ko?" Cike da mamaki take kallona sannan tace min.
"Reni kuma?"
Dariya nayi sannan nace mata.
"Maza jeki amshi dogo me dogon zamani, yan lawailawai, mai tagwayen abokai."

Na fada ina dariya, sai lokacin ta fahimci abinda nake nufi tsaki taja tare da dawowa zata zauna, nace mata.
"Ke bana son sakarci, gwara ki tafi wallahi." Ba musu ta mike tare da nufar hanyar dakin mijinta tana tafiya kamar wacce kwai ya fashe mata a cikinta, duk sai ta bani tausayi, dole ta fuskanci haka, domin shine tambarin kimarta. Koda ta shiga dakin ta same shi yana tsaye daure da towel.

Mika mata hannu, yayi ta isa gaban shi, a hankali ya janyo ta, tare da cewa.
"Baki gaji bane? Naga daga zuwa sai hira, har kin gama tsorata da jirgin ne!"
Boye fuskarta tayi a kirjin shi tare da bubbuga kafarta a kasa, wuyarta ya sumbata, tare da jan igiyar doguwar rigarta, sannan ta zame rigar, cikin shashantar da ita, ya shiga kiss ɗinta, har sai da ya dangana da ita bango.

Sake kai hannun shi bayan yayi ya ɓalle bra din ta, yana kuma wani irin kiss, wanda ya sanya jin kamar zata zube a kasa, ya matse ta da bango, tare da kai hannun shi yana matsa bom-bom ɗinta, yana kuma kara cafke harshen ta, ji yaƙe kamar zai cinye ta danye. Zunzurutun yadda take bashi haɗin kai.

Jin yadda jikinta yake rawa yasa shi rabuwa da ita, suka shiga ban daki, ruwa ya cika a tub sannan ya shiga tare da janyo ta, suka shiga. Tunda suka shiga suke kallon juna. Lumshe idanun ta tayi ya kai hannun shi ta zare mata wani munafikin pant dinta, ya zare shi kan shi pant din ya burge shi, kananun kitson wibin din kanta ya shafa tare da....
🤧🤧 Wallahi yau ganda nake ji[12/11, 9:19 PM] Anum Muhammad Bello❤️: "wannan kitson yayi min kyau, duk da nasan ba, lallai ki samu a nan ba, amma."

Had'iye sauran maganar yayi sakamakon, sanya hannunta da ta rufe mishi baki, sannan ya d'ago kanta tana kallon shi cikin wani irin yanayi, wanda ya kasa rike kan shi. Ya kuma birkice mata.idan bai yi karya ba rabon shi da mace ya manta domin tun ranar da aka same shi da Sidrah, a dakin shi bai kuma niman Nadrah ba kamar wanda aka hanashi kusantar Nadrah. Dan haka ya zuba mata yau.

Idan yaji yana bukatar mace, sai dai ya had'iye pills, dan kamar wanda aka fada mishi wani abu akan matar shi ya juya mata Baya, tare da yasan wacece ita ba. Idan kuma yasan wacece ita ina ga hmm.

Dan haka ya baki daya ya tattaro kayan shi na watanin yana son juyewa Saratu.(🤓🤣) Ko tausayin ta bai ji ba,ya shiga murzata a cikin ruwan wanka yar banza dake ta zauna da yan duniya, sai bata wani razana da shi ba, haka ya gama jagulata, sannan suka fito, tare da gabatar da sallar dake kan su, sannan ya daura musu da nafilla. Bayan sun idar ne ya kalleta.
"Baki jin yinwa ne?"

Murmushi tayi tare da mik'ewa. Tana made abin sallah, tace.
"Barci nake ji!"

"Toh amarya kwanta ki huta." Ya fada mata tare da mik'ewa ya ficce, tana tashi ta cire hijab ɗinta, tana son zuwa gurin Sidrah. Amma yadda take jin barci da gajiya yasa ta kwanta tare da cewa zuwa anjima zata lekata.

Saukowa yayi kasa ya hango tayi shiru, amma tana goge fuskarta tare da ajiyar zuciya, alamar kuka take, ka rasowa yayi inda take.

Zama yayi yana kallon yadda take kokarin kame kanta a gaban shi, tare da gyara zaman rigarta.
"Kiyi hakuri da abinda ya faru."

D'ago kai tayi tare da sauke shi ƙasa tana fadin.
"Bana rike kome ya faru dani, sai tunanin mijina, don Allah ku gaya min inda yake."
Wato idan ya fahimci Sidrah da Aalim, sun gina rayuwar su da kaunar juna, shi yasa take wannan damuwar, gyara zama tayi tare da kallon ta, yana faɗin.
"Zan kai ki inda yake amma kiyi min alkawarin, ba zaki d'aga hankalinki ba"

Da sauri ta gyad'a mishi kai, murmushi yayi sannan ya mike zai bar gurin, yace mata.
"Wancan ranar da abin nan ya faru, ko zaki iya tuna ya kayi kika shiga dakina?"

Shiru tayi tare da sunkuyar da kanta, tana wasa Apple din hannunta. bata kuma ji tace mishi kome ba.
"Sidrah baki ji tambaya ta ba?"
"Toh me zance? A sanin ka zan iya rayuwa da wani namiji bayan Ina da Zaki a gabana? Akwai namijin da zai cika rayuwata karshi ne? Ban tab'a sanin yana sona haka ba sai watan da ya gabata da na shiga wancan store naga hotunar da ya zanani.

Tun bai ganni ba, bai san wacece ni ba, yake da yakinin ina nan a duniya. ƙaddara rayuwa ta sa kome ya lalace min. Shima ya manta wacece ni, da bai manta haka ba nayi imani da Allah ba zai yanke alakata da shi ba. Amma Ni da zan same shi da wani abu, ba zan tab'a zargin shi ba.
A shirye nake na tsaya mishi, ba zan tab'a juya mishi ba, kamar yadda ya juya min, da yasan yadda yake a gurina, har abada ba zan tab'a barin shi ba."

Ta faɗa cikin kuka, tare da shasheka.
"Mijinki yana Asibiti a London bai da lafiya, tare ne ranar da ya bar gida ya gamu da hatsari. Asalima yana cikin coman bai san waye a kanshi ba, yanayin da na ganshi yasani cewa ace ya rasu."
Kuka ne ya kwace mata tare da rike bakinta, tana wani irin kuka, idanun ta akan shi tare da girgiza mishi kai.
"Me yasa ka zabi sanar da mutuwar shi akan rayuwar shi? Kasan yadda yake mutuwa akan ka kuwa? Duk rikicin da muke dashi bawai dan ta mu tana hada ni dashi bane! Kasan akan waye ya juya min baya? Sabida kai da iayalinka, a ranar da abin ya ishe ni naje na same ka ku daidaita kanku ko nima na sami kulawar shi, abun ya kuma rincabewa.

. A iya fahimta ta akan rayuwar ku, dole ku rabu da junan ku, domin kowannen zai iya samun nutsuwa idan abokin Haihuwar shi baya tare dashi, naso na fahimtar da shi haka ban sami kan shi ba, shine naje na same ka amadadin haka sai kuma na kuma Kunno wata gobarar da ta kasa mutuwa ta dad'i, don Allah ka kai ni inda yake."

Ta faɗa cikin kuka, tare dake kanta, mik'ewa yayi ya bar mata falon, wato shine dai baho, karfi da yaji an mai dashi jaki, gashi nan dai amma lissafin shi sak na jakuna (🤣😳😲 Wayyo Allah na) idan ya fahimci wani abu akwai jikakkiyar alaka tsakanin Nadrah da Aalim, wanda shigowar shi da Sidrah yasa kome ya jagule, shiru yayi tare da tuna abinda Aalim yake gaya

mishi.
_Ka fahimce ni, akwai matsala a gidan ka, ka magance shi sai mu fahimci juna, abokin Abba da kake mu'amala dashi bai min ba, ina laifin baban Matar?_

Toh ai Alhaji Abubakar ya dade yana mishi ingiza mai kantu ruwa, toh meye ya faru.

*Kai fa zab'in iyayena ne, amma idan duniya da gaskiya kamata yayi a ce Sidrah ce matar ka, Nadrah matar Aalim,.haka tsarin yake, Amma mutane suka sauya Mana ƙaddara.*

Idan ya fahimci maganar Aalim da Nadrah, kenan ita Aalim take so, shi kuma Sidrah yake so taya haka ta faru? "Sidrah zaka tambaya zata baka amsa!"

Da sauri ya dawo inda ya barta, ya zuba gwiwar shi a gaban ta,yana kallon yadda tayi kuka har tana jan majina.
"Me kika sani tsakanin Aalim da Nadrah?"

D'ago jajjayen Idanunta tayi akan shi, murmushi tayi kadan sannan tace mishi.
"Me kake zargin shi da aikatawa?"
"A'a ba zargi bane! Lissafin ne ya zo min haka,"

Rintsa idanun ta tayi, kwalla suka zubo mata, take abubuwan da suka yi ta faruwa suna dawo mata, wanda tasan ta shanye ne dan a zauna lafiya, tare da shakkar mijinta, tana tsoro fadar shi, da yadda yake kunce mata, yasa ta zuba mata, abinda tayi ta mata ko kishiyar ta, sai haka.

... Duk wannan hirar da suke, a kunnen Aamil, wanda bakin ciki ya gama cin zuciyarshi, qarami dai wancan yarinyar sai da tayi abinda ta saka kanta, duk da dakatar da ita da yayi ta fita hanyar dan uwan shi da matar shi.
--- washi gari da safe, kafin kowa ya tashi ya rigasu. Asibitin ya nufa, tana shiga ya cire hular rigar shi, yana kallonta jikinta ne yayi sanyi, dan idan tare suke zata iya banbance su, a gaban mutane ya finciko rigarta ta baya, a razane ta juya jikinta na rawa tace mishi.

"Don Allah kayi hakuri! Wallahi ban san haka zai tab'a kimar ka bane, da banyi ba. Ka rufa min asiri."
"Ke wacce irin karuwa ce? Na gaya miki ina da mata na, har da ciki. Idan na gayawa Yan sanda kinyi kidapping dina tare da cutar dani kinsan hukuncin shi a kasar nan? Wawuya karuwa kawai, sabida kazamin tunanin ki kin rasa kimar ki na ya mace." Ya ture ta ta fadi. Sannan ya juya na fita abin shi, tana kallon Dr Salim da Kawarta Neeha, suka wuce abinsu, ko takan ta basu bi ba..kunya da abinda Aalim yayi mata, ya sata barin asibitin baki daya, tana komawa gida ta dauki wayarta ta tura video da hotunar su, ga Number Sidrah da ta dauka jiya a wayar shi.

---
Har karfe goma na safe basu tashi ba, shigowar sako yasa su farkawa, tare da dubawa Abinda ya faru ne, ta gani murmushi tayi tare da cewa.
"Alhamdulillahi! Kai malam tashi ashe dama haka jiya ta gama zagaye ka, babu aikin da kayi mata. Shine har da kuka kayi zina."

Tashi yayi, yana kallon videon, duk jarabatar, Shugaban karamar hukumar wandon yaki tashi sabida karfin maganin da ace mace ce aka bawa zai yi aiki domin.....
Kuyi hakuri don Allah ina fama da jiri ne...
[12/14, 9:35 PM] Anum Muhammad Bello❤️: 72. Zuba mata ido yayi sannan ya amshi wayar ya kashe baki daya.
"Me yasa kika yarda dani haka?"
"Sabida bani da wanda yafi ka?"
"Me yasa da kika ga na karkace baki d'aga hankalin ba?"

"Sabida na rigada na kira Allah, kuma wallahi nasan ya amsa min, akan me zan kuma damuwa akan haka? Zanyi fushi ne nace nayi yaji a kwatar min hakkina ko zan zauna ina kallon yarinyar da bata cewa sa'ata ba tana juya min hankali? Bani da uwa bani da Uba, sai dangi! A wannan lokacin waye zan kaiwa kuka na sai ALLAH, dan haka idan nace zan ja rigimar tayi tsamari nice a ciki.

Dan wani lokaci tun ana baka gaskiya sai a koma a gundura dai kai, karshe a shiga cewa ina da taurin kai bana jin magana na cika kafiya. Dan haka na rufawa kaina asiri, domin idan naje jan rikicin kamar na bawa wancan me kananun idanun damar shiga jikin ka ne, dan haka ban sa a ka ba, inji barawon hula!"

"Yau ina son muje wani taro dake ne, daga nan mu tattara ma mu bar musu kasar, dan na gaji da kasar, amma dole sai na cimma kudirin kasuwanci da yake gaba na," ya faɗa tare da shafa cikin ta.
"Allah ya nufa."
Ta faɗa a sanyayye, tare da kwanciya a jikin shi, tana kallon shi.
--
Kallon Saratu yayi yaga tana shiryawa cikin doguwar rigar atamfa, dan har yanzun yaki sake jiki da ita, tana saka dan kunne, ya gyara murya dan ta tsaya a gaban madubin, tana gyara fuskar

ta, matsa mishi tayi daga jikin mirror din,  yana shiga shiryawa.
Bata ce mishi cikanka ba, amma ya lura yau ko ina kwana da take gaya mishi baya amsawa yau, bata yi ba itama fuskarta a tamke yaƙe, ta madubin ya hango jakar kayan ta, cike da mamaki yaga passport dinta, a saman gado.

Juyawa yayi daure da towel,
"Meye nufinki?" Shiru tayi tare da hada kayanta, zata fita komawa jikin kofar yayi, cikin tsare gida. Ya kalle ta sake towel ɗin dake k'ugun shi yayi, da sauri ta juya bayanta jikinta na rawa, takowa yayi ya rungume ta, tare da d'aukarta cak zuwa gado. Cikin tsiwa ta shiga ƙoƙarin raba kanta dashi. Zuba mata ido yayi ta gama shirmen ta, kafin ya saka karfin shi ya murɗa ta, sai da ya cire kayan jikin ta, sannan ya shiga aika mata da irin nashi darasin, sai ga Saratu me bori tayi lankwasa.
Cikin girmamawa tare da tarin soyayyar gaskiya, me hade da mutuntaka, Aamil ya amshi martaba matar shi, bayan ansha dambe da yakushi dan da yazo garin munafata, hana shi tayi, sabida yadda yake mata, sai da ya daddage, sannan ya zuba mata shugaban karamar hukumar wandon. Tuni ta rikice da kuka tare da bashi hakuri, ganin haka ya sashi sassauta mata, ya bida ita a nutse. Shi kan shi bai tab'a kawowa jarumi ne har haka ba, sai gashi yayi nisan tafiyar da tasaka shi dole sai da ya zage sosai.  Sannan ya kyale. Cikin tareraya hade da so da kulawa, ya kaita ban daki. Yana kai hannu zai taimaka mata ta buge hannun cikin kuka tace mishi.
"Kyale ni! Hankalin ka ya kwanta, nan kayi ta wulakantani akan abinda ban sani ba, yanzun gashi ka rabani da kimata, kuma a haka ba mutunta Ni zakayi ba. Cigaba da wulakanta ni zaka yi."

Rufe mata baki yayi, amma fir taki tare da ture shi ta gama wankanta ta fita ta bar shi, kayanta, ta saka tare da bar mishi dakin, ta nufi gurin Sidrah da kuka. Suna cikin shirin fita.
"Ke lafiya?" Kuka ta sake tare da bata labarin abinda yayi mata musamman wulakancin da yake mata.
Sake baki tayi tana kallon ta, kafin ta kuma cigaba da kallonta.
"Ba zaki min magana bane? Kinga."
"Dakata! Dakina kika biyo ni, toh sai me dan yayi miki wulakancin? Irin wannan rashin uzurin yasa ake zargin hausawa da ahalin su. Ban san meye illar Bahaushiyah ko bahaushe ba da kullum sai an gaya mishi magana kuma ba kome ya janyo haka ba, sai wannan d'abi'ar namu.

Sabida rashin rike aure da muhimmanci, shi yayi miki laifi, kin dibo jiki kina kuka, a kwatar miki hakkin ki, karshen batar basira ki dauka ki kai wani gurin a zauna a zagi mijin, idan an gama dake kuma za a zagi hausawa.

Ban san meye laifin kabilar Hausa da muke wulankata ta ba, domin tun daga kan gidan auren mu, muke wulankata kabilar mu, bamu da aiki sai son ganin laifin kabilar mu, musamman mazajen mu na Hausawa, babban burin mu shine mu fadi namiji ya cuce mu, kowa ta bude baki yace Chaii!  Ko sau daya kin tab'a ganin matar Ibo tace mijinta ya cuceta? Sabida ta san darajar shi a cikin kabilar, zai yi wuya beyarabiya ta gaya miki mijinta ya cuce ta? Amma wallahi zan iya kirga gidan Malam bahaushe da zaka samu ta fito tana cewa an cuce ta!

Yau kafin mazajen hausawa su fara sakewa matan su ragamar gidajen su, Kabilar ibo da sauran suka fa sakewa matar su hidimar iyalin su, zo kiga matar tana soya kosai a bakin hanya mijin yana can gefe yana taya ta bawa mutane,. A iya nan kawai zai tsaya amma duk wani abun da zata yi na rayuwar yaranta ita ce?

Sau nawa zaki ga mace miji ya dake ta, ya watsa kayanta waje, ta rarrafa ta koma cikin gidan tana rokon shi yayi hakuri ta zauna, tasan gidan Ubanta zata sami kome, amma kwanciyar hankalin yaranta yana nan gidan Uban su.

Muna sara bamu tab'a duba bakin Gatari ba, burin mu kawai mu zagi bahaushe ko hausawa, eh mazan mu ba da laifi amma ki godewa Allah da ya baki namijin da kai tsaye yake rayuwar shi, bai baki namijin da kece kullum zaki yi mishi uzuri ba, Hmm! Muna rena kan mu shi yasa kowacce kare da doki take rena mu, idan aka ce kowa ya dauki kabilar shi toh wasu ba zasu tab'a daukar kabilar su ba, sabida kan su bata waye haka ba.

Al'adu da dabi'un hausawa turawan mulkin mallaka ma sunzo sun same shi, balle kuma kai huhhun, kace wai baka da abun zagi sai mijin Bahaushiyah, ke nan kin rena kanki akwai wanda suke jiran su sami kamar naki ko kasa da naki.

Wallahi ki ji tsoron Allah, ki ajiye ya raba ki da kimar ki, sabida yaji dadin shi, idan aka barki da budurcin Uwar me zaki yi da kayan hawa kai? Idan kika ki kuwa akwai irin su Anyah dayawa, kuma zasu iya kwace miki shi ga kuma matar shi tana nan zata iya kome dan mijinta.

A wannan zamanin da maza suke tsada kuma duk tsiyar zai yi wuya ki ga mata ta kashe aurenta duk rena kulawar da take samu, tana manne da mijinta koda kuwa yagarta yake, amma ke kin samu ma zaki wani yiwa mutane iyayi ya rabaki da kayan banza, Wallahi a wannan zamanin wani abin dariya yake bani? Ke da kike cikin gidan godiyar Ubangiji zaki yi da Allah ya rufa miki asiri.

Bawai ki tashi ki kai karar mijinki gurin Budurwan da take niman mijin aure ba! Kiyi nazarin abin! Tunda kika iya zama dashi na wata shida kinfi wacce bata zauna da shi na kwana shi da ba, me zata nuna miki?

Wato zamanin baya, iyayen mu sun zauna da mazajen su lafiya sabida babu kazamin wayewar da budurwa zata gaya miki yadda zaki rayu a gidan mijin ki bane, domin lokacin kafin ki sami bazawara a cikin unguwa sai kinyi da gaske, sannan kafin kiga budurwa tayi maganar da matar aure suke sai kinyi da gaske, idan kuwa aka samu labarin haka, hmm sunanta sorry domin zata gayawa iyayen ta a ina taji wannan labarin da take kararwa. Amma zamani yazo yayi garambawul da al'adar mu, yayi tafiyar bazata da dabi'ar mu.

Yarinya karama zata zauna ta tsara miki yadda zaki yi da mijinki alhalin ita bata samu ta shiga daga cikin ba. Shi yasa zama na a dubai, na zauna a cikin manyan mata kuma sun gaya min rayuwar da muke yi ba sauki, dole namiji kai mishi uzuri. Dole kayi mishi adalci a zaman ku,

dole ka ɗauke kanka daga gare shi, da zaran ka rike haka toh wallahi babu namijin da ya isa ya miki Iskanci.

Amma a zamanin sai kiji wai tana duba wayar mijinta, sabida kar ya fita niman mata ko me? Dauke kanki shi da kanshi zaki ga ya sha jinin jikin shi, akan abinda yake, ai mutane ne ba dabbobi ba.

Kuma sun san me suke, wallahi idan na gaya miki abinda ya faru dani Sarah, sai kin tambaye ni wani irin zuciya ce a kirjina? Meye Aalim yayi min da nake hakuri dashi haka, kawai abinda a sani sirrin mu a boye yake kuma zan cigaba da boye shi. Har ila masha Allah, babu amfanin na fito na tonawa kai na asiri bayan ni duniya zata zarga, sannan cikin jikina ban mishi adalci ba gurin bayyana sirrin mahaifin shi, don Allah ki zauna lafiya da mijinki, da zaran kika cire jin dadin na rayuwar aure kika mai da ibada a kan rayuwar aure, wallahi kinji na rantse miki, babu abinda zaki yi Allah bai baki Sa'a akai ba?

Ita kanta rayuwar auren ibada ce karki yarda wani yace miki jin dadi ne, kice mishi ibada ne, kuma zaman da kike zaman ibada ne, zaki ga yadda Allah zai daukaka alamarinki. Mafiya yawan rigingimu da ake samu a gidajen ma'aurata, Wallahi basu gina auren bisa ka'ida ibada bace da an daura a mizanin ibada babu wanda ya isa yaji ihun su sai dai idan Ubangiji ya kawo haka domin ya zama izina gare mu.

Toh damuwar mu, jin dadin aure, wanda kowa fatar shi ne, bamu kaunar wahala ko yaya ne, sam burin mu, mu zama Latest couples of the year, bayan idan muna son haka sai mun yarda muna bautar Allah ne a cikin rayuwar auren mu zamu zama dai-dai. Zai yi wuya ka ga mace na zaune zaman lafiya ba ace ta gama da mijin ba, wata zaka samu bata fashin sallah dare, azumin Alhamis da Litinin, sada zumunta, kyautata alaƙarta da makotanta tare da mahaliccinta.

Rike mijinta da gaskiya koda kuwa yana cutar da ita,.ba zata gayawa kowa haka ba, burinta kawai ta rufawa kanta asiri a gidan mijin, da za'a sami yar caburus, tana zuwa zata ce mata kutt? Irin wannan wahalar, irin wannan cin kashin kuma kika zauna? Wallahi ki kashe auren, bayan zaki samu ita bata da auren ma! Wallahi duk wanda zai baki shawara akan aurenki ki duba yanayin rayuwar shi, kafin kiyi kokarin daukar shawaran shi. Fatan mu Ubangiji ya sa mu dace duniya da lahira, yan uwan mu Zawarawa da yan mata, Ubangiji ka kawo musu maza na gari, Ya Allah kasa zaman su ya zame musu jinkirin Alkhairi. Mu kuma masu auren Ya Allah ka bamu zaman lafiya da kwanciyar hankali da mazajen mu. Yaran mu kuma ka saka musu albarka a rayuwar su. Ka basu ilmi mai amfani, ka shirya su tafarkin addinin Muslunci, ka kare su da miyagun mutane, Ya Allah mazajen mu, ka tsare mana imanin su, ka basu ikon kula samu da adalci, ya Rabb ka rabasu da shaidanun mata da shaidanun abokai, Ya Munyi tawasalli da kyawawan sunayen ka masu Tsarki ka sanya mana hakuri da juriya da kowa....
[12/15, 11:14 AM] Anum Muhammad Bello❤️: 73. Jikin Saratu ne yayi masifaffe sanyi, dan tana kallon Sidrah ne bata tab'a sanin tana da baki da hikimar da zata warware mata laifinta ba.

Gashi cikin sauki da adalci ta warware mata laifinta da kuma kuskuren da take son aikatawa, kallonta tayi sannan tace mata.
"Nagode sosai, Aammin baby, kin sani Naji kunya sosai, kin nuna min gaskiyar da nake shirin takawa.

Nagode da kuka tsame ni daga cikin kuskuren da nake dab da fadawa, badan kinyi min haka ba, da wallahi ba karamin laifi zan aikata ba, da zai tabibiyata har karshen rayuwata, sai kika nuna min nayi hakuri tare da uzuri, nagode sosai. Insha Allah ba zan tab'a barin wani yasan abinda yake damuna balle har fuskana ta zamewa mutane madubin kawar kansu.

Nagode sosai, wallahi Naji dadin wannan nasihar, domin babu wanda ya tafa fada min yadda miji yaƙe, kawai ance min nayi hakuri ne dashi, toh gashi nan kin gaya min shi din Uzuri yake bukata a zaman mu, nagode sosai."

Haka tayi ta godewa tana kuma hango kuskuren da Sidrah ta dakatar da ita ga aikatawa da shikenan, tana tashi ta zama kamar Anum, wacce ta rena mijin hausawa ta gwammace da ta auri bahaushe mai karamin karfi gwara ta auri, wata kabila wanda bai kai bahaushe kula da iyalin shi, Alhamdulillahi tayi a zuciyarta da Allah ya bata Sidrah wacce ta dawo ita cikin duniyar da take shirin bari. Mikewa tayi tare da yiwa Sidrah sallama, sannan ta koma dakin su, yana zaune ya zubawa gadon su idanu.

Tunda ta fita ta barshi yake nazarin abinda ya faru a tsakanin su, tare da auna daren shi na farko, da Nadrah. Da yadda Nadrah take rena mishi hankali akan jarumtar shi, yau ma gashi Sarari ta rena jarumtar shi, tana mishi kallon mara adalci, meye yayi da ya za mara Sa'a.

Jiya yana jin yadda Sidrah take bawa mijinta uzuri, duk abinda zai mata zata ce ta mishi uzuri, kuma haka bai hanata ta kyautata mishi ba. Da ace hannun agogo na juyowa tabbas da ya juyar da ƙaddarar shi da Sidrah ta dawo daidai kamar na koyawa, da ace haka zai sami mace mai hakuri da juriya irinta tabbas da a lokacin da aka bashi ita da ya rike ta da amana, tare da zuciya daya, yau yaki Sidrah duk macen da ya kalla sunan aure juya mishi baya take, dama akan haifi mara Sa'a ne irin shi?

A hankali ta taki zuwa bayan shi, ta daura kanta bayan shi, tare da sake mishi kuka sosai, lumshe idanun shi yayi yana jin wani kwarya-kwaryan nutsuwa tana saukar mishi, bai ce mata kome ba yana jin yadda take kuka tare da kara mannewa a jikin shi, ya sanya shi saduda yarinyar tana yin shi.

Ya kuma yarda zata iya zama dashi a haka, Alhamdulillahi da bai yanke hukunci cikin sauri ba, da yayi saki na dafe, juyowa da ita yayi tare da zuba mata ido, boye fuskarta tayi tana sheshrkar kuka.
"Supergirl kiyi hakuri!"
Boye fuskarta tayi, tare da rike hannun shi da yake shafa fuskarta, a hankali ya zare hannun ya cigaba da shafa bayanta, har yaji tayi shiru.
"Me yasa kika dawo?"

"Sidrah! Ta gaya min gaskiya" murmushi yayi tare da rungume ta sosai, har abada ba zai dain kaunar Sidrah ba, yarinyar tayi mishi kome, ta kuma dawo mishi da kome da yake shirin rasawa.

--- Bayan sun je taron ya hadu da manyan taurarin nan dai da suka taka rawa a cikin labarin mai-dambu, ya kuma hada matar shi da matan su, aka yi zumunci, anan Sidrah ta haɗu da Safinah Ashraf, wato me kan dankli (🤣🙄) suka zauna suna hira amma hankalin ta sam baya kan su, tana yi tana kallon mijinta ita da Husnah Manga, me kan kwakwa itama, gwara ma Husnah akan Safinah Ashraf, domin Husnah ta nutsu akan mijinta ne, ita kuma Safinah Ashraf tana fama da waya tana fama da mijinta, kwace wayar Rahilah tayi tare da kallonta.

"Kina gudun kafin ki d'ago kanki wata tayi gaba da mijinki ne? Ko kina tsoron kishiya ce?" Ajiyar zuciya tayi sannan tace.
"Tsakanina da shi, sako ne ki duba wayar sakon muke musayar shi."

Shiru suka yi sannan Amrah da tafi su Shekaru tace.
" Wato a wannan zamanin mun zama Allah sarki, rayuwa ta koma abin tsoro da tausayi. A zamanin baya,mata biyu sama da biyu suna zaman a matsayin matan mutum daya, amma a wannan lokacin wata tana harin ta shigo tayi waje dake ne!"

Murmushi Maryam Sajida tayi sannan tace.
"Sabida bamu dauki rayuwar auren da Muhimmanci ba! Burin mu mazajen mu su kwanta mu juya su kamar yadda muke juya rigar nono.

Miji irin Daddyn Hudah, bayi da sauki domin ba zaka juya shi ba ba zaka kuma sami rarrashi ba,sai dai ki rarrashe shi, koda kuwa kece da gaskiya,  mu uku ne a gurin shi, kuma nice karama a tsakanin su, bamu tab'a kallon kanmu da wance itace gwanar Baban Hudah, sabida rashin kirki shi ba iya ke zai tsaya ba, idan ya kwayance mana har kan  yaran shi yake ajiyewa.

Matsalar mu, shine saka musu ido da muka yi, idan zai fita Allah Allah muke muji ina zai je, idan yana waya, kallon wayar muke muji da wa yake magana,taya namiji ba zai rena ki ba.

Wallahi a wannan lokacin akwai matan da zunzurutun mutunta su da mazan su suke, basa waya a gaban su!  Saboda kawar da kai da suka yi akan duk abinda mazan suke, ya sama musu zaman lafiya a rayuwar su."

"Amma kuma Maman two ban tare ki ba, kin san meye tashin hankalin mu? Yadda matan basu zuwa da kyakyawan niyya, duk wacce zata shigo kanki dakyar ne ta shigo miki da niyya me kyau burinta tana zuwa tayi waje dake."
"Mrs Ruma ban katse miki hanzarin ki ba, ba kuma na manta da irin wadannan matan bane. Sai dai ki sani suma zawarawa da Yan matan wallahi abin tausayawa ne? Domin idan da zaki

duba yanayin rayuwar su, abun a jinjina musu ne.

Sannan duk macen da tayi zawarci ita kadai ce zata gaya miki taya ta fuskanci rayuwarta kafin tayi aure, idan muka gyara niyyar mu akan kome, Allah zai tsaya miki kuma ya baki kariya, duk macen da ta amsa sunanta mace, bata saka Idanunta akan abinda namiji yake!

Sannan idan yasan ciwon kan shi baya yarda ya b'ata ki a gaban abokiyar zaman ki da zai shigo da ita, sannan abinda zaki duba halin mazan mu daya ne fa! Ba me kudi ba talaka, idan auren ta ciyo su wallahi ki da gidan shi kanzo ake tirarawa, zaki samu sai yayi auren, wasu dabi'a ce! Wasu kuma halin matar gidan ya ja musu kamar Rahilah da Rahimah, da kuma Nima halayyar matan mazajen mu suka sanya su kara aure.

Wasu kuma shegen kishin da babu amfani, wanda shi yake kawo kishiya."
Shiru Sidrah tayi tana kallon yadda goggagun mata suke tattaunawa akan rayuwar auren. Gyara murya tayi suka kalleta itace me karancin shekaru a cikin su..
"Toh me ke kawo yan mata suke bin maza haka, kamar zasu cinye su!"

Lashe bakinta tai tare da gyara zama, sannan tace musu.
"Tun ban kai haka ba, nake fuskarta irin wannan case din kuma dani? Kodan mijina ya kasance ruwa biyu ne?"

Murmushi Aanih tayi sannan tace mata.
"Babban laifin na iyayen mu ne! Sai kuma laifi na gaba laifin yan matan ne. Nima na fuskanci haka. Sai dai abinda na Fahimta mun iyayen mu, abinda suka nuna kunya da kamun kai, yayinda wasu iyayen suka manta da wannan batun.

Mace an santa da kamun kai, tare da kaf-kaf da kanta, amma wannan zamanin zaka ga mace tana cewa. Allah ya bata miji ready made, me saje da kyakyawan kwanciyar hankali. Bayan bata nemi miji na gari ba, sannan shi wannan da kike addu'o'in akan shi yana da tashi rayuwar, yana da matar da yake buri,.yana da duniyar da yaƙe ginawa, Ya rayuwar shi take?

Wani zaki ganshi tass a waje, amma da zaki shiga gidan shi, zaki ga abinda ya dame ki, sabida matar shi ta boye asalin shi ta fidda zahirin shi Kai Mata A gaishe ku🙏🏼, zai yi yiwa ta nunawa duniya waye mijin ta, kullum cikin rufa mishi asiri take, amma a haka da zaran wata ta ganshi zata san yadda zata yi ta raba wannan amanar da aka gina da sirrin da suke b'oyewa, ta raba shi da matar shi ita kuma ta ki zama ko kuma ta hana shi sukuni"

"Amma kuma wani abu da na Fahimta?"
"A'a matar Sultan Ashraf!" Suka fada, cikin yanga tare da jin kanta ya wani fashe tace musu.
"Iyayen mu, sun koya mana haerekuri da juriya tare da boye sirrin mazajen , amma me yasa bamu iya dauka ba?

Ummina ta sami matsala da Abba sabida ni, ya kuma sake ta, saboda ni amma har Ummi ta

koma gidan su bata tab'a gayawa yan uwanta cewa ga abinda mijinta yayi mata.

Da zan auri Dr tayi kokarin ganin na zauna lafiya da mijina babu kawo kara, Ummi ta min nasiha da yadda zan zauna lafiya da mijina, da muka rabu na koma gidan Ashraf, sai da tayi min da gaske, akan uwar mijina itace matsalar mijina da ni kaina,  amma a wannan karnin mace ko kawo karar mijinta ga yan uwan shi kafa sadarwan zamani. Sabida mun zama yan talla, sai kiji tace. Admin boye suna na, anyi kaza kaza dangin mijina sunyi kaza kaza.

Kwanan na gani a face book, wata yarinya tayi dalilin da mijin da zata aura ya kara aure su biyu a rana daya. Sabida rashin hakuri irin namu. Ina ruwanta da Kanwar shi tana juya shi? Ina ruwanta da kome sai abinda Kanwar shi yasa shi.

Ni ina da careless, idan aka ɗauki irin halina wallahi babu abinda ya dame ni, abu daya na sani ina da shegen taurin kai da kafiya. Amma dan mijina zai karo min irin su Natashah Alhamdulillahi tazo ina mara ba da ita!"

"Kuma ni abinda zai dame ki, shine me yasa ba zamu gane idan muka bada labarin abinda mazajen mu suke mana, akwai yan mata da suke niman kaman mazajen mu da muke kai karar su. Wani idan Baban hudah yaso ya cika mu cika hudu babu abinda ya dame ni, Ina da Umma da Mama Amarya, uwa irin namu sai dai kiyi hakuri ki dauki halin manyan bayin Allah, domin bana mantawa Baban Huda zane ni kuma ya min wulakancin, da na kira ina kuka cewa tai nayi hakuri.

Tun daga ranar na fahimci, iyayen mu, burin su muyi irin rayuwar da nasarar da suka samu, abu daya taki dauka shine duka, anan na fahimci duk wani gidan da aka sami nagartattun mutane toh ki bincika suwaye tushen gidan? Wani tallabi iyayen suka bada? Meye nasarar su a rayuwar su."

.kusan wannan itace tattaunawar da suka yi ta yi, har mazan su, suka gama abunda zasu yi suka taso a gurin taron. Sannan Sidrah suka tawo gida...

---

_Eh toh! Duk da nasan wacece ni 🙏🏽 amma ina ganin kamar bari nayi mana wani tishi da abinda muke bukata a rayuwar mu! Da gaske gidajen mu sun kama da wuta bamu sani ba! Na farko mu mata mun zama harijai karfi da yaji! Da maza aka sani da wannan halin! Na biyu mun zama marasa hakuri karfi da yaji! Kullum ba duniya muna niman shawara akan ya zamu yi da mazajen mu, uku mun rena kan mu? Idan aka yi magana sai kice shi namijin me yasa ba a cewa ya gyara! Ba kowani namiji bane yake saurаron Wa'azin Kabir Gombe ko Isah Ali! Ko malam tijjani guruntun! Ba kowani namiji bane yake zama ya saurari wa'azi akan iyalin shi dan ya gyara!  Mazan mu basu da dadi! Amma akan mu kai karar su me zai hana muyi kokarin koyan hakuri da su! Kin zama mabukaciya toh ba damuwa! Idan kina son shi ya zama haka, sai ki zauna kuyi yarjejeniya ni dashi, Baban dan Albarka! Me zai hana mu gyara rayuwar auren mu, ina cutuwa! Idan zaka gyara bismillah idan ba zaka gyara ba wallahi zan mai ka kara

manyan su shiga maganar tunda ni dai Allah ya gani mabukaciya ce! Baku san wani abu bane mazajen mu suna da saukin kai! Idan kika biyo ta inda ya dace, wallahi zai amince ya amshi tayinki, idan ma yace ba zai iya sayan maganin ba, mata muna da dabara wallahi ki saya, ki bashi ku gyara mu'amalar ku, sai a zauna! Kuma su ma mazajen abinda ke kai su leka waje! Billahil azim nonuwarki sun kwanta ne? Malama jeki nemi Dara, kiyi bincike akan Dara, ki gwada yana gyara nono mazan mu suna son nono, ki nime bra me d'aga su,.wanda yana shigowa ki d'ago kirjin yana mishi sigana, ki nemi bra wanda rabin nononki suna waje, don Allah ki gwada yin dinki wanda za a miki tsagun kirjin, idan ana kallo yaran mu Mayun kallon fim ne musamman labarina Barsu su kalla, hard'e kina dan tab'a wayarki koda baki bude data ba, yana zaune amma hankalin shi ana kanki_
Maybe idan na sami lokaci na cigaba...#Mai_Dambu🤯
[12/16, 8:39 AM] Anum Muhammad Bello❤️: Wannan shafin sadaukarwa ce ga re ki Y'a guda ba bari ba, Barka da zagayowar shekarar haihuwar ki, Duk da Maamah tayi lati, a karbi uzurina ❤️🍰🍮🎂🍩🍪🍿🥧🍦🍫🍡🍥 Allah ya albarkaci rayuwar ki, ya kuma shirya mana ku tafarkin addinin Muslunci, ya kare ku da kariyar shi, ya tsare ku da tsarin shi, Ya Allah duk wanda zai zamewa Al'ummar musulmi masifa ya Allah munyi tawasalli da sunayenka kyawawa tsarkaka masu daraja, Ya Allah ka yi mana maganin su, Ya Allah ga Y'ay'an mu. Bamu da tsumi bamu da dabara ya Rabbi kai ne mafi hikima Ubangiji ka kare mana Zuri'ar mu.. Ya Allah Yaran al'umma da aka kwashe su, Ubangiji kai kasan nauyin zuciyar Uwa! Ya Allah kai kake zana kaddarar kowa, Ya Allah mun yarda da kaddara me kyau ko akasin haka, Ya Allah Nagode, Alhamdulillahi Ubangiji ka kawowa iyayen yaran nan mafita 🙏🏽😢 albarkacin Alqur'ani.Amin Ya Allah

74.Tun a hanya take kallon shi, cikin sanyin jiki, hannunta ta kai saman nashi, sannan tace mishi.
"Nagode da zab'a na a matsayin matar ka!"

D'ago kanta yayi tare da cewa.
"Ni nayi nasara da zab'a na a matsayin mijinki kuma abokin rayuwarki." Murmushi suka sake lokacin gudu, tare da hade goshin su, suna kallon juna, har suka isa gida, a ranar aka gaya mishi rasuwar Abba, naga tashin hankalin shi sosai, dan kasa barci yayi, duk juyin da nayi zan gann shi zaune. Yana kallon hoton Abba da yake laptop din shi, cikin tsannanin damuwa.

"Ka kwanta mana!"
"Baby bazan iya barci ba."
"Zaka iya mana kasaka a ranka zaka yi barci, idan ba zaka iya ba, bari na tashi muyi alola!"
Na fada mishi a hankali tare da da mik'ewa ina dade baya na, da yake barazanar kamar zai ɓalle.

Rike ni yayi muka yi alola, sannan muka fito shi ya shimfid'a mana abin Sallah, har kusan asuba muna sallah, muna kwanciya ana kiran sallah asuba, haka muka koma tashi muka yi sallah, muna idarwa muka muka kwanta, na samu damar barci amma shi tashi yayi zuwa ban daki yayi wanka,sannan ya shirya ya fita.

Karfe goma sha biyu na tashi a hankali, na samu ya gama hada mana kayan mu, sannan ya zauna yana shafa kafaffuna da suka kumbura sakamakon nauyin cikin. Dan an gaya mana a asibitin. Mikewa zanyi ya kai hannun shi na rike sannan na tashi zaune.

"Tashi muyi wanka yau zamu bar kasar, ku zaku zauna a U.s har ki haihu. Insha Allah zan zo idan na gama abinda muke!" Ya faɗa mata, kallon shi take sannan tace mishi.
"Ni..ni tsoron kar su kuma cutar da kai nake."

Shafa fuskarta yayi sannan ya mikar da ita zuwa ban daki,a tare suka yi wanka. Sannan suka fito kallonta yayi yaga ta masifar bashi sha'awa, murmushi yayi tare da rike hannun ta.
"Sidrah! Hmm"
"Toh ai hakkinka ne"

"Na sani!" Zare towel ɗin yayi, daga nan Al'amarin ba a cewa kome, dan sai da yaga sauyi a kan fuskarta, sannan ya mike domin shi kan shi yasan ya murzata sosai, ya gurza ta gurzu a hannun shi, taimaka mata yayi.

Karfe uku suka fito, bayan ta ciwo yake mata, amma bata nuna mishi haka ba, asalima tsoron kar ya zargi bata son yayi tafiyar ne.

Dukkan su, suka nufi Airport.
Tunda ta zauna ban da fitsari babu abinda yake kuma d'agata.

***Dutse.
Ghali shi ya dauki kakar su, zuwa asibiti. Aka mata duk abinda ya dace, sai dai Hajiya bata magana kome da ido take kallon shi, asalima kamar gefenta ya shanye. Sau daya yawa zaka ganta tana kuka, tare da kallon mutanen da suke tare da ita..

Ya Hindatu kuwa, dakyar ta zauna a jikinta domin tun rasuwar Abba, da aka raba gado. Tayi ta kwashe na Hajiya tana b'arnantawa, dan haka bata cika zaman gidan ba. Yanzun ma da ciwon ya kama Hajiya, kullum mita take akan me Hajiya ba zata mutu ta huta ba.
(Dama akwai zamanin da Y'ay'an da aka haifa zasu juyawa iyayen su baya, gashi nan ya faru)

Idan ta fadi haka, murmushi Hajiya keyi hawaye na zuba mata, sabida yau yar da ta haifa take ce mata me yasa take raye. Bayan tafiyarta tayi kuka sosai wanda haka yaso tab'a lafiyar idanunta. Domin bayan gama kukan ne ya fara gani dishi dishi.
A hankali take jinya amma babu magana, bayan an sallame ta ya dawo da ita gidan, wallahi rayuwar tsohuwar akwai ban tausayi, karshe dai daukarta yayi ya kaita gidan Hajiya Uwani, ranar da ya kai ta, tayi kuka tayi alama ta rasa ya zata yi ta nuna farin cikin ta.

.. duk wani abinda take bukata, duk Ummi tana mata. Domin ta mai da hankali akan gina rayuwar su, kuma Alhamdulillahi yaran ta, suna cikin koshin lafiya da kulawar Aamil. Da baya

nan din nan duk wata yana tura mata kudi, kuma wannan duwatsun da ya bata daya ta sayar ya zame mata alkhairi yanzun kasuwanci take sosai, hakkin yaranta kuma suna bank. Ita da Hajiya ta tsana yau gashi itace gatar ta.

Shi yasa a rayuwa, karka tsani mutum, domin baka san ta inda zai taimaka maka ba, haka kawai sai kaga wani ya tsane ka, babu dalili da zaran kayi magana ya juyar da maganar, zuwa anjima ya shiga zage zage, sabida ya tsane ka, gaskiyar malam ne yace kaskantace baya shiga matsala da mutane, sannan jahili baya shiga matsala da mutane, talaka futuk baya shiga matsala da mutane, amma idan ka duba rayuwarka sai ka samu, sabida wata halitta da Allah yayi maka yasa zaka juya ka zama wani abu, wasu daga cikin mutane suna ji kamar zasu kashe ka! Suna ji kamar gwara ka mutu ka huta. Allah kasa mu dace..

.haka suke kula da Hajiya kuma a takaita Asibiti, a bata duk wani kulawa, a duk lokacin da Hajiya ta kalli Ummi, sai ta share kwalla. Sosai take dana sanin abinda ta aikata a baya. Musamman idan ta tuna da yadda tayi ta cutar da Ummi da magana.

Amma gashi ya wuce kamar bai tab'a faruwa ba. Ummin ta rike ta hannu bibbiyu, kamar mahaifiyarta, wannan yanayin ba kowa ke fahimtar shi ba,

---

"Yarana zaki bani, domin kuwa ina shirya musu rayuwa me kyau ba irin taki rayuwar da kika taso ba." Ya faɗa mata yana kallon fuskarta.

Murmushi tayi sannan ta shiga saka kayanta, bayan ta fito daga ban daki.
"Amma ka sha ruwa mana."
Ture ruwan yayi ya mike tare da zuba hannun shi a kafad'arta.
"Nasan kan makirci tun ba a haife ki ba, Yarana nake bukata zan kai su inda ya dace."

"Toh Alhaji Abubakar naji zan kawo maka su, amma ba zan bar maka su ba, domin Janan bata wani girma ba, wannan jaririn kuma bai kai yadda zan baka shi ba."
Takaici ya ishe shi, dan haka ya juya ya shiga ban daki, itama ta shirya ta bar gidan, tare da goyonta. Tana niman hanyar da zata kawar da Alhaji Abubakar, tare da saka sunan yaranta a dukiyar shi.

..... "Arianah amma me yasa kika damu da ita?" Girgiza kai tayi sannan tace mata.
"Kawai yadda take tozarta aure ne yake min ciwo, bani da aure amma wallahi abinda Nadrah take ba zan iya aikata shi ba, tun ranar da na fara ganin haka ban kuma aikata wani abu da zai zama cutarwa ga Addinina ba. Ni Amanar iyayena naci da Addini na naci,"

Ita kuma taci amanar iyayenta, amanar aurenta, taci amanar mijinta, taci amanar ƴaƴan ta, kasan yadda duniya zata kalle ta, maybe baka san yadda iyayenta zasu ji bane, ita daya suka haifa, Kuma ita daya suka ajiye yau idan suka san da haka ya zasu ji? Wallahi na tausayawa mijinta da Mahaifinta."

"Kamar ya taci amanar mahaifinta?" Kallon shi tayi sannan tace mishi..
"Shi mutumin aminin mahaifin tane tun suna yara. Har girman su..Insha Allah zan dakatar da wannan wulakancin ya ishe ni"
.ta fara tare da jan motar, domin tunda daga ranar da ta fahimci abin duk ta watsar da abinda take, tabi Nadrah ta daina taki, tayi tayi taki. Har barazana tayi mata.
Dariya tayi sannan tace mata.
"Ba zan hanaki gayawa iyayena ba, amma ki sani rayuwarki zakiwa, domin ni dai nasanni zan iya aikata kome akan ka b'ata min nasarata ta gobe."

Daga haka ta juya abinta, tare da barin gurin, jikin Arianah yayi sanyi musamman yadda taga tsagwaron gaskiya a maganar Nadrah. Shi yasa ta rungume rayuwarta kwanan ne ta kuma dawowa da bibiyar Nadrah.

***

Karfe biyu na safiyar Litinin suka sauka a garin Abuja, sannan suka nufi Kano, daga Kanon ne kuma aka dauko su zuwa gidan Hajiya Uwani, dan ita suka gayawa suna zuwa. Suna isa Ghali da yazo duba Hajiya ya same su, ganin Aalim juyawa yayi zai labta a guje, sai da Aamil ya rike shi.

Yana dariya, sannan yace mishi.
"Bai mutu ba fa, sanin ana niman shi yasani cewa ya mutu! Amma yau Insha Allah zamu ji me ya faru."

Ajiyar zuciya ya sauke sannan ya dawo ya zauna, dariya Aalim yayi sannan yace.
"A ranar da muka sami sab'anin da Sidrah, nayi kokarin ganin nayi mata adalci, amma na kasa..sabida da ciwo ace matar ka da dan uwanka, a gado daya. Da nayi nisa a tafiyar da nake, duk da ana ruwan sama bai hanani fahimtar ana bina ba,.dan haka nayi kokarin barin garin, amma ina sun cimma ni, dan haka suka yi ta buge motana har muka iso wudil, gashi ana ruwan sama kamar da bakin kwarya. Dan ga kuma babban mota a bayana, ban san me ya faru ba, sai gani nayi motar ta kama da wuta, ta bayana garin na sauka akan hanyar mukayi tahada hanya, karshe ya zama hatsari babba, inda motana ya kwace a hannuna zuwa cikin ruwan wudil.

Sun bini kamar masu ceton rayuwata, daga nan suka fidda ni, zuwa gurin motar su, suka juya dani Dutse.

Iya azaba na sha, kuma akan Aamil wai sai dai na basu dukiyar Aamil ba'a son ya sani idan ya sani, toh za a kashe shi.

Ni kuma naki, shine wasu mutane guda biyar da na sani, suka shiga raunatani, har sai da suka ga bana motsi, kafin suka dauke ni zuwa inda muka yi hatsarin aka wurgani cikin ruwan."

Cikin huci ya mike zai fita, riko hannun shi Aalim yayi sannan yace mishi.

"Baka da kirki! Babu inda zaka, zamu tafi tare yin amfani haka zai sanya su fahimci basu isa kome ba."

"Toh suwaye mutanen?" Ya tambaya cikin tsawa, murmushi yayi sannan yace mishi.
"Suna nan mana, kawai zaka sha mamaki idan ka gansu, kuma rasuwar Abba suna da hannu a cikin shi, domin kuwa sun jima suna bibiyar rayuwar shi. Allah bai nufa ba."

Kamar karamin yaro yayi ta zunduma ihu, tare da ture kome, sai da Aalim da Ghali suka rike shi, sannan yayi shiru kuka ya fashe da shi.
"Duk a kaina ne? Me yasa baka gaya min kome ba?"
"Lokacin da nake binka Baka saurare ni ba, asalima kaki fahimtar abinda ake bukatar na gaya maka, a gaban kowa kake cewa sai kaga bayana."

Gyada kai yayi sannan yace.
"Wallahi anyi haka? Toh ya zanyi? Taya zan gano makiyan mu?"
"Abinda na fahimta daya ne, kuma shine shawarar da na yanke, idan kome ya lafa, zan koma U.s da zama, domin matukar muna tare a nan ba zamu tab'a fahimtar juna ba, Zan koma sabida rashina a kusa yasa wasu abubuwan a can sun nemi durkushewa.

Hakkinka yana nan a email address din ka, abinda na sani shine kawai zaka yi kokarin mu gano mutanen da suke niman rayuwar mu ne, sannan babu kai babu cin abincin kowa sai na gidan nan."

Kallon su Hajiya tayi cikin kuka, tana son gaya musu kome amma saboda nauyin da bakinta yayi yasa tana kallon su, bata iya cewa kome ba, sai gyada kanta take kawai, tana zubda kwalla, tare da mika musu hannu, hannun da ya wulakanta Mahaifiyarsu, yau shi yake kokarin niman yafiyar su..

______

_Eh akwai wasu abubuwan da nake bukatar tuna muku! Mu rage amfani da kafi zabuwa! Vendan, ajinamoto, mangyada! Sannan madarar awara, asalima suna da maikon da suke rage karfin namiji! Ga jikinki kuma mace ki rage amfani da yaji domin yana kona ni'imar ki. Sannan bance kuyi ta durawa maza magani ba fa, amma ku fahimci juna, sabida shi maganin nan yana da karfi sannan jijjiyar zuciyar d'a namiji yana hade da gaban shi ne! Dan haka kuyi kokarin ganin an sami masalaha_
[12/16, 7:02 PM] Anum Muhammad Bello❤️: Da yamma likis, suka shirya su uku, zuwa sannan suka nufi cikin gidan, abin mamaki kowa sai da ya rud'e.
"Dama baka mutu ba?" Inji Faruq yana kallon Aamil.
"Eh kuna bukatar na mutu ne?"
"A'a kan me zamu so ka mutu sai dai da mamaki ace kana raye."

"Allah ko?"
Shiru yayi, sannan suka shiga cikin gidan, yaga yadda gidan ya. Koma take kewar mahaifinsu ya dawo musu, sai gani suke kamar yana nan. Idanun Aalim ne ya cika da kwalla, rike hannun

shi Aamil yayi tare da cewa.
"Kayi hakuri!"
Haka suka shiga gidan, cikin wannan Hajiya Surayyah tana aiki tana ganin su, sai da gabanta ya fadi, sake wankin hannunta tayi tare da zaro idanu.

"Waye Aamil waye Aalim?"
"Dukkan mu suna mu sunan mu Aalim" da sauri ta juya zata shiga daki ta zame ta fadi a gurin, zunzurutun ta razana, ajiyar zuciya take saukewa tare da kallon sun.

-- Juyawa suka yi Abin su, dan jikin Aamil yayi mugun sanyi, suka fitowa harabar gidan Ali da Faruq suka shigowa tare, ganin kowanne su ya nufi part din shi ya sasu Fahimtar wato Aalim yana raye kenan.

..... A cikin kwanaki ƙalilan suka fara farfaɗo da tattalin arzikin kasuwar su, tare da daura alhakin haka akan Aalim.

Gyara shagunan aka yi tare da sake zuba wasu abubuwan da suka kone, suna cikin haka aka kira Aamil a waya. Yana jin muryan mace ya kashe wayar ya kira Aalim, cikin sa'a ya dauka.
Ajiyar zuciya ya sauke tare da cewa.
"An kirani da wani number ne ma zata kai ne a cikin wani hali shine na kashe na kira ka."
Murmushi yayi sannan yace mishi,'
"Alhamdulillahi, ina cikin koshin lafiya. Kai fa?"
"Masha Allah, nima ina cikin nutsuwa."
Sun jima suna tattaunawa kafin suka yi sallama.

Haka dai me kiran nan ta cigaba da takura Aalim, har ya gaji ya dauka tace mishi.
"Ko zamu iya hadu a gidan gonan ku na da?"
"Ok ba damuwa," ya faɗa sannan ya kira Aalim ya gaya mishi, kasuwa yazo ya dauki Aamil suka tafi tare, tun daga nesa ta hango su, amma bata ce kome ba.
Suna isa ta tadda motarta, tare da barin gurin, dan tasan ba lallai bane Aalim ya iya yarda da ita, haka suka ji haushi suka juya, tsaki Aamil yake tayi, Aalim yana murmushi.
"Kai baka damu ba?"
"Toh a kame zan zama damamme irinka, bayan bani da damuwar da ta dame Ni? Abinda kake irinta mutanen da suka damu da damuwar wasu ce, kai koda yaushe sai ka saka karfi akan aikin gabanka."

Juyawa yayi cikin jin haushi, ashe ya sake hannun shi, da sauri Aalim ya kwace kan motar suka kusan kifawa a titi, kallon juna suka yi.
Wani Gwauron numfashi Aalim yaja, sannan yace mishi.
"Kana kasada da rayuwar ka, kuma baka san darajar su ba, idan wani abu ya same mu, ya kake tunanin Mommy zata ji? Kasan halin da Saratu da yaranka zasu shiga? Balle ni mijin mareniya! Ka sassautawa rayuwarka daukar zafi ba naka bane, dan dai baka dauka abubuwa

da muhimmanci ne amma ai na nuna maka. Amma ba ka fahimta ba me zan maka, Sannan kayi kokari ka dawo da matarka"

Toh wannan iya maganar da Aalim yayi yasa Aamil Fushi, sosai dakayar yaja su zuwa gida, kamar Aalim zai mishi magana sai ya kyale shi dan yasan halin shi sai ya kuma birkice mishi. Haka yayi ta kokarin b'oye yanayin da suke ciki, yana bin shi. Har dai wani tafiya ta kama Aamil zuwa cotonuo, dake Aalim yasan da tafiyar bai mishi magana ba, abinda yayi mishi shine dawo mishi da Nadrah.

Inda yaje a matsayin shi na Aamil, kuma aka bashi ita suka dawo, nan kanta ya fara rawan kai, bai bi takanta ba, suna dawowa gida, yace mata.
"Na dawo dake ne, domin kome yazo min cikin sauki, dan haka ki zuba ido zaki ga abinda zai dame ki!"

Yana fadar haka ya bude motar ya fita, tana ganin ya shiga shashin Sidrah, jikinta yayi mugun sanyi.

Tabbas Aalim ne, kan Bala'i. Idan Aamil yasan itace ta aikata abubuwa dayawa zata shiga uku.

--Kwana biyu, tsakanin Aalim ya tafi kasuwa da motar shi Toyota new brand, suna ta kaiwa da komowa, sabida kayan da Aamil ya tafi zuwa dashi sun iso, shine dai yake hanya, tare da gayawa dan uwan shi zai wuce U.s, yace mishi koda wasa ya dawo matar shi tana jiran shi.

Bayan ya gama abinda zai yi, ya fito zai tafi kawai motar shi ta tsaya, gashi yamma tayi..dan haka ya ɗan tsaya a gama gyara mishi, motar kawai me zai faru. Ghali yazo tare da mika mishi hannu yana faɗin.
"Ya Aalim! Lafiya?"
"Motar keda matsala kuma ina son zuwa bank kafin na wuce gida, domin zan shiga Hadeja gobe Insha Allah"
"Toh ka dauki nawa mana, idan yaso sai na jira motar ka,"

Alamarin Ubangiji ba ayi mishi wayo ko dabara, kuma idan ya shirya abu duk duniya babu wanda ya isa ya ture abun, wannan shine tsarin Ubangiji, cewa yake kasance sai ya kasance, toh amma rayuwa irin ta d'an adam, gani yake kamar yana da ikon kome, kuma yana da damar kome, dan haka Ghali ya tsaya a gurin motar Aalim ya dauki motar Ghali.

Haka ya wuce bank yana zuwa aka barshi ya shiga sabida yayi waya da Manajan bankin. Lokacin da ya shiga aka gama mishi kome, sannan ya kira Ghali ya ji wayar tana kara amma ba a dauka ba, ya kuma kira ba a dauka ba, kawai sai ji yayi gaban shi ya fad'i.

Cikin wani irin mugun tsoro da bai tab'a jin irin shi ba,.ya fito daga bankin ya nufi hanyar da zata kai shi gida. Motar yan kwana kwana ya hango, tare da cincirindon al'ummar a gurin da

hayaki yake tashi, hantar cikin shine yake kadawa, kamar wanda aka sanya shi a cikin ruwan ƙanƙara.

A hankali ya sauke motar a gefen hanya, ya sauka cikin tashin hankali yayi ta kutsa cikin mutane, har ya isa gaban jama'a nan yayi mugun gani, ba kowa bane sai gawar Ghali da wani mutum, wanda shima ya kone, ji yayi kamar jiri zai kwashe shi ya zube akan gwiwar shi, ya dafe goshinsa, tare da kiran sunan Allah. Kwalla ne ya zuba mishi zunzurutun tashin hankali. Shigowar Ali cikin gurin tare da saka hannun biyu akai yana kallon Aalim da yake zaune a gurin yana kallon gasar Ghali wanda fuskar shi take sake kamar ba mutuwa yayi ba.

Wuta bata ci fuskar shi ba, sai jikin shi.

"Wallahi daga zuwan shi fa aka tare shi, muka can muna kallon su, kawai ya tsaya zai fito suka danne kofar motar dayan su ya watsa fetur, kafin kace me har zuba sun kista ashana."

Kai hannu Aalim yayi zai tab'a Ghali Ali ya ture hannun tare da ture shi gabaki daya.

"Azzalumin macuci! Ka kashe mana dan uwa, mugu maha'incin. Me yasa ka barshi ya tawo da motar ka? Ka amshi motar shi."

"Kaka Ni bana son damuwa, wallahi da nasan cewa, karban motana zai iya sakawa ya rasa rayuwar shi da ban fara ba. Allah ya gani." Duk yadda Aalim yaso mishi bayani yaki karshe haka suka dauko gawar cikin tashin hankali da damuwa.

Lokacin da Hajiya Surayyah ta ga gawan D'anta me ladabi da biyayya, yaron da yafita Zakka a cikin yaranta, zama tayi tana kallon shi, tare da kallon Ali. Ashe kuka rahama ce! Tana ji tana gani sai yayyafa mishi ruwa aka yi tare da nad'e shi a surutar shi, zuwa gidan shi na gaskiya, Ghali ya sami shaidar mutane, Ghali mutumin kirki ne, yana da hakuri ga zumunci.

Ga baki daya kowa ya shaida da halin shi na gari,. matar shi kuwa suma tayi jini ya b'alle mata sakamakon cikin da bata san dashi ba.

Kiran Layin Mommy take yaki karewa, hankalinta a tashe lokacin kuma suna makabarta, suna fitowa ya dauka tare da cewa.

"Mommy!"

"Alhamdulillahi! Toh zamu taso domin.an kira mu Sidrah ta dauka, ban san me aka gaya mata ba, wallahi kawai yarinyar nan ta kama yunkurin Haihuwa, yanzun haka muna Asibiti, na kira ne domin naji mene faru."

Kwalla ne ya cika mishi ido, yace mata.

"Sunyi kokarin kashe ni ne, Allah bai nufa ba, shine ya faɗa kan Ghali, shikenan idan ta sauka ku tawo kawai."

Ya kashe wayar ya ja motar yana tafiya amma zuciyar shi tana girgiza, haka ya dawo gidan..yana Shigowa yana ganin hango wani na shiga dakin Nadrah, a tunanin shi mahaifinta ne dan haka bai kawo kome ba, shima part din shi ya shiga.

--- washi gari da asuba Aamil ya iso, shima ya kadu da mutuwar Ghali, dan haka suka haɗu shi da Dan uwan shi suna tattaunawa, wayar Aamil yayi kara, tashi yayi bayan ya saka a kunne, zuwan Haruna da Babangida, suka zauna kanen Ghali ne yaran Hajiya Surayyah.
"Yaya Hajiya da Ya Ali tare da Yaya Faruq, sai Goggo Hindatu Sune Suka bawa abokan Musa kudi su kona ka amotar ka, an dade ana son kashe ka, shine yau Suka samu nasara,."

Mikewa yayi, sannan yace musu.
"Zaku iya fada a gaban yan sanda !"
Gyada mishi kai suka yi, bai nemi karamin branch na yan sanda ba headquart ya nufa suka yi bayani a gaban Mataimakin Kwamishina, sannan Aalim yasa aka fita dasu, sannan yace.
"Yanzun gidan da mutane, idan aka tafi haka zasu iya fassara abun da wata manufa.

Mutanen nan ba yau suka fara ba, gashi wannan shine Shaidan farkon na yunkurin kashe ni, hatsarin da nayi, wannan kuma shine shaidar kisa na biyu, na kashe mahaifin mu, sabida lokacin da abin ya faru,mun yi magana dashi yake gaya min ana tura mishi barazana da rayuwar shi, amma record na asibiti ya nuna bugun zuciya ne, Ni kuma na tabbatar ba shi bane, domin a hannun shi na dama akwai smart watch, yana hade ne da wani laptop dina wanda kamfani na take sarrafawa, tunda ya gaya min haka sai na bashi wannan agogon, duk abinda mutum zai yi yana ƙoƙarin dauka ta camerar shi. Wannan zaka gwada zaka sha mamaki. Matar shi da Kanwar shi tare da Dan shi, da kuma yaron da ya rike suka kashe shi ta hanyar danne kanshi da pillow, dan dama na rigada nayi sittings din kome. Sai kashe Ghali shima ai kaji daga bakin Yaran."

Cire hula Mataimakin Kwamishina yayi tare da jinjina al'amarin, sannan yace mishi.
"Toh karka damu, Insha Allah zan duba Alamarin kuma nan da sati daya za a fara kome."

Gyada kai yayi, sannan suka yi sallama da juna suka fito, shi kuma ya dawo gida, kiran Mommy yana Shigowa, dauka yayi dan dama yayi kokarin nimanta wayar a kashe..
"Alhamdulillahi! Ka zama Dad, Sidrah ta sauka lafiya an sami baby...
🤣🙄... Mai_Dambu
[12/17, 9:55 AM] Anum Muhammad Bello❤️: "Ta sami baby boy!" Fada mishi tare da murmushi.
"Alhamdulillahi! Mommy tana iya ne?"
"Tana cikin dakin Haihuwar yanzun suka sanar mana" ta bashi amsa.

"Toh ni kam ban san me zance ba! Wallahi ina cikin alhinin mutuwar Ghali ga kuma haihuwa, ki shafa min kan su.." bai kai aya ba ya kuma jin ana cewa Mommy ta kuma Haihuwa, mace ta samu,
Kasa magana yayi kawai ya kashe wayar, yana fadin "Alhamdulillahi" ya faɗa hawaye na zuba mishi, zama kusa dashi Aamil yayi sannan yace mishi.
"Ya Sidrah ta sauka lafiya? Dan Sarah ta turo min wai suna asibiti tana haihuwa."

Kwantar da kanshi yayi a kafad'ar Aamil,.yana kallon shi.

"Ta haihu domin ta sami yan biyu, mace da namiji."
"Alhamdulillahi! Barka da samun karuwa!"
"Sai dai ina tsoron Allah ina tsoron kawo su gidan nan! Wallahi bana son a kawo ta gidan nan"

"Da damuwa, ai na kusan gama gidana, wuta ne ya rage babu. Amma kome na kammala zan koma can kafin na tattara su mu koma can da zama,"
"Toh ya zaka yi da part din ka? Ina da gida a waje me zanyi dashi,tunda kai baka fara naka ginin ba sai ka zauna da Saratu a cikin shi mana, domin kaga idan akayi suna dole zata tafi gida.

Kuma kaga kafin ta dawo na gama kome, dan haka karka damu."

"A'a nima zan tashi daga gidan nan" Inji Aamil,
Kallon shi Aalim yayi na wani lokaci, kafin ya kuma mai da hankalin shi kan dan uwan na shi.
"Zama ya zama dole, domin dai babu inda zaka, idan ka gama shirin ka ka fara ginin ka sai ka fara aramar tashi,"

B'ata rai yayi, a hankali suka ci-gaba da tattaunawa, har aka kira sallah magarib, suka tafi tare. Suna dawowa suka nufi cikin gidan, domin gaishe da Hajiya Surayyah da sauran matan gidan, suna shiga ana cewa.
"Eh! Motar ai ba tashi bane, sannan yadda kowa yake hasashe an zo kashe Dan uwan ne aka kashe shi. Amma batun ace shi ya kashe shi ai bai taso ba, domin ko Daddy Nadrah da ya isa gurin abinda yaji kenan a gurin da abin ya faru."

"Allah ya tona asirin masu hannu a cikin wannan lamari." "Amin Ya Allah"

Gaishe su, suka yi sannan suka shige dakin Hajiya Surayyah, suka gaida yan uwan ta, kallon su tayi cikin bakin ciki da hassada tare da ji a ranta sai ta kashe su, sai ta fanshi jinin Ghalinta yaron da babu ruwan shi da badakalar da yake faru. Haka tayi ta shirya yadda zata kashe su, sai ta raba su da duniyar nan matukar tana numfashi. Haka suka gama gaishe su, sanan suka fito. Bayan sun fito ne suka shiga gyara part din Mommy, dake dakuna biyu ne kuma Sarah zata zauna a dayan
Nan suka gama kome, sannan suka gayawa Ummi haihuwar Sidrah, bayan sun gaya mata itama ta gayawa Hajiya kaka, murna kamar ta zuba ruwa a kasa ta sha, Mahakurci mawadaci.

Ranar da aka yi addu'ar uku, a ranar Mommy suka taso da Sidrah.
Kallon shi take cikin damuwa tace mishi.
"Baban Janan meye yasa baka sauke hakkin da yake kanka ne?"
"Sabida koda na sauke zaki rena iyawata ne, kuma na manta na gaya miki, ga wannan ki sayi duk abinda kike bukata, amma nayi aure, kuma zasu zo da Mommy zuwa gobe dan sun taso"

Kamar wanda ya gaya mata wani labarin mutuwa, sai da ta diro daga gadon, tare da fashewa

da dariya, tana tafawa.
"Wallahi baka isa ka rena min hankali ba, na rantse da Allah babu shegiyar da zata raba makwancin da mijina."

Shiryawa yayi abinshi yana murmushi, sannan yace mata.
"Anyi kuwa? Domin dai har an wuce gurin, kawai dai Allah ya kiyaye na gaba ne kawai, amma ai tuni na manta da mun wuce gurin."

Ihu ta saka tare da rike rigar shi..
"Wacce karuwa ka auro min? Wallahi sai na dafata da ruwan zafi, amanata zaka ci? Meye na rage ka dashi."

"Wannan kuma ke ta shafa" ya saka kai ya fita abun shi, tunda ai ya gama fita hakkinta.

Kuka tayi shi babu iya, tare da kiran Alhaji Abubakar, zata zo. Daukar Yaronta tayi suka fita. Tana isa gidan Alhaji Abubakar, ta fashe da kuka, tana gaya mishi abinda ya faru, tsaki yayi tare da janta zuwa dakin shi, sannan ya amshi Yaron shi me sunan Abba Ma'aruf, ya gama mishi wasa, sannan ya kalle ta, yana faɗin.
